# Zaɓaɓɓun Littattafai

Na

Shehu Usmanu Ɗanfodiyo

Sihili Na

4

© Iqra'ah Publishing House

**ISBN: 978-978-56201-6-0**

**Bugawa:**

**Iqra'ah Publishing House,**
15, Shehu Usmanu Ɗanfodiyo Road,
Barakallahu, Gusau, Zamfara State

Tel: +2347069412770
+2349065566498
+2349079999124
**Email: iqragroup99@gmail.com**

## Abubuwan Da Ke Ciki

1. Gabatarwa Daga Sarkin Musulmi ………………………………….v
2. Saƙo Daga Mai Maɗaba'a ………………………………………. vii
3. Matakan Ilimin Tauhidi ………………………………..………..1
4. Rana Ga 'Yan'uwa……………………………………….……9
5. Kare Fahimta Daga Rundunar Wahami ……………….…………69
6. Bambanta Musulmi Daga Kafirai ……………………...……..161
7. Shiryar Da Ɗalibai ……………………...…………….……185
8. Tabbatar Da Kiyayewar (allah) Ga Dukkan Matakan Wannan Al'umma…..………………………………………………...317
9. Shiryar Da Masu Faifayewa Da Masu Sake Zuwa Ga Daidaitacciyar Hanya……………………………………………………..337

## Gabatarwa Daga Sarkin Musulmi
## Da sunan Allah Mai rahama Mai jin-ƙai

Dukkan godiya da yabo sun tabbata ga Ubangijin wannan rana da Ranar Sakamako. Shi kaɗai muke bautawa kuma Shi ne muke neman taimako a gare Shi.

Tsira da amincin Allah su tabbata ga Annabi Muhammad (saw), fiyayyen talikai kuma cikamakin Annabawa sannan shugaban dukkan waɗanda suka kaɗaita Allah da iyalansa da sahabbansa da dukkan waɗanda suke bin tafarkinsu har zuwa ranar Sakamako da kyautatawa.

Bawa mai tsananin buƙatar rahamar Ubangijinsa, Muhammad Sa'ad Abubakar, Sarkin Musulmi na yanzu kuma jika ga Mujaddadi Shehu Usman Ɗanfodiyo Allah ya lulluɓe shi da rahamarSa yana godiya ga Allah (swt) tare da farin ciki game da damar da na samu don gabatar wa jama'a da rukuni na biyu na zaɓaɓɓun littattafai da rubuce-rubuce (ƙasida) guda ɗari (100) na shugabannin Daular Sakkwato a matsayin ci gaba da ƙoƙarinmu na tattaro dukkan rubuce-rubuce da tabbatar da su a matsayin littattafai na Shugabannin Daular Sakkwato- Shehu Usman Ɗanfodiyo da Shehu Abdullahi Ɗanfodiyo da Sarkin Musulmi Muhammad Bello Allah ya yi jin-ƙai a gare su don fassara su zuwa Harsunan Larabci da Hausa da Turanci da buga su.

Godiya ta tabbata ga Allah, an yi sowa tare da yin maraba da rukunin farko na waɗannan littattafai duk da dai akwai ƙorafe-ƙorafe sai dai an yi ƙoƙarin magance waɗannan ƙorafe-ƙorafe a cikin rukuni na biyu na littattafan. Buƙatarmu da yardar Allah Mai girma kuma Mabuwayi ita ce ci gaba da inganta abin da muka sanya a gaba na ganin an kammala dukkan littattafan shugabannin kamar yadda muka yi alƙawari tare da raba su fisabilillah ga jama'a don amfanin ɗaukacin 'yan'adam.

An mayar da hankali na musamman a cikin rukunin littattafai na biyu a kan batutuwan da ake magana a kansu a yanzu kamar jihadi da tsarin tarayya da shugabanci da dalilin wanzuwar gwamnati da rawar da ake sa ran shugabanni su taka da zaman tare lami lafiya a tsakanin Musulmi da waɗanda ba Musulmi ba da ke zaune a ƙasa guda da sauransu. Addu'armu da fata su ne Allah ya sanya waɗannan littattafai su amfani jama'ar yanzu da masu zuwa a nan gaba masu tunkarar matsalolin shugabanci da na ginin ƙasa.

Haka kuma ina gode wa gwamnan Jihar Sakkwato, Alhaji Aminu Waziri Tambuwal, game da ɗaukar nauyin buga littattafan da Sarkin Argugun, Alhaji Sama'ila Muhammadu Mera wanda ya kasance mai sadarwa da bayar da shawarwari a kan wannan aiki da jami'in tabbatar da sahihancin rubuce-rubuce na Larabci, Alhaji Isa Talata Mafara da Malam Mande Faru da Murjanatu Aminu Ibrahim waɗanda suka ƙirƙiro wannan aiki tare da ganin haƙarsu ta cimma ruwa da ɗaukacin Ma'aikatan Gidan ɗab'i na Iqrah.

Har ila yau, ina gode wa Malam Tukur Isyaku da dukkan editoci da masu fassara da masu sarrafa na'ura mai ƙwaƙwalwa da sauran jama'a masa yawa da ba za a iya ambata dukkan sunayensu ba. Allah ya saka masu da alhairanSa, amin

Ina addu'a ga Allah Maɗaukakin Sarki da Ya amshi wannan aiki daga gare mu kuma Ya ba mu babbar kyauta a wannan duniya da a gobe ƙiyama.

Wassalam.

Sarkin Musulmi Sa'ad Abubakar III
Sarkin Musulmi

## SAKO DAGA MAI MAƊABA'A

**Da sunan Allah Mai rahama Mai jin-ƙai**

Dukkan yabo da godiya sun tabbata ga Ubangijin talikai. Tsira da amincin Allah su tabbata ga Annabi Muhammad da alayensa da mafifitan Sahabansa da dukkan masu bin tafarkinsa da taƙawa har zuwa Ranar Sakamako. Bayan haka: Bawa mai tsananin buƙatar rahamar Allah ga kansa da iyayensa da iyalinsa da 'yan'uwansa da ma'aikatansa da dukkan waɗanda suka bayar da gudummuwowinsu a wajen ganin kammaluwar wannan muhimmin aiki mai suna Muhammadu Basharu wanda aka fi sani da Mande Faru yana cewa, wannan aiki ne da ake sa ran kowane Musulmi ya yi shi.

Shehu Usman Ɗanfodiyo Allah ya lulluɓe shi da rahamarSa ya yi tsaye a wajen yin bayani a kan ɗabi'u guda goma waɗanda haƙiƙa a bayyane suke daga kalaman Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi (saw) da Sahabansa yardar Allah ta tabbata a gare su (ra). Ya fara da bayanin cewa, batutuwan da suka shafi falsafa ba su taɓa zama a gaban Annabi Muhammadu (saw) ba. Babban abin da ke gabansa (saw) shi ne Sahabbin shiga addinin Allah wato Musulunci waɗanda suka furta Kalmar Shahada ta babu abin bautawa da gaskiya face Allah kuma Annabi Muhammad (saw) bawanSa ne kuma ManzonSa ne. Allah ne Ke da masaniya game da gaskiyar furucin da suka yi daga zukatansu ta ke ko ba daga zukatan ba. Shehu ma ya yi nuni da wannan cewa ba damuwarsa ce ko ta wani ba..

Malaman falsafa za su ci gaba da yin muhawara a tsakaninsu game da batun rashin imani da yin imani. Annabi (saw) da Sahabansa (ra) ba su taɓa waigawa a kan wannan batu ba haka shi ma Shehu. Wannan batu dai daga baya ne ya kunno kai a lokacin da waɗanda ba Musulmi ba suka fara ƙaluɓalantar matsayin falsafa a Musulunci a game da batutuwa masu dama. Game da wanda ya miƙa wuya ga Allah, ya mayar da hankalinsa a kan bauta wa Allah kamar yadda Annabi (saw) ya nunar masa.

Wanda ya karanta littattafai guda biyu na farko ba zai yi wata tantama ba cewa, suna yin ƙalubale ne a game da batun a wani lokaci ne ake amincewa da Musulmi a matsayin Musulmi kuma a yaushe ne za a ɗauka ya bar addin? Shehu ya ɗauki ma'ana mafi sauƙi ta musulmi a matsayin "Matuƙar dai babu wata shaida cewa, an ga mai imani da Allah yana bauta wa abubuwan da ba Allah ba don haka ba za a ce ya bar addinin Musulunci ba." A nan an fahinci ana aikata zunubai da kurakurai amma kuma kada a zaƙe a wajen fassara waɗannan.

Daga nan Shehu ya taɓo ilimin da lallai ne kowane Musulmi ya biɗe shi. Waɗannan ilimummuka sun haɗa da ilimin Alƙur'ani da na Sunnar Annabi (saw). Sai samun ilimummuka a kan asullan addinin Musulmi da asulan fiƙihu da fiƙihu da sububban saukar aya da Larabci da Nahawu da luga da hadisai da sanin ƙira'a da badi'I da bayani da ma'ani da sauransu, to, daga nan sai ya fara wa'azi da tafsiri.

Ya kawo rukunonin masu yin wa'azi daban-daban. Ya nuna damuwa matuƙa don haka ya rubuta wata wasiƙa zuwa ga "wani wanda bai cancanci yin tafsiri ba."

Dangane da muhawara a game da bambanci a tsakanin mai imani da Allah da wanda bai yi ba da yanayin dangantaka a tsakaninsu, Shehu ya rubuta wani littafi yana gargaɗin Musulmi da su nisanci amsar duk wani abu da ba shi da tushe a Musulunci da hannu bibbiyu don akwai matsanantan abubuwa marasa daɗi waɗanda za su biyo bayan yin haka.

Shehu Usman Ɗanfodiyo mai yin wa'azi ne kuma shugaba ne. Kuma a matsayin Sufi, abin da ke gaba gare shi shi ne yadda za a yi salla yadda ya kamata sannan ga salonsa na yin munajati.

A matsayinsa na mai yin wa'azi kuma mutumin da gina Al'uma ta Musulunci ke gabansa, sai bai tsaya a kan yin wa'azi ba kawai ya rubuta littattafai masu yawa a kan addinin Musulunci da muhimman batutuwa na addinin. Kuma mene ne Musulmi zai fi mayar da hankali a kansa da yadda shi ko ita za su bauta wa Mahalicci. Ya yi rubuce-rubuce a kan yin ibada da zamantakewa da jagora ga matasa musamman a kan kaucewa daga bin daidaitacciyar hanya da bin ruɗin Sheɗan la'ananne.

Daga cikin littattafai da ya rubuta akwai "Jagora ga ɗalibai" wanda ya ƙunshi batutuwa kamar Tashin Alƙiyama da Mi'iraji da dawowar Annabi Isa Alaihissalam (as) da matsayin Mala'iku da na Annabawa da umurce-umurce a kan abubuwan da ake son a aikata su da waɗanda ba a son a aikata su. Ya kawo ayoyi daga Alƙur'ani mai girma da Hadisan Manzon Allah (saw). Shi wannan littafi ya ƙunshi rayuwar Musulmi ta yau da kullum.

Haka kuma ya yi rubutu a kan ayyukan ibada kamar tsafta da salla da azumi da dangantaka a tsakanin mutane da uwa uba "Kare kai daga bin karkatacciyar hanya mai jagoranci zuwa ga ɓatawa." Haka kuma wannan littafi ya ƙunshi batutuwa ɗaiɗai har sama da ɗari waɗanda ake taƙaddama a kansu. Ya ambata ɗaya bayan ɗaya har sama da abubuwa ɗari waɗanda ake

ɗaukar su, su, gaskiya, ne alhalin su ba gaskiya ne ba. Kuma ya yi bayani a kan kowanne ta kawo hujjoji daga littattafai daban-daban kafin ya kai ga wata matsaya.

Ya ci gaba da cewa, Musulmi dai Musulmi ne kuma akwai koyarwar Musulunci don haka lallai ne kada Musulmi ya rungumi wata ɗabi'a ido rufe sai fa abin da Allah ya umurta a Alƙur'ani da Hadisan Manzon Allah (saw). Ya kawo abubuwan da shehunnan malamai suka rubuta a littattafansu daban-daban don yin bayanin dalilin da ya sanya ya kawo abu. Har ila yau, akwai littattafan Shehu a kan kyautata ɗabi'un Musulmi, da yadda za a kai ga samun ɗabi'un, da a kan abubuwan da Allah ya haramta da a kan Tawassul da shugabanci da naƙaltar yin magana.

Dukkan waɗanda suka karanta rubuce-rubucen Shehu Usman da idon basira za su kai ga matsaya cewa, yana da salo da alƙibla kuma waɗannan salo da alƙibla na Musulunci ne. Ya san abin da yake so kuma ya san yadda zai kai ga samun abin da yakle so da yardar Ubangijin. Yana son ganin wanzuwar al'uma ta Musulunci a ƙarƙashin tsarin shugabanci na Musulunci. Don haka ya yi rubutu a kan shugabancin; ya yi wa'azi a kansa; ya yi kamfe a kansa; ya tayar da jama'a a tsimi kuma ya yi yaƙi don ganin wanzuwarsa. Haƙiƙa, ya yi abin tarihi kuma waɗannan littattafai nasa da ƙaruwar yawan Musulmi a Afirka suna yin nuni da wannan tarihi.

Ya Allah Ka saka wa Shehu Usman Ɗanfodiyo da sauran Shgabannin Daular Sakkwato a bisa kyawawan ayyukan da suka gudanar na ɗaukaka Kalmar Allah da alhairanka, amin.

Muna roƙo Allah Ya amshi wannan aiki. Muna roƙo ga jama'a duk wanda ya lura da inda muka yi kure, ko kuma fassara ba ta yi dai-dai ba, don Allah ya taimaka ya lurar da mu. Allah Ya bada lada. Amin

## GODIYA

Dukkan yabo da godiya sun tabbata ga Allah Ubangijin taliaki kuma tsira da amincin Allah su tabbata ga Annabi Muhammadu da alayensa da Sahabansa da masu bi masu da taƙawa har zuwa Ranar Sakamako. Ina amfani da wannan dama don yin godiya mai tarin yawa ga Mai alfarma Sarkin Musulmi, Alhaji Sa'ad Abubakar III, a game da ɗaukar ɗawainiyar kuɗi kan tattaro rubuce-rubuce na Shugabannin Daular Sakkwato, Shehu Usman Ɗanfodiyo da Shehu Abdullahi Ɗanfodiyo da Sarkin Musulmi Muhammad Bello, da fassara su da buga su ba tare da gazawa ba. Allah ya

saka masa da Jannatul Firdausi tare da biya masa dukkan buƙatunsa na alhairi a nan duniya da a gobe ƙiyama don albarkar waɗannan littattafai.

Haka kuma ina godiya ga Mai Martaba Sarkin Argungu, Alhaji Sama'ila Muhammadu Mera, game da haɗa mu da mai alfarma Sarkin Musulmi da ƙarfafa mani gwiwa da yin haƙuri da ni tare da taimakawa. Bai taɓa sassautawa yin ƙasa da gwuiwa ba a game da ƙoƙarinsa na ganin an buga waɗannan littattafai tun da aka fara gudanar da wannan aiki. Allah ya sanya shi tare da Sarkin Musulmi a cikin amintattun jama'ar Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi (saw) a Ranar Alƙiyama.

Har ila yau, ina yin godiya ga Malam Muhammad Isa Talata Mafara game da yin gyare-gyare a littattafai na harshen Larabci. Tare da daidaita fassara littattafan zuwa harshen Hausa da Turanci da Malam Tukur Isyaku ya yi, kuma da fassarar harshen Hausa da Malam Faruk Ingawa ya yi gyare-gyare a littattfan da aka fassara su zuwa harshen Turanci. Allah Ka biya masu dukkan buƙatunsu na alhairi a wannan duniya da a Ranar Alƙiyama.

Ma'aikatana masu sarrafa na'ura mai ƙwaƙwalwa, Malam Alhassan Hassan da Usama Isama'il, sun yi aiki tuƙuru a wajen sanya gyare-gyaren da aka yi tare da taimakawa a wajen tsara yadda waɗannan littattafai za su kasance. Allah Ka taimaka masu su ci gaba a aikinsu tare da ci gaba da kasancewa nagari a addini da a ayyukan ɗaukaka Kalmar Allah.

Game da matata, Malama Murjanatu Aminu Ibrahim, da 'ya'yana waɗanda suka yi haƙurin jure rashin zamana a gida a wasu lokuta, ina addu'ar Allah ya cika masu burinsu na alhairi a wannan duniya da a Gobe Kiyama, amin.

Akwai kuma mutane masu tarin yawa waɗanda ba za a iya ambata sunayensu ba. Allah ya saka masu da alhairanSa game da ƙarfafa gwiwa tare da taimakawa. Ina godiya ga kowa da kowa kuma Allah ya albarkace ku tare da mu, amin.

Mande Faru,
Shugaba/Babban Edita

# معراج العوام

# إلى سماع علم الكلام

# MATAKAN ILIMIN TAUHIDI

Na

Shehu Usmanu Ɗanfodiyo

Mai Fassara:
Dr. Rufa'i Usman Isma'ila Rungumi

## Da Sunan Allah Mai Rahama Mai Jin-ƙai

Tsira da amincin Allah su tabbata ga Shugabanmu, Muhammadu da Alayensa da Sahabbansa.

Bawa Mabuƙaci ga rahamar Ubangijinsa mai ƙasƙantar da kai don munin ayyukansa, Usumanu ɗan Muhammadu ɗan Usumanu Alfulati ga Nasaba kuma Ash'ari ga Aƙidah, ya ce : Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin Talikkai, tsira da amincin Allah su tabbata ga Shugabanmu, Muhammadu cikamakin Annabawa kuma Shugaban Manzanni, Allah ya daɗa yarda da Sahabban Manzon Allah baki ɗaya da Mabiyansu da waɗanda suka bi su da kyautatawa har zuwa Ranar Sakamako.

Bayan haka, wannan littafi ne mai bayyana manufofin Ilimin Tauhidi da taimakon Allah, na kuma ambace shi da sunan: Matakan Ilimin Tauhidi don fahimtar da mara Sani. Ina neman taimakon Allah, Ma'ishinmu Madogaranmu.

Ina mai cewa tun farko,tsarki ya tabbata gare Ka (Allah). Ba Ilimi gare mu sai abin da Ka sanar da mu haƙiƙa Kai ne Mai hikima.

Ka sani Ilimin Tauhidi ya kasu zuwa kashi Uku :

**Kashi na Ɗaya:** Siffofin da suka keɓanta ga Allah wato yana bayani a kan abubuwan da suka wajaba ga Allah da waɗanda suka koru gare Shi (Waɗanda ba a jinginawa gare Shi) da kuma waɗanda suka inganta gare Shi.

**Kashi na Biyu:** Siffofin da suka keɓanta da Annabawa wato yana bayani a kan abubuwan da suka wajaba ga Annabawa tsira da amincin Allah su tabbata gare su da waɗanda suka koru gare su da kuma waɗanda suka inganta gare su.

**Kashi na Uku:** Abubuwan da aka ji (Na gaibi) wato yana bayani a kan abubuwan da manzanni tsira da amincin Allah su tabbata gare su suka bada labari game da shi na lamarin abubuwan da ba mu gani ba waɗanda suka shafi Ilimin gaibi.

Amma Kashi Na Ɗaya: Game da Siffofin da suka wajaba ga Allah, to, su ne : Samuwa, wannan Siffa wajiba ce ga Allah (Wato lallai Allah Samamme ne), Kishiyar wannan siffa ita ce rashi (Wato a ce babu Shi). Wannan siffa ta koru gare Shi. Da gabata, wannan siffa wajiba ce ga Allah Maɗaukaki, kishiyarta kuma ita ce Faruwa wadda ta koru ga Allah

Maɗaukaki. Da wanzuwa, wannan siffa wajiba ce ga Allah Maɗaukaki, kishiyarta kuma ita ce Karewa wadda ta koru ga Allah Maɗaukakin Sarki. Da kuma saɓawa ga Fararru (wato Halittun da Allah ya yi). Wannan siffa wajiba ce ga Allah Maɗaukaki. Kishiyarta ita ce Tamka ko yin kama da wata halitta wadda ta koru ga Allah Maɗaukaki. Kasancewar Allah ba Mai jiki irin na sauran halittu ba, wannan siffa wajiba ce ga Allah Maɗaukaki. Da tsayuwa ko dogaro da kai, wajibi ne ga Allah Maɗaukaki. Kishiyarta ita ce buƙatuwa zuwa ga mahalli ko wani keɓantaccen wuri, wannan ya koru ga Allah Maɗaukaki. Da Kaɗaita, wajiba ce ga Allah Maɗaukaki wadda kishiyarta ita ce ƙididdiga a cikin ZatinSa ko SiffofinSa ko ayyukanSa. Wannan ta koru ga Allah Maɗaukaki. Da Iko, wannan siffar wajiba ce ga Allah Maɗaukakin Sarki, kishiyarta kuma ita ce Kasawa wadda ta koru ga Allah Maɗaukakin Sarki. Da Nufi, wannan siffar wajiba ce ga Allah Maɗaukakin Sarki. Kishiyarta kuma ita ce tilastawa wadda ta koru ga Allah. Da Ilimi, wajibi ne ga Allah Maɗaukaki. Kishiyarta kuma shi ne Jahilci wanda ya koru ga Allah Maɗaukaki.

Da Rayuwa, wajiba ce ga Allah Maɗaukakin Sarki. Kishiyarta kuma ita ce Mutuwa wadda ta koru ga Allah. Da ji, wajibi ne ga Allah Maɗaukaki. Kishiyarsa ita ce kurumta (Kurmantaka) wadda ta koru ga Allah. Da Gani, wajibi ne ga Allah Maɗaukaki. Kishiyarsa ita ce Makanta wadda ta koru ga Allah. Da Magana, wajiba ce ga Allah Maɗaukaki.Kishiyarta kuma ita ce bebantaka wadda ta koru ga Allah. Da kasancewarSa Mai (Cikakken) Iko, wajibi ne ga Allah Maɗaukakin Sarki. Da kasancewarSa Masani, wajibi ne ga Allah Maɗaukaki. Kishiyarsa shi ne kasancewarSa Mara Sani, wannan ya koru ga Allah Maɗaukakin Sarki. Da kasancewarSa Mai Ji, wajibi ne ga Allah Maɗaukaki. Kishiyarsa ita ce kurmantaka wadda ta koru ga Allah. Da kasancewarSa Mai Gani, wajibi ne ga Allah Maɗaukakin Sarki. KishiyarSa kuma shi ne Ya kasance Makaho, wanda ya koru ga Allah. Da kasancewarSa Mai Magana, wajibi ne ga Allah Maɗaukaki. Kishiyarsa kuma shi ne Ya kasance Bebe, wanda yake wannan siffa ta koru ga Allah Maɗaukaki.

Bayan abin da aka ambata, mun yi imani da cewa kamala dukaninta wajiba ce ga Allah Maɗaukakin Sarki; naƙasa kuma dukaninta abin korewa ce ga Allah.Kuma dukanin abin da muka ambata daga farkon littafi zuwa nan shi ne abin da ya wajaba ga Allah da abin da ya koru gare Shi (Wato abin da ba a jinginawa gare Shi).

Amma abin da ke inganta ga Allah Maɗaukaki aikata shi, shi ne aikata dukanin abin da ke samuwa ko yiwuwa ga aikata shi ko barin sa. Mun

kuma ambaci abin da ya wajaba gare Shi da wanda ya koru gare Shi da ma wanda ya inganta aikata shi ga Allah Maɗaukaki.

Manufa a nan yanzu shi ne kawo dalillai a kan haka. Dalilin samuwar Allah Maɗaukaki shi ne samuwar Talikai (Halittu). Bayan rashin su domin ba zai yiwu samun aiki ba alhali ba wanda ya yi shi. Wannan korarren abu ne.

Amma dalilin samuwar gabatar Allah Maɗaukaki shi ne da Bai kasance gabatacce ba da Ya kasance fararre da kuma Ya kasance fararre da Ya kasa samar da waɗannan halittun.

Amma dalilin wajabcin kasancewarSa (Allah Maɗaukaki) Wanzajje shi ne domin kasancewarSa gabatacce, domin duk wanda ya tabbata cewa Shi ya gabaci kowa da komi, to, tabbas ya koru a ce Shi ba Wanzajje ba ne.

Amma dalilin kasancewarSa wanda Ya saɓa wa halittu (Talikai) shi ne da Ya kasance mai kama da wani abu na halittunSa, to, da kenan Shi fararre ne da kuwa Ya kasance fararre da Ya kasa samar da halittu (Talikai dukaninsu) .

Amma dalilin tsayuwarSa da kanSa shi ne rashin buƙatarSa ga kowa ko ga komi, domin da Ya kasance mabuƙaci zuwa ga wani mahalli ko wani abu na daban da Bai iya samar da waɗannan halittu ba.

Amma dalilin kasancewarSa Maɗaukakin Sarki wanda ake siffantawa da Mai cikakken iko da nufi da ilimi da rayuwa shi ne domin da Bai kasance abin siffantawa da waɗannan siffofin ba da Bai iya samar da waɗannan halittu ba.

Amma dalilin ingancin aikata kowane samammen abu ko barin sa shi ne domin da siffantuwa da kowace siffa ta wajaba gare Shi da kenan wasu siffofi ba su koru gare Shi ba, ko kuma su inganta gare Shi na aikatawa ko bari.(Wato da an samu akasi kenan).

Amma Kashi Na Biyu: Shi ne wanda ya danganci(Haƙƙoƙin Annabawa) Wannan kuma shi ne : Gaskiya, wajiba ce ga Manzanni tsira da aminci su tabbata gare su, su kasance masu gaskiya, wadda take ita ce kishiyar ƙarya wadda ta koru gare su ( wato ba a jingina ƙarya gare su).

Da kuma amana, wajiba ce ga Manzanni, tsira da aminci su tabbata gare su, kuma kishiyar amana ita ce yaudara wadda take ta koru gare su.

Da kuma iyar da manzanci ( Wato sanar da saƙon Allah ga Mutane) Wajibi ne gare su. Kuma kishiyar iyar da manzanci shi ne ɓoye manzanci ga mutane, wannan kuma korarre ne gare su.

Sannan mun yi Imani da cewa kowace kamala ta Ɗan'adam wajiba ce gare su yayin da kowace naƙasa ta Ɗan'adam korarra ce gare su.

Dukanin abin da muka ambata tun daga farkon kashi na Biyu har zuwa nan, to, su ne abubuwan(Siffofin) da suka wajaba da waɗanda suka koru gare su tsira da amincin Allah su tabbata gare su.

Amma abin da ya inganta gare su (A Matsayinsu na 'yan'adam) Shi ne gittawar wasu halaye irin waɗanda ke samuwar 'yan'adam kuma ba su kai ga naƙasa, kamar masassara (Zazzaɓi) ko ciwon kai ko makamancin haka ba.

Haƙiƙa, waɗannan su ne abubuwan da suka wajaba da waɗanda suka koru da waɗanda suka inganta ga Annabawa tsira da amincin Allah su tabbata gare su.

Ga kuma dalillai a kan wannan: Amma dalilin wajabcin gaskiya ga Manzanni shi ne Mu'ujizojin da Allah ya ba su. Amma dalilin wajabcin kasancewarsu masu Amana, shi ne Umurnin da Allah ya yi na yin koyi da su.Amma dalilin wajabcin iyar da saƙon Allah ga Mutane shi ne domin kasancewar Amana wajiba ce a gare su.

Waɗannan su ne dalillai a kan abin da ya wajaba da wanda ya koru da wanda ya inganta ga haƙƙin Annabawa da Manzannin Allah tsira da amincin Allah su tabbata gare su.

Amma Kashi Na Uku: Shi ne game da ''Sam'iyyat'' wato abubuwan da muka ji kuma muka yi Imani da su tare da cewa ba mu gan su ba kamar Littattafan da Allah ya aiko wasu manzanni da su zuwa ga Mutane gaskiya ne, da Mala'iku, gaskiya ne da Ranar Lahira, gaskiya ce da Mutuwa in Ajali (Lokacin Mutuwa) ya yi, gaskiya ce da Tambayar "Munkar da Nakirin" (Wato Mala'iku Biyu masu tambaya) a cikin ƙabari gaskiya ce, da Azabar ƙabari da Ni'imarsa, gaskiya ce, da Tayar da Matattu, gaskiya ne da Tattara Mutane wuri guda domin hisabi, gaskiya ne da yin Hisabi, gaskiya ne da bayar da Littattafai(Na ayyukan da aka aikata a Duniya), gaskiya ne da auna ayyuka, gaskiya ne da Ceto, gaskiya ne da Ganin Muminai gare Shi Maɗaukakin Sarki a Ranar Lahira, gaskiya ne da Siraɗi, gaskiya ne da

'Alkausara; gaskiya ne da Aljanna, gaskiya ce da Wuta, gaskiya ce da dukanin abin da Annabi Muhammadu ya zo da shi, gaskiya ne.

A nan ne kashi na uku ya tuƙe, wanda ke bayani game da abubuwa na 'gaibi' waɗanda muka yi Imani da su alhali ba mu gan su ba, wato 'sam'iyyat'.

Amma dalili a kan abin da muka ambata, haƙiƙa, kasancewar Manzanni masu gaskiya ya isa ya kasance dalili a kan haka. Da kuma tuƙewar wannan fasali na uku, littafin Matakan IliminTauhidi ya kammala. Kammala shi kuma ya kasance ne Ranar Laraba da hantsi a shekarar Dubu da Ɗari ɗaya da Casa'in da Tara ta Hijirar Annabi tsira da aminci su tabbata gare Shi.

Ina roƙon Allah ya amfani Mawallafinsa da wanda ya karanta shi ya kuma yi aiki da shi ko ya yi wani aiki a kan sa. Ina kuma roƙon Allah Mai girma kariya daga sharrin Mai hasada yayin hasadarsa.

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin Talikkai, tsira da aminci su tabbata ga shugabanmu, Muhammadu da kuma tarsashin 'yan'uwansa Annabawa da Manzanni, kuma Allah shi daɗa yarda da Sahabban Manzon Allah dukaninsu baki ɗaya tare da waɗanda duk suka bi sawunsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako.

Karshen Du'a'inmu shi ne: Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin Talikkai, tsirar Allah ta tabbata ga Annabi Mai girma.

# شمس الإخوان

# RANA GA ‘YAN’UWA

Na

Shehu Usmanu Ɗanfodiyo

Mai Fassara:
Harshi Bello Gyal-Gyal

## ABUBUWAN DA KE CIKI

**Shafi**

BUƊEWA………………………………………………………….………...13

GABATARWA........................................................................................ 15

FASALI NA ƊAYA: Bayanin Taƙawa Ga Neman Ilimin Fardu-Aini ....... 17

FASALI NA BIYU: Bayanin Abin Da Allah Ya Yi Baiwa Da Shi Ga Mutane...............................................................................................22

FASALI NA UKU: Bayanin Sanin Asullan Addini Da Rarrabewa Tsakaninsa……………………………………..……………………..34

FASALI NA HUDU: Ga Bayanin Haƙiƙa Annabi (Saw) Ya Tabbatar Da Asullan Addini A Cikin Sunnarsa.............................................................. 45

FASALI NA BIYAR: Bayanin Ƙa'idodin Ilmul-Kalami ............................ 53

KAMMALAWA: Bayanin Cewa Ɓarna Ba Za Ta Game Aƙidojin Jama'a Duka Ba Har Kiyama Ta Tsayu ................................................................. 62

## BUƊEWA

***Ina Farawa da Sunan Allah Mai Rahama Gamamma a Duniya, Keɓaɓɓa a Lahira.***

Allah Shi yi jin-ƙai da tsira a kan Shugabanmu, Muhammad (saw) da alayensa da Sahabbansa, Amin.

Bawan Allah mai tsananin buƙata ga rahamar Ubangijinsa shi ne Usmanu ɗan Muhammadu ɗan Usmanu wanda aka fi sani da Ɗanfodiyo. Allah ya lulluɓe shi da rahamarSa, amin. Ya ce:

Godiya ta tabbatar wa Allah wanda Ya yi ni’ima ta imani da Musulunci a kanmu, Ya shiryar da mu da Shugabanmu, Uban gidanmu, Muhammadu. Mafificin jin-ƙai da sallama daga Allah mafi tsarki su tabbata a kansa. Bayan haka: Wannan littafi ne wanda aka tara mai suna *Shamsul-Ikhwani* (Rana ga ‘yan’uwa) waɗanda suke amfani da haskenta wajen asullan addini. Littafin ya taƙaita a kan gabatarwa da fasulla biyar da kammalawa.

### Fasali Na Ɗaya

Ya zo a kan bayanin taƙawa ga neman farillah wanda aka sani da faɗar Manzon Allah (saw)

(طلب العلم فريضة على كل مسلم)

***“Neman sani farilla ne a kan kowane Musulmi”***

### Fasali Na Biyu

Yana bayanin abin da Allah ya yi baiwa da shi a kan mutane, sanar da su dalilai na saninSa wanda shi ne halitta ta addini da abin da ake gani da abin da aka jiya jin da ba ya karɓar ƙarya da nazari da abin da ba sai an yi wani nazari ba.

### Fasali Na Uku

A kan bayani game da ilimin asullan addini da bambanci tsakaninsa da tsakanin (ILMUL-KALAMI) shi ne wanda ake kafa dalilai na hankali kuma a cirato maganganun masu falsafa da bayanin wajabcin riƙon aƙidodi na asullan addini a cikin Alƙur’ani mai girma da cewa Allah ya tabbatar da asullan nan cikin Alƙur’ani mai girma.

### Fasali Na Huɗu

Ga bayanin cewa Annabi (saw) ya tabbatar da asullan addini kuma a cikin sunnarsa.

### Fasali Na Biyar

A kan bayanin ƙa'idoji na (ILMUL-KALAMI) wanda dole ne wanda ke nufin karatunsa ya san su.

## GABATARWA

Gabatarwa a kan bayanin cewa, hukunce-hukuncen shari'ah an gina su a kan bayyane. Ina cewa daidaitawa ga sawaba tana ga Allah.

Ya 'yan' uwana ku san duk wanda ya bayyana Musulunci ba a ce masa kafiri, kamar yadda ya zo a cikin Alƙur'ani da Sunna da (Ijma'i) (shi ne haɗuwar Malamai). A cikin Alƙur'ani, Allah (swt) ya ce:

﴿وَلَا تَقُولُوا۟ لِمَنْ أَلْقَىٰٓ إِلَيْكُمُ ٱلسَّلَٰمَ لَسْتَ مُؤْمِنًا﴾ النساء: ٩٤

***"Kada ku ce ga wanda ya yi muku sallama kai ba mumini ba ne" An-Nisa'i: 95***

Ya zo a Hadisi a cikin Bukhari da Muslim daga ibnu Umara, Manzon Allah (saw) ya ce:-

(أمرت أن أقاتل الناس حتى يشهدوا أن لا إله إلا الله، وأن محمدا رسول الله، ويقيموا الصلاة، ويؤتوا الزكاة، فإذا فعلوا ذلك عصموا منى دمائهم وأموالهم إلا بحق الإسلام، وحسابهم على الله)

***"An hore ni in yaƙi mutane har su shaida babu wanda ya cancanci bauta sai Allah, kuma Muhammadu, Manzon Allah ne, su tsayar da sallah, su bada zakka. Idan suka aikata waɗannan sun kiyaye jinainansu da dukiyoyinsu daga gare ni sai da alhakin Musulunci hisabinsu yana ga Allah."***

Amma Ijma'i ko Ahlussunnah sun haɗu a kan duk wanda ya yi furuci da shahada biyu waɗanda aka ambata cikin Hadisi, hukunce-hukuncen Musulunci suna gudana a kansa kamar auratayya da shi da yi masa sallah idan ya mutu da yi masa wanka da turbuɗe shi a maƙabartar Musulmi matsawar kafircinsa bai bayyana ba ga aiki kamar sujada ga gunki ko kuma da zance kamar musun abin da aka sani ga addini.

Wanda yake bayyane, Malam Abdussalami ɗan Ibrahima Al-Laƙƙani ya faɗa a cikin littafinsa, *Ithaful Muridi,* imanin da ke isar mutum a duniya shi ne wanda ya faɗa bayyane. Hukunce-hukuncen Musulunci za su gudana a kansa a nan duniya ba za a ce kafiri ba ne sai in ya bayyanar da aikin da ke nuna kafircinsa kamar sujada ga gunki.

Alƙali Iyad ya ce: a cikin littafinsa, *Ashfa;* "hukunce-hukucen Musulunci waɗanda suka ratayu ga shugabanni da masu hukunci na Musulmi su ne yin hukunci bisa ga abin da yake bayyane don ba a ba wa mutane hanya ba ga abin da yake ɓoye kuma ba a hore su ba da bincikensu har ma shari'ah ta hana hukunci da abin da yake ɓoye. Don haka Manzon Allah (saw):

(هلا شققت عن قلبه)

***"Ya zargi wanda yake haka har ya ce: ma wani me ya hana ka tsaga zuciyarsa ka ga abin da ke ciki"***

Wannan ya nuna rashin yarda da hukuncin abin da ba bayyane ba.

Shaikh Sanusi ya faɗa a cikin littafinsa, *Al'umda Sharhul Kubra;* wajen gina hukunce-hukuncen duniya bayyane don Sunnah ta faɗi rashin bincike daga abubuwan da suke ɓoye sai dai ranar ƙiyama za su bayyana ranar da ake bayyana asirai. A nan wannan maganar ta tuƙe.

Na ce kuma ba ya halatta mu munana zato ga Mumini ɗaya daga cikin Musulmi. Shehu Sanusi ya ce: a cikin *Sharhul Wusɗa;* "amma mutum a kan kula da ɓangaren wani mutum jahili ne ga halin abin da yake cikin zuciyar, wani mutum ba zai yiwu ba ya yi yanke ga abin da waninsa yake ciki ga haƙiƙani. Haka sai dai in Manzon Allah (tsira da aminci su tabbata a gare shi) ya yanka a kan mutum da abu wannan kam za a yi yanke da haka ne don Allah Shi ne Mafi sani da ManzonSa, amma duk da haka mu bai yiwuwa gare mu mu munana zato ga ɗaya daga cikin Musulmi, jahili ne ko ba jahili ba, don sani wurinsa zuciya haka ne sai idan shi, mutum, ya bayyana abin da ke nuna abin da ya ɓoye na mugunyar aƙida. Wannan dole ne a bi hanya mai sauƙi a sanadinsa har a yi masa maganin wannan ciwo da yadda yake yiwuwa. Allah ne ake neman taimako a wajenSa. A nan maganar malamin ta tsaya kuma a nan gabatarwa ta ƙare. Yanzu za mu shiga ga bayanin fasullan littafi.

## FASALI NA ƊAYA

### Bayanin Taƙawa Ga Neman Ilimin Fardu-Aini

Wanda aka sani da cewa Manzon Allah (saw) ya ce:

(طلب العلم فريضة على كل مسلم)

***"Neman ilimi farilla ne a kan kowane Musulmi"***

Ina mai cewa daidaitawa ga sawaba tana wurin Allah. Ya 'yan' uwana ku sani haƙiƙa ilimin da Manzon Allah (saw) ya sanar a wannan Hadisi shi ne ilimin aikacewa wanda aka kallafa wa baligi mai hankali. Ya balaga ne da mafarki ko da shekaru ko kafiri ne ya Musuluntа. Misali da hanci, farkon wajibi a kansa kalmar shahada da lura da ma'anarta ta kusa da lafazinta. Wannan shi ne aka sani tauhidi a zamanin Manzon Allah (saw) da Sahabbansa da tabi'ansa da masu binsu duka. Don haka ya zo a cikin sharhin *Kaukabu* na Abdurrahman As-Suyuɗi. Sa'adda aka tambayi Maliki Ilmul-kalami da tauhidi, sai ya ce: Ba zai yiwu ba mu zaci Annabi (saw) ya sanar da al'ummarsa ko da kama ruwa kuma bai sanar da su Tauhidi ba. Tauhidi wanda Annabi (saw) ya faɗa:

(أمرت أن أقاتل الناس حتى يقولوا لا إله إلا الله)

***"An hore ni in yaƙi mutane har su ce La'ilaha Ilallahu"***

Abin da ake tsare dukiyar mutum da jininsa don shi, shi ne tauhidi na haƙiƙa, zuwa ga reshe ne. Kurɗabi ya yi nuni inda yake cewa "farkonsu tauhidi." A nan wannan maganar ta tuƙe.

Na ce Shugabana mai yara ya faɗa a cikin *Ad-durrus Saminu* ya ce:. An tambayi Sanusi, shin an sharɗanta ga imanin baligi mai hankali ya san ma'anar kalimar shahada bisa ga fuska, wannan da ka ambata a cikin *Aƙidatus-Sugra* ko ba a sharɗanta ba? Sai ya ce: wannan ba a sharɗanta shi ba sai dai don kamala ga imani amma dai abin da aka sharɗanta ga inganci sanin ma'ana bisa fuska wanda ya ƙunshi tafsili (rarrabewa). Sannan ya ce: Babu shakka abin da ya fi rinjaya ga Muminai, jahilansu da malamansu, shi ne sanin wannan don kowane ɗaya daga cikinsu ya san Allah Shi ne Mai halitta kuma ba a halicce Shi ba kuma Shi ne Mai azurtawa ba wani mai azurta Shi. Wannan shi ne ma'anar wadatassa (Jalla wa'azza).

Bai neman buƙata daga kowa kuma kowa na neman buƙata zuwa gare Shi, kuma sun san ba a sallah, ba a azumi, ba a hajji sai don Shi, Kuma ba wani wanda ake bautawa sai Shi. Shi ne ma'anar cewarSa "Shi ne macancancin bauta ba waninSa ba." A nan wannan magana ta tsaya.

Abin nufinmu a kan kawo wannan Magana shi ne faɗakar da mutane fara karatu da littattafai masu Ilmul-kalami. Bai ayyana ba a kan kowane ɗaya ga barin neman sanin abin da yake tsayar da addininsa kamar yadda jahilai daga masu neman ilimi suke faɗa.

An tambayi ibnu Rashdin daga hukuncin wasu jama'a cikin masu Ilmul-kalami suna cewa fara karatun littattafan masu Ilmul-kalami ya ayyana a kan malami da jahili tun kafin mutum ya san al'amarin addininsa kamar alwala da sallah da sauran ibadodi waɗanda suke farilla a kansa har suna kafirta wanda ya saɓa wa wannan Magana. Sai ya ce: ai wannan abu da suka zo da shi shi ne kafirci domin suna nufin cewa, mutane ba za su yi sallah ba, ba za su yi azumi ba, ba za su yi zakkah ba har sai sun san Allah ta wannan hanyar mai zurfi takan yiwu ba za su iya gane wannan ba sai bayan zamani mai tsawo ko hankalinsu ya kasa fahimta; su kasa saninsa sai su fita cikin taron Musulmi. Manjuri ya kawo wannan a cikin *Sharhul Muhassal.*

Na ce kwatankwacin waɗannan, Abul-Abbasi ɗan Shuraihu ya ce: a cikin sharhin *Kaukabu* na Abdurrahmani As-Suyuɗi sa'adda aka tambaye shi daga tauhidi sai ya ce:. "Tauhidin mutanen sani da jama'ar Musulmi shi ne kalmomi biyu na shahada, cewa babu wani abin bauta da cancanta sai Allah, kuma Muhammadu manzonSa ne." Tauhidi masu ƙarairai shi ne kutsawa ga siffofi da cikaikai. A nan wannan maganar ta tsaya.

Malam Gazali ya ce: a cikin littafinsa, *Ihya'u Ulumuddini,* gun ambaton Hadisin neman sani farilla ne ga kowane Musulmi ba wani ilimi da ake nufi sai ilimin ayyukan da aka kallafa wa baligi mai hankali, su ko kashi uku ne; "Ilimin Aƙida da Aiki da Bari.

To, idan yaro ya balaga ta mafarki ko ta shekaru ko kafiri ya musulunta farkon yini ga misali, farkon wajibi a kansu shi ne sanin kalmomi biyu na shahada da lura da ma'anarsu. Ba wajibi ba ne a kansa sai ya yi nazari ya yi bincike ya kafa dalilai, abin da ya isa shi gasganta a cikin zuciyarsa kawai ya yi yanke domin kuwa Manzon Allah (saw) da Larabawan da ba su san addini ba suka je wajensa, ya gamsu da gasgatawar da suka yi da faɗi a bakinsu ba tare da ya sanar da su kafa dalilai a kan haka ba.

To, idan mutum ya faɗa kamar yadda suka faɗa ya bada wajibi ne na cikin lokacin, a kan haka ilimin da yake farilla a kansu a cikin wannan lokaci, sanin Kalmar Shahada da lura da ita a cikin wannan lokaci da ya mutu bayan haka, ya mutu mai yi wa Allah ɗa’a ba mai saɓo ba, sai dai daga baya abubuwan da ke wajaba za su gitto. Waɗannan abubuwa da ke gittowa imma su zamo ga aiki ko ga bari ko ga aƙida. Amma aiki ga wanda ke rayuwa daga hantsi har lokacin azuhur ya zama sabo ne gare shi kamar sanin tsarki da sallah da abin ya tsaya ne har rana ta gushe bai samu cika neman sanin da aikin ba takan yiwu lokaci ya fita da ya shagala da neman sani, To, mafi kusa wanda yake bayyananne ya wajaba ya gabatar da neman sanin a kan lokaci yakan yiwu a ce wajabcin sani wanda yake sharaɗi ne ga aiki; yakan zo bayan wajabcin aiki; ba shi wajaba gabanin gushewar rana.

Sanin ba ya wajaba kafin gushewar rana, haka ga sauran salloli. Kuma idan ya rayu har zuwa ga Ramadana kuma ilimi ya sabunta sanin wajabcin azumi, ya sabunta gun isowar Ramadana, shi ne daga safe zuwa faɗuwar rana kuma wajibi gare shi niyya da kamewa daga ci da saduwa da iyali kuma zai miƙe har zuwa ga fita wani wata.

Idan ya samu dukiya ko yana da dukiya lokacin balagarsa, ya lizimta ya nemi sanin abin da ya wajaba a kansa na zakkah. Kuma ba a cewa yanzu sai ya san shi amma idan shekara ta yi kusa sai ya san shi tun daga lokacin da ya musulunta idan kafiri ne. Kuma idan dukiyarsa raƙumma ne kawai ba dole ba ne a kansa ya nemi sanin zakkar tumaki, haka nan sauran abubuwan da aka wa zakkah gun cika shekara daga sa’adda ya musulunta.

Idan watannin Hajji suka shiga ba dole ba ne ya yi gaggawa zuwa ga sanin Hajji tare da cewa, aikin yana da jinkiri, to, saninsa ba dole ba ne yanzu-yanzu amma ya kamata malaman Musulunci su farkar da shi a kan cewa Hajji farilla ne a kan jinkiri ga duk wanda ke da guzuri da abin hawa. Idan dai ya mallaki abin har da yawa, yakan yi hattara da kansa sai ya yi gaugawa. To, idan ya yi niyyar Hajji, dole ne ya san yadda ake Hajji da sanin *Rukunan Hajji* waɗanda hajji bai tsayuwa sai da su da wajibansa amma babu dole sai ya san nafiloli amma saninsu shi ma ba farillah ba ne.

Haramcin yin shuru a kan faɗakarwa bisa ga wajabcin asalin Hajji a yanzu yana da nazari, nazari wanda wurin da za a san shi littattafan *fiƙihu.* mataki ga ilimin sauran ayyuka waɗanda suke farilla ne.

Amma barin saninshi ya wajaba bisa gwargwadon halin da ke sabunta shi kuwa yana saɓawa ga halin mutum don ko sanin maganar da ke haramun

ba wajibi ne ba a kan bebe. Haka nan ba wajibi ne a kan makaho ya san abin da dubinsa ya ke haram, haka nan mutumin jeji ba dole ba ne ya san wurin da zama yake halatta gare shi a garuruwa. Irin waɗannan sun danganta a kan abin da hali ya nuna, abin da aka san ba ya tare da shi ba dole ba ne ya nemi saninsa kamar abubuwan da suka gabata amma abin da yake tare da shi, ya wajaba a faɗakar da shi a kansa, kamar lokacin da ya musulunta yana sanye da alhariri ko yana cikin gidan ƙwace ko yana dubin haram. To, wajibi ne a sanar da shi waɗannan abubuwan yadda suke ga shari'ah. Amma abin da bai tare da shi amma zai sadu da shi a kusa kamar cin abinci idan yana cikin garin da ake shan giya, ana cin alade, to, wajibi ne a sanar da shi haramcinsu. A taƙaice duk abin da neman saninsa yake wajibi, to, wajibi ne a sanar da shi, wannan.

**Aƙida da Ayyuka na Zuciya:-** Saninsu ya wajaba gwargwadon tunane-tunane idan kokwanto ya gitta masa ga ma'anonin kalmar Shahada. To, wajibi ne a kansa ya nemi sanin da ke gusar da kokwanto, Idan kuma wannan tunanin bai zo masa ba har ya mutu tun bai ƙudurta cewa Maganar Allah ba ta da farko kuma cewa Allah Mai saɓani ne ga fararru da sauran abubuwan da ake Ambato ga aƙida, to, ya mutu a kan Musulunci bisa ga haɗuwar Malamai. To, sai dai waɗannan tunane-tunane da ke gitta wa aƙida sashensu daga ɗabi'a ne sashensu ko ji ne ga mutanen gari idan ya zama cikin garin da maganar bidi'a ta watsu. To, ya kamata a tsare shi a cusa masa gaskiya tun farkon balagarsa don kar abin da ba gaskiya ba ya rigaya cikin zuciyarsa, da abin da ba gaskiya ba ya faɗa a cikin zuciyarsa dole ne a gusar da shi da yawa gusar da shi yake wuyata.

Haka idan wannan Musulmin ya zamo ɗan kasuwa a cikin garin da riba ta watsu, to, dole ne a tsoratar da shi daga riba. Wannan shi ne gaskiya ga sanin Farlu-Aini.

Malam Gazali ya ce: bayan ya yi wata magana; "abin da ya kamata tun farko a yi gaugawar jefa masa imani da cewa akwai aljannah da wuta da tayar da mutane da tara su har ya yi imani da shi kuma shi gasganta idan ba daga wani addini ya fita ba. To, sanin waɗancan abubuwan yana daga cikar kalmomi biyu na shahada. Haƙiƙa, bayan ya gasgata Manzo (saw), to, ya kamata a sanar da shi manzancin da Manzo ya zo da shi. Shi ne cewa wanda ya bi Allah da ManzonSa zai samu aljannah, wanda ya saɓa wa Allah da ManzonSa zai shiga wuta. Idan kake da waɗannan matakai, za ka san wannan hanyar gaskiya ce:, za ka tabbatar da cewa kowane bawan Allah a kan halayensa da ke gudana; yininsa da darensa ba zai wofinta daga abubuwan da

ke abkuwa a cikin ibadodinsa da mu'amalarsa waɗanda ke sabunta a kansa bisa wajibi ba.

Ya wajaba ya tambaya dukkan abin da ya ga ya auku gare shi daga cikin abubuwan da ke lizimta, to, dole ne ya yi gaugawa ya nemi sanin abin da zai auku kusa mafi rinjiya. Haƙiƙa dai, ya bayyana nufin da Manzon Allah (saw) yake nufi da ilimi inda yake cewa "*Ɗalabul Ilmi Faridatun*" yana nufin aikin da aka shedi wajabcinsa ga Musulmi, to, a nan fuska kuwa ga wajabcinsa ta bayyana.

## FASALI NA BIYU

### Bayanin Abin Da Allah Ya Yi Baiwa Da Shi Ga Mutane Shi Ne Ba Su Dalilan Saninsa Su Ne Halitta Ta Addini Da Gani Da Ji Wanda Ya Wuce A Karyata Da Nazari Da Abin Da Ba Sai An Yi Nazari Ba

Halitta ta addini ita ce wadda Allah Maɗaukakin Sarki ya ce:

﴿فِطْرَتَ ٱللَّهِ ٱلَّتِى فَطَرَ ٱلنَّاسَ عَلَيْهَا ۚ لَا تَبْدِيلَ لِخَلْقِ ٱللَّهِ﴾ الروم: ٣٠

***"Halitta ta Allah wadda Ya halicci mutane da ita babu canji ga halittar Allah" Rum: 30***

Manzon Allah (saw) ya ce:

(كل مولود يولد على الفطرة، فأبواه يهودانه أو ينصرانه أو يمجسانه)

***"Dukkan abin haihuwa ana haihuwarsa a kan halitta ta addinin Musulunci amma uwarsa da ubansa su za su mayar da shi Bayahude ko Banasare ko Bamaguje."***

Gazali ya ce: a cikin *Ihya'u;* don haka Allah ya aiko Annabawa dukkansu don kiran talikai ga kaɗaita Allah don su faɗi kalmar Shahada, ba a hore su ba su ce muna da wanda Ya halicce mu ko talikai suna da Ubangiji. Haƙiƙa, sanin wannan ya zamo tun ga halitta hankulansu tun daga farkon tsatsawarsu da farkon ƙuruciyarsu. Don haka Allah Maɗaukakin Sarki ya ce:

﴿فَأَقِمْ وَجْهَكَ لِلدِّينِ حَنِيفًا ۚ فِطْرَتَ ٱللَّهِ ٱلَّتِى فَطَرَ ٱلنَّاسَ عَلَيْهَا ۚ لَا تَبْدِيلَ لِخَلْقِ ٱللَّهِ﴾ الروم: ٣٠

***"Ka tsayar da fuskarka ga addini na gaskiya halittar da Allah ya halicci mutane a kanta (ba canji ga halittar Allah)" Rum: 30***

Wannan shi ne addini daidaitacce don haka halittar mutum ga shaidar da Alƙur'ani ya zo da ita ta wadatar daga kafa dalili.

Abdulwahabi Ash-Sha'arani ya faɗa a cikin littafinsa, *Alyawaƙitu Wal-Jawahir;* Ibnu Arabi ya ce: a cikin babi na tis'in da tara (99) abin da ya bayyana shi ne; Allah (swt) ya halicci rai cikakke mai hankali kuma wanda ya san kaɗaita Allah Ta'alah ya tabbata cewa, Allah Shi ne Ubangijin

wannan halitta ta addini wadda Ya halicci mutane a kanta kamar yadda Hadisi ya nuna

(كل مولود يولد على الفطرة، فأبواه يهودانه أو ينصرانه أو يمجسانه)

***"Dukkan abin haihuwa haƙiƙa ana haihuwarsa a kan halittar addinin Musulunci amma uwarsa da ubansa su za su mayar da shi Bayahude ko Banasare ko Bamaguje."***

A nan maganar ta tuƙe.

Na ce abin da kafirai ke nufi ga bauta wa gumaka shi ne kusanta zuwa ga Allah, Allah ya ce:

﴿وَالَّذِينَ اتَّخَذُوا مِن دُونِهِ أَوْلِيَاءَ مَا نَعْبُدُهُمْ إِلَّا لِيُقَرِّبُونَا إِلَى اللَّهِ زُلْفَىٰ﴾ الزمر: ٣

***"Waɗanda suka riƙi ba Allah ba, abin bauta suna cewa ba mu bauta musu ba sai don su kai mu kusa ga Allah." Zumar: 3***

Abduljalil ya ce: a cikin *Shu'abil Imani;* "Talikai dukansu, an bauta musu ba Allah ba" sa'annan ya faɗi dukkan nau'o'in waɗanda aka bautawa sai ya ce: abin neman masu bauta wa Allahn da ake yi wa bauta don ya tabbata ga halitta ta addini ba makawa akwai mai halitta kuma sun haɗu a kan kasancewarsa Allah sai dai sun yi saɓani ga Allahn wane ne Shi? Shi wane irin abu ne? A nan maganar ta tuƙe.

Don haka Shehu Sanusi ya ce: a cikin littafinsa, *Nurus-Sa'adati* sharhin littafinsa, *Sugra;* ba jayayya ga cewa akwai Allah Jalla Wa'azza gun dukkan masu hankali daga dai wanda ya kafirce ya kafirce ne da ƙara wanin Allah. Don haka kore wasu Alloli shi ne ake buƙata kuma da shi tauhidi yake tabbata. Ka lura da wannan. A nan magana ta tuƙe.

Abdulwahabi Ash-Sha'arani ya faɗa a cikin littafinsa, *Al-Yawaƙitu Wal-Jawahiru;* mutane dukansu suna nuna akwai Mai halitta Ya girma Ya ɗaukaka. sai dai hanyoyinsu sun saɓa sun jahilci haƙiƙanin Zati. Don haka Annabawa da Manzanni ba su zo ba ne kawai don su sanar da mu akwai Mai halitta, a'a sun zo ne don su kira mu ga kaɗaita Shi da sanin cewa, jin-ƙai da aminci su tabbata a kansu. Da sun zo don su sanar da mu akwai Allah da Allah bai ce:

﴿ فَٱعۡلَمۡ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا ٱللَّهُ ﴾ محمد: ١٩

*“Ka san haƙiƙanin ba wanda ya cancanci bauta sai Allah” Muhammad: 19*

Da cewa Zai yi ka san kana da Mahalicci. Haka inda Ya ce:

﴿ وَلِيَعۡلَمُوٓاْ أَنَّمَا هُوَ إِلَٰهٞ وَٰحِدٞ ﴾ إبراهيم: ٥٢

*“Don su san Allah Shi ne Makaɗaici.” Ibrahim: 52*

Idan aka ce da wane irin abu masu kafa dalili ga wannan suka shiga? Jawabi; sun shiga wannan don halitta da ke tsinkaya zuwa ga wancan abin, kamar kafa dalili da samar da samammu bisa ga abin da ya rinjaya da kama da Shi. Kuma sun san abin da halittar addini ta sheda da shi, shi ya fi kusa da talikai kuma shi ya fi kusa ga hankali domin abin da ke yiwuwa halal ne da abin da ke faruwa wanda ke nuna wanda ya fara shi. Waɗannan sun tsayu a kan nazari ingantacce. Wancan kuwa abu ne wanda ba sai an yi nazari ba.

Allah Ta’ala ya ce:

﴿ أَمَّن جَعَلَ ٱلۡأَرۡضَ قَرَارٗا ﴾ النمل: ٦١

*“Wane ne ya sanya ƙasa matabbata” Namli:61*

Kuma ya ce:

﴿ أَمَّن يُجِيبُ ٱلۡمُضۡطَرَّ إِذَا دَعَاهُ ﴾ النمل: ٦٢

*“Wane ne ke karɓa wa matsattse idan ya kira shi?” Namli:62*

Kuma Ya ce:

﴿ أَمَّن يَبۡدَؤُاْ ٱلۡخَلۡقَ ثُمَّ يُعِيدُهُۥ ﴾ النمل: ٦٤

*“Wane ne ke ƙaga halitta? Sa’annan Ya mayar da ita? Namli:64*

Da wasu Ayoyi waɗanda ba waɗannan ba waɗanda suke sun zo da kamar tambaya amma tabbatarwa ce. Kamar dai Allah Ta’ala ya tabbatar wa BayinSa abin da Ya halicce su a kansa, don haka Hadisi ya zo. Annabi ya ce:

(أن الله خلق العباد على معرفته؛ فما بعث الرسل إلا للتذكير بتوحيد الفطرة وتطهيره عن تسولات الشيطان)

***"Allah Ya halicci Bayi Ya sa sun san Shi, Bai aiko Manzanni ba sai don tunatarwa da tauhidin fiɗira (halitta ta addini) da kuma tsarkake su daga ƙawace-ƙawacen Sheɗan."***

A nan wannan maganar ta tuƙe.

Amma abin da ake gani, haƙiƙa, Allah Ta'ala ya ce:

﴿وَإِذْ أَخَذَ رَبُّكَ مِنۢ بَنِىٓ ءَادَمَ مِن ظُهُورِهِمْ ذُرِّيَّتَهُمْ وَأَشْهَدَهُمْ عَلَىٰٓ أَنفُسِهِمْ أَلَسْتُ بِرَبِّكُمْ ۖ قَالُوا۟ بَلَىٰ ۛ شَهِدْنَآ ۛ أَن تَقُولُوا۟ يَوْمَ ٱلْقِيَـٰمَةِ إِنَّا كُنَّا عَنْ هَـٰذَا غَـٰفِلِينَ ﴿١٧٢﴾ أَوْ تَقُولُوٓا۟ إِنَّمَآ أَشْرَكَ ءَابَآؤُنَا مِن قَبْلُ وَكُنَّا ذُرِّيَّةً مِّنۢ بَعْدِهِمْ ۖ أَفَتُهْلِكُنَا بِمَا فَعَلَ ٱلْمُبْطِلُونَ ﴿١٧٣﴾﴾ الأعراف: ١٧٢ – ١٧٣

***"Ka ambaci sa'adda Ubangijinka ya yi riƙo daga 'ya'yan Adama, zuriyarsu a cikin bayansu, (Ya fitar da sashensu cikin sashe, wasu na haihuwar wasu) sai Ya sheda musu ga kawunansu, shin Ban zama Ubangijinku ba? Sai suka ce mun sheda da haka. Shedarsu wannan fa don kar ranar Alƙiyama su ce ai mu mun zamo rabkanannu ga tauhidi ba mu san shi ba, ko su ce haƙiƙa ubanninmu suka yi shirka tun gabaninmu. Mu kuma mun zamo zuriya bayansu sai muka yi koyi da su. Shin za Ka halaka mu a kan abin da uwayenmu maɓarnata suka aikata?." A'araf:172-173***

Abdulwahhabi Ash-Sha'arani ya faɗa a cikin littafinsa, *Al-Yawaƙitu Wal-Jawahir:* To, in duka rayuka sun karɓa sun ce na'am, to, don me wasu suka karɓa wasu suka ƙiya? Kamar yadda Alhakimu At-Tirmizi ya faɗa inda ya ce: Haƙiƙa, Allah Ta'ala ya bayyana ga rayukan kafirai da ban tsoro da Ya tambaye su sai suka karɓa da cewa, Shi ne Allahnsu don tsoronSa sai imaninsu bai amfane su ba, kamar imanin munafukai. Sai Ya bayyana ga muminai da rahama sai suka karɓa maSa a kan ɗa'a sai imaninsu ya amfane su.

Sa'annan ya ce: Shaikh Abu Ɗahir Al-ƙazwini ya tsawaita magana ga wannan sa'annan ya ce: abin da ke inganta a wajena; kafirai da suka karɓa suka ce Ubangijinsu ne sun yi jawabi ne daidai da tambaya don kuwa Allah

Ta'ala ya tambaye su daga Ubangijinsu bai tambaye su daga abin bautarsa ba, su kuwa lokacin ba su zama cikin zamanin kallafa bauta ba, a lokacin suna cikin halin tabbatarwa da gani (wato tabbatar da cewa akwai Ubangiji wanda Shi ne halitta ta addini) don haka lokacin da Ya ce: shin Ni ba Ubangijinku ba ne? Sai suka ce Kai Ubangijinmu ne don ganin da suka yi a lokacin gani na halarce sai suka gasgata dukansu.

Sa'adda suka zo ga zamanin kallafa ibada da kuma bayyanar abin da Allah Ta'ala ya hukunta da saninSa wanda ya rigaya da zamowa wani mai arziki wani mara shi sai ya zamo daga cikinsu akwai wanda ƙudurtawarsa ta yi daidai da abin da Ya faɗi a farko kuma daga cikinsu akwai wanda ya saɓa. Da Allah Ta'ala Ya tambaye su shin ba Ni kaɗai Nike ba? Suka ce Kai kaɗai Kake da ba zai yiwu ba ɗaya daga cikinsu ya yi shirka, ka lura. A nan wannan maganar ta tuƙe.

Amma maganar da ta wuce a musanya cewar da Allah ya yi:

﴿ وَلَئِن سَأَلْتَهُم مَّنْ خَلَقَهُمْ لَيَقُولُنَّ ٱللَّهُ ﴾الزخرف: ٨٧

***"Idan ka tambaye su wane ne ya halicce su? Za su ce Allah" Zukruf:87***

﴿ وَلَئِن سَأَلْتَهُم مَّنْ خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ وَسَخَّرَ ٱلشَّمْسَ وَٱلْقَمَرَ لَيَقُولُنَّ ٱللَّهُ ﴾العنكبوت: ٦١

***"Kuma idan ka tambaye su wane ya halicci sammai da ƙassai, ya hore rana da wata? Za su gaya ma Allah." Ankabuti:61***

Haka Allah ya ce:

﴿ قُلْ مَن يَرْزُقُكُم مِّنَ ٱلسَّمَآءِ وَٱلْأَرْضِ أَمَّن يَمْلِكُ ٱلسَّمْعَ وَٱلْأَبْصَٰرَ وَمَن يُخْرِجُ ٱلْحَىَّ مِنَ ٱلْمَيِّتِ وَيُخْرِجُ ٱلْمَيِّتَ مِنَ ٱلْحَىِّ وَمَن يُدَبِّرُ ٱلْأَمْرَ فَسَيَقُولُونَ ٱللَّهُ ﴾يونس: ٣١

***"Wane ne ke azurta ku daga sama da ƙasa? Ko wane ne ke mallakar ji da gani? Kuma wane ne ke fitar da mai rai daga matacce kuma ya fitar da matacce daga mai rai? Kuma wa ke zartar da al'amari? Za su ce Allah." Yunus:31***

Kuma Allah Ta'ala ya ce:

﴿ قُلْ مَن رَّبُّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ ٱلسَّبْعِ وَرَبُّ ٱلْعَرْشِ ٱلْعَظِيمِ ﴿٨٦﴾ سَيَقُولُونَ لِلَّهِ ﴾

المؤمنون: ٨٦ – ٨٧

***"Musu wane ne Ubangijin sammai bakwai kuma Ubangijin Al'arshi mai girma? Za su ce na Allah ne." Mu'uminina:86-87***

Kuma Allah Ta'ala ya ce:

﴿ فَلَا تَجْعَلُوا لِلَّهِ أَندَادًا وَأَنتُمْ تَعْلَمُونَ ﴿٢٢﴾ ﴾ البقرة: ٢٢

***"Kar ku sanya tamkoki ga Allah alhali kuwa kun san Bai da tamka" Baƙara:22***

Abdulwahhabi Ash-Sha'arani ya ce: duka tarsashin mutane a sassan ƙasa, rayukansu sun amince da cewa akwai wanda ya halicce su ba tare da wani ya sanar da su ba kuma ba tare da tabbatar musu hujja ba, kuma ba wani abu da suka haɗu a kansa game da gano hakan, mutanen kuwa da Kurɗawa da Turkawa da mutanen jeji da na Indiya da China da waɗanda kira bai kai gare su ba (waɗanda ma ba su san Musulunci ba ko kafirci). A nan wannan maganar ta tsaya.

Na ce ka san haƙiƙa Tawaturi yana amfanar da ilimi wanda ba sai an yi tunani ba, haƙiƙa, Abdussalami binu Ibrahim Al-Laƙƙani ya ce: a cikin *Ithahul Muridi Bijauharatit Tauhidi;* "babu wani saɓani ga sanin Allah ga wanda ya tashi a cikin gidajen Musulunci cikin manyan birane da ƙananan garuruwa ko cikin sahara koko ya samu labari katamamme ga halin Annabi (saw) ga abin da ya zo da shi a mu'ujizoji (kawo abin da hankali ke ɗaukar ba ya yiwuwa sai ga Manzon Allah). A nan wannan maganar ta tuƙe.

Don haka Abdul'azizi Al-Andulisi ya ce: sanin da ba sai an yi tunani ba, haƙiƙa, wanda ya san Annabi (saw) ya ga mu'ujizarsa ko labari tabbatacce ya zo gare shi har ya samu sani a cikin labarin, to, haƙiƙa shi ya zamo masani ga abin da ya tabbata gare shi ko aka gaya masa ba tare da ya yi nazari na hankali ba ko ƙiyasi na Ilmul manɗiƙi (wanda a cikinsa ilmul kalami ya fito).

﴿ أَفَلَمْ يَنظُرُوٓا۟ إِلَى ٱلسَّمَآءِ فَوْقَهُمْ كَيْفَ بَنَيْنَٰهَا وَزَيَّنَّٰهَا وَمَا لَهَا مِن فُرُوجٍ ﴿٦﴾ وَٱلْأَرْضَ
مَدَدْنَٰهَا وَأَلْقَيْنَا فِيهَا رَوَٰسِىَ وَأَنۢبَتْنَا فِيهَا مِن كُلِّ زَوْجٍۭ بَهِيجٍ ﴿٧﴾ تَبْصِرَةً وَذِكْرَىٰ لِكُلِّ عَبْدٍ مُّنِيبٍ
﴿٨﴾ وَنَزَّلْنَا مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءً مُّبَٰرَكًا فَأَنۢبَتْنَا بِهِۦ جَنَّٰتٍ وَحَبَّ ٱلْحَصِيدِ ﴿٩﴾ وَٱلنَّخْلَ بَاسِقَٰتٍ لَّهَا
طَلْعٌ نَّضِيدٌ ﴿١٠﴾ رِّزْقًا لِّلْعِبَادِ ۖ وَأَحْيَيْنَا بِهِۦ بَلْدَةً مَّيْتًا ۚ كَذَٰلِكَ ٱلْخُرُوجُ ﴿١١﴾ ﴾ ق: ٦ - ١١

***“Haƙiƙa, Allah Ta’ala ya ce: “E ba su yi dubi ba zuwa ga sama’u wanda ke sama gare su, yaya Muka gina shi kuma Muka ƙawata shi, babu wasu tsagunne gare shi Kuma Muka shimfiɗa ƙasa Muka jefa duwatsu tabbatattu a cikinta? Kuma Muka tsirar da kowaɗanne nau’o’i biyu masu ban sha’awa a cikinsa domin lurarwa da kuma tunatarwa ga dukkan Bawa mai komawa ga ɗa’arMu kuma Mun saukar da ruwa mai albarka daga sama Muka sanya gonaki suka yi tsiro da shi, da shuka wadda ake girbewa kuma da dabinnai alhali masu tsawo suna da gunda wanda ya hau juna duk don ɗai azurta Bayi, kuma Muka raya gari matacce da waɗannan ruwan. Kamar wannan rayawa fita daga ƙabari yake.” Kaf:6-11***

A cikin tafsirin *Al-Jalalaini Na Mahalli;* wannan kamar tambaya ce: amma tabbatarwa ce, kamar dai sun yi dubi sun san abin da aka ambata. A nan wannan maganar ta tuƙe.

Na ce don wannan nazarin mai sauƙi ne domin kowa na iya gane shi, Shaikh Sanusi ya ce: a cikin *Al-Umdah Sharhu Kubra;* “wannan nazarin ya isa ga sanin Allah Ta’ala ko da kuwa wani bai sanar da kai ba, Sai dai Isma’ilawa sun saɓa.” Don haka ya ce: a cikin *Nurul Sa’adati;* “wannan nazari ba mai nisa ba ne don ko tabbatuwarsa ga mafi yawan wannan al’umma koko ga dukkansu” don haka ya ce: A cikin sharhin *Alƙasidatu Aljaza’iriyya;* “Wannan nazarin da mai kaifin hankali da wanda ba ya da shi da mai ƙarfi da mai rauni duk ɗaya suke gare shi” don haka Ahmadu binu Hajarin Al-Haisani ya ce: a cikin *Alfathul Mubini;* “Da ƙyar za ka ga mai ratayuwa ga maganar wani ga imani da Allah Ta’ala domin muna samun maganar jahilai cike da kafa dalili ga samuwar Allah Ta’ala ga siffofinSa.” A nan wannan magana ta tuƙe.

Abdulwahhabi Ash-Sha’arani ya ce: a cikin *Yawaƙitu Wal-Jawahir;* Malamin Malamanmu, Shaikh Kamaluddini binu Hammamu ya ce: kawo Taƙlidi (ratayuwa ga maganar wani kawai) ga matsalolin imani yana da wuya

ƙwarai da ƙyar za ka ga ɗaya muƙallidi da imani ga Allah da ManzonSa ba tare da dalili ba, ko da jahilai ne don kuwa maganarsu da suke yi a cikin kasuwanni cike take da kafa dalili ga halittu da samuwar Mai halitta da siffofinSa.

Don haka Abdurrahmanu As-Sayuɗi ya ce: a cikin sharhin *Kaukabu;* Shehu Diya’uddini Al-Karani ya zama yana da geme mai tsawo har ƙasan ƙafafunsa wanda idan ya hau dabba zai raba gashin biyu, duk wanda ya gan shi daga jahilla sai su dinga cewa tsarki ya tabbatar wa Mai halitta; shi kuma yana cewa na sheda jahillai muminai ne da nazari domin sun kafa dalili da aiki a kan wanda Ya yi shi.

Sheikh Sanusi ya ce: a cikin sharhin *Kasidatul Jaza’iriyya;* wannan nazari shi ne hanyar Allah ga tabbatar da dalilai cikin LittafinSa mai girma, sa’annan Sunnar zaɓaɓɓenSa ManzonSa (saw); “me ya fi albarkar wannan hanyar? Kuma me ya fi ta nasiha ga shiryarwa don ƙumsawarta, shiriya gamamma da samun biyan buƙata da dukkan wanda aka daidaita yana neman saduwa zuwa ga gaskiya?”

Na ce misalin wannan nazari a cikin Ayoyin Alƙur’ani cewar da Allah Ta’ala ya yi;

﴿إِنَّ فِي خَلْقِ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَٱخْتِلَٰفِ ٱلَّيْلِ وَٱلنَّهَارِ وَٱلْفُلْكِ ٱلَّتِي تَجْرِي فِي ٱلْبَحْرِ بِمَا
يَنفَعُ ٱلنَّاسَ وَمَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مِن مَّآءٍ فَأَحْيَا بِهِ ٱلْأَرْضَ بَعْدَ مَوْتِهَا وَبَثَّ فِيهَا مِن كُلِّ
دَآبَّةٍ وَتَصْرِيفِ ٱلرِّيَٰحِ وَٱلسَّحَابِ ٱلْمُسَخَّرِ بَيْنَ ٱلسَّمَآءِ وَٱلْأَرْضِ لَءَايَٰتٍ لِّقَوْمٍ يَعْقِلُونَ ﴿١٦٤﴾

﴾ البقرة: ١٦٤

***“Haƙiƙa Ayoyi masu gwada ikon Allah ga mutane masu hankali sun tabbata da halittar sammai da ƙassai da saɓawar dare da rana da jirage waɗanda ke gudu a cikin gulbi da abin da ke amfanar mutane da abin da Allah ya saukar daga sama na ruwa, Ya raya ƙasa da shi bayan mutuwarta, Ya watsa a cikinta daga duk abin da ke tafiya a kan ƙasa da jujjuya iskoki da giragizzai waɗanda aka hore tsakanin sama da ƙasa.” Baƙara:164***

Kuma da cewar da Ya yi:

﴿ وَفِي الْأَرْضِ قِطَعٌ مُتَجَاوِرَاتٌ وَجَنَّاتٌ مِنْ أَعْنَابٍ وَزَرْعٌ وَنَخِيلٌ صِنْوَانٌ وَغَيْرُ صِنْوَانٍ يُسْقَىٰ بِمَاءٍ وَاحِدٍ وَنُفَضِّلُ بَعْضَهَا عَلَىٰ بَعْضٍ فِي الْأُكُلِ ۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَآيَاتٍ لِقَوْمٍ يَعْقِلُونَ ﴿٤﴾ ﴾ الرعد: ٤

***"A cikin ƙasa akwai wurare waɗanda suka saɓa suna kusa da juna da gonaki na Inibbai, shuka da dabinnai waɗanda suke tawaye ne (waɗanda suka fito ga ginda ɗaya suka rarrabu) da kuma waɗanda suka fito su kaɗai ana shayar da su da ruwa ɗaya, kuma Muka sanya wasu suka fi wasu a wajen ci, za ka samu mai zaƙi da mai tsami." Ra'adi:4***

﴿ أَلَمْ تَرَ أَنَّ اللَّهَ أَنْزَلَ مِنَ السَّمَاءِ مَاءً فَأَخْرَجْنَا بِهِ ثَمَرَاتٍ مُخْتَلِفًا أَلْوَانُهَا ۚ وَمِنَ الْجِبَالِ جُدَدٌ بِيضٌ وَحُمْرٌ مُخْتَلِفٌ أَلْوَانُهَا وَغَرَابِيبُ سُودٌ ﴿٢٧﴾ وَمِنَ النَّاسِ وَالدَّوَابِّ وَالْأَنْعَامِ مُخْتَلِفٌ أَلْوَانُهُ كَذَٰلِكَ ﴾ فاطر: ٢٧ – ٢٨

***"Haƙiƙa, ayoyi sun tabbata ga waɗannan abubuwan ga mutanen da ke lura. Kuma da cewar da Ya yi; "E, saninka bai sadu ba haƙiƙa Allah ya saukar da ruwa daga sama ba, kuma Muka fitar da 'ya'yan itace waɗanda launukansu suka saɓa da ruwan? Kuma da hanyoyi farare da jajaye a cikin duwatsu waɗanda suke launinsu ya saɓa? Da manyan duwatsu baƙaƙe? Haka daga mutane da dabbobi da dabbobin da ake ci waɗanda launinsu ya saɓa kamar yadda launin itace da duwatu ya saɓa?" Fatir:27-28***

Waliyyin Allah, Ibn Abi Jamrata, ya ce: a cikin *Bhajatul Nufusi* Sharhin Bukhari; Haƙiƙa, wannan nazari shi ne mutum ya riƙi nazari da kafa dalili bisa ga abin da Allah ya yi horo a cikin LittafinSa, shi ne nazari bisa ga abin da ke sama na taurari bisa ga saɓawarsu da rana da wata da kwanukan duhun wata da cikar haskensa da abin da ke cikin ƙasa na wurare da saɓaninsu. Haka nan abin da ke cikin ƙasa na ruwaiwai masu daɗi da masu zabci, haka nan abin da ke cikin 'ya'yan itace da saɓawar ɗanɗanonsu tare da zamowarsu, an shayar da su da ruwa ɗaya kuma sun fito a wuri ɗaya. Wannan nazari da kafa dalili kamar yadda muka nuna ya isa ga cikar imani. A nan wannan maganar ta tuƙe.

Na ce wannan yana isuwa ga cikar imani domin kuwa mutum na zamowa masani ga wannan nazari. Don haka Ahmadu binu Zikra ya ce: A

cikin *Muhassinul Maƙasidī;* “sanin Mai halitta yana tabbata bisa ga dalilai na sassa daban-daban da rayuwa.” Don haka Jawarini ya ce: a cikin *Aƙidatul Muwahhidin;* “ana sanin wanda ya yi halitta da ganin halitta, kamar da ganin sana’o’i ake sanin wanda ya yi su.” Kuma a wajen cuta, haƙiƙa, Allah Ta’ala ya ce:

﴿ ثُمَّ إِذَا مَسَّكُمُ ٱلضُّرُّ فَإِلَيْهِ تَجْـَٔرُونَ ﴾ النحل: ٥٣

***“Idan cuta ta same ku, zuwa ga Allah za ku ɗaukaka sauti kuna roƙo” Nahli:53***

Kuma Allah Ta’ala ya ce:

﴿ وَإِذَا مَسَّكُمُ ٱلضُّرُّ فِى ٱلْبَحْرِ ضَلَّ مَن تَدْعُونَ إِلَّآ إِيَّاهُ ﴾ الإسراء: ٦٧

***“Idan wahala ta same ku a cikin gulbi, waɗanda kuke kira ba Allah ba, duk sai su ɓace muku sai ku dinga kiran Allah” Isra’i:67***

Kuma Ya ce:

﴿ وَإِذَا غَشِيَهُم مَّوْجٌ كَٱلظُّلَلِ دَعَوُا۟ ٱللَّهَ مُخْلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَ ﴾ لقمان: ٣٢

***“Idan taguwar ruwa ta zo musu tamkar duwatsu masu inuwa ƙasa gare su sai su kira Allah suna masu farance addini gare su.” Luƙman:32***

Abdulawahhabi As-Sha’arani ya ce: a cikin *Yawaƙitu Wal-Jawahiru;* Idan aka ce mene dalili bisa ga cewa sanin Allah Ta’ala tabbatacce ne? Ai dalilin wannan sanin mai sauƙi ne don kuwa idan mutum ya matsu, hanyoyi suka doɗe gare shi, ba makawa sai ya dogara ga Allah, ya koma a wajenSa yana dogara gare Shi domin Ya kuranye masa musifar, zuciyarsa ta ɗaukaka wajen sama sai idanunsa su turo zuwa sama don kuwa sama shi ne alƙiblar addu’a ga dukkan Talikai sai ya nemi agaji ga wanda Ya halicce shi kuma ya ƙaga shi ba tare da wata wahala ko dubara ba.

Irin wannan, ana samunsa har ga namun jeji da dabbobi, suna bayyana tsoro da tsammani, suna ɗaukaka kanuwansu sama idan suka rasa ciyawa da ruwa, ta san za ta halaka ta ƙare. Haka mun ga ‘yan jarirai gun tsanani suna ɗaukaka manunayyensu wajen sama. Wannan ya zamo ga halittar dabbobi balle mutum mai hankali? Wannan ita ce halittar Addini wadda aka ambata cikin Alƙur’ani da Hadisi sai dai mafi yawa mutane sun shagala a lokacin sauƙi sai dai idan wahala ta zo su koma ga Allah.

Allah Ta’ala ya ce:

﴿ وَإِذَا مَسَّكُمُ ٱلضُّرُّ فِي ٱلۡبَحۡرِ ضَلَّ مَن تَدۡعُونَ إِلَّآ إِيَّاهُۖ ﴾الإسراء: ٦٧

***“Idan wahala ta same ku a cikin gulbi wadanda kuke kira sai su ɓace muku sai Allah kawai kuke kira.”Isra’i:67***

Sa’annan Ya ce: bayan wata magana, idan aka ce cewar da Manzon Allah S.A.W. ya yi; na hore ka da addinin tsofaffi, shin hani ne ga kafa dalili na hankali ko ba hani ba ne? Wannan bai zamo hani ba ga kafa dalili na hankali, warkarwa ce daga abutar wancan hali wanda ya hankalci amintattun mutane a kansa daga sababbi da tsofaffi.

Shehu Abu Ɗahirin Alƙazwini ya cirato cewa ya gani a cikin littafin (Addinan Larabawa) cewa Manzon Allah (saw) ya ce wa Imrana binu Hussaini:

(كم لك من إله ؟"، فقال:" عشرة "، قال:" فمن لهمك، ولكربك، والأمر العظيم إذا نزل بكودهاك؟"، فقال:"الله"، فقال النبي ﷺ:" فما لك يا عمران بن حصين من إله إلا الله)

***“Allah nawa gareka? Ya ce: goma. To, wane ne Allanka lokacin da wani muhimmin abu ya dame ka da baƙin ciki da kuma wani al’amari mai girma ya sauka a kanka ya dame ka? Sai ya ce: Allahu, sai Manzon Allah (saw) ya ce: Kai, Imranu binu Hussaini, ba ka da wani Ubangiji sai Allah sai ya musulunta.”***

Daga wannan fuska ce cewa Allah Ta’ala:

﴿ فَلَمَّا رَأَوۡاْ بَأۡسَنَا قَالُوٓاْ ءَامَنَّا بِٱللَّهِ وَحۡدَهُۥ وَكَفَرۡنَا بِمَا كُنَّا بِهِۦ مُشۡرِكِينَ ٨٤ ﴾ غافر: ٨٤

***“Sa’adda suka ga tsananinMu sai suka ce mun yi imani da Allah Shi kaɗai mun kafirce wa abin da muka zamo muna tarayya da Allah.” Gafir: 84***

A nan wannan magana ta tuƙe.

Na ce don cewa wahala tana daga cikin sabubban sanin Allah. Ahmadu binu Zikra ya ce: a cikin *Muhassilul Maƙasiɗi;* ‘Ɓawa idan wahala ta same shi, zai san Allah ba sai an sanar da shi ba.” Don haka Ibn Aɗa’illahi

ya ce: a cikin *Alhikamu;* "Idan Allah ya buɗa maka hanyar saninSa, to, kar ka damu ko da aikinka ƙanƙane ne."

Idan ka fahinci abin da ya gabata na dalilan sanin Allah Ta'ala waɗanda Ya yi baiwa da su ga mutane daga halitta ta addini da abin da ake gani da jin da ya wuce a musanya da nazari da abin da ba sai an yi nazari ba. Maganar da Shaikh Sanusi da ya yi a cikin *Sharhul Wusɗa* za ta bayyana a gare ka, abin da ya ce: ba zai yiwu ba gare mu mu munana zato ga ɗaya daga Musulmi, ya zama jahili ko ba jahili ba, don kuwa sani, wurinsa zuciya. Don haka ba za mu yi yanke ba ga mutum don cewa ya ratayu ga maganar wani don kawai halshensa ya gaza da dalilai na aƙida. Takan yiwu ya zamo ya sani sai dai ba zai iya bayanin da ake ganewa ba, Malaman Zayyawa sukan kasa bayanin abin da ke cikin zukatansu, to, balle jahilai. A nan wannan magana ta tuƙe.

Kuma maganar Shaikhul Islami Zikra Al-Ansariyyu ta bayyana gare ka cewa aƙidojin jahilai ingantattu ne da haɗuwar dukan masu bin shari'a masu hankali na ƙwarai ko da ba su yi dubi ba ga littattafan masu Ilmul-kalami. Kuma maganar Abubakar ibnu Fauraki a cikin *Annizam* ta bayyana gare ka cewa "jahilai dukansu sun san Allah." Kuma maganar Abu Mansurin ta bayyana a gare ka cewar da ya yi; "abokanenmu sun haɗu a kan cewa jahilai muminai ne kuma sun san Ubangijinsu kuma suna cike da Aljanna kamar yadda Hadisai suka zo da shi kuma haɗuwar Malamai ta tabbata da shi." A nan wannan magana ta tuƙe.

## FASALI NA UKU

### Bayanin Sanin Asullan Addini Da Rarrabewa Tsakaninsa Da Ilmul Kalami Da Bayanin Riƙon Aƙida Ta Asullan Addini Daga Alƙur'ani Mai Girma Kuma Haƙiƙanin Allah Ta'ala Ya Tabbatar Da Asullan Addini A Cikin Alƙur'ani Mai Girma

(Ina cewa, Allah ne Mai daidaitawa ga sawaba) amma iyakar da ake sanin asullan addini shi ne kamar yadda Abdurrahman Sayuɗi ya faɗa a cikin littafinsa, *Annuƙaya*; "Ilimi ne wanda ka bincika daga abin da yake wajaba a ƙudurta shi a wajen Allah." Ya kuma ce a cikn sharhin *Kaukabu*; Ilimi ne wanda ka bincika daga abin da ƙudurta shi ke wajaba da kuma abin da yake wajaba gare shi da abin da ke hanuwa gare shi daga siffofi da aiko Manzanni da halullukan makoma (Lahira) bisa ga ƙa'ida ta Musulunci.

Amma bambamci tsakaninsa da ilimin kalami, Sayuɗi ya ce: A cikin *Itmamud-Diraya Sharhun-Nuƙaya* inda ya ambaci asullan Addini ya ce: "Ilmul kalami shi ne wanda ake kafa dalilai na hankali kuma a cirato maganganun masu falsafa." Kuma ya ce: a cikin sharhin *Kaukabu;* Mai *Jam'ul-Jawami'i* ya kasa shi kashi biyu (2), Na aiki shi ne wanda ƙudurta shi yake wajaba, na ilimi kuwa ba na aiki ba, shi ne wanda sanin shi ba dole ba ne ga aƙida, yana cikin ƙarin ilimi kawai. Sannan ya ce: abin da a haƙiƙa; wannan kashi na biyu ba za a ce mishi asullan addini ba sai dai a ce yana daga cikin (Ilmul-kalami). Ko na farko idan kafa dalilai na hankali ya zo tare da kawo maganganun mutane, bidi'a ga masu falsafa, ko shi ma *Ilmin kalami* ne. Idan kuma bai haɗe da maganar mutane ba bidi'a da falsafa, to, shi ake cewa asullan addini waɗanda ake ganewa ba da wani dogon tunani ba.

Sannan ya ce: na shafe wannan kashi na biyu amma na zo da na ɗaya don shi ne asullan addini waɗanda ake ganewa ba da tuntuni ba. Sannan ya ce: Zan yi bayaninsa a nan bisa ga hanyar mutanen Sunnah kamar yadda ya zo a cikin Alƙur'ani da Hadisai waɗanda suka taro masu yawa suka ruwaito bisa ga hanya mai amfani, wani bai rigaye ni ba ga wannan bayani. A nan maganar ta tuƙe.

Amma bayanin wajabcin riƙon aƙida daga asullan addini da a cikin Alƙur'ani mai girma;`hakika, Abdulwahhabi Sha'arani ya faɗa a cikin littafinsa, (Al-yawakitu wal-jawahiru). Ibn Arabi ya ce: cikin littafinsa, (Al-futuhatu). Idan mutun ya yi imani da Alƙur'ani kuma ya tabbata maganar Allah ne, abin da ke wajibi kansa ya riƙi aƙidarsa da ke gare shi ba tare da

biɗar wata ma'ana ba, kuma ba tare da bin dalilai na hankali ba waɗanda ba na shari'a ba. Amma Alƙur'ani dalili ne tabbatacce ga ji da kuma hankali.

Amma bayanin cewa Allah ya tabbatar da waɗannan asullah cikin Alƙur'ani mai girma ya 'yan'uwana ku san Allah Ta'ala ya tabbatar da duka asullan addini daga wajen Ubangiji da Annabawa da abubuwan da aka jiya a cikin Alƙur'ani mai girma don kuwa Ya tabbatar da asulin imani da cewar da Ya yi:

﴿ءَامِنُواْ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ﴾ النساء: ١٣٦

*"Ku yi imani ga Allah da ManzonSa." Nisa'i:136*

Ya tabbatar da rukunnan imani (waɗamda bai tsayuwa sai da su) inda Yake cewa;

﴿وَلَٰكِنَّ ٱلْبِرَّ مَنْ ءَامَنَ بِٱللَّهِ وَٱلْيَوْمِ ٱلْءَاخِرِ وَٱلْمَلَٰٓئِكَةِ وَٱلْكِتَٰبِ وَٱلنَّبِيِّـۧنَ﴾ البقرة: ١٧٧

*"Amma mai nagarta shi ne wanda ya yi imani da Allah da ranar Lahira da Mala'iku da Littattafan Allah da Annabawa" Baƙara:177*

Kuma Ya tabbatar da haƙiƙanin imani shi ne gasganta duk abin da Annabawa suka zo da shi gaba ɗaya da cewar da Ya yi:

﴿قُولُوٓاْ ءَامَنَّا بِٱللَّهِ وَمَآ أُنزِلَ إِلَيْنَا وَمَآ أُنزِلَ إِلَىٰٓ إِبْرَٰهِـۧمَ وَإِسْمَٰعِيلَ وَإِسْحَٰقَ وَيَعْقُوبَ وَٱلْأَسْبَاطِ وَمَآ أُوتِىَ مُوسَىٰ وَعِيسَىٰ وَمَآ أُوتِىَ ٱلنَّبِيُّونَ مِن رَّبِّهِمْ لَا نُفَرِّقُ بَيْنَ أَحَدٍ مِّنْهُمْ وَنَحْنُ لَهُۥ مُسْلِمُونَ ﴿١٣٦﴾﴾ البقرة: ١٣٦

*"Ku ce mun yi imani da Allah da abin da aka saukar muna da abin da aka saukar wa Ibrahimu da Isma'ilu da Is'haƙa da Yaƙuba da Asbaɗu da abin da aka ba Musa da Isah da abin da aka ba Annabawa daga Ubangijinsu, ba mu bambantawa tsakanin ɗaya daga gare su, mun musulunta mun bada gaskiya gare Shi." Baƙara:136*

Ya tabbatar da faruwar Talikai inda Yake cewa:

﴿ٱللَّهُ خَٰلِقُ كُلِّ شَىْءٍ﴾ الزمر: ٦٢

*"Allah Shi Ya halicci kowane abu" Zumar:62*

Ya tabbatar da cewa Samamme ne inda Yake cewa:

﴿ ذَٰلِكَ بِأَنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلْحَقُّ ﴾ الحج: ٦

*"Haƙiƙa, Allah Shi ne Mai tabbataciyar samuwa" Hajji:6*

Kuma Ya tabbatar da rashin farkonSa da rashin ƙarshe inda Yake cewa:

﴿ هُوَ ٱلْأَوَّلُ وَٱلْآخِرُ ﴾ الحديد: ٣

*"Shi ne Mara farko kuma Mara ƙarshe" Hadid:3*

Ya tabbatar da rashin kamarSa da Talikai inda Yake cewa:

﴿ لَيْسَ كَمِثْلِهِۦ شَىْءٌ ﴾ الشورى: ١١

*"Ba wani abu wanda ke kama da Shi" Shura:11*

Kuma Ya tabbatar da kaɗaitarSa inda Yake cewa:

﴿ إِنَّ إِلَٰهَكُمْ لَوَٰحِدٌ ﴿٤﴾ ﴾ الصافات: ٤

*"Allanku ɗaya ne" Safat:4*

Ya tabbatar da wadatarSa daga kowa inda Yake cewa Shi ne mawadaci. Ya tabbatar da ikonSa da cewarSa:

﴿ إِنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ﴿٢٠﴾ ﴾ البقرة: ٢٠

*"Haƙiƙa, Allah Mai iko ne bisa ga kowane abu" Baƙara:20*

Kuma Ya tabbatar da nufinSa da cewa:

﴿ فَعَّالٌ لِّمَا يُرِيدُ ﴿١٦﴾ ﴾ البروج: ١٦

*"Shi mai yawan aikata abin da Yake nufi ne" Buruji:16*

Kuma Ya tabbatar da saninSa da cewa:

﴿ أَنَّ ٱللَّهَ بِكُلِّ شَيۡءٍ عَلِيمٌ ﴾ البقرة: ٢٣١

*"Allah ya san komai" Bakara:231*

Kuma Ya tabbatar da dauwamarSa da cewa:

﴿ هُوَ ٱلۡحَيُّ ﴾ البقرة: ٢٥٥

*"Shi ne dauwamamme." Bakara:255*

Haka Ya tabbatar da jinSa da ganinSa da cewar da Ya yi:

﴿ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡبَصِيرُ ﴾ الإسراء: ١

*"Shi ne Mai ji Mai gani." Isra'i:1*

Kuma Ya tabbatar da maganarSa da cewar da Ya yi:

﴿ وَكَلَّمَ ٱللَّهُ مُوسَىٰ تَكۡلِيمٗا ﴾ النساء: ١٦٤

*"Allah ya yi magana da Musa." Nisa'i:164*

Kuma Ya tabbatar da dukan Siffofi na cika sun tabbata gare Shi inda Yake cewa:

﴿ وَلِلَّهِ ٱلۡمَثَلُ ٱلۡأَعۡلَىٰ ﴾ النحل: ٦٠

*"Misali, Madaukaki yana a wajen Allah" Nahli:60*

Da cewar da Ya yi:

﴿ وَلِلَّهِ ٱلۡأَسۡمَآءُ ٱلۡحُسۡنَىٰ ﴾ الأعراف: ١٨٠

*"Sunaye kyawawa sun tabbata a gare Shi" A'araf:180*

Da cewar da Ya yi:

﴿ سُبۡحَٰنَ رَبِّكَ رَبِّ ٱلۡعِزَّةِ عَمَّا يَصِفُونَ ﴾ الصافات: ١٨٠

*"Tsarki ya tabbatar wa Ubangijinka Ubangijin girma." Safat:180*

Ya tabbatar da cewa Mai yin yadda Ya so ne ga aikatawa da bari inda Yake cewa:

﴿وَرَبُّكَ يَخْلُقُ مَا يَشَاءُ وَيَخْتَارُ﴾ القصص: ٦٨

***"Ubangijinka yana halittar abin da Ya so kuma Yana yin yadda Yake so." Kasasi:68***

Kuma Ya tabbatar da cewa Ya aiko Manzanni kafin Annabi Muhammadu (saw) inda Yake cewa:

﴿وَلَقَدْ أَرْسَلْنَا رُسُلًا مِّن قَبْلِكَ﴾ غافر: ٧٨

***"Haƙiƙa, Mun aika Manzanni gabaninka." Gafir: 78***

Kuma Ya tabbatar da Muhammadu, ManzonSa ne kuma cikon Annabawa ne inda Yake cewa:

﴿مَّا كَانَ مُحَمَّدٌ أَبَآ أَحَدٍ مِّن رِّجَالِكُمْ وَلَٰكِن رَّسُولَ ٱللَّهِ وَخَاتَمَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ﴾ الأحزاب: ٤٠

***"Muhammad ba Uban ɗaya ba ne daga cikin mazajenku sai dai Manzon Allah ne cikon Annabawa." Ahzaf:40***

Ya tabbatar da gaskiyar Manzanni da cewarSa:

﴿هَٰذَا مَا وَعَدَ ٱلرَّحْمَٰنُ وَصَدَقَ ٱلْمُرْسَلُونَ ۝٥٢﴾ يس: ٥٢

***"Wannan abin da Mai rahama Ya yi muku alƙawali ne kuma Manzanni sun yi gaskiya" Yasin:52***

Ya tabbatar da amincin Annabawa inda Yake cewa:

﴿إِنِّي لَكُمْ رَسُولٌ أَمِينٌ ۝١٠٧﴾ الشعراء: ١٠٧

***"Ni, Manzo nike amintacce zuwa gare ku." Shu'ara'i:107***

Ya tabbatar da sun idar da Manzanci inda Yake cewa:

﴿ٱلَّذِينَ يُبَلِّغُونَ رِسَٰلَٰتِ ٱللَّهِ﴾ الأحزاب: ٣٩

***"Waɗannan da ke ida Manzancin Allah" Ahzaf:39***

Ya tabbatar da cewa suna aure da cewa:

﴿ وَجَعَلْنَا لَهُمْ أَزْوَاجًا وَذُرِّيَّةً ﴾ الرعد: ٣٨

*"Mun sanya mataye gare su da zuri'a." Ra'adi:38*

Kuma Ya tabbatar da cewa suna cin abinci, suna saye da sayarwa inda Yake cewa:

﴿ إِنَّهُمْ لَيَأْكُلُونَ الطَّعَامَ وَيَمْشُونَ فِي الْأَسْوَاقِ ﴾ الفرقان: ٢٠

*"Suna cin abinci, suna tafiya a cikin kasuwanni." Furƙan:20*

Ya tabbatar da Mala'iku da littattafan sama cewa:

﴿ كُلٌّ آمَنَ بِاللَّهِ وَمَلَائِكَتِهِ وَكُتُبِهِ ﴾ البقرة: ٢٨٥

*"Muminai sun yi imani da Allah da Mala'ikunSa da littattafanSa" Baƙara:285*

Kuma Ya tabbatar da mutuwa da ƙarin kwana inda Yake cewa:

﴿ وَمَا كَانَ لِنَفْسٍ أَنْ تَمُوتَ إِلَّا بِإِذْنِ اللَّهِ كِتَابًا مُؤَجَّلًا ﴾ آل عمران: ١٤٥

*"Ba ya yiwuwa ga rayuwa ta mutu sai da izinin Allah, kuma an rubuta mata ajali" Ali-Imrana:140*

Ya tabbatar da muminai za su yi jawabi inda ake tambayarsu a cikin ƙabari, kuma Ya tabbatar da ɓacewar kafirai daga jawabi da cewar da Ya yi:

﴿ يُثَبِّتُ اللَّهُ الَّذِينَ آمَنُوا بِالْقَوْلِ الثَّابِتِ فِي الْحَيَاةِ الدُّنْيَا وَفِي الْآخِرَةِ ۖ وَيُضِلُّ اللَّهُ الظَّالِمِينَ ۚ وَيَفْعَلُ اللَّهُ مَا يَشَاءُ ﴿٢٧﴾ ﴾ إبراهيم: ٢٧

"*Allah yana tabbatar da muminai ga magana tabbatatta a nan duniya da lahira, Yana ɓatar da kafirai." Ibrahim:27*

Kuma Allah yana yin yadda Yake so. Kuma Ya tabbatar da ni'imar barzahu (bayan mutum ya mutu kafin tashin ƙiyama). Cewar da Ya yi:

﴿ فَأَمَّآ إِن كَانَ مِنَ ٱلْمُقَرَّبِينَ ﴿٨٨﴾ فَرَوْحٌ وَرَيْحَانٌ وَجَنَّتُ نَعِيمٍ ﴿٨٩﴾ ﴾ الواقعة: ٨٨ – ٨٩

*"Amma wanda ya zamo daga makusanta yana samun hutawa da ƙamshi da aljannar ni'ima" Waƙi'ah:88-89*

Da kuma inda Yake cewa:

﴿ وَأَمَّآ إِن كَانَ مِنْ أَصْحَٰبِ ٱلْيَمِينِ ﴿٩٠﴾ فَسَلَٰمٌ لَّكَ مِنْ أَصْحَٰبِ ٱلْيَمِينِ ﴿٩١﴾ ﴾ الواقعة: ٩٠ – ٩١

*"Idan ya zamo a cikin mutanen dama, aminci ya tabbatar wa daga cikin mutanen dama" Waƙi'ah: 90-91*

Kuma Ya tabbatar da azabar barzahu da Yake cewa:

﴿ وَأَمَّآ إِن كَانَ مِنَ ٱلْمُكَذِّبِينَ ٱلضَّآلِّينَ ﴿٩٢﴾ فَنُزُلٌ مِّنْ حَمِيمٍ ﴿٩٣﴾ وَتَصْلِيَةُ جَحِيمٍ ﴿٩٤﴾ ﴾ الواقعة: ٩٢ – ٩٤

*"Amma idan ya zamo daga masu ƙaryatawa ɓatacce, abin da za a ba shi ya sha tun daga farko shi ne ruwan zafi da ƙuna a cikin wuta." Waƙi'ah: 94*

Ya tabbatar da Kiyama za ta zo inda Yake cewa:

﴿ إِنَّ ٱلسَّاعَةَ لَءَاتِيَةٌ لَّا رَيْبَ فِيهَا ﴾ غافر: ٥٩

*"Haƙiƙa, Kiyama mai zuwa ce ba kokwanto gare ta" Gafir:59*

Kuma Ya tabbatar da tayar da matattu da cewarSa:

﴿ وَحَشَرْنَٰهُمْ فَلَمْ نُغَادِرْ مِنْهُمْ أَحَدًا ﴿٤٧﴾ ﴾ الكهف: ٤٧

*"Mun tara su ba Mu bar ko ɗaya daga cikinsu ba" Kahfi:47*

Kuma Ya tabbatar da hisabi da cewarSa:

﴿ يَوْمَ يَقُومُ ٱلْحِسَابُ ﴿٤١﴾ ﴾ إبراهيم: ٤١

*"Ranar da hisabi ke tsayuwa" Ibrahim:41*

Ya tabbatar da bada littattafai da cewarSa:

﴿فَأَمَّا مَنْ أُوتِيَ كِتَٰبَهُۥ بِيَمِينِهِۦ﴾ الحاقة: ١٩

*"Amma wanda aka bai wa littafinsa da damarsa" Al-Haƙƙah:19*

Muminai ke nan, da kuma inda Ya ce:

﴿وَأَمَّا مَنْ أُوتِيَ كِتَٰبَهُۥ بِشِمَالِهِۦ﴾ الحاقة: ٢٥

*"Wanda aka bai wa littafinsa da hagunsa" Al-Haƙƙah:25*

Kafirai ke nan. Kuma Ya tabbatar da awon ayyuka da cewar da Ya yi:

﴿وَٱلْوَزْنُ يَوْمَئِذٍ ٱلْحَقُّ﴾ الأعراف: ٨

*"Awo ranar nan gaskiya ne" A'araf:8*

Kuma Ya tabbatar da siraɗi inda Ya ce:

﴿فَٱهْدُوهُمْ إِلَىٰ صِرَٰطِ ٱلْجَحِيمِ ﴿٢٣﴾﴾ الصافات: ٢٣

*"Ku gaugauta su zuwa ga siraɗi na wuta" Saffat:23*

Kuma Ya tabbatar da *Kausar* (Tabkin Annabi (saw)) da cewarSa:

﴿إِنَّآ أَعْطَيْنَٰكَ ٱلْكَوْثَرَ ﴿١﴾﴾ الكوثر: ١

*"Haƙiƙa, Mun ba ka AlkausarAlkausar" Kausar:1*

Kuma Ya tabbatar da wuta da cewarSa "Haƙiƙa Mun yi tattalin wuta ga azzalumai" kuma Ya tabbatar da Aljanna da cewarSa:

﴿إِنَّآ أَعْتَدْنَا لِلظَّٰلِمِينَ نَارًا﴾ الكهف: ٢٩

" *Ya saka musu da Aljannah da alharir a kan haƙurin da suka yi" Kahfi:29*

(Yana nufin Muminai), kuma Ya tabbatar da ceto da cewa:

﴿وَجَزَىٰهُم بِمَا صَبَرُوا۟ جَنَّةً وَحَرِيرًا ﴿١٢﴾﴾ الإنسان: ١٢

*"Ana tsammanin Ubangijinka zai tayar da kai matsayi godadde" Insan:12*

Da kuma cewarSa:

﴿عَسَىٰٓ أَن يَبۡعَثَكَ رَبُّكَ مَقَامٗا مَّحۡمُودٗا ٧٩﴾ الإسراء: ٧٩

*"Ubangijinka Zai yi ma baiwa har ka yarda", Isra'i: 79*

Da kuma cewarSa:

﴿وَلَا يَشۡفَعُونَ إِلَّا لِمَنِ ٱرۡتَضَىٰ﴾ الأنبياء: ٢٨

*"Ba su ceto sai wanda Allah ya yarda su ceta" Al-Anbiya'i:28*

Kuma Ya tabbatar da cewa muminai za su gan Shi a lahira da cewarSa:

﴿وُجُوهٞ يَوۡمَئِذٖ نَّاضِرَةٌ ٢٢ إِلَىٰ رَبِّهَا نَاظِرَةٞ ٢٣﴾ القيامة: ٢٢ – ٢٣

*"Fuskoki ranar nan masu haske ne, suna dubin Ubangijinsu." Al-Kiyamah:22-23*

Waɗannan su ne asullan addini na wajen Allah da ManzanninSa da abubuwan da aka jiya, dukansu Allah ya tabbatar da su a cikin Alƙur'ani mai girma kuma Ya wajaba a kan dukkan baligi mai hankali ya ƙudurta su kamar yadda suka zo domin dukansu sun zo ga nassi wanda ya tabbata kuma ya wuce a yi musunsa don kuwa Alƙur'ani dukansa tabbataccen abu ne wanda ba hanyar musunsa ko ta yaya.

Abdulwahabi Ash-sha'arani a cikin littafinsa, *Al-yawaƙitu Wal-jawahir* Ibn Arabi, ya ce: a farkon littafinsa, *Al-Futuhatu;* duk makewayar ingancin aƙida a kan yanke da ita ko da ya riƙi imaninsa a kan ratayuwa ga magana wadda take yanke wadda ta zo ga mai shar'antawa Shi ne Allah. To, haka nan ya zama mafi amincewa daga wanda ke riƙon imaninsa a kan kafa dalilai don kuwa mai kafa dalilai yana yiwuwa ya samu ɗimuwa ko rikici a kanta.

Ya kuma ce a cikin wannan littafin da aka ambata; haƙiƙa, ratayuwa ga wanda aka tsare daga son rai da kure, ai kamar ilimi take kuma ta fi ilimin nazari ƙarfi kamar yadda karɓar shedarmu a kan al'ummomi waɗanda suka shuɗe cewa Annabawansu sun iyar musu aiken Allah, ga shi kuwa ba mu cikin zamanin da aka iyar musu saƙon sai dai mun gasgata Allah da abin da

Ya gaya muna a cikin LittafinSa, daga labarin mutanen Nuhu da Adu da Samudu da Fir'aunu da wasun su. Wannan shedar ba za a karɓe ta ba a ranar Alƙiyama sai ga wanda tun a nan duniya ya tabbatar a zuciyarsa haka lamarin yake. A nan maganar ta tuƙe.

Malam Sanusi ya ce: a cikin littafinsa, *Al-Umadatu Sharhul-Kubra* yana mai kawo maganar Ibnu Arafata cikin littafinsa, *Shamil.* "Abin da yake ratayuwa ga maganar wani shi ne yin yanke ga abin da wanda ba tsararre ba ga kure ya faɗa." To, ashe ban da yin yanke ga abin da Annabi Muhammad (saw) ya faɗa da abin da Malamai duk suka taru a kansa da sanin abin da Kalmar shahada ta nuna.

Manjuri ya ce: Kudurta abin da wanda aka tsare daga son rai ya faɗa, ba ratayuwa ga maganar wani ne ba, shi sani ne cikakke domin shi ya yi yanke da ingancinsa da gaskiyarsa domin wancan da ya faɗa dalili kuwa sanin mu'ujiza, abin da Allah ke ba Annabawa wadda ta wuce hankalin mutum. Kamar tsagewar wata biyu da maganar dabbobi. A nan wannan maganar ta tuƙe.

Na ce wannan da aka faɗa duka yana ga wanda ya ratayu ga Alƙur'ani ba tare da ya yi nazari ga dalilansa ba, amma wanda har ya yi nazari ga dalilan Alƙur'ani ba saɓanin cewa masani ne wanda ya kai ƙoli kuma ya yi nesa ga duk wani rikici domin kuwa dalilan a bayyane suke.

Malam Sanusi ya ce: A cikin sharhin *Alƙasidatul-Jaza'iriyya;* Wanda ya binciki masani ga wurin da jinjirin wata zai tsayi har ya gan shi da idonsa a wurin nan, kamar wanda ya yi binciken Alƙur'ani a wajen ɗaya daga cikin Malaman gaskiya har ya nuna masa wurin kowace aƙida da dalilanta har ya gan ta bayyane matuƙar bayyanawa. Sannan ya ce: ba ɓoye yake ba ga dukkan mai hankali cewa wanda ya ga aƙida ga Alƙur'ani da dalilanta kuma bisa basira, to, masani ne wanda ya kyautata sani. Ba za a ce masa mai ratayuwa ga maganar wani ba amma ya zama wanda ke shiriya zuwa ga dalilai waɗanda ya gani na aƙidar tauhidi a cikin Alƙur'ani.

Gazali ya ce: A cikin *Ihya'u* amma abin da ya tattaru a cikin Alƙur'ani daga dalilai bayyanannu waɗanda suke hankali zai karɓe su da wuri (a cikin lokaci) da jinsu, to, wannan abin shi ne sananne ga kowa. Ilimi na cikin Alƙur'ani shi ne ilimi duka.

Na ce misalin dalilan Alƙur'ani bayyanannu shi ne cewar Allah Ta'ala:

﴿ لَوۡ كَانَ فِيهِمَآ ءَالِهَةٌ إِلَّا ٱللَّهُ لَفَسَدَتَا ﴾ الأنبياء: ٢٢

*"Da akwai wasu Alloli gare su ba Allah ba, da sun ɓace" Al-Anbiya'i:22*

Da cewar da Ya yi kuma:

﴿ قُل لَّوۡ كَانَ مَعَهُۥٓ ءَالِهَةٌ كَمَا يَقُولُونَ إِذًا لَّٱبۡتَغَوۡاْ إِلَىٰ ذِي ٱلۡعَرۡشِ سَبِيلًا ۝٤٢ سُبۡحَٰنَهُۥ وَتَعَٰلَىٰ عَمَّا يَقُولُونَ عُلُوًّا كَبِيرًا ۝٤٣ ﴾ الإسراء: ٤٢ – ٤٣

*"Da akwai wasu alloli tare da Shi kamar yadda suke faɗa, da allolin sun nemi hanya zuwa ga Ubangijin al'arshi, Allah ya tsarkaka kuma Ya ɗaukaka daga wannan abin da suke faɗa, ɗaukaka mai girma" Isara'i:42-43*

Kuma da cewarSa:

﴿ وَمَا كَانَ مَعَهُۥ مِنۡ إِلَٰهٍۚ إِذًا لَّذَهَبَ كُلُّ إِلَٰهِۭ بِمَا خَلَقَ وَلَعَلَا بَعۡضُهُمۡ عَلَىٰ بَعۡضٖۚ سُبۡحَٰنَ ٱللَّهِ عَمَّا يَصِفُونَ ۝٩١ ﴾ المؤمنون: ٩١

*"Ba wani Allah tare da Shi, idan kuma da akwai alloli da kowane Allah ya tafi da abin da Ya halitta kuma da sashensu ya girmama a kan sashe, tsarki dai ya tabbatar wa Allah ga abin da suke siffantawa." Mu'uminuna:91*

## FASALI NA HUDU

### Ga Bayanin Haƙiƙa Annabi (SAW) Ya Tabbatar Da Asullan Addini A Cikin Sunnarsa, Ina Cewa Daidaitawa Bisa Ga Sawaba Tana Ga Allah

Ya ‘yan’uwana ku sani haƙiƙa Manzon Allah (saw) ya tabbatar da asullan addini a cikin sunnarsa don kuwa ya tabbatar da asulin imani kamar yadda ya zo a cikin *Sahihul-Bukhari* daga Mu’azu (ra):

**(ما من أحد يشهد أن لا إله إلا الله وأن محمدا رسول الله صدقا من قلبه إلا حرمه الله على النار، يعني: نار الخلود)**

***“Wanda ya shaida ba wanda ya cancanci bauta sai Allah kuma Muhammadu Manzon Allah ne da gaskiya a cikin zuciyarsa sai Allah ya haramta shi daga wuta”***

Yana nufin wutar dauwama.

Kuma ya tabbatar da rukunnan asullan addini kamar yadda suka zo a cikin Hadisin *Muslim* daga Umar Ɗan Haɗɗabi:

**(أن تؤمن بالله وملائكته وكتبه ورسله واليوم الآخر وتؤمن بالقدر خيره وشره)**

***“Ka yi imani da Allah da Mala’ikunSa da LittattafanSa da ManzanninSa da ranar Lahira, ka yi imani da ƙaddara ta alkhairi da sharri.”***

Ya tabbatar da gasgantawa ga duk abin da ya zo da shi kamar yadda ya zo a cikin *Ashfa* daga Abu Huraira;

**(أمرت أن أقاتل الناس حتى يشهدوا أن لا إله إلا الله وحتى يؤمنوا بي وبما جئت به)**

***“An hore ni da in yaƙi mutane har su shaida ba wanda ya cancanci bauta sai Allah kuma har su bada gaskiya gare ni ga abin da na zo da shi.”***

Ya tabbatar da faruwar talikai kamar yadda ya zo a cikin *Sahihul-Bukhari* daga Imrana ɗan Hussaini da cewarsa:

**(كان الله ولم يكن شيء غيره)**

***“Allah samamme ne tun ba kowa waninSa.”***

Kuma ya tabbatar da samuwar Allah Ta'ala kamar yadda ya zo cikin *Sahihul-Bukhari* daga Ibnu Abbas da cewarsa:

(اللهم أنت الحي وأنت نور السماوات والأرض)

***"Allah Kai ne Mai dauwamammiyar samuwa kuma Kai ne annurin sammai da ƙassai"***

Kuma ya tabbatar da rashin farko da rashin ƙarshenSa da cewar da ya yi:

(اللهم أنت الأول فليس قبلك شيء وأنت الآخر وليس بعدك شيء)

***"Allah Kai ne Marashin farko babu wani abu gabanin Ka kuma Kai ne Marashin ƙarshe babu wani abu bayan Ka"***

Kuma ya tabbatar da saɓawarSa ga fararru da cewarsa:

(اللهم أنت العلى الكبير القدوس)

***"Allah Kai ne Maɗaukaki Mai girma abin tsarkakewa daga siffofin fararru"***

Kuma ya tabbatar da wadatarSa da zatinSa cewa:

(اللهم أنت الحي القيوم)

***"Allah Kai ne Mai dauwamammiyar wanzuwa wanda Ya wadata da ZatinSa daga wani"***

Kuma ya tabbatar da kaɗaitarSa da cewarsa:

(اللهم أنت الواحد الأحد الفرد الصمد)

***"Allah Kai ne Makaɗaici wanda Shi kaɗai wanda ake nufi da buƙata"***

Kuma Ya tabbatar da ikonSa da nufinSa da ilminSa da dauwamammar wanzuwa da cewar da ya yi:

(اللهم أنت القدير المقتدر الفعال لما يريد العالم الحي)

***"Allah Kai ne Mai iko Mai yawan aikata abin da Yake nufi, Masani Mai dauwamammiyar wanzuwa"***

Haka kuma ya tabbatar da jinSa da ganinSa da maganarSa a lokacin da ya wuce ga mutane suna shayar da ruwa suna kiran Allah bayyane sai Ya ce musu:

(يا أيها الناس أرفقوا على أنفسكم فإنكم لا تدعون أصم ولا أعمي ولا أبكم ولا غائبا وإنما تدعون من هو سميع بصير متكلم حاضر)

***"Ya ku mutane ku sauwaƙa wa kanuwanku domin haƙiƙa ku ba kurma ba ne kuke kira ba makaho ba, ba bebe ba, ba wanda ba ya nan ba, sai dai Wanda kuke kira Mai ji ne, Mai gani, Mai magana kuma Yana halarce."***

Kuma ya tabbatar da cewa Allah Mai yin yadda Ya so ne ga aikatawa da bari da cewarsa:

(ما شاء الله كان وما لم يشأ لم يكن)

***"Abin da Allah Ya so zai kasance, abin da Bai so ba, ba zai kasance ba."***

Waɗannan Hadisai, Abubakar ɗan Muhammadu ɗan Abubakar shi ya zo da su a cikin littafinsa, *Hujjatul-Mas'uli fi Ilmit-Tauhidi.* Ya tabbatar da rashin farkon Allah da rashin ƙarshenSa, har zuwa nan, kuma ya tabbatar da gaskiyarsa ga dukan abin da ya bada labari da cewarsa:

نعم، فإني (لا أقول إلا حقا؛ )

***"Haka ne ni ba zan faɗa ba sai gaskiya"***

Jawabin da ya yi wa Abdullahi Ibn Umara lokacin da ya ce: masa haka ne in rubuta duk abin da na jiya daga gare ka ko lokacin hushi ko ba da hushi ba? Abudawuda ya ruwaito wannan Hadisin kuma ya tabbatar da amanarsa sa'adda ya ce: wa namijin da ake kira Zil-khuwaisirati:

(ويلك من يعدل إن لم أعدل)

***"Kaiconka! Idan ban yi adalci ba wa ke yi"***

*Sa'adda Zil-khuwaisarati ya ce: masa yi adalci.* Hadisin ya zo cikin *Sahihul-Bukhari* daga Abu Sa'idul-khuduri kuma ya tabbatar da idar da Manzancinsa sa'adda ya ce wa Sahabbansa:

(ألا هل بلغت؟، قالوا:" نعم"، قال: اللهم اشهد! فليبلغ الشاهد الغائب)

***“Ku saurara ku jiya shin na iyar sai suka ce na’am sai ya ce: Allah Ka shaida ku kuma wadanda ke nan ya iyar wa wadanda ba su nan”*** Hadisin ya zo a cikin *Bukhari* daga Abubakar.

Ya tabbatar da halalcin siffa ta mutum ga kansa da cewarsa:

(والله إني لأخشاكم واتقاكم له، لكني أصوم وأفطر، وأصلي وأرقد، وأتزوج النساء، فمن رغب عن سنتي فليس مني)

***“Wallahi, hakika, ni na fi ku tsoron Allah” duk da haka ina azumi kuma ina ci ina sallah, ina kwana, ina auren mata, wanda ya ki Sunnata bai tare da ni”***

Kamar yadda ya zo a cikin *Sahihul Bukhari* daga Anas. Kuma kamar yadda ya tabbatar wa kansa amana da idar da manzanci da siffofi na mutum, ya ayyana su ga dukan ‘yan’uwansa Manzanni, don zamansu Annabawa kuma mutane.

Ya tabbatar da Mala’iku da cewarsa:

(يتعاقبون فيكم ملائكة بالليل وملائكة بالنهار)

***“Mala’ikun dare da Mala’ikun rana suna mayeyeniya a cikinku”***

Tamkar yadda ya zo a cikin *Sahihul-Bukhari*. Kuma ya tabbatar da mutuwa sai da karewar kwana da cewarsa:

(وكل إلى أجل مسمي)

***“Kowa zai kai zuwa ga ajalin da aka ambatar masa”***

Kamar yadda ya zo a cikin Hadisin Usamatu ibn Zaidin a cikin labarin mutuwar dan diyar Annabi (saw). kamar yadda ya zo a cikin *Sahihul-Bukhari*.

Ya tabbatar da tambaya a cikin kabari da cewarsa:

(إن العبد إذا وضع في قبره وتولي عنه أصحابه، آتاه ملكان فيقعدانه فيقولان له: "ما تقول في هذا النبي ﷺ ؟"، فأما المؤمن فيقول: "أشهد أنه عبد الله ورسوله"، وأما الكافر أو المنافق فيقول: "لا أدري)

***“Idan aka saka bawa a cikin ƙabarinsa, waɗanda suka zo da shi suka juya sai Mala’iku biyu su zo mishi; su zaunar da shi, su ce masa me ka ce ga wannan Annabi (saw)? Amma mumini zai ce na sheda haƙiƙa shi, Bawan Allah ne kuma ManzonSa, amma kafiri zai ce ban sani ba.”***

Kamar yadda ya zo a cikin *Sahihul-Bukhari* daga Anas. Kuma ya zo a cikin Abu Dawuda; “Mala’ikun biyu za su ce mishi wane Ubangijinka? Mene addininka, wane ne wannan namiji da aka aiko a cikinku? Mumini zai ce Ubangijina, Allah; addinina, Musulunci; namijin da aka aiko; Manzon Allah ne. Kafiri kuwa a wajen tambayoyin nan uku zai ce ban sani ba.”

A cikin *Tirmizi* ana cewa ɗayan Mala’ikun, Munkarun; ɗayan kuwa Nakiru.

Haka kuma ya tabbatar da azabar ƙabari da ni’imarsa da tayar da matattu, da cewarsa:

(إن أحدكم إذا مات عرض عليه مقعده بالغداوه والعشى إن كان من أهل الجنة فمن أهل الجنة، وإن كان من أهل النار، فمن أهل النار فيقال هذا مقعدك حتى يبعثك الله يوم القيامة)

***“Haƙiƙa, ɗayanku idan ya mutu za a nuna mashi masaukinsa safe da marece, Idan ya zamo daga cikin ‘yan-Aljanna, to, daga ‘yan-Aljanna, idan kuwa ya zamo cikin ‘yan-wuta, to, daga cikin ‘yan-wuta. Za a ce masa wannan shi ne wurin zamanka har Allah ya tayar da kai ranar Alƙiyama”***

Kamar yadda ya zo a cikin *Sahihul-Bukhari* daga Ibnu Umara. Kuma ya tabbatar da azabar ƙabari da cewarsa:

(عذاب القبر حق)

***“Azabar ƙabari gaskiya ce:”***

Tamkar yadda ya zo a cikin *Sahihul-Bukhari* daga A’isha.

Ya tabbatar da ma’auni da cewarsa:

(كلمتان خفيفتان على اللسان، ثقيلتان في الميزان، حبيبتان إلى الرحمن، سبحان الله وبحمده، سبحان الله العظيم)

***"Kalmomi biyu masu sauƙi ne ga halshe, masu nauyi a cikin ma'auni kuma masoya ne ga Rahmanu (Ubangiji Mai rahama) su ne Subhanallahi Wabihamdi, Subhanallahil Azimi"***

Kamar yadda ya zo a cikin *Sahihul-Bukhari* daga Abu Huraira.

Ya tabbatar da takardar nan da Mala'iku marubuta da cewarsa:

**(يصاح برجل من أمتي على رؤوس الخلائق وينشر عليه تسع وتسعون سجلا كل سجل مثل مد البصر ثم يقال: أتنكر من هذا شيئا؟ أظلمك كتبتي الحافظون؟ فيقول: لا يا رب. فيقول: أفلك عذر؟ فيقول: لا يا رب. فيقول: بلي إن لك عندنا حسنه وأنه لا ظلم عليك اليوم. فتخرج بطاقة فيها أشهد أن لاإله إلا الله وأشهد أن محمدا رسوله. فيقول أحضر وزنك. فيقول: يا رب ما هذه البطاقة مع هذه السجلات؟ فيقول: إنك لا تظلم. فتوضع السجلات في كفة والبطاقة في كفة فطاشت السجلات وثقلت البطاقة ولا يثقل مع اسم الله شيء)**

***"Za a yi kururuwa ga namiji daga cikin al'ummata a kan talikai a buɗe takardun nan casa'in da tara (99). Kowace takarda tsawonta iyakar ganin mutum sa'annan a ce masa kana musun wani abu a cikin takardar nan shin ko marubutaNa matsara sun zalunce ka? Sai ya ce: a'a ya Ubangiji, sai Ya ce:, to, kana da uzuri? Sai ya ce: a'a ya Ubangiji, sai ya ce: Haka ne amma ai kana da aikin lada a wajenMu haƙiƙa yau ba za a zalumce ka ba sai a fitar da takarda wadda akwai Kalmar Shahada a cikinta sai ya ce:, to, ka je wajen awon ayyukanka. Sai ya ce: Ya Ubangiji wannan ƙanƙanuwar takarda me take dangane da manyan takardun rubutattu? Sai Ya ce: Haƙiƙa ba za a zalumce ka ba sai a aza tulin takardun can a cikin bakin ma'auni, wannan takardar kuma a cikin baki ɗaya na ma'auninsa, takardun can su tashi wannan ƙanƙanuwar takardar sai ta fi su nauyi, babu wani abu wanda zai yi nauyi tare da sunan Allah."*** *Tirmizi ya ruwaito shi.*

Ya tabbatar da siraɗi da cewarsa;

**(ويضرب جسرا على جهنم فأكون أول من يجوز)**

***"Za a aza kadarko (gada) a kan jahannama in za ni ni ne farkon wanda ke tsallakewa"***

Kamar yadda ya zo a cikin *Sahihul-Bukhari* daga Abu Huraira. Kuma a cikin *Sahihul Muslim*

(جسر ممدود على ظهر جهنم، أدق من الشعر وأحد من السيف)

***"Gada ce wadda aka miƙe bisa kan jahannama ta fi gashi zama silili kuma ta fi takobi kaifi"***

Kuma ya tabbatar da Kausara da cewarsa:

(حوضي مسيرة شهر، ماؤه أبيض من اللبن، وريحه أطيب من المسك، وكيزانه كنجوم السماء، من شرب منه فلا يظمأ أبدا)

***"Tafki ne yawansa kamar tafiyar wata ɗaya, ruwansa ya fi nono fari kuma ya fi miski ƙamshi, kofukanshi kamar taurarin sama wanda ya sha shi ba zai yi ƙishirwa ba har abada."***

Kamar yadda ya zo a cikin *Sahihul-Bukhari* daga Abdullahi Ibnu Umara. Ya tabbatar da Aljanna da wuta da cewarsa;

(ما من شيء كنت لم أره إلا قد رأيته في مقامي هذا حتى الجنة والنار)

***"Ba abin da ban gani ba sai na gan shi a yanzu a matsayin nan nawa har aljanna da wuta"***

Tamkar yadda ya zo a cikin *Sahihul-Bukhari* a cikin babin sallar tafiyar hasken rana. Daga Hadisin Asma'u.

Ya tabbatar da ceto da cewarsa;

(شفاعتي لأهل الكبائر من أمتي، ومن لم يكن من أهل الكبائر فماله والشفاعة)

***"Cetona yana ga masu manya-manyan zunubai a cikin al'ummata, wanda bai zo cikin masu manyan zunubbai ba, ai ba sai an cece shi ba."*** *Tirmizi ya zo da shi* daga Jabiru.

Ya tabbatar da ganin Muminai ga Allah Ta'ala da cewarsa;

(إنكم سترون ربكم جل ثناؤه عيانا)

***"Haƙiƙa, ku za ku ga Ubangijinku, yabonSa ya girma, za ku gan Shi ganin ido"***

Kamar yadda ya zo a cikin *Sahihul-Bukhari* daga Jabiru Ibnu Abdullahi.

To, Hadisan ilimin asullan addini sun yi tawaturi (jama'a masu yawa suka ruwaito su waɗanda ba za su haɗu ba a kan abin da ba gaskiya ba) sai dai mun taƙaita ga kawo sashen Hadisan.

Wannan shi ne asullan addini a wajen Ubangiji da Annabawa da abubuwan da aka jiya. Haƙiƙa, Annabi (saw) ya tabbatar da ita a cikin sunnarsa tamkar yadda Allah Ta'ala ya tabbatar da ita a cikin Alƙur'ani mai girma. Abdulwahabi Ash-Shu'arani ya ce: a cikin littafinsa, *Addurarul-Mansuratu fi Bayani Zubadil Ulumi Al-Mashhurati*.

Waɗannan asulla dukansu sanannu ne tabbatattu gun kowane Musulmi wanda ke tare da mutanen Musulunci. A nan maganar ta tuƙe.

## FASALI NA BIYAR

### Bayanin Ka'idodin Ilmul-Kalami Waɗanda Dole Ne Wanda Ke Nufin Shiga Karatun Littattafan Ilmul-Kalami Ya San Su Don Shi Samu Amfaninsa Kuma Ya Tsira Daga Cutarsa

Ina cewa, daidaitawa ga sawaba sai Allah. Ya 'yan'uwana ku san haƙiƙan ƙa'idojin Ilmul-kalami manyansu sun taƙaita a kan sanin lamurra goma (10):

(1) Sanin iyakacin abin da ake ce wa Ilmul-kalami.

(2) Sanin hukuncinsa ga zamanin da ya shuɗe can baya.

(3) Sanin hukumcinsa ga zamani na daga baya.

(4) Sanin hukumcinsa ga jahilai.

(5) Sanin abin da ke kawo mummunan zato wanda aka jarrabi mafi yawan almajirai idan sun shige shi.

(6) Sanin abin da aka dogara a kansa, ingancin imani muƙallidi (wanda ya ji an faɗi abu na tauhidi ya karɓa ba tare da ya yi bincike ba).

(7) Sababin yin littafi a kan Ilmul-kalami.

(8) Sanin hujjojin Ilmul-kalami ba za su tabbata ba sai da abin da yake yanke kamar Alƙur'ani ko Hadisi.

(9) Sanin lamarin mutanen wannan zamanin da suka cinye lokaci ga karatunsa kuma babu dole ga yin hakan.

(10) Sanin al'amarin Bayin Allah ga yi take ga mayar da martani daga kowane ɗaya daga cikin mutanen da suka rarraba a cikin Musulunci da kuma abin da suka samu ga bincike a kan Ilmul-kalami.

Amma haƙiƙanin Ilmul-kalami, haƙiƙa, Abdussalam ɗan Ibrahim Al-Laƙani ya faɗa a cikin littafinsa, *Ithaful-Muridi bi Jauharatit-Tauhidi,* ya ce: ilimi ne wanda da shi ake samun iko ga tabbatar da ƙa'idoji na Musulunci waɗanda za a iya gaya wa wani kuma a kawo masa hujjoji kuma a tunkuɗe masa rikitta.

Amma hukuncinsa a zamanin magabata, haramun ne ba shakka domin a wancan lokacin babu bidi'o'in da ke juyar da mutum daga biyar Alƙur'ani da Hadisi ga mafi rinjaye. Abdurrahmani As-Suyuɗi ya ce: a cikin sharhin *Kaukabu,* Abu Amrin ya ce: an tambayi Huzaimatu daga magana ta Ilmul-kalami wajen sunayen Allah da siffofinSa, sai ya ce: bidi'o'i ne da suka ƙaga domin kuwa shugabannin Musulmi da shugabannin mazhabobi da shugabannin addini kamar su, Maliki da Sufyanu da Auza'i da Shafi'i da Ahmadu da Is'haƙu da Yahaya ɗan Yahaya da Ibnu Mubaraki da Abu Hanifa da Muhammad Bnu Hasani da Abu Yusufa, suna yin maganganu a kan Ilmul-kalami suna hani daga kutsawa a cikinsa suna kafa dalilai ga jama'ar da ke tare da su a kan Alƙur'ani da Sunnah.

Gazali ya ce: a cikin littafin *Ihya'u Ulumid-Dini* Shafi'i da Maliki da Ahmadu bnu Hambali da Sufyanu da dukan jama'ar Hadisi cikin magabata sun tafi a kan haramcin Ilmul-kalami.

Abdurrahmani As-Suyuɗi ya ce: a cikin *Itmamul-Di*raya *Sharhun-Niƙaya,* wajen ambaton asullan addini ya ce: Ilmul-kalami wanda ake kafa dalilai na hankali a cikinsa a cirato maganganun masu falsafa haramun ne a kan haɗuwar magabata. A nan maganar ta tuƙe.

Amman bayanin hukuncin Ilmul-kalami a cikin zamanin da suka zo daga baya, halal ne babu shakka kuma farlu kifaya ce: (Farillar da wani ke isamma wani a kanta) don kuwa bidi'o'in da suka bayyana masu yawa kuma suna juyar da mutane daga Alƙur'ani da Sunnah a cikin zamanin waɗanda suka zo daga baya. Haƙiƙa, Abdurrahmanu As-Suyuɗi ya ce a cikin *Itamamd-Diraya Sharhun-Nuƙaya,* ka san haƙiƙa Ilmul-kalami haramun ne a kan haɗuwar magabata.

Gazali ya ce: a cikin *Ihya'u Ulumid-Dini,* ka san tabbataccen abin da Ilmul-kalami ya tattara a kansa su ne dalilai waɗanda aka amfana da su waɗanda suke Alƙur'ani da Hadisai sun tattara a kansa abin da ya fice daga gare su ko da shi zamo jayayya ce kawai ko kuwa husuma, babu wani abu daga gare shi wanda ya zama an san shi a zamani na farko kuma kutsawa a cikinsa nau'i ne na bidi'a amma a yanzu hukuncinsa ya canza domin kuwa bidi'o'i waɗanda ke juyawa daga Alƙur'ani da Hadisi sun faru kuma jama'a sun bayyana sun kawo rikitta a ciki sun jera wasu maganganu sai abin da aka hana na Ilmul-kalami ya zamo ba hananne ba a kan lalura har ma ya zama farlu-kifaya.

Sheikh Sanusi ya ce a cikin sharhin *Kubra*, ba mutum ɗaya ba ne ya ce: Wannan sanin farlu kifaya ne bisa ga mutanen kowane yanki na ƙasa, inda wani ba zai iya saduwa ba da shi zuwa ga waninsa. A nan maganar ta tuƙe.

Sheikh Sanusi ya ce a cikin sharhin *Wusɗa;* Farlu-kifaya ne, malamin da duk ya tsayu da shi a cikin kowane yankin ƙasa, to, ya isar wa waninsa. A nan maganar ta tuƙe.

Ahmadu bnu Zikra ya ce: a cikin *Muhassilul-Maƙasibi;* hukumcin kutsawa cikin wannan ilimin da kafa dalilai da kyakkyawar fahimta da gusar da rikitta bisa ga kula, to, farlu-kifaya ce: babu wata gardama. Wanda ƙafarsa ta tsaya ga sanin asulla da fannoni na hankali da abubuwan da aka cirato, to, zai ɗauke wa waninsa karatun Ilmul-kalami.

Manjuri ya ce: a cikin sharhin baitoci ya wajaba ya kasance a kowane yankin ƙasa da saduwa da shi yake wahalarwa ga wani a samu wanda ya tsayu da gaskiya da wannan sanin wanda zai iya mayar da martani ga ‘yan-bidi’a kuma ya tare masu kawo abin da ba daidai ba ya nuna musu gaskiya, da an rasa wanda ke ɗauke musu wannan, to, sai su fita dukansu su nemo. Amma ba mai zama ga wannan siffar ta ɗaukar wannan matsayi ga wannan siffar sai wanda ya cika da fannoni na hankali da na karatu don kuwa ilimummuka wasu sun haɗu da wasu kuma wannan sashe na buƙatar wani sashe.

Amma hukumcinsa a kan jahilai haramun ne babu wata shakka domin ana tsoron musu idan suka kutsa cikinsa su faɗa a cikin rikitta masu ɓatarwa.

Sheikh Sanusi ya ce: a cikin *Al-Umdatu Sharhu-Kubra;* zato yakan garwayu da hankali wajen riƙo abu kuma ƙarya takan iya yin kama da gaskiya a wajen bincike don haka mutanen gaskiya sun hana kutsawa cikin wannan ilimi gwargwadon abin da ya wuce lalura sai ga ɗaiɗaikun mutane masu kaifin hankali.

Kuma ya ce a cikin *Sharhu-Wusɗa;* wannan fa aikin malamai ne waɗanda suka tsayar da ƙafa ga sani. Ya zo a cikin *Alyawaƙitu-Wal-Jawahiru* na Abdulwahhabi Ash-Sha’arani, Sheikh Sa’adu Ad-Dini At-Taftazani da waninsa sun ce abin da ke haƙiƙa ga matsalar zargin kutsawa ga Ilmul-kalami, haƙiƙa, nazari ga wannan abu ga hanyar masu Ilmul-kalami shi ne a ce dalillai da haɗa ta da ture kokwanto da gusar da rikitta daga gare shi, farlu-kifaya ce: ga waɗanda suka cancanta su yi domin idan suka yi, sun

ɗauke wa wasu. Amma waɗanda ba su cancanta ba, waɗanda ake yi wa tsoron idan sun kutsa cikinsa za su sanya kansu a cikin rikitta waɗanda ke ɓatar da su, to, waɗannan an hana su.

Ya zo a cikin *Muhasil* na Ahmadu Bnu Zikra; ba a samo labarin bincike da wannan ilimin ba daga magabata a kan jahilai don haka aka ce masa bidi’a ce a cikin addini, don haka a sake shi yana wajaba da ayyanawa har a zaci. Sahabbai taƙaitawa ne suka yi, abin da suka yi sun bi da jama’a ga al’amurra masu sauƙi, suka sanar da su kamar sanarwar Annabi ga ƙa’idodin Musulunci da lamari wanda yake bayyane.

A cikin sharhin *Kaukabu* na Abdurrahmani As-Suyuɗi; Gazali ya wallafa littafi a ƙarshen rayuwarsa, inda ya yi masa suna *Iljamul-Awami An Ilmul-kalami* (Lizzami a bakin jahilai don kada su karanci Ilmul-kalami) ya ce: Mutane dukansu jahilai ne ga wannan fanni, masu fiƙihu da wasunsu sai ƙwarori kaɗan wanda da ƙyar za ka samu ɗaya a cikin zamani. Nan wannan maganar ta tuƙe.

Ya kamata wanda zai keɓanta da sanar da wannan sanin ya zamo yana da ɗabi’u uku (3):

(1) Ba ya da wata manufa sai ilimi da kwaɗayi a kan ilimi; haƙiƙa mai tafiya zuwa neman abin duniya, to, wannan abin da yake nema zai shagaltar da shi daga kamala, abin da ake so da gusar da shakka idan ta zo.

(2) Ya zamo mai kaifin hankali mai wayo mai fasaha; haƙiƙa wawa ba zai amfana da fahimta ba kuma ba zai amfana da hujjojinsa ba, don haka ana yi masa tsoro daga cutar da ke cikin Ilmul-kalami kuma ba a yi masa tsammanin amfanin da ke cikinsa.

(3) Ya zamo ɗabi’arsa zama na ƙwarai da bin addini da tsoron Allah kuma ya zamo shawoyi ba su rinjaye shi ba; haƙiƙa, fasiƙi yakan iya sawance wa addini a kan ƙaramin rikici. A nan wannan maganar ta tsaya.

Amma sababin mummunn zato wanda aka jarrabi mafi yawan ɗalibai da shi idan suka shiga cikin Ilmul-kalami; za su sanya tabbatar aƙidodi na addini da dalilai na hankali a wajen ƙaga aƙida ta imani, ba za su ɗauke shi ba a kan basira ga daidaitar abin da aka cirato da kuma abin da hankali ya gano da tabbatar da ƙarfin imani da dalilan.

Abu Muhammadin Abduljalili ya ce a cikin *Shu'abul-Imani;* Hanyar sanin Allah wanda tsarki ya tabbatar maSa, ta hanyar ji shi ne karɓar abin da Ya bada labari daga ZatinSa ko ManzonSa (saw) daga abin da litattafanSa suka faɗa kuma ManzanninSa suka bada labari da shi, daga siffofinSa da sunayenSa mutum ya gasganta, haka labarin siffofi kamar yadda suka zo. Amma hanyar sanin Allah daga jihar nazari na hankali da nazari na kafa dalili, bincike ga abubuwan da aka halitta da lura da ita da kuma lura da Hadisai da Ayoyi.

Misalin waccan magana ta farko wadda take jihar ji, ka gasganta duk abin da Allah (swt) ya tabbatar da shi ga ZatinSa ko ManzonSa (saw) daga abin da LittattafanSa suka faɗa kuma ManzanninSa suka bada labari da shi daga siffofin Allah da sunayenSa waɗanda aka sani da waɗanda ba a sani ba sai ka gasganta duka gasgantawa ta yanke bisa ga wajabci sai ka zamo cikin muminai waɗanda suka gasganta. Kuma bayan wannan, nazari ga halitta zai zo da lura da abubuwan da aka kawo a Nassance sai hankali ya ga abin da zuciya ta gasganta sai gasgantawar zuciya ta yi ƙarfi da ganin hankali sai imani ya ƙaru kuma sani ya girmama domin tabbatar yaƙini (tabbas).

Abdulwahhab Ash-Sha'arani ya ce a cikin littafinsa, *Alyawaƙitu Wal-Jawahir;* Ɗan'uwana ka yi nazari zuwa ga Annabinmu (saw) sa'adda Yahudawa suka ce masa gaya muna dangantakar asulinSa ya take? Sai ya karanta musu ce Allah Shi ne Makaɗaici, babu wani dalili gare su na nazari ko ɗaya,

Cewar da Allah ya yi ***“Makaɗaici ne”***, ya tabbatar da samuwarSa ya kore ƙidayuwa, Ya tabbatar da cewa Shi kaɗai Yake ba Ya da abokin tarayya kuma Ya ce: Shi ne Allah wanda kowa zai nufa da buƙatarsa. A nan ya kore a ce jiki ne.

Cewar da Ya yi “Bai haihu ba, ba a haife Shi ba" ya kore cewa Yana da ɗa ko uba, cewar da Ya yi babu ɗaya wanda ya zama tamkar Shi; ya kore cewa yana da aboki ko wanda suke tarayya. Shin ana neman wani dalili na yanke tare da kawo hujja bisa ga ingancin waɗannan ma'anoni ta hanyar hankali bayan ta tabbata da dalili wanda yake yanke? Wannan jahilci ne babba.

Ya kaiton sanina wai mai neman sanin Allah daga dalili kuma yana kafirta wanda bai yi nazari ba ga dalilin. To, shi yaya halinsa yake tun gabanin nazari, shin mumini ne ko ba mumini ba? Shin ya tabbata a wajensa cewa akwai Allah kuma Muhammadu BawanSa ne ko bai tabbata ba? Shin

yana sallah yana azumi? To, in ya zama ya ƙudurta waɗannan duka, to, wannan halin jahilai ne ya bar su da shi kada ya kafirta kowa daga gare su. Amma idan har ya zan bai ƙudurta waɗannan lamurra ba sai bayan nazari a cikin Ilmul-kalami da shagaltuwa wajen nemansa, to, mu kam muna neman Allah tsari daga wannan hanya sa'adda mummunan nazari ya kai shi zuwa ga fita daga imani. A nan wannan maganar ta tuƙe.

**Bayanin maganar da aka dogara a kanta: Kasancewar mai ratayuwa ga maganar wani wajen tauhidi Mumini ne:-** Ka san haƙiƙa Abdurrahmani As-Suyuɗi ya faɗa a cikin sharhin *Kaukabu;* ya ce mai Jam'ul Jawami'i ya ce: abin da yake haƙiƙa idan ana nufin ratayuwa ga maganar wani, mutum ya kama maganar wani ba tare da hujja ba kuma a kan ɗaukar kokwanto ko wahami kamar yadda ake ratayuwa ga maganar Imami (Shugaban mazhaba) a wajen furu'a tare da cewa yana yiwuwa ya zamo ba ya tare da gaskiya, to, irin wannan ba zai isa ba a wajen imani gun kowa. *Ash'ariyi da waninsa.*

In ana nufin ƙudurtawa wadda take yanke ba tare da komai ba, wannan ta isa ga imani. Ba wanda ya saɓa a wannan maganar sai Abu Hashim.

Abdulwahhabi Ash-Sha'arani ya ce a cikin littafinsa, *Al-yawaƙitu Wal-jawahiru,* bayan ya kawo maganar Sheikh Tajuddini binu Subki, haka Jalalul Muhalli ya faɗa kuma ita ce maganar da ake dogara a kanta. A nan wannan maganar ta tuƙe.

**Bayanin Sababin Wallafa Ilmul-kalami:-** Ka san cewa Malaman Sunnah (Allah ya yarda da su) ba su wallafa littattafan Ilmul-kalami ba don su tabbatar wa kawunansu ko wasunsu daga mutanen Sunnah, sanin Allah da Ilmul-kalami, don kuwa Allah sananne ne da halitta ta addini da abin da ake gani da jin da ya wuce a musanya da nazari na halittar addini da abin da aka sani ba sai an yi nazari ba kamar yadda muka yi bayani a cikin fasali na biyu ga wannan littafi. Amma sun yi waɗannan littattafai don su sanar da mutane hanyoyin kafa dalili waɗanda ake mayar da martani ga mai jayayya kamar Falasifatu da Mu'utazilatu (masu aƙidar da ba ta Sunnah ba). Kuma don mutane su sami sauƙi a wajen neman ilimi da sanar da shi.

Ra'aini ya ce a cikin sharhin *Shilali Jiyatu*: Ai dalilai da hujjoji suna a wajen fuskar hanyar kafa dalili don haka Sheikh Sanusi ya ce a cikin *Al-Umdatu Sharhu Kubra;* "Haƙiƙa, waɗanda suka zo daga baya sun fara abin da suka fara domin su samu sauƙi lokacin neman ilimi da sanar da shi ba don cewa nan kaɗai gaskiya take ba" don haka Abdulwahhabi Ash-Sha'arani ya

ce a farkon *Alyawaƙitu Wal-Jawahir* “Ka sani Allah ya ji-ƙanka haƙiƙa Malaman Musulunci ba su wallafa littattafai ba ga sanin aƙidoji don su tabbata sanin Allah ga kansu, amma sun aza wannan ilimin don kwatse masu jayayya waɗanda ke musun abin da imani da shi ke wajaba shari’ance”

Sai Malaman Musulunci suka nemi tsayar da dalilai bisa ga waɗannan mutanen don su dawo zuwa ga abin da yake wajaba a yi imani da shi ba don wani abu ba. Don haka malamai suka aza Al-Jauharu (Asulin abu) da Ardu (siffa) suka shimfiɗa magana a kan waɗannan, don haka mutum ɗaya ya isa a cikin zamaninsa a kan wannan. A nan wannan magana ta tuƙe.

**Bayanin Cewa Hujjojin Ilmul-kalami ba su tabbata sai da abubuwan da suke yanke:-** Haƙiƙa, mun faɗa a ƙarshen fasalin sanin asullan addini cewa daga sharuɗɗan wajabcin ƙudurta abu shi ne samun nassi wanda ya wuce a yi musunsa kuma mun faɗa a cikin farkon fasalin, abin da yake Ilmul-kalami shi ne sanin da ake samun iko da shi a kan tabbatar da aƙidoji na addini yadda za ka faɗa wa wani kuma dole ya yarda don kawo mishi hujja da kawar da rikitta sai ya kasance dukkan aƙida ba ta tabbata sai da lamurra huɗu waɗanda suke yanke:

(1) Dalili na hankali

(2) Nassin Alƙur’ani

(3) Hadisin da ya zamo mutawatiru (wanda taro suka karɓo)

(4) Haɗuwar Malamai a kan abu.

Asheikh Ɗahir ya yi nuni a kan waɗannan abubuwa huɗu a cikin *Nazmul-Kubra* inda yake cewa wannan ilimi yana tabbata da dalilai na hankali da abubuwan da aka cirato a yanke. To, wannan idan wanda ke jayayya yana karɓar dalili na shari’a amma idan bai karɓar dalilin shari’a kamar Barhami, shi kam ba za a kawo masa hujja ba sai da dalili na hankali kamar yadda muka ambata.

Idan ka fahimci abin da aka ambata, za ka san hujjojin wannan ilimin ba su tabbata ga zahirin Alƙur’ani da zahirin Sunnah ba kuma ba da nafsin Hadisi ba daga cikin Hadisi Ahadu (wanda bai kai Mutawatir ba) don kuwa su, al’amurra, ne na zato ba su tabbata sai ga rehhu. To, idan ka san wannan duka, za ka san cewa hujjojin wannan ilimi ba za su tabbata ba ga zancen kowane mujtahidi don kuwa ijtahidi kamar yadda Sanusi ya faɗe shi a cikin

sharhin Kaukabu; masanin fiƙihu ya yi gwargwadon ikonsa domin tabbatar da zato ga hukumci.

Ya faɗa a cikin *Jam'u-Jawami'i;* Ibnul Hajibi ya ƙara sharaɗi ya ce ban da idan wanda ba masanin fiƙihu ba ne ya yi iyakar ƙoƙarinsa kuma ya ce faƙihi ya yi iyakar ƙoƙarinsa kan tabbatar da zato da hukumci na hankali. A nan wannan maganar ta tuƙe.

Mai *Kaukabu* ya faɗa cewa; Faƙihi ya yi iyakar ƙoƙarinsa ga tabbatar da zato daga hukunce-hukunce yana daga dalili.

Amma sanin lamarin mutanen zamani ga cinye lokaci ga karatun Ilmul-kalami kuma babu abin da ya wajabta musu hakan. Haƙiƙa, Abdulwahhabi Ash-Sha'arani ya ce a cikin *Al-Yawaƙitu Wal-Jawahir* Sheikh Muhyiddini ya ce: "Bai kamata ba ga Mumini ya mance iyakokin da Allah ya ƙallafa masa a cikin wannan gida na duniya, ya ƙare mafi yawan rayuwarsa ga shagala da mayar da martani ga mai jayayya wanda yake ba a same shi ba ayyananne a cikin garuruwansu kuma da kawar da rikittan da takan yiwu ba za su faru ba ko har ma sun faru a yi takobin shari'a, shi zai katse su kuma shi kwatse su."

Ya zo ga Hadisi:

(أمرت أن أقاتل الناس حتى يقولوا لا إله إلا الله وحتى يؤمنوا بي وبما جئت به)

***"An hore ni in yaƙi mutane har su ce babu wanda ya cancanci bauta sai Allah kuma har su yi imani da ni da abin da na zo da shi."***

To, Manzon Allah (saw) bai tura mu ba a kan jayayya da su don kuwa mutanen zamani a yau abin da ke shagaltar da su ke nan suka ƙare rayuwarsu a cikin shagala da mayar da martani a kan jayayya wadda ake zaton ta faru ko an same ta a kan abin da mazhaba ta lizamtar, wannan ba mazhaba ba ce bisa ga zancen da ya rinjaya sai mai Ilmul-kalami ya ga kamar yana magana da wani ne alhali kuwa da kansa ne yake magana, don haka aka san magabata ba su aza littattafan Ilmul-kalami ba sai don kwatse masu jayayya na lokacinsu kamar yadda muka ambata, Allah Ta'ala ya amfane su da nufinsu.

Sai ya ce kuma mai hankali wanda ya shagala a yau da ilimummukan shari'a don ko ta wadatar daga Ilmul-kalami domin addini da shi yake tsayuwa da mutum ya mutu bai san magana a kan Jauharu da Ardu ba Allah Ta'ala ba zai tambaye shi ba a ranar Alƙiyama daga waɗannan. Sa'annan

idan mutum ya yi buƙata zuwa ga mayar da martani ga mai jayayya wanda ya faru a cikin garuruwansu yana musun shari'o'i ga misali, ya wajaba gare mu mu ture wannan hanyar tasa da al'amurra na hankali ba kafa dalili ba a kansa da shari'a kamar Barhami. Shi bai karɓar dalili na shari'a.

To, sai mu ɓata abin nan da ya ambata na baƙuwar hanya wadda ke sukar shari'a domin shari'a ita ce wadda muke jayayya tsakaninmu da shi, don haka muka ce ba ya da magani sai a mayar masa martani da nazari na hankali, sai mu yi maganinsa don za mu ce masa ka duba da hankalinka ga wannan matsala tabbatar da nazari. A nan wannan magana ta tuƙe.

Amma sanin lamarin bayin Allah ga gittawa ga mayar da martani bisa ga ɗaya daga cikin mutane waɗanda suka rarraba a cikin Musulmi da kuma rabonsu su a kan bincike ga Ilmul-kalami; Abdulwahhabi Ash-Sha'arani ya faɗa a cikin littafinsa, *Al-Yawaƙitu Wal-Jawahiru;* Muhyiddini (ra) ya kasance yana cewa ba ya cikin lamarin Bayin Allah su gitta zuwa ga mayar da martani ga ɗaya daga Musulmin da a 'rarraba' sai idan sun saɓa wa nassoshi ko sun yage ijma'in Malamai, to, idan ba haka ba, wanda ya gitta zuwa ga mayar da martani a kan ɗaya daga cikinsu ba za a amince ba ya yi musu musun al'amari. Wanda yake gaskiya ne ga haƙiƙan lamari don haƙiƙa mutane Musulmi matsawar suna cikin kewaye na Musulunci ba za su ƙudurta abu ba sai na gaskiya ko abin da yake yana da kama da gaskiya saɓanin wanda ya fita daga cikin Musulunci. A nan wannan magana ta tuƙe.

Ya kuma faɗa a cikin babi na talatin (30) daga *Futuhatu;* daga lamarin Bayin Allah Ta'ala shi ne ba su sukar aƙidar ko mutum ɗaya daga cikin aƙidoji na Musulunci amma sha'aninsu shi ne bincike daga mai jayayya ta aƙida don su san masu aƙidar a ina suka same ta. Wane ne ya bayyanar da ita har aka ƙudurta ta, kuma za ta taɓa wani abu a cikin arzikinsu na lahira ko ba ta taɓawa? Wannan shi ne rabon Bayin Allah daga bincike ga Ilmul-kalami. A nan wannan magana ta tuƙe.

Waɗannan ƙa'idodi goma (10) dole ne mai nufin shi ga karatun littattafan Ilmul-kalami ya san su don ya samu amfaninsa kuma ya tsira daga cutarsa. A kan haka ne Ahmadu binu Zikra ya nuna a cikin *Muhassal* inda yake cewa; "wanda bai kyautata waɗannan ƙa'idojin ba, to, ya nisanta ga gittawa ga waɗannan manufofi" Abdulwahhabi Ash-Sha'arani ya ce a cikin farkon *Al-Yawaƙitu Wal-Jawahir,* inda yake ambaton waɗannan ƙa'idoji; ya ce su ne ƙa'idoji da abubuwan da aka rubuta waɗanda mai nufin ya zamo babban masani ga Ilmul-kalami yana buƙata gare su.

## KAMMALAWA

**Bayanin cewa ɓarna ba za ta game aƙidojin jama'a duka ba har Kiyama ta tsayu, bayyanar jama'a ɓatattu masu ɓatarwa a cikin zamanin Alhasanu Al-Yusi; suna ƙaga cewa wanda bai san ma'anar Kalmar shahada ba bisa ga tabbatar da abin da Malamai suka tabbatar kafiri ne kamar yadda ire-irensu suka bayyana a cikin zamaninmu.**

Bayanin cewa ɓarna ba za ta game aƙidoji na jama'a baki ɗaya har zuwa tsayuwar ƙiyama ba haƙiƙa Ahmadu Binu Zikra ya faɗa a cikin *Muhassilul Maƙasidi,* Al'Ustaz Abu Mansurin ya cirato haɗuwar mutanen gaskiya a rubuce; "haƙiƙa, jahilan Musulmi Muminai ne kuma sun san Ubangijinsu, kuma nassi ya zo cewa suna cike a Aljannah, mafi yawansu wawaye ne." Mutanen sunnah sun haɗu a kan haka.

Manjuri ya ce: a cikin sharhin *AL-Muhassilu,* wajen sharhin waɗannan baitoci inda ake cewa; "mafi yawan 'yan-Aljannah wawaye ne." Mutanen Sunnah sun haɗu a kan haka. Sai ya ce nuni ne zuwa ga cewar Manzon Allah (saw):

(أن أكثر أهل الجنة البله)

***"Mafi yawan 'yan-Aljannah Talakkawa ne"***

Sashen Malamai ya cirato ƙari cewa, mutanen Illiyyina su ko masu hankali ne (Illiyina shi ne littafin da ya tara Ayyukan alkhairi na Mala'iku da muminan mutane da aljannu, ko kuma wuri ne a cikin sama ta bakwai "7" a ƙarƙashin Al'arshi). Sa'annan ya ce wannan Hadisi nuni ne ga dukan Musulmi domin suna da rabkana ba su sadu ba da hankalinsu zuwa ga haƙiƙa sai su zamo cikin mutane Illiyyin kuma hankalinsu bai karkace su daga hanya ba har su ɓace da kafirci ko bidi'a. Lafazin Bulahu (wawaye) ya zo da alifun da lamun, don haka ga ƙa'idar Larabci ya nuna gamewa.

Don haka Ahmadu binu Zikra ya ce a cikin *Muhassilul Muƙasidi* bayan waɗannan baitoci; "idan ka ce wannan hukunci ga jahilan da suka wuce yake wai bai game kowaɗanne jahilai ga kowane lokaci ba, sai in ce gamewa tabbatacciya ce ga tsarin maganar don haka ko su ma suna cikin wannan hukunci. Kuma idan ka ce ka ɗauki dukansu a kan ɓarna don wasunsu suna ɓarna, to, ka saɓa wa hukuncin hankali da dalilan da aka cirato. In har ɓarna ta bayyana, to, ai wannan abin ƙi ta sai a canza ta da abin da ba a

ƙi ba ta lamari mafi sauƙi ba da mafi tsanani ba don kar lamarin ya koma ga halaka.

(Manjuri) ya ce a cikin sharhin waɗannan baitoci; idan ka ce alif da lamun waɗanda ke ga *Albalahu* suna nuna gamewa, don haka ya nuna 'tarsashin' magabata ba za ya karɓu gare mu ba, cewa abin da ya game ga mutane, to, ya game ga duk kowane zamani har ya game tarsashin wannan zamani waɗanda ake magana a kansu. To, mun yarda a kan gamewa ga kowaɗanne mutane da kowane zamani kamar yadda ya tabbata ga asullan *fiƙihu;* lafazi mai gamewa ga dukkan kowane zamani kuma tsarin maganar ya nuna hakan nunawa a bayyane, to, ba za a karkata ba ga waɗannan sai ga dalili, a kan haka babu mai fita cikin jahilan da aka ce suna shiga Aljannah sai wanda aƙidarsa ta ɓaci. Wannan kuwa za a samu ga wani sashe amma ba duka ba. To, ɗaukar dukansu a kan ɓarna don sashensu ya ɓaci, ba ya inganta ga hankali da kuma abin da aka cirato ga nassi.

Haka ne idan ɓarnar ɗayansu ta bayyana, to, abin ƙi ne kuma wajibi ne a canza ta amma idan ba ta bayyana ba, abin da a asuli shi ne tsira daga abin ƙi da shiga cikin waɗanda Hadisi ya ce sun fi yawa a cikin Aljannah. To, canza wancan munkarin ya tabbata da abin da kowa yake karɓa kuma ba ya musunsa, su ne dalillai bayyanannu masu sauƙi na kusa ga dukkan mutane amma kar ya gauraya masa abubuwan da masu Ilmul-kalami suka haɗu a kansu waɗanda suke wawa ba zai fahimce su ba. Abin da ake nufi ba zai tabbata da su ba, kuma kar ya kawo rikici ko da ba tare da rikicin ba domin wawa idan an kawo masa rikici zai ƙara ɓaci. A nan wannan magana ta tuƙe.

Amma bayanin bayyanar jama'a ɓatattu masu ɓatarwa cikin zamanin Alhasanul Yusi; suna kira cewa wanda bai san Kalmar shahada ba bisa ga tabbatarwa wanda malamai suka faɗi, shi, kafiri ne. Haƙiƙa, Alhasanul Yusi ya ce a cikin *Muhadaratai;* na zamo ga shekara ta dubu da saba'in (1070) na nufin ziyarar Shehinmu mai albarka kuma wanda muke koyi da shi, uban Abdullahi, Muhammadu ɗan Nasiru (Allah ya shayar da ƙasarshi,) sai na shuɗe ga garin Sajlamasata na sami fitina ta motsa tsakanin ɗalibai ga ma'anar *kalimatul Ikhlasi* (ita ce Kalmar shahada).

Sashen ɗalibai ya tabbatar da abin da Shehu Sanusi ya faɗa cewa abin da yake korarre tamkar wanda aka ƙaddara sai wanda ya zamo shugaba ne ga matsalolin fiƙihu da hukunce-hukuncen shari'a ya musanya wa wancan sai na ce gaba ina tabbatarwa, iƙirari ga waɗancan masu musun kalmar ta fuska wadda ke kusantawa tsakanin maganarsu kuma fuskar da ke gyarawa

tsakanin masu jayayya sai ba su lura da wannan ba, suka ci gaba da barin saurare. Kuma irin wannan fitinar ta auku a garin Marakish ba da daɗewa ba a tsakanin ɗalibansu har sashensu ya nuna sashen ɓatacce ne, don haka sai na wallafa littafi mai suna *Manahijul Ikhlasi Min Kalimatil Ikhlasi* tamkar yadda na yi tambihi a kan wannan a farkon littafin kuma littafin ya zama mai warkarwa ga rashin lafiya da godiyar Allah.

Na dawo kuma wata ziyara, bayan wannan kuma na shuɗe ga Sajlamasata na ishe fitina mafi ɓaci daga wannan kuma mafi muni ta auku ga waɗannan mutane tare da jahilan Musulmi gamamminsu da keɓantattunsu. Abin da ke nan, duk sa'adda suka yi dubi ga maganar wanda ya kwaɗaitar ga shugabanni a kan nazari ga Ilmul-tauhidi kuma ya tsoratar daga jahilci a kansa kuma ya tsoratar daga ratayuwa ga maganar wani sai suka ci gaba suna tambayar mutane a kan aƙidodinsu, suna kallafa musu jawabi da sai sun bayyana abin da yake daidai.

A kan haka da yawa suka yi dubi a kan wanda ya taƙaita bayani a kan abin da ke cikin zuciyarsa ko halshensa bai faɗi daidai ba domin ya ɗimauta, ko kuma bai san abin da ke suka ga aƙida ba, ko suna zaton abin mai suka ne ga aƙida kuma ba haka ba ne sai su dinga aibanta shi da jahilci da kafirci. Kuma sa'annan suka watsa cewa ɓarna ta game ga aƙidojin mutane sai suka ci gaba suna tabbatar da aƙidu ga jahilai sai kuma abin ya watsu a wajensu. Duk wanda bai san ma'anar kalmar shahada ba, to, shi ne kore wanin Allah da tabbatar da Allah bisa ga tabbatarwa wadda malaman suka tabbatar da shi, kafiri, ne a kan haka wani lamari babba ya shiga a cikin jahilan Musulmi da kuma tsoro babba.

Sa'adda na shiga gari sai mutane suka zo mini jama'a-jama'a suna kai ƙara daga wannan lamari, kuma ai ba kowane irin mutum zai kai ga fahimtar abubuwan da malamai suka faɗi ba. Sai na ce musu haƙiƙa Allah Ta'ala ya sa ku yi maSa bauta da aƙida ta gaskiya a cikin rayukanku. Shin ba ku sheda Allah Ta'ala tabbatacce ba ne kuma samamme? Suka ce mun sheda. Ya ce shin ba ku san Allah Shi kaɗai Yake a cikin mulkinSa ba kuma ba Ya da abokin tarayya kuma babu wani tare da Shi kuma duk abin da aka yi wa bauta in ba Allah ba, to, ba gaskiya ba ne? Sai suka ce haka ne. Kai! Waɗannan duka tabbatattu ne a wajenmu ba kokwanto. Na ce musu, to, wannan shi ne ma'anar *Kalimatul ikhlasi* wadda aka nema a wajenku. Ku ƙudurta ta duka ɗaya ne ko kun san ta da lafzinta ko ba ku san ta da shi ba.

Haƙiƙa, kalma Balarabe da Ba’ajame ba ta da wani abu da suka gwadi ga abubuwan da ta shiryar amma dai ya ishi mutum bayanin abin da ta ƙumsa, ya ƙudurta shi, kuma haka aƙidoji dukansu, abin da ake nema shi ne mutum shi ƙudurta ma’ana ba a sharɗanta ba sai ya lura da lafuzza waɗanda ake lurarwa da gare ta cikin littattafan malamai kuma ba sai ya san haddodinta da alamomi waɗanda aka san ta da su ba.

Haƙiƙa, fahimtar waɗannan lalurori da kewayewa ga waɗannan haƙiƙai da abubuwan da aka tabbatar ilimi ne wani, ba a kallafa wa jahili shi ba. Lokacin da na yi musu wannan jawabi sai suka tafi suna masu farin ciki masu godewa, sa’annan shugaban wannan fitinar ya zo mini ya tambaye ni daga matsaloli na daga wannan manufa? Sai na karɓar masa sa’annan na gabatar masa nasiha. Na ce masa mafi yawan waɗanda ke ganin son ransu shi ne addini da mafi yawan jama’a ɓatattu sun fito a cikin wannan ilimin, to, idan ka yi nufin amfanin mutane, ka tabbatar da su ga aƙidoji gwargwadon yadda suke kai. Ka ba mutane labari da abin da suke lura kamar yadda ya zo a cikin Hadisi babba; “Ka daina wannan jarrabawa da abubuwa waɗanda ba su bayyana sosai ba da rikitta” waɗanda hanyar mutanen addini ba ta bi a nan ba, cikin zamani daga zamunna, sai ko aka gauraya masa wannan sai ya samu damar muzahara (rashin amincewa) sai na ga ganewarsa ta ja-baya daga yadda na san shi gabanin haka. Muna roƙon Allah lafiya.

Sai ya doge a kan wancan abu. Jahilai suka taru a kansa har suka saurari abin da yake ce musu sai ya ci gaba yana runtsewa yana tabbatar da aƙidoji da bayanin samuwar saɓani da makamancin haka bisa ga bayanin da babu wani buƙata gare shi har ya faɗa cikin abin da ya zama mummunan ladabi ne ga alhakin Allah Ta’ala. Ya ci gaba da abin da wanda duk akwai ƙanshi na girman Allah a cikin zuciyarsa ba zai iya faɗin wannan abu ba.

Sai wawaye ƙauyawa daga Jirarata da makamantansu sukan halara a majalisarsa, idan suka dawo zuwa ga mutanensu sai su tafi da waɗannan maganganu sai su dinga jefa tambayoyi a cikin wannan manufa ga ‘yan’uwansu makiyaya, sai suna ce musu ina Allah ya kwana? Ina Ya yi safiya? Ina Ya yini? Ina Shike? Har su kai ga abin da ya fi wannan muni wanda ba zan faɗe shi ba amma na yi faɗakarwa a kan wani abu daga wannan ma’ana a cikin littafina wanda na ambata, sa’annan suka watsa cewa jahilan Musulmi ba a cin yankansu, ba a aurewa da su don tsoron su zama ba su san tauhidi ba.

Masani mai tarewa da ni a kan wannan abin da nake yi managarci uban Abdullahi, Mubarak ɗan Muhammadu Al-Ambari Al-Magribi (Allah ya yi masa rahama), ya ba ni labari cewa wani Balaraben daji a cikin waɗannan jama’ar ya zo da mutane daga garuruwan Towat sun zamo idan suka dafa abincinsu na guzuri, wannan yana cikinsu sai shi ƙi ci tare da su.

Sai ya ce Mahaucin da ya yanke wannan dabbar ba mu sani ba cewa ya san tauhidi ko bai sani ba. Da ya shisshiga gari, aka zo da abinci akwai nama a sama kuma manyan jama’a suna a nan wurin suka kira shi don ya ci sai ya ƙi. Ya ce ba wanda ya yanke wannan abin yankan ba mu sani ba cewa ya san tauhidi ko bai sani ba? Suka ce ai ba Bawa ya yanke ta ba, wanda ya yanke ta Maula wane maɗaukaki daga cikinsu sai dai ya ƙi ci, ya kwana hanji naɗe.

Sa’annan su masu wannan aƙidar suka ci gaba da kece alfarmar jahilan Musulmi sai Allah ya jarrabe su da kece alfarmar malamansu kuma, suka ci gaba da cuta wa masu fiƙihu na lokacinsu suka afku a kan mutanen ilimi da addini da kuma waɗanda suke suna bisa a kan hanyoyi shiryayyu suka ce ɓatattu ne tunda ba su ce jahilai ɓatattu ne ba. Sai ya zama abin da ya auku ga Rahilawa, shi ya auku gare su don kuwa su, Rahilawa, sun kafirta Sahabbai sa’adda ba su gabatar da Aliyu ba. Allah ya girmama fuskarsa sa’annan suka kafirta Aliyu saboda bai yi jayayya ga haƙƙinsa ba.

Da na fito sai mutanen gari suka biyo ni ina kan hanya da tambaya ga abin da ya shuɗe na hukuncin yanke-yankensu da makamantansu. Tambayar a cikin takarda sai na karɓa musu da abin da aka sani a addinin Musulunci; duk wanda ya yi shedar gaskiya (kalmar shahada) haƙiƙa ana cin yankansa, ana aurewa da shi, ana turbuɗe shi maturbuɗar Musulmi matsawar ba wani abu aka gani gare shi ba wanda ya saɓa wa bayyanensa da kuma irin wannan maganar. Sa’adda aka kai wa waɗannan mutane jawabi sai suka ce “Tsarki ya tabbatar ga Allah.” Mun kasance muna ƙirga wane a cikin Malamai sa’annan ya taƙaita ga irin wannan magana kuma ya isu da ita? Wato maganar da na yi musu ba su ko riƙe ta wani abu ba. Don na taƙaita a kan buƙata kuma ita ce gaskiya don ban shagala da maganar da ba ta da wani amfani ba da ɓata.

Da kafin wannan fitina, sun yi karatu ga Malaminmu, Al-Imamu Nasiru, sun riƙi alƙawarinsa. Sa’adda bai shagala da abin da suka shagala da shi ba sai suka yi masa musu. Sannan ya ce bayan ya yi wata magana; “waɗannan mutane fitinarsu ta hasu har ta kusa ta fita zuwa sassa duka sa’annan Allah Ta’ala ya bice ta da falalarSa, annoba ta zo a shekarar dubu

da casa'in (1090) sai ta cire babbar itaciyarsu daga saman ƙasa ba ta samu matabbata ba." A nan wannan magana ta tuƙe.

Na ce ire-iren waɗannan sun bayyana a cikin zamaninmu kamar yadda nuni zuwa gare shi ya shuɗe sai Allah ya tumɓuke ƙarfinsu da littattafan da muka wallafa na Arabiyya da na Ajami kamar yadda Allah ya tumɓuke bidi'o'i zargaggu da al'adu ƙasƙantattu albarkacin littattafan; sunna ta kafu sa'annan bayan haka Allah ya tumɓuke babbar ittanya ta kafirci.

# حِصْنُ الأَفْهَامِ مِنْ جُيوشِ الأَوْهَامِ

# KARE FAHIMTA DAGA RUNDUNAR WAHAMI

Na

Shehu Usmanu Ɗanfodiyo

Mai Fassara:

Sirajo Musa Mafara

## ABUBUWAN DA KE CIKI

**Shafi**

Gabatarwa……………………………………………………………….83

1. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu A Cikin (Kalmar) (لا إله إلا الله) Cewa: (لا إله) Kafirci Ne, Ita Kuma (إلا الله) Musulunci Ne, Wannan Ɓata Ne Kuma Wahami Ne A Kan Haɗuwar Malamai................. 85

2 - Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: “Wannan Kalma Maɗaukakiya Wadda Take Ita Ce: La’ilaha Illa Allah (لا إله إلا الله) Ba Ta Ci Karo Da Gumaka Ba Sai Dai Ta Ci Karo Ne Da Misalin Wanda Ake Kaddartawa. ............................................................................ 86

3- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: “Korewar Da Kalmar La-Ilaha Illa Allah (لا إله إلا الله) Take Yi Ta Shafi Mulkin Sarakunan Duniya, Wannan Shi Ma Ɓarna Ne Kuma Wahami Ne A Kan Haɗuwar Malamai Domin Wancan Mulki (Maja’zeene), Korewar (La) (لا) Daga La-Ilaha Illa Allah Ba Ta Shafuwarsa, Domin Allah Ta’ala Ya Tabbatar Da Wannan Mulki Maja'zee Da Cewarsa:.................................... 90

4. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu A Cikin Ma’anar Cewa Babu Abin Bautawa Da Cancanta Sai Allah, A Cikin Tafsirin Ma’anar Wannan Kalma Mai Daraja Cewa Abin Da Yake Nufi Shi Ne Babu Abin Bautawa Da Gaskiya Sai Allah, Wannan Shi Ma Ɓarna Ne Kuma Wahami Ne A Kan Haɗuwar Malamai, Domin Ma’anar Cewa Babu Abin Bauta Da Cancanta Sai Allah Shi Ne: Babu Wanda Ya Cancanci Ibada Sai Shi, (Duka Ɗaya) An Bauta Masa Ko Ba A Bauta Masa Ba, Domin Munafiki Yana Bauta Masa Alhali Ba Da Gaske Yake Nufi Ba A Cikin Ibadarsa, Saboda Haka (Allah) Ya Ce:......................................................................... 91

5. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: “Hukunci An Gina Shi Ne A Kan Abubuwa Na Ɓoye Ba A Kan Abubuwa Na Bayyane Ba. ........................................................................................ 91

6. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Miƙa Wuyan Sashensu A Kan Cewa: “Hukunci An Gina Shi Ne A Kan Abubuwan Da Ke Bayyane Sai Dai Tare Da Munana Zato A Cikin Aƙidun Jahilan Musulmi.................................... 92

7. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: “Babu Wani Da Ake Hukunci A Gare Shi Da Imani Ko Musulunci Sai Bayan Sanin Aƙida Da Dalilanta, Da Sanin Abin Da Zai Iya Yin Munazara (Tattaunawa) Da Abokin Jayayya Da Sanin Abin Da Ake Warware Shubuha Ta Hanyar Malaman Tauhidi, Tare Da Kiyayewa Da Iyakancewa Da Kuma Samun Iko A Kan Yin Bayani Da Sukan Wannan. .................................................. 92

8. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: “Dukan Kafirai A Zamanin Manzon Allah Tsira Da Amincin Allah Su Tabbata A Gare Shi Masana Ne, Saboda Haka Ake Hukunci A Gare Su Da Musulunci Lokacin Da Suka Yi Huruci Da Kalma Maɗaukakiya, Wannan Shi Ma Ɓarna Ne Kuma Wahami Ne A Kan Haɗuwar Malamai, “Faɗar Allah Maɗaukaki A Cikin Haƙƙinsu: .................................................................................. 93

9. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu: Lokacin Da Suka Ji Cewa “Lallai Sahabbai Dukansu Masana Ne Sai Suka Kaifafa Magana A Cikin Aƙidu Suka Harhaɗa Nau’o’in Harhaɗa Dalilai. ............ 94

10. Yana Daga Cikin Wannan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa; “Duk Wanda Bai Nemi Sanin Littattafan Ilimin Tauhidi Ba Za A Yi Hukunci Da Cewa Shi, Musulmi, Ne Idan Ya Bayyanar Da Musulunci Amma Ba A Hukunci Da Cewa Shi, Mumini, Ne Saboda Shi Bai Nemi Ilimin Sa Ba, Wannan Shi Ma Ɓarna Ce Kuma Wahami Ne A Kan Haɗuwar Malamai.” 95

11. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: “Lallai Su, Jahilai Daga Cikin Jahilan Musulmi A Cikin Waɗannan Zamunna Na Karshe, Ana Yi Musu Hukunci Da Zamansu Kafirai Ko Da Kafircinsu Bai Bayyana Ba Ta Hanyar Zance Ko Aiki, Saɓanin Zamunnan Da Suka Gabata Saboda Rashin Daidaitarsu A Babin Neman Ilimi, Kuma Suna Kafa Dalilai Da Maganar Ɗan Umar A Cikin Fasali Na Farko: Sa’annan Lallai Su, Mutanen Zamanin Da Ya Gabata, Duk Wanda Kafircinsa Bai Bayyana Ba Daga Cikinsu, To, Aurensa Da Yankansa Sun Halatta. ............................... 96

12- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: “Kafa Hujjar Da Sheikh Assunusi Ya Yi A Kan Kafirta Mukalladi A Cikin Littafin Al-Umdah Sharhin Al-Kubra An Gina Shi Ne A Kan Babin Haƙiƙa Da Yanke Hukunci Ba A Kan Babin Tsanantawa Ba.” .................................... 97

13. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: ‘Wanda Ke Kafirta Ma’abuta Bidi’a Waɗanda Suka Musanta Abin Da Aka San Cewa

Manzo (Tsira Da Amincin Allah Su Tabbata A Gare Shi) Ya Zo Da Shi A Kan Nazari Amma Ba Su Musanta Abin Da Aka San Cewa Manzo(S.A.W) Ya Zo Da Shi A Kan Lalura, Cewa Yana Da Dalili Ne Yankakke A Cikin Wannan.” ........................................................................................ 98

14. Akwai Daga Cikin Wancan Wahami Kudurtawar Sashensu Cewa: “Binciken Da Mukallifi Zai Fita Daga Taƙalidi Ta Hanyarsa Babu Makawa Ya Kasance Ta Hanyar Malami.” ................................................................ 99

15. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: “Yin Bincike Ta Hanyar Malaman Tauhidi Yana Wajaba A Kan Kowane Mukallafi, Wannan Shi Ma Ɓarna Ce Kuma Wahami Ne A Kan Haɗuwar Malamai.” ........................................................................................ 100

16 Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu A Kan Ittifaƙin Malaman Sunna A Kan Halaccin Ilimin Tauhidi...................................... 100

17. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: “Sanin Salon Maganar Malaman Tauhidi (Almutakallimuna) Da Waɗanda Ake Kira(Assab'atu Almaɗa'libu) Da Kaifafa Magana A Kan Aƙidoji Da Jeranta Su Tare Da Laƙubbansu Da Kuma Sanin Yadda Ake Shigar Da Su A Karƙashin Kalma Maɗaukakiya (Kalmar Shahada) Da Rarrabe Bayanin Dangantakar Siffofi Da Nau'ukan Harhaɗuwar Dalilai, Cewa Duk Wannan Wajibi Ne A Kan Mukallafi(Baligi). ....................................................... 102

18. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: “Wajabcin Yin Bincike Haƙiƙa Ya Zo Ne Nassance A Cikin Alƙur'ani Da Sunna. ........................................................................................ 103

19. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: “Neman Ilimin Aƙidoji Ba Tare Da Sanin Lugar Larabci Ba Ba Ya Isar Ba'ajame (Wanda Ba Balarabe Ba). ........................................................ 103

20. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu A Cikin Ma'anar Maganar Muhammadu Salihu Ɗan Abdulrahman Ɗan Sulaimu Al-Aujali A Cikin Littafin Dalilil Ka'idi A Cikin Bayanin Alaƙar Gyara Da Samun Iko: ........................................................................................ 104

21. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: “Iyakar Inda Jiki Yake Tarewa Shi Ne Ainihin Wurin Da Ba Komi..................... 104

22. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: “Abin Da Ake Nufi Da Al-Kha'riju Shi Ne Abin Da Ke Bayyana A Ganin Ido, “A Cikin Fassararsu Ga Maganar Malamai Cewa: “Su, Siffofi Na Ma’ani, Akwai Su A Sarari,” ........................................................................................ 105

23. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: “Haƙiƙa, Dalili Ya Zo A Kan Ganin Waɗancan Siffofi Saboda Jin Su Ga Abin Da Ake Faɗa A Kan Kaddartawa Cewa: “Da Dai An Kware Mana Shamaki Da Mun Gan Ta........................................................................... 105

24. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: “Dukan Lafazi Wanda Ma’anarsa Take Koruwa Ga Allah Yana Haramta A Faɗe Sa Gare Shi Ba Tare Da Rarrabewa Ba.” ....................................................... 105

25. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Ga Fassarorin Malamai A Cikin Ayoyi Da Hadisai Masu Rikitarwa Sai Su Ɗauke Su A Matsayin Hukunci Da Aka Yanke: ............................................................ 105

26. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Mayarwar Sashensu: Ma’anar Musulmi Zuwa Ga Ma’anar Munafuki Saboda Haƙiƙanin Musulmi A Wurinsu Shi Ne Wanda Ke Bayyanar Da Musulunci Alhali Shi Ba Mai Imani Ba Ne A Cikin Zuciyarsa Kuma Wannan Shi Ne Haƙiƙanin Munafunci. 106

27. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: “Ana Gane Mumini A Kan Ayyanawa Ba Tare Da Shaidar Mai Shari’a Ba Tsira Da Aminci Su Tabbata A Gare Shi.” ........................................................ 106

28. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: “Da Masani Da Muƙallidi Da Wanda Bai Kai Ga Matsayin Taƙalidi Ba Sanannu Ne A Kan Ayyanawa.”.................................................................................. 107

29. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: “Ijtiha'di, An Gina Shi Ne A Kan Yankakken Hukunci, Ba A Kan Zato Ba,” Saboda Haka Idan Aka Ce Musu: “Wane Ya Dawo Daga Maganarsa Ta Kaza, Suna Mamaki Ga Wannan Saboda Su Suna Kudurta Cewa Wannan Shi Ne Abin Da Allah Da Manzonsa Suke Nufi A Cikin Wannan Hukunci A Yanke.” ......................................................................................... 109

30. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Ƙudurtawar Sashensu Cewa: "Dukan Saɓani Da Ya Auku Tsakanin Ahlu Assunnan Saɓani Ne Na Lafazi Ba Na Ma'ana Ba." ........................................................................................ 109

31. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Ƙudurtawar Sashensu Cewa: Kuskuren Duk Wanda Ya Zamo Daga Cikin Ahlussunna Ba A Mayar Da Shi Da Cewa Wannan Ɓarna Ce,..................................................................... 110

32. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Ƙudurtawar Sashensu Cewa: Annabci Wahayi Ne Kawai, Wannan Shi Ma Ɓarna Ce Kuma Wahami Ne A Kan Haɗuwar Malamai. .............................................................................. 110

33. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: Kafirta Musulmi Ga Wanda Ke Kafirta Shi Ko Ga Wanda Bai Kafirta Waninsa Ba Daga Cikin Musulmi Ba Tare Da Tawili Ba (Wannan) Ta'assubi Ne Kuma Kiyayya Ce. ........................................................................................ 111

34. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Duk Wanda Ya Faɗi La Ila'ha Illa Allahu Muhammadun Rasulullahi, Zai Shiga Al-Janna, Ko Da Bai Fahimci Ma'anarta Ba Wanda Ingancin Imani Yake Dogara A Kan Fahimtarsa." ..................................................................... 119

35-Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Ba A Samun Kafirai A Cikin Waɗannan Ƙasashe Na Sudan Tun Asali. ........... 120

36 – Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: Kowane Bafulatani Musulmi Ne. .............................................................. 122

37 – Yana daga cikin wancan wahami: Ƙudurtawar sashensu cewa: "Waɗansu jama'a sun tarar da iyayensu da shugabanninsu da malamansu a kan al'adu munana sai suka sanya samunsu a kanta (matsayin) hujja a kan sunna." ........................................................................................ 122

38 – Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Sunnar (Sanya) Rawani Ta Keɓanta Da Malamai Ne." .......................... 123

39 - Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Cewa Sashensu Ba Ya Umurni Da Alhairi, Ba Ya Hani Daga Munkari Saboda Galibin Mutane Ba Su Karɓar Wannan, Kuma Yana Sanya Wannan Cewa Uzuri Ne A Gare Shi A Cikin

Barin Umurni Da Hani, Wannan Shi Ma Ɓarna Ne Kuma Wahami Ne A Kan Haɗuwar Malamai......................................................................... 124

40 – Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Yin Kawaici Daga Magana Abin Da Ake Nema Ne A Cikin Kowane Hali, Suna Kafa Dalili Da Cewar (Manzon Allah) Tsira Da Amincin Allah Su Tabbata A Gare Shi "Duk Wanda Ya Yi Kawaici, To, Ya Kuɓuta.".......................... 124

41 – Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kafa Dalilin Sashensu A Kan (Halaccin) Biyar Al'Adu Abin Zargi Da Maganar Da Ta Yaɗu A Cikin Garuruwa Cewa: "Al'adar Gari Kamar Sunna Ne.".................................. 125

42- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Wajibcin Umurni Da Alhairi Da Hani Daga Munkari Ya Dogara Ne A Kan Bayyanar Shugaba," Wannnan Shi Ma Ɓarna Ce Kuma Wahami Ne A Kan Haɗuwar Malamai......................................................................... 125

43- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Su, Jahilai, Babu Wajen Da Za Su Shiga A Cikin Umurtar Mutane Da Alhairi Da Hana Su Daga Munkari." ............................................................ 126

44- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: Wajibcin Umurni Da Alhairi Da Hani Daga Munkari Ya Keɓanta Ne Da Wanda Yake Da Tsentseni. ........................................................ 126

45- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: Faɗar (Manzon Allah) Tsira Da Amincin Allah Su Tabbata Agare Shi Cewa: Addini Sauƙi Ne......................................................................... 127

46- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: Masu Kissoshi Masu Kawatarwa Da Masu Wa'azi Waɗanda Ke Tunatarwa Dukansu Ɗaya Ne. ....................................................................... 127

47- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Barin Sanya Lulluɓi (Hijabi) Ga Mata Da Cuɗanyar Su Da Maza Da Riƙon Su Da Kabilanci Da Yin Kari A Kan Mata Huɗun Da Kore Maraya Daga Haƙƙinsa Da Wanin Wannan Daga Cikin Ayyukan Saɓo (Zunubi) Cikin Abin Da Malaminsu, Jibrilu, Ya Lisafta Shi A Cikin Ayyukan Kafirci.................. 128

48- Yana Daga Cikin Wancan Wahami Cewa: Sashensu Yana Umurtar Yara Da Yin Sallah Amma Bai Umurtar Su Da Yin Alwala Kuma Yana Kudurta Cewa Shi Ya Aikata Alhairi....................................................................... 130

49- Yana Daga Cikin Wancan Wahami Cewa: Sashensu Yana Umurtar Bawansa Kafiri Da Yin Sallah Kafin: Ya Umurce Shi Da (Shiga) Musulunci, Kuma Shi Yana Kudurta Cewa Yana Aikata Alhairi Ne.......................... 130

50- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Duk Wanda Ke Yin Sallah Ba Tare Da Tsarki Ba Kuma Ba Tare Da Wani Uzuri Na Shari'a Ba Ana Lisafta Shi Cikin Masu Sallah, Kuma Sallarsa Tana Daga Abin Da Ake Koyi Da Shi Domin Shi Yana Aikata Haka Saboda Allah."130

51- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Duk Wanda Ya Yi Wankan Janaba Kamar Yadda Allah Ya Umurce Shi Sai Dai Shi Bai Bambantawa Tsakanin Farillai Da Sunnoni Da Mustahabbai Daga Wannan Dukan Sa, Ko Wannan Dukan Sa Bai Inganta A Gare Shi A Kan Ijma'in Malamai."........................................................................... 131

52- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Sashen Malamai Da Ke Jinkirtar Sallah Daga Lokutanta Da Aka Sani Cewa Suna A Kan Daidai."...................................................................... 132

53- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu A Cikin Shigar Lokutan Sallah A Kan Hisabin Abee Miƙra'i A Cikin Cewarsa: *Ɗazhu-Jaba-Abadah-Hayyu.* Suna Kudurta Cewa Wannan Ya Game Dukkan Garuruwa Da Kuma Dukan Zamunna. ...................................................... 132

54- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Sashen Malamai Wanda Ke Fatawa Da (Halaccin) Kome Ga Wanda Ya Saki Matarsa Saki Uku Kafin (Wani) Miji Cewa Yana Da Madogara Wadda Ake Lura Da Ita A Cikin Wannan Saboda Yawan Iliminsa. ..................... 132

55- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: Shi, Ilimin Sufanci, Ba Ya Daga Cikin Farillan Aini Sai Dai Shi Ya Keɓanta Ne Da Waliyyai Ba Tare Da Rarrabewar Bayani Ba. .................................... 133

56- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: Yin Uzba (Barin Aure) Da Barin Abin Da Babu Makawa Gare Shi Na Mafarai (Hanyoyin Nema) Yana Daga Cikin Tsari Na Zuhudu (Gudun Duniya). . 134

57- Yana Daga Cikin Wancan Wahami; Kudurtawar Sashensu Cewa: “Abin Da Yake Daidai Shi Ne Haɗuwar Mutane Don Karatun Alƙur’ani A Cikin Daren Ashirin Da Bakwai Ga Ramadhan Ko Da Tare Da Abin Da Mutane Suka Saba Da Shi A Cikin Wannan Zamani A Cikin Wannan Daren Na Haɗuwar Maza Da Mata Da Murna Wadda Ta Wuce Wuri A Cikin Karatu Da Jayayya A Cikinta Ta Hanyar Wasa Saboda Kasancewar Wannan Yana Kwaɗaitar Da Yara Ga Yin Koƙari Wajen Haddar Alƙur’ani. ................. 134

58- Yana Daga Cikin Wancan Wahami; Kudurtawar Sashensu Cewa: Lallai An Ruwaito Cewa; Annabi Tsira Da Amincin Allah Su Tabbata A Gare Shi Ya Sallaci Wata Salla Lokacin Da Ya Sallama Daga Gare Ta Sai Ya Shimfiɗa Hannuwansa Ya Yi Addu’a Sai Mamu Suka Ce “Ameen” A Kan Addu’arsa, Kuma Ya Jiyar Da Duk Mai Saurare A Kan Wannan Kamar Yadda Aka Sani Kuma Yadda Aka Saba A Yau A Cikin Waɗannan Zamunna........................................................................................ 135

Faɗakarwa:........................................................................................ 136

59- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Mayarwar Sashensu Ma’anar Kasawa Daga Riƙon Sabubba(Hanyoyin Nema) Cewa Shi Ne Ma’anar Tawakkali.......................................................................................... 137

60- Yana Daga Cikin Wancan Wahami; Mayarwar Sashensu Ma’anar Ta’anibi Zuwa Ga Ma’anar Nasiha.......................................................... 137

61- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Mayarwar Sashensu Ma’anar Son Shugabanci Zuwa Ga Ma’anar Son Kira Zuwa Ga Allah.......................... 138

62- Yana Daga Cikin Wancan Wahami; Mayarwar Sashensu Ma’anar Guluwwu(Wuce Wuri) Zuwa Ga Ma’anar Jjtihadi.................................... 138

63- Yana Daga Cikin Wancan Wahami; Mayarwar Sashensu Ma’anar (Azzullu) Wulaƙanci Zuwa Ga Ma’anar Afuwa....................................... 138

64- Yana Daga Cikin Wancan Wahami; Mayarwar Sashensu Ma’anar Ɗemuwa (Teehu) Zuwa Ga Ma’anar Ɗaukakar Rayuwa........................... 138

65- Yana Daga Cikin Wancan Wahami; Mayarwar Sashensu Ma’anar Kiyayya (Hiƙdu) Zuwa Ga Ma’anar Damuwa........................................... 138

66- Yana Daga Cikin Wancan Wahami; Mayarwar Sashensu Ma'anar Ɓarna (Assarfu) Zuwa Ga Ma'anar Kyauta (Al-Ju'd). ........................................ 139

67- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Mayarwar Sashensu Ma'anar Girman Kai (Al-Kibru) Zuwa Ga Ma'anar (Haiba) Kwarjini. .................. 139

68- Yana Daga Cikin Wancan Wahami; Mayarwar Sashensu Ma'anar Wulaƙanci (Mahanah) Zuwa Ga Ma'anar Tawali'u (Kanƙan Da Kai). .... 139

69- Yana Daga Cikin Wancan Wahami; Mayarwar Sashensu Ma'anar Munanan Zato (Su'u Azzanni) Zuwa Ga Ma'anar Kariya (Al-Ihtizaz)..... 139

70- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Mayarwar Sashensu Ma'anar Haƙiƙanin Guri (Tamanni) Zuwa Ga Ma'anar Raja'i. ............................. 140

71- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Mayarwar Sashensu Ma'anar (Al-Jaza'u) Raki Zuwa Ga Ma'anar (Arriƙƙah) Sassautawa. .......................... 140

72- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Mayarwar Sashensu Ma'anar Bushewar Zuciya (Al'ƙasawah) Zuwa Ga Ma'anar Haƙuri. ..................... 140

73- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Mayarwar Sashensu Ma'anar Rashawa Zuwa Ga Ma'anar Kyauta. ........................................................ 140

74- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Mayarwar Sashensu Ma'anar Koke (Shakawa) Zuwa Ga Ma'anar Ambaton Halayya. .................................... 140

75- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Mayarwar Sashensu Ma'anar (Balaha Al-Kƙlbu) Shi Ne Zuciyar Da Babu Komi Cikinta Zuwa Ga Ma'anar Kuɓutarsa. ........................................................................................ 141

76- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Mayarwar Sashensu Ma'anar (Alfakharu) Zuwa Ga Ma'anar Godiya (Ash-Shukru). .............................. 141

77- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Cewa: Sashensu Hasada Tana Makantar Da Shi Sai Ya Ce: Abin Da Yake Daidai Shi Ne Barin Shagaltuwa Da Wallafa Littattafai A Yau Domin Wallafe – Wallafen Malamai Mashahurai Waɗanda Suka Gabata Ba Su Bar Komi Ba Wanda Ake Buƙata Zuwa Gare Shi, Kuma Su Ne Mafi Cikakken Ilimin A Kan Waɗanda Ke Wallafe-Wallafe A Yau. .............................................................................. 142

78- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Ƙudurtawar Sashensu Cewa: "Barin Cuɗanya Da Mutane Shi Ne Ya Fi Ga Kowane Mutum Ɗaya." ............... 142

79- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Ƙudurtawar Sashensu Cewa: Maganar (Imam) Ashshafi-I Allah Shi Yarda Da Shi Cewa: "Duk Wanda Aka Nemi A Fusatar Da Shi Sai Bai Yi Fushi Ba, To, Shi Jaki Ne)." Wannan Yabo Ne A Kan Kowane Irin Fushi. ......................................................... 143

80- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Ƙudurtawar Sashensu Cewa: Sharuɗɗan Fassara Alƙur'ani A Kan Hanyar Ijtihadi Ana Sharɗanta Su A Kan Wanda Ke Fassara Shi Ta Hanyar Hikaya. ....................................... 144

81- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Ƙudurtawar Sashensu Cewa: Tafsirin Alƙur'ani Ba Ya Halatta Domin Shi Ne Dalilin Samun Fari Da Fitinoni. 145

82- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Ƙudurtawar Sashensu Cewa: Fassara Alƙur'ani Ya Halatta Sai Dai Mu Ba Mu Cimma Fahimtar Haƙiƙaninsa. 145

83- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Ƙudurtawar Sashensu Cewa: Yana Halatta A Fassara Alƙur'ani Sai Dai A Cikin Daji Ba A Cikin Birane Ba.145

84- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Ƙudurtawar Sashensu Cewa: Yana Halatta A Fassara Alƙur'ani Sai Dai Ga Tsoho Ba Ga Saurayi Ba. .......... 146

85- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Ƙudurtawar Sashensu Cewa, Ba Ya Halatta Ga Mai Wa'azi Ya Tunatar Da Ayoyin Alƙur'ani. ....................... 146

86- Yana Daga Cikin Wancan Wahami Cewa: A Wajen Neman Shiriya, Sashensu Yana Kula Ne Da Maganar Malaman Tauhidi Kawai A Cikin Tauhidi, Amma A Cikin Wannan Ba Ya Kula Da Abin Da Ake Ambata Masa A Cikin Tafsirin Alƙur'ani. ....................................................................... 148

87- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Ƙudurtawar Sashensu Cewa: Samun Izini (Ijaza) Daga Malamai Ba Sharaɗi Ba Ne A Cikin Halaccin Kafuwa Ga Aikin Karantarwa Da Fa'idantarwa Ta Hanyar Koyar Da Kowane Fanni Daga Cikin Fannonin Ilimi Da Yin Fatawa. ............................................. 149

88- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Ƙudurtawar Sashensu Cewa: Abin Da Aka Cirato Daga Malamansu Na Kuskure Bayyananne A Cikin Karatu (Na Alƙur'ani) Kamar Musanya Alif Da Ya'un A Wajen (Kalmar) {آمنتم} Da {آلهتنا} Da Wanin Wannan Daga Cikin Abin Da Suke Yin Kuskure A Cikin

Karatu Cewa Daidai Ne Domin Sun Yi Kuskure Ne Don Suna Neman Dacewa Da Kira'ar Nafi'u. ........................................................................ 149

89- Yana Daga Cikin Wancan Wahami Cewa: Sashensu Yana Korewar Cewa: Allah Yana Buɗi (Fatahi) Ga Wani Daga Cikin Mutanen Karshe Irin Abin Da Bai Yi Buɗinsa Ba Ga Waɗanda Suka Gabata Daga Cikin Malamansu A Cikin Babin Ilimi. .............................................................. 150

90- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Barin Mu'ahadah (Yawan Maimaitawar) Karatun Lafuzzan Alƙur'ani Wanda Aka Haddace Saboda Neman Ilimin Farillan Aini Daga Ilimi (Suna Cewa Yin Haka) Daidai Ne Kuma Uzuri Ne Na Shari'a. .......................................... 150

91- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: Dukkan Abin Da Suka Samu Cikin Littattafan Tafsiri Gaskiya Ne Domin Fassara Ce Ta Maganar Allah. ...................................................................................... 151

92- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: Hadisai Ingatattu Suna Dacewa Da Mazhabobi Guda Huɗu Saboda Haka Yana Gaugawa Ga Aiki Da Kowane Hadisi Ingantacce Wanda Ya Ji. .............. 151

93- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: Faɗar Malamai Cewa, Wannan Hadisi Ne Ingantacce (Sahihi Ne), Wannan Hadisi Ne Mai Kyau (Hasan), Wannan Hadisi Ne Mai Runi (Dhaeefi), An Gina Wannan Magana A Kan Hukunci Yankakke. ........................................... 152

94- Tana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Manufar Gittawar Mujtahidi A Kan Mujtahidi (Irinsa) Shi Ne Nuna Kiyayya." ................................................................................................ 152

95- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Tsanance-Tsanancen Masu Ijtihadi A Cikin Babin Jayayya Da Waninsa, An Gina Shi Ne A Kan Yankakken Hukunci." ............................................... 152

96- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Ba A Karɓa A Cikin Ilimin Tauhidi Sai Abin Da Sheikh Assunusi Ya Faɗa." "Ba A Karɓar Abin Da Waninsa Ya Faɗa Daga Cikin Malaman Sunna Idan Ya Saɓa Wa Maganarsa." ................................................................... 154

97- Yana Daga Cikin Wancan Wahami Cewa: Ana Mayar Da Magana Wadda Masu Shauƙi Suka Keɓanta Da Ita Ko Kuma A Yi Koyi Da Shi(Mai Shauƙi) Ba Tare Da Sanin Manufofinsa Ba Da Matsayinsa. .................... 154

98- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: Duk Wanda Yake Da Wani Rabo Daga Shugabancin Wani Abu Daga Cikin Siffofin Mutane Ba Zai Bayyana A Gare Shi Ba Ko Da A Kan Nadiri. ... 156

99- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Duk Wanda Ya Kasance Daga Cikin Ma'abuta Kashfi Yana Inganta A Yi Koyi Da Shi A Cikin Hanyar Suluki Zuwa Ga Allah Maɗaukaki." .................. 156

100- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Duk Abin Da Ya Wuce Hankalinsa Na Ilimummukan Kashfi, To, Shi Abin Mayarwa Ne." ........................................................................... 157

101- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Duk Abin Da Ake Faɗa A Zahirin Hukuncin Shari'a Babu Wanda Ya San Haƙiƙaninsa Sai Allah, Kamar Yadda Ake Faɗa Ga Ayoyi Da Hadisai Masu Rikitarwa. Haka Kuma Kamar Misalin Mas'alar Haƙiƙanin Ruhi, Allah Bai Tsinkayar Da Wani A Kansa Kuma Dukan Mutane Daidai Suke A Cikin Wannan A Kan Haɗuwar Malamai. .......................................................... 157

Gabatarwa

*Ina farawa da sunan Allah Mai rahama Mai jin-ƙai*

Allah ya daɗa tsira ga shugabanmu, Muhammadu da iyalan gidansa da sahabbansa, Ya daɗa aminci cikakken aminci.

Bawa talaka mai tsananin buƙata ga rahamar Ubangijinsa, Usmanu ɗan Muhammadu ɗan Usmanu wanda aka fi sani da Ɗanfodiyo, Allah ya rufe shi da rahamarSa Amin ya ce:

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, mafificin tsira da mafificin aminci su tabbata ga shugabanmu, Muhammadu da iyalan gidansa da sahabbansa baki ɗaya, Allah Maɗaukakin Sarki Shi yarda da shugabanni masu biya da malamai masu aiki da shugabanni guda huɗu masu ijtihadi (ƙoƙari) da duk wanda ya bi su da kyautatawa har zuwa ranar sakamako.

**Bayan haka:** Wannan littafi mai suna (KARE FAHIMTA DAGA RUNDUNAR WAHAMI) mai amfani ne in Allah ya so ga duk wanda ya dogara kansa. Ina faɗa dacewa ga Allah take:

Sheikh Malam Assunusi ya faɗa a cikin littafin Al'umdah sharhin Al'kubra: Wahami yana rikita hankali ga abin da yake kamawa, Ɓarna kuwa tana kama da gaskiya a cikin hanyoyin bincikenta, saboda haka ma'abuta gaskiya suka ƙaranta matuƙa.

Ya faɗa kuma a cikinsa a wani mahalli a cikin bayanin haƙiƙanin abin da ake nufi da **mugalaɗah**: Ita ce duk abin da ya haɗu na abubuwan da ke gabata masu kama da gaskiya amma babu gaskiya a ciki. Ana kuma kiranta da **Safsaɗah**, ko kuma ta yi kama da abubuwan da suka gabata waɗanda suka shahara, waɗannan ana kiransu **Mushagabah**, ko kuma abubuwa suka gabata na wahami da ƙarya, kamar idan ka ga igiya wadda aka yi ta kamar maciji, za ka san cewa igiya ce amma idan aka jefa ta a gare ka za ka ji tsoronta saboda wahami sau da yawa yakan rinjayi hankali, babu abin da ya ja ka kamar wahami, Zuciya tana cewa: "Wannan ya yi kama da maciji ko kuma wannan daidai yake da maciji, duk kuwa abin da zai kasance kamar irin haka, to, abin tsoro ne, ko kuma guje masa shi ne himma. Da irin wannan wahami ne da yawa daga cikin mutane suka faɗa cikin nau'o'in bidi'a daban-daban da kuma ɓata." A nan ya tsaya a taƙaice.

**Na ce:** Haƙiƙa, Malam ya faɗi gaskiya domin daga wannan babi ne mafi yawan jahilan ɗalibai suka nutse a cikin tekun ɓata suka faɗi

maganganu na banza waɗanda duk mutum mai hankali ba zai yarda ya faɗe su ba, suka riƙi jahilci shi ne madogararsu, bidi'a ita ce abin jinginarsa, ɓarna mai ƙawatarwa ita ce shimfiɗarsu, suka yi watsi da sunna da hanyoyinta, suka zaɓi bidi'a suka buɗe ƙofofinta, su a haƙiƙa kamar yadda mai waƙa ya faɗa:

"Su marasa lafiya ne a kan ayyukan alkhairi sun nutse a cikin tekun halaka kuma babu wani mai kira zuwa ga hanya mafi daidai.

Sun yi barci daga manufa kuma ba su farka ba da sannu farkawarsu za ta kasance ga wani babban lamari mafi girma (musiba)."

Lamurran da suka kasance ta hanyar su ne ake kore ƙirƙiro abin da bai cikin addini kamar yadda Ahmad Zaruƙ ya faɗa a cikin (littafin) Umdatul murid Assa'diƙ, guda uku ne:

**Na farkonsa:** Ingantar da Imani ta fuskar da zai kai ga tsayar da alfarmar Mai shari'a (Ubangiji) ga abin da Ya yi umurni da shi. Da abin da Ya yi hani daga gare shi, da sanya lura a cikin addini. Haƙiƙa, Allah Maɗaukaki ya ce:

﴿ وَمَآ ءَاتَىٰكُمُ ٱلرَّسُولُ فَخُذُوهُ وَمَا نَهَىٰكُمۡ عَنۡهُ فَٱنتَهُواْ ﴾ الحشر: ٧

***"Abin da Manzo ya zo maku da shi ku riƙe shi, kuma abin da ya hane ku daga gare shi ku bari." Hashri: 7***

Kuma Mai girma da ɗaukaka Ya ce:

﴿ فَلۡيَحۡذَرِ ٱلَّذِينَ يُخَالِفُونَ عَنۡ أَمۡرِهِۦٓ أَن تُصِيبَهُمۡ فِتۡنَةٌ أَوۡ يُصِيبَهُمۡ عَذَابٌ أَلِيمٌ ﴿٦٣﴾ ﴾ النور: ٦٣

***"Waɗanda ke saɓa wa umurninSa su yi saunar fitina ta same su ko azaba mai tsanani ta same su." Al-Nur: 63***

Allah Mai girma da buwaya Ya ce:

﴿ قُلۡ هَٰذِهِۦ سَبِيلِيٓ أَدۡعُوٓاْ إِلَى ٱللَّهِۚ عَلَىٰ بَصِيرَةٍ أَنَا۠ وَمَنِ ٱتَّبَعَنِي ﴾ يوسف: ١٠٨

*"Ka ce wannan ita ce hanyata, ina kira zuwa ga Allah a kan Basirah (Ilimi) ni da duk wanda ya bi ni" Yusuf: 108*

Da wannan ne ya bayyana cewa fahimta a cikin addini asali ne daga ciikin asullansa.

**Na biyu:** Bincike game da hukunce-hukuncen Allah ga abin da yake da shi a cikin motsi da sukuni da abin da yake zo masa na fuskantowa da juyawa, wannan duka ba ya inganta sai da kula da halayensa, ba zai yi aiki da wani abu ba sai da ilimi da kuma koyi da wanda yake inganta a yi koyi da shi, kamar malami mai tsentseni ko wani masani wanda ba shi da son rai.

**Na uku:** Ilimi a kan asullan hanyar da yake son biyarta. A nan ya tsaya.

Idan ka fahimci wannan (bayani) dukansa za ka san cewa rashin sanin waɗannan lamurra guda uku shi ne ya nutsar da mafi yawan ɗalibai masu jahilci cikin tekun wahami.

**1. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu A Cikin (Kalmar) (لا إله إلا الله) Cewa: (لا إله) Kafirci Ne, Ita Kuma (إلا الله) Musulunci Ne, Wannan Ɓata Ne Kuma Wahami Ne A Kan Haɗuwar Malamai.**

Muhammad Salihu ɗan Abdulrahman ɗan Sulaimu Al-Aujaly. Ya faɗa a cikin littafinsa mai suna (Al-Mazeedil A-idi) Sharhin Littafi mai suna (Dalilul Ka'idi):

Irin wannan ƙaddartawa mara kyau tana lizimta kafirtar da wanda ya yi furuci da farkonta ko da ya koma zuwa ga imani da kasawarta, kuma a kan wannan ƙaddarawa ɓatatta tana lizinta cewa duk wanda ya yi furuci da La'ilaha Illa Allah (لا إله إلا الله) zai kasance mai ridda ko da ya koma zuwa ga imani a lokacin da ya faɗi Illa Allah (إلا الله) domin dukan aikinsa ya ɓaci, ya rabu da matarsa, kuma dukiyarsa ta zama fai-i ga Musulmi, ko da mutuwa ta auko masa bayan ya faɗi (لا إله) kafin (ya faɗi) (إلا الله), to, ya mutu kafiri. Allah ya yi muna tsari daga wannan. Maganarsa a nan ta tsaya.

**2 - Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Wannan Kalma Maɗaukakiya Wadda Take Ita Ce: La'ilaha Illa Allah (لا إله إلا الله) Ba Ta Ci Karo Da Gumaka Ba Sai Dai Ta Ci Karo Ne Da Misalin Wanda Ake Kaddartawa.**

**Na ce:** A kan wannan ƙaddartawa yana lizimta haramcin faɗar lafazin (لا إله إلا الله)La'ilaha Illa Allah, muna neman tsari da Allah daga wahami da munanan fahimta.

Wannan shi ma ɓarna ne kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai, saboda dalilin shar'anta ta kamar yadda da yawa daga cikin malaman tauhidi suka bayyana shi ne domin raddi a kan kafirai a cikin ƙudurtawarsu ga tarayya da Allah a cikin cancantar Ibadah. To, wannan abin mayarwa ce a kansu kuma mai kore ulu'hiyya ne ga dukan wanda ba Allah Maɗaukaki ba, kamar gunki da dutsi da icce da rana da wata da wanin wannan na sauran abin da ake bautawa da wanin Allah, ko kuma ba a bauta masa ba, littafin Alƙur'ani da littattafan Tafsiri (masu bayyanawa ne a cikin wannan, kuma wannan (bayani) duk wanda ke rarrabewa tsakanin korewa da tabbatarwa zai fahimce shi.

Haƙiƙa, sashen waɗanda ba su da tahaƙƙuƙi ya yi kuskure mummuna (munana), sai ya riyanta cewa (wannan kalma) ba ta gitta wa gumaka ba sai dai ta gitta wa misali ne wanda ake ƙaddartawa. To, wannan magana tana daga cikin baƙin maganganu mafi ban mamaki, babu wani daga cikin mushirikai waɗanda ke bautar gumaka da ya faɗe ta, (su mushrikai) sun fahimci cewa (wannan kalma) ta gitta wa gumakansu kuma ta yi masu raddi saboda su, (mushrikai), masana Larabci ne sai dai sun yi jayayya ne a kan kasancewar abin da Kalmar La'ilaha Illa Allah (لا إله إلا الله) ta kore da ya zama gaskiya. Ba ka duba zuwa ga faɗar Allah Maɗaukaki:

﴿ إِنَّهُمْ كَانُوٓا۟ إِذَا قِيلَ لَهُمْ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا ٱللَّهُ يَسْتَكْبِرُونَ ﴿٣٥﴾ ﴾ الصافات: ٣٥

***"Lalle su sun kasance idan aka ce musu babu wanda ya cancanta a bautawa sai Allah sai su rinƙa girman kai" Asswa'ffat : 35***

Ba domin (wannan aya) ta yi raddi a kansu ba da ba su yi musu ba, kuma da ba su gudu ba, saboda su ba su yi da'awar Uluhiyya ba saboda wani misali abin ƙaddartawa wanda ba su san shi ba.

Ka yi duba zuwa ga faɗarsu cewa:

﴿ أَجَعَلَ ٱلۡأٓلِهَةَ إِلَٰهٗا وَٰحِدًاۖ إِنَّ هَٰذَا لَشَيۡءٌ عُجَابٞ ۝٥ ﴾ ص: ٥

*"Ko ya sanya abin bautawa ya zama abin bauta ɗaya" Swa'd: 5*

Haƙiƙa, Malam Manjuree ya yi magana a kan wannan ma'ana da Sayyid Abdulrahman Al-fasy da Sayyid Al-araby Alfasy da waninsu sun aibanta a kan wanda ya yi wahamin gittawarta a kan gumaka.

A cikin (Littafin) Hashiyyah na Sayyid Abdulrahman Al-fasy, abin da ya nassata: Al-Imam Ibn Marzuk ya faɗa a cikin sharhin Bukhary:

Lokacin da (Mutanen) Jahiliyya suka kasance suna ƙudurta zaman wanin Allah a matsayin Allah da kuma cewa Allah yana da abokin tarayya sai aka shar'anta kalmar shahada wadda ta ƙunshi cewa: "Babu wanda ya cancanta a bautawa sai Allah kuma babu abin bauta (da cancanta) sai Shi." Domin shafe abin da suka kasance a kansa na ɓatattar aƙida da (tabbatar da) aƙidar gaskiya.

Ma'anar shahada shi ne: "Tabbatar da cewa babu wani Ubangiji wanda ya cancanta a bauta masa sai Allah kuma haƙiƙa Annabi Muhammadu Manzon Allah ne."

Malam Sayyid Zaruk Allah ya ji-ƙansa ya ce: "Kalmar Ilahu, Larabawa sun aza ta a kan duk wani abin da ake bautawa, an bauta masa da cancanta, ko da ƙarya, sai shari'a ta zo ta kore duk abin da suka shigar, shi ne (sai ta zo da) faɗar (Kalmar) La'ilaha Illa Allah (Babu wanda ya cancanta da a bauta masa sai Allah).

Ibnu Zikri ya ce: "An zo da korewa da tabbatarwa a cikin kalma mai daraja (La'ilaha Illa Allah) don raddi a kan duk wanda ke ƙudurta shirka sai ya kasance daga babin taƙaita siffa ga wanda aka siffanta, kamar faɗarmu cewa: Ba marubuci sai Zaidu, a wajen magana da wanda ke ƙudurta tarayyar Zaidu da Amru a cikin rubutu."

Malam Assunusi ya faɗa a cikin sharhin Assugra cewa: "Wanda ya kafirta ya kafirta ne saboda ƙara wani abin bauta na daban."

Al-Sheikh Al-ha'fiz Sayyid Al-Maƙarri ya ce: "Faɗarsa cewa wanda ya kafirta ya kafirta ne ……)" yana nufin daga cikin mushrikai lokacin da suka sanya abokan tarayya tare da Allah, suka kuma halatta sanya adadi ga

haƙiƙanin Uluhiyyah domin sun faɗa lokacin da aka umurce su da su ce La'ilaha Illa Allah (sai suka ce)

﴿ أَجَعَلَ ٱلْءَالِهَةَ إِلَٰهًا وَٰحِدًا إِنَّ هَٰذَا لَشَىْءٌ عُجَابٌ ﴿٥﴾ ﴾ ص: ٥

*"Ya sanya ababen bauta sun zama abin bauta ɗaya" Saa'd: 5.*

Sai kuma ya ce: Duk wanda bai kore abin bautarsu da (La) ba (لا), to, shi mai ƙiyayya ne kuma mai makantattar basira ne, wanda aka rufe zuciyarsa, ko kuma jahili ne yana faɗar maganganu game da Ubangiji.

**Na ce:** Lamarin ba a ɓoye yake ba cewa kai idan ka ce: Babu masani sai Zaidu, kuma ka yi magana da mai ƙudurta cewa Amru da Khalidu masana ne, to, wannan korewa ta hau kansu kuma a haka Kalmar La'ilaha Illa Allah take, tana hawa a kan gumaka. Waɗansu da yawa daga cikin malaman sunna sun faɗakar a kan wannan, Babban malamin nan mai suna Sayyid Al-Araby Al-Fasy ya ce:

"Wannan (lamari) a bayyane yake matuƙa ta yadda babu mutun biyu daga cikin masu hankali da suka yi saɓani a cikinsa."

Haƙiƙa, Sayyid Ibn Al-araby ya yi jayayya (munaza'a) da Ibnu Abee Mahalliy Allah shi yarda da shi tare da sashen ɗalibai a cikin wannan mas'ala sai suka kurunce (suka doge) a kan waccan aƙida ɓatatta wanda yake duk wani mai iya rarrabe lamurra (mumayyazy) ba zai yarda da ita ba. Za ka gan su suna kafa dalilai da waɗansu lamurra waɗanda Allah Mai girma da buwaya ya ɓata su saboda bayyanar tanaƙuli a cikinsu, babu wata magana da suka yi furuci da ita face Allah Maɗaukakin Sarki ya ɓata sashen ta da sashe saboda bayyanar tanaƙuli. Wannan babu buƙatar wani dalili tare da shi, godiya ta tabbata ga Allah, da yawa Ya shiryar da wanda Ya so daga cikin bayinSa, da haskenSa mai bayyana bayan duhun jahilci da ɓata.

Yana daga cikin abin da suka kafa dalili da shi cewa: "Lalle su, gumaka ba, Alloli ba ne saboda haka korewar da ke cikin kalma mai daraja bai hawa a kanta, ka duba Allah ya yi mana rahama da kai (ka yi duba) ga wannan tanaƙuli bayyananne, lalle faɗarsu cewa: "Ba Alloli ba ne wannan shi ne haƙiƙanin korewa wanda yake cikin kalma mai daraja domin Kalmar (Laisa) (ليس) ba kamar Kalmar (La) (لا) take ba a cikin ma'anar korewa, wannan a bayyane yake."

Sun kuma kafa dalili da cewa mushrikai sun yi da'awar zaman gumaka Alloli sai suka bauta masu, to, ibadarsu ta soku kuma abin da ya riga ya faɗi ba zai tashi ba.

Ka duba kuma Allah ya sa mu dace tare da kai (ka dubi) wannan magana yasassa kuma lalatatta tare da kasancewar ta lalatatta za ta koma a kansu a cikin da'awarsu.

Amma lalacewarta, bayaninsa shi ne cewa: "Lalle korewa a cikin (Kalmar) La'ilaha Illa Allah bai yi tasalluɗi a kan da'awar mushrikai ba da Ibadarsu ɓatatta, domin wannan ya riga ya auku, sai dai ya yi tasalluɗi ne a kan wanda ake da'awa a kansa, shi ne cancantar gumaka da a bauta masu da zaman su Alloli (abin nufi shi ne) waɗannan gumaka da kuke bautawa kuma kuna da'awar cewa Alloli ne, to, ba Alloli ne ba domin babu Ilahu (wanda ya cancanci bauta) sai Allah Maɗaukakin Sarki sai dai wanda bai rarrabewa tsakanin da'awa da wanda ake da'awa a kansa."

Amma bayanin komawarsa a kansu, lallai mu mun yi iddi'a'in (da'awar) samun cin karo tsakanin kalma Maɗaukakiya (Kalmar shahada) da gumaka. Kuma da'awar cin karo (taa'rudhi) abu ne da ya auku ta hanyar ganin bayyanar jayayya (da ke ciki) sai a ce masu: Korewarku ga ta'arrudhi (cin karo) tare da cewa mu mun yi da'awar ɗauke aukuwa a kan abin da kuka tafi zuwa gare shi yake nunawa a cikin wannan mas'ala kanta.

Idan suka ce: "Lallai abin da muka kore shi ne abin da kuka yi da'awa na (samun) ta'arrudhi (cinkaro) cewa gaskiya ne ba haƙiƙanin da'awarku ba wadda ta auku."

**Sai mu ce:** "Irin wannan shi ne abin da muke nema ga Kalmar La-Ilaha Illa Allah (لا إله إلا الله) ku kuwa kun hana shi ko da da irin wannan fahimta, wannan kuwa warware magana ne. Ka dubi sharhin Al-mufeedah na Al'shaikh Muhammad bin Abi Mahally za ka samu dukan abin da muka ambata cikin lamarin wannan jayayya."

**3- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: “Korewar Da Kalmar La-Ilaha Illa Allah (لا إله إلا الله) Take Yi Ta Shafi Mulkin Sarakunan Duniya, Wannan Shi Ma Ɓarna Ne Kuma Wahami Ne A Kan Haɗuwar Malamai Domin Wancan Mulki (Maja’zeene), Korewar (La) (لا) Daga La-Ilaha Illa Allah Ba Ta Shafuwarsa, Domin Allah Ta’ala Ya Tabbatar Da Wannan Mulki Maja'zee Da Cewarsa:**

﴿وَكَانَ وَرَآءَهُم مَّلِكٌ يَأۡخُذُ كُلَّ سَفِينَةٍ غَصۡبٗا ٧٩﴾ الكهف: ٧٩

*“Ya kasance a gaban su akwai wani Sarki yana karɓe kowane jirgin ruwa a kan ƙwace.” Kahfi 79.*

Da kuma faɗarSa:

﴿وَٱللَّهُ يُؤۡتِي مُلۡكَهُۥ مَن يَشَآءُ﴾ البقرة: ٢٤٧

*“Allah yana ba da mulkinSa ga wanda Yake so” Baƙara 247.*

Da kuma faɗarSa:

﴿وَقَالَ ٱلۡمَلِكُ ٱئۡتُونِي بِهِۦ﴾ يوسف: ٥٠ – ٥٤

*“Sai sarki ya ce ku zo man da shi”, Yusuf: 50-54*

Da kuma faɗarSa:

﴿قُلِ ٱللَّهُمَّ مَٰلِكَ ٱلۡمُلۡكِ تُؤۡتِي ٱلۡمُلۡكَ مَن تَشَآءُ وَتَنزِعُ ٱلۡمُلۡكَ مِمَّن تَشَآءُ﴾ آل عمران: ٢٦

*" Ka ce ya Ubangiji Mamallakin mulki Kana ba da mulki ga wanda Kake so kuma Kana karɓe mulki daga wanda Kake so" Ali-Imrana : 26*

Da waninsu daga cikin Ayoyi.

**4. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu A Cikin Ma'anar Cewa Babu Abin Bautawa Da Cancanta Sai Allah, A Cikin Tafsirin Ma'anar Wannan Kalma Mai Daraja Cewa Abin Da Yake Nufi Shi Ne Babu Abin Bautawa Da Gaskiya Sai Allah, Wannan Shi Ma Ɓarna Ne Kuma Wahami Ne A Kan Haɗuwar Malamai, Domin Ma'anar Cewa Babu Abin Bauta Da Cancanta Sai Allah Shi Ne: Babu Wanda Ya Cancanci Ibada Sai Shi, (Duka Ɗaya) An Bauta Masa Ko Ba A Bauta Masa Ba, Domin Munafiki Yana Bauta Masa Alhali Ba Da Gaske Yake Nufi Ba A Cikin Ibadarsa, Saboda Haka (Allah) Ya Ce:**

﴿وَلَهُۥٓ أَسۡلَمَ مَن فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ طَوۡعٗا﴾ آل عمران: ٨٣

***"Kuma duk waɗanda ke a cikin sammai da ƙasa a gare Shi suka miƙa wuya a kan ɗa'a"*** Al'Imrana: 83.

Ai ta ɓangaren masu Imani. {وكرها} da kuma a kan tilas) Ai ta ɓangaren munafakai

**5. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Hukunci An Gina Shi Ne A Kan Abubuwa Na Ɓoye Ba A Kan Abubuwa Na Bayyane Ba.**

Wannan shi ma ɓarna ne kuma wahami ne, a kan haɗuwar malamai, saboda faɗarsa tsira da amincin allah su tabbata a gare shi:

(أُمرت أن أُقاتل الناس حتى يقولوا: لا إله إلا الله، فإذا قالوها عصموا مني دماءهم وأموالهم إلا بحقها وحسابهم على الله)

***"An umurce ni da in yaƙi mutane har sai sun faɗi cewa babu wanda ya cancanta a bautawa sai Allah, idan sun faɗe ta sun kare jinannensu da dukiyoyinsu daga gare ni kuma hisabinsu yana wurin Allah).***

Al-sheikh Assunusi ya faɗa a cikin Al-Umdah Sharhin Al-Kubra: cewa: "(Ginin Hukunce-hukuncenta) yana nufin (duniya) yana a kan abubuwa na bayyane." Sai ya ce bayan Maganganu: "Saboda sunna ta shuɗe a kan rashin bincike a kan abubuwan da ke cikin Zuciya sai dai ita ana bayyanar da ita a lahira ne a ranar al-ƙiyama

﴿يَوۡمَ تُبۡلَى ٱلسَّرَآئِرُ ۝٩﴾ الطارق: ٩

*"Ranar da ake jarraba asirrai" Adɗarik: 9*

**6. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Miƙa Wuyan Sashensu A Kan Cewa: "Hukunci An Gina Shi Ne A Kan Abubuwan Da Ke Bayyane Sai Dai Tare Da Munana Zato A Cikin Aƙidun Jahilan Musulmi.**

Wannan shi ma ɓarna ne kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai."

Sheikh Assunusi ya faɗa a cikin sharhin Al-wusɗa: Amma shi, mutun, dangane da kansa shi ne mafi sani da shi kuma ba a tambayar waninsa game da shi.

Sai kuma ya ce; "Amma shi, mutum, dangane da waninsa, rabonsa shi ne Jahiltar halin zuciyarsa da rashin yanke (hukunci) da wani abu a cikin haƙƙinsa dangane da abin da ke cikin wannan lamari, sai dai idan mai shar'antawa tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya yi shaida ga wani da wani abu sai a yanke (hukunci) gare shi a cikin wannan lamarin, domin Allah Maɗaukaki da manzonSa su ne suka fi sani, sa'annan tare da haka ba zama a kanmu ba na mu rinƙa munana zato ga imanin wani mutun daga cikin Musulmi, jahili ne ko waninsa.

Sai kuma ya ce: "Sai dai idan ya bayyana a kan harshen mutum abin da ke nuna abin da ke ɓoye a cikin zuciyarsa na ɓatattar aƙida, to, abin da yake wajibi a wannan lokaci shi ne a tausasa a wajen koyar da shi da maganin cutarsa gwargwadon abin da ya sauƙaƙa." Allah ne abin neman taimako.

**7. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Babu Wani Da Ake Hukunci A Gare Shi Da Imani Ko Musulunci Sai Bayan Sanin Aƙida Da Dalilanta, Da Sanin Abin Da Zai Iya Yin Munazara (Tattaunawa) Da Abokin Jayayya Da Sanin Abin Da Ake Warware Shubuha Ta Hanyar Malaman Tauhidi, Tare Da Kiyayewa Da Iyakancewa Da Kuma Samun Iko A Kan Yin Bayani Da Sukan Wannan.**

wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai.

Shugaba malami wanda ya kai matuƙa ga ilimi kuma mai tahƙeeƙi Mahmud ɗan Ahmad Al-ƙaunawy ya faɗa a cikin sharhin Al-umdah ta Malam Annasfy! Abin da ke tabbatar da ɓacin mazhabarsu (Hanyarsu) shi ne cewa Manzon Allah mai tsira da aminci bai aikata wannan ba a zamaninsa,

kuma (Abubakar) Siddiƙ a cikin khalifancinsa bai aikata haka ba a kan waɗanda suka yi ridda haka Umar Allah ya yarda da shi a zamanin khalifancinsa bai bai aikata wannan ba ga mutanen Zaɗɗa (waɗansu jinsin mutane ne daga Sudan da Hindu) da mutanen Ambaɗu, lokacin da ya ci tsakiyar Iraƙi da yaƙi tare da karamcin hankalinsu da kuma taƙaitacciyar fahimtarsu. Kuma babu wani daga cikin sahabban Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi da ya aikata wannan. Haka nan duk wanda ya tsaya a matsayinsu har zuwa wannan lokaci namu. Da a ce abin da suka riyanta ya zama gaskiya da sun shagala da ɗayan lamari biyu: Ko da bijirewa daga karɓar musuluncinsu ko kuma da kafa wani masanin tauhidi mai hazaƙa da sanin dalilai, kuma masani a kan yadda ake jayayya da hujjoji don ya sanar da tauhidi bayan haka sai su yi hukunci da tabbatar da imaninsu, to, a lokacin hanuwarsu da hanuwar duk wanda ya tsaya matsayinsu har zuwa yau. Daga wannan ne ya bayyana cewa lallai abin da suka tafi zuwa gare shi ɓarna ne domin ya saɓa wa aikin Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi da sahabbansa masu girma da waninsu daga cikin shugabanni masu girma.

**8. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Dukan Kafirai A Zamanin Manzon Allah Tsira Da Amincin Allah Su Tabbata A Gare Shi Masana Ne, Saboda Haka Ake Hukunci A Gare Su Da Musulunci Lokacin Da Suka Yi Huruci Da Kalma Maɗaukakiya, Wannan Shi Ma Ɓarna Ne Kuma Wahami Ne A Kan Haɗuwar Malamai, "Faɗar Allah Maɗaukaki A Cikin Haƙƙinsu:**

﴿وَإِنْ أَحَدٌ مِّنَ ٱلْمُشْرِكِينَ ٱسْتَجَارَكَ فَأَجِرْهُ حَتَّىٰ يَسْمَعَ كَلَٰمَ ٱللَّهِ ثُمَّ أَبْلِغْهُ مَأْمَنَهُۥ ۚ ذَٰلِكَ

بِأَنَّهُمْ قَوْمٌ لَّا يَعْلَمُونَ ﴿٦﴾﴾ التوبة: ٦

***"Idan wani daga cikin mushrikai ya nemi mafaka da kai, to, ka ba shi mafaka har sai ya saurari maganar Allah sannan sai ka kai shi wajen da yake da aminci, wannan saboda su jama'a ne da ba su da ilimi" Attaubah: 6***

Da kuma faɗar (Allah) Maɗaukaki a cikin haƙƙinsu:

﴿وَلَٰكِن ظَنَنتُمْ أَنَّ ٱللَّهَ لَا يَعْلَمُ كَثِيرًا مِّمَّا تَعْمَلُونَ ﴿٢٢﴾﴾ فصلت: ٢٢

*"Sai dai kun yi zaton cewa Allah bai san mafi yawa daga abin da kuka kasance kuna aikatawa ba" Fussilat: 22*

Da kuma faɗar Maɗaukaki a cikin haƙƙinsu:

﴿ فَسْـَٔلُوٓاْ أَهْلَ ٱلذِّكْرِ إِن كُنتُمْ لَا تَعْلَمُونَ ﴾ النحل: ٤٣

*"Ku tambayi ma'abuta ilimi idan kun kasance ba ku sani ba" An-Nahlu: 43.*

Da kuma faɗar Maɗaukaki a cikin haƙƙinsu:

﴿ بَلِ ٱدَّٰرَكَ عِلْمُهُمْ فِى ٱلْءَاخِرَةِ ۚ بَلْ هُمْ فِى شَكٍّ مِّنْهَا ۖ بَلْ هُم مِّنْهَا عَمُونَ ﴾ النمل: ٦٦

*"A'a sai dai iliminsu game da lahira ya kammala, A'a sai dai su suna cikin shakka game da ita. A'a sai dai su makafi ne game da ita." Annamlu: 66*

Shin ko kana ganin cewa waɗannan siffofi, siffofi ne na masana?, A'a wallahi lalle su, sifofi, ne na Jahilai. Ai da suna nufi da waɗancan kafirai cewa su ne ahlul kitabi, to, da sun yi gaskiya domin su, masana, ne kafin zuwan (Manzo) Al-Mustapha tsirar Allah da amincinSa su tabbata a gare shi, ba ma'abuta gumaka ba. Saboda haka mai Ikitirahi – Taƙiyyuddini ya kafa hujja da Malam Izuddini da Malam Amidi saboda ingancin imanin muƙallidi ba tare da saɓonsa ba domin mafi yawan waɗanda suka shiga Musulunci a zamanin mai tsirar Allah da aminci ba su kasance masana ba da mas'aloli na asuli sai Annabi tsirar Allah da aminci su tabbata a gare sa ya yi hukunci da musuluncinsu.

Al-sheikh Assunusi ya yo hikayarsa a cikin Al-umdah sharhin Al-kubra.

**9. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu: Lokacin Da Suka Ji Cewa "Lallai Sahabbai Dukansu Masana Ne Sai Suka Kaifafa Magana A Cikin Aƙidu Suka Harhaɗa Nau'o'in Harhaɗa Dalilai.**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai domin nazari wanda ake jinginawa a gare su sanya lura (kula) wanda ta hanyarta ne suka san gaskiya har suka kasance a kan basira ta ilimi a cikin addini.

Wannan nazari wanda aka jingina a gare su shi ne wanda ke wajaba a kan dukan mukallafai a wurin wanda ke faɗar wajabcin yin bincike domin shi

an aza shi ne a kan hanyar jahilan mutane ba bincike ba ne wanda aka aza ta hanyar malaman tauhidi, kamar yadda bayaninsa zai zo in Allah ya so. Sai dai 'kakarfin' bincikensu shi ne mafi ɗaukaka, kuma mafi zurfi a kan binciken malaman tauhidi, saboda abin da ya cuɗanya da su na albarkar Al-Musɗapha tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi. Ba shakka lallai binciken da aka aza ta hanyar jahilan mutane ba ya nesa ga duk wanda labarin halayyar Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya zo masa.

Shehin malami ya faɗa cewa: "Babu saɓani a cikin lamarin waɗanda suka rayu a cikin gidajen Musulunci na daga birane da alƙaryu da sahara, kuma labari ya zo musu da yawa na halayen Annabi tsira da amincin su tabbata a gare shi da abin da ya zo da shi na mu'ujizoji, kuma (babu saɓani) ga waɗanda ke yin tunani game da halittar sammai da ƙasa da saɓanin dare da wuni, a cikin kasancewarsu dukansu daga masu bincike da kafa dalilai ne."

Ya zo a cikin Durarul Ƙala'idi:

وذاك فـــيمن نشـــأ خلـــوا باديـــة          والغيـــر عـــن ريقـــة التقليـــد محلـــول

Wannan ga wanda ya tashi keɓance a ƙauye, waninsa shi ne wanda ya warware daga ɗaurin nan na taƙaleedi.

**10. Yana Daga Cikin Wannan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa; "Duk Wanda Bai Nemi Sanin Littattafan Ilimin Tauhidi Ba Za A Yi Hukunci Da Cewa Shi, Musulmi, Ne Idan Ya Bayyanar Da Musulunci Amma Ba A Hukunci Da Cewa Shi, Mumini, Ne Saboda Shi Bai Nemi Ilimin Sa Ba, Wannan Shi Ma Ɓarna Ce Kuma Wahami Ne A Kan Haɗuwar Malamai."**

Abul Hasan Al-Maliki ya faɗa a cikin Al-kifayah sharhin Arrisalah: Ba ya inganta a cikin shari'a a yi hukunci ga wani cewa shi, mumini, ne ba Musulmi ba ne, ko cewa Musulmi ne ba mumini ba ne.

**11. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Lallai Su, Jahilai Daga Cikin Jahilan Musulmi A Cikin Waɗannan Zamunna Na Karshe, Ana Yi Musu Hukunci Da Zamansu Kafirai Ko Da Kafircinsu Bai Bayyana Ba Ta Hanyar Zance Ko Aiki, Saɓanin Zamunnan Da Suka Gabata Saboda Rashin Daidaitarsu A Babin Neman Ilimi, Kuma Suna Kafa Dalilai Da Maganar Ɗan Umar A Cikin Fasali Na Farko: Sa'annan Lallai Su, Mutanen Zamanin Da Ya Gabata, Duk Wanda Kafircinsa Bai Bayyana Ba Daga Cikinsu, To, Aurensa Da Yankansa Sun Halatta.**

Ba a ƙiyasin zamaninmu da zamanin da ke gabaninsa saboda yawan kafirci a cikinsa da ƙaruwarsa. Saboda haka na dakata ga yin (hukunci) game da wanda halayyarsa ta ɓoyu, ko yana daga cikin wanda ake gabatar da hukunci galibi a kansa ko kuma yana daga cikin nadiri (abin da bai cika faruwa ba)?"

Idan an lura cewa yana daga cikin galibi, to, an haramta auren sa da yankansa, amma idan an lura da cewa nadiri ne (bai cika faruwa ba), to, ba a haramta ba…….. mene ne mafi karamcinsa ?, Mun kasance muna sayen nama daga waɗanda muka karantar da aƙida (Tauhidi).

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne, a kan haɗuwar malamai, domin maganar Ibnu Umar ta keɓanta ne ga hukuncin mu'amala da wanda ba a san halayyarsa ba a cikin waɗannan zamunna na ƙarshen, amma tare da haka maganarsa ba abin karɓa ce saboda abin da aka sani ne a cikin wannan mas'alah cewa, duk wanda ke bayyanar da Musulunci mu'amalarmu da shi ta halatta matuƙar kafircinsa bai bayyana ba ta hanyar magana ko aiki, halinsa ya bayyana ko bai bayyana ba, amma a cikin zamunnan da suka gabata dalilin gabatar galibi bisa nadiri shi ne saboda yawan neman ilimi a cikinta, amma a cikin waɗannan zamunna na ƙarshe wanda neman ilimi ya ƙaranta a cikinsu saboda kasancewar waɗannan mas'aloli suna daga cikin mas'aloli waɗanda ake gabatar da nadiri a kan galibi domin rahama ga al'umma, kamar yadda wannan ya tabbata a cikin ilimin ƙa'idoji (na Usuluddini).

Sai dai ibnu Umar Allah ya yarda da shi a cikin ra'ayinsa game da waɗannan zamunna a kan mu'amalar wanda ba a san halinsa ba daga Jahillan Musulmai saboda ƙarancin neman ilimi a cikinsa, domin shi (Ibnu Umar) Mujtahidi ne shi, mujtahidi kuwa, ba ya bin (Ra'ayin) waninsa.

Haka kuma yana kamata a ɗauki cewa dakatawarsa daga ma'amalar wanda ke bayyanar da Musulunci amma halinsa bai bayyana gare shi ba (ya yi hakan) ta hanyar tsanantawa, kuma bai kamata a ɗauke shi ba ta hanyar

kafirtawa, kamar a kudurta cewa shi, kafiri, ne, ko ya ce masa kai kafiri ne, ko ya kira shi da cewa: “Ya kafiri, alhali bai ga wani abu daga gare shi ba daga abin da yake warware Musulunci ba, kuma bai ji ba daga gare shi.” muna neman tsari da Allah, kuma wannan ya koru daga gare shi, domin wannan yana daga cikin abin da yake a ɓoye babu wanda ya san shi sai Allah Mai girma da buwaya.

Da mun ƙaddarta cewa wannan malami ya gina wannan dakatarwa ta hanyar yanke hukunci ba ta hanyar tsanantawa ba da ya kasance mai saɓawa ga abin da ijma’in ahlis sunna yake a kansa, muna neman Allah tsari daga a yi zato da wannan.

**12- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: “Kafa Hujjar Da Sheikh Assunusi Ya Yi A Kan Kafirta Mukalladi A Cikin Littafin Al-Umdah Sharhin Al-Kubra An Gina Shi Ne A Kan Babin Haƙiƙa Da Yanke Hukunci Ba A Kan Babin Tsanantawa Ba.”**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne, a kan haɗuwar malamai, domin wannan mas’ala babu mashigar ra’ayi a cikinta, kuma wani nassi mai yankakken hukuncin shari’a bai zo ba game da ita, kuma da a ce maganarsa a cikin wannan ita ce gaskiya wadda aka yanke hukunci da ita, to, da ya kasance duk wanda ya saɓa a cikin wannan ya fita daga Zagayen (sahun) ahlissunna, wannan kuwa ɓarna ce yanke, a’a sai dai kafa hujjarsa an gina shi ne a kan tsanantawa.

Malam Manjuri Allah ya yi masa rahama ya faɗa a cikin sharhin maganar Sheikh Allah ya yi masa rahama a cikin littafin Al-umdah, cewarsa: “Abin da jamhurin malamai suke a kansa da masu tahƙi cikin ahlissunna yana nufin Jamhurin Malaman Tauhidi kamar yadda ya bayyana a cikin sharhin Al-wusɗa, domin idan ba haka ba ai su, jamhurin malaman Fiƙihu da malaman hadisi, sun tafi a kan cewa shi, muƙallidi, mumini ne, kuma yana cikin masu samun tsira. Malam Al-Iraƙee ya faɗi wannan a cikin sharhin Jam'ul Jawa'mi-u cewa: “Abin da tsarin maganar mai littafi ke nunawa da manufarsa a nan shi ne cewa abin da yake nufi su ne Jamhurin malaman sunna a gaba ɗaya, wannan tsanantawa ne a kan muƙallidi daga Sheikh Allah ya yi masa rahama Ya kuma amfane mu da shi.”

**An ce:** Saboda shi ne malaman zamaninsa suka yi jayayya da shi daga cikin malaman garin Tilimisana kamar: Malam Ibnu Zikri suka yi masa musu a kan kafirta muƙallidi da kuma jingina wannan zuwa ga Jamhurin malamai.

Ana cewa: “Lallai littafinsa na Al-kubra shi ne farkon abin da ya wallafa daga cikin aƙidojinsa, kuma haƙiƙa ya dawo daga wannan tsanantawa a cikin sharhin Assugra da kuma Al-muƙaddimatu.” A nan maganar ta tsaya.

Sayyid Abu Abdullahi Muhammad binu Mukhtar binu Al-a'amash Al-alawiy ya faɗa a cikin sharhin littafin Idha’atu Addujunnah: cewa: “Malam ya tsananta a cikin sharhin Al-kubra saɓanin aƙidojinsa amma haƙiƙa shi ya dawo zuwa ga sassauci.”

**Na ce:** “Abin da ya kai su zuwa ga wahamin cewa kafa hujjar malam a cikin wannan mas’ala, an gina ta ne a kan yankakken hukunci shi ne: Saboda rashin sanin su ga bambanci tsakanin abin da ke nuna yankakken hukunci kamar nassi da wanda bai nunawar haka, kamar abin da yake zahiri da hadissan da suka keɓanta da ɗaiɗaikun masu riwaya, ba su san cewa shi, malam, ya kafa hujja ne da (nassi). Zahiri da kuma hadisan ɗaiɗaiku a cikin wannan mas’ala, kuma duk wannan bai nuna yanke hukunci, abin da kawai ke nuna yankakken hukunci shi ne nassi mutawaturi, kuma shi bai zo a cikin wannan ba, kuma bayani ya gabata cewa shi ra’ayi ba shi da wani fage a cikin wannan mas’ala.

Idan ka fahimci wannan magana za ka san cewa lallai kafa hujjarsa ya ginu ne a kan tsanani.

**13. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: ‘Wanda Ke Kafirta Ma’abuta Bidi’a Waɗanda Suka Musanta Abin Da Aka San Cewa Manzo (Tsira Da Amincin Allah Su Tabbata A Gare Shi) Ya Zo Da Shi A Kan Nazari Amma Ba Su Musanta Abin Da Aka San Cewa Manzo(S.A.W) Ya Zo Da Shi A Kan Lalura, Cewa Yana Da Dalili Ne Yankakke A Cikin Wannan.”**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai domin wanda ke kafirta su daga cikin ahlus'sunna yana kafirta su ne da abin da ya lizimta su kuma ba su lizimta ba da shi kuma babu kafirta da Lizimtawa kawai.

Alƙali Iyal ya faɗa a cikin As’shifa’u cewa; “Abin da yake daidai shi ne barin kafirta su da kawar da kai daga wajibta hukunci a kansu da cewa sun yi hasara.”

Sheikh Assunusi ya faɗa a cikin Sharhin Al-ƙaseedatul Jaza'iriyya, cewa: "Abin da yake mafi bayyana shi ne dakatawa)" yana nufin dakatarwa daga kafirta su. Domin shi ne mafi dacewa sai idan nassi yankakke ko ijma'i a kan kafirtar wani, sai a bi shi a yayin haka. A nan ya ƙare.

Alƙali Iyal kuma ya faɗa cewa: "Malam Sahnun ya ce: "Babu sakewa ga wanda ya yi salla a bayansu, ya ce: kuma wannan shi ne zancen dukan Almajiran Malik."

Haƙiƙa, Mai tsirar Allah da aminci ya ce:

(فإذا قالوها – يعني الشهادة – عصموا مني دماءهم وأموالهم إلا بحقها وحسابهم على الله)

***"Idan suka faɗe ta – yana nufin Kalmar shahada – sun kare Jinannensu da dukiyoyinsu daga gare ni sai da haƙƙinta kuma hisabinsu yana wurin Allah"***

Ita, Ismah (kariya), an yanke hukunci da ita tare da kalmar shahada kuma ba a ɗaukewa kuma ba a halatta ba a yi saɓaninta sai da hukunci yankakke, kuma babu mai yanke hukunci sai daga shari'a kuma ba a yin ƙiyasi a kansa, lafuzzan hadisan da suka zo a cikin wannan babi suna a kan ta'wili. Malam Assunusi ya yi hikayarsa a cikin Sharhin Al-Mukaddimatu, kuma ya faɗa a cikinsa a wani mahalli ya ce: Fa'idar sanin abin da yake lalura ne da wanda ake buƙatar yin nazari a cikin hukuncinsa na sharia, shi ne: sanin abin da ke wajibtar da musunsa ga kafirci da abin da ba ya wajibtar da shi.

Idan mai musantawa ya yi musun abin da aka sani cewa lalura ne, to, shi, kafiri, ne, saɓanin wanda ya yi musun abin da yake a ɓoye wanda babu wanda ya san shi sai 'yan kaɗan (daga cikin malamai).

**14. Akwai Daga Cikin Wancan Wahami Kudurtawar Sashensu Cewa: "Binciken Da Mukallifi Zai Fita Daga Taƙalidi Ta Hanyarsa Babu Makawa Ya Kasance Ta Hanyar Malami."**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai.

Sheikh Assunusi ya faɗa a cikin littafin Al-umdah Sharhin Al-kubra bayan ya ambaci lamarin bincike: Sannan wannan bincike ya isa ga sanin

Allah Maɗaukakin Sarki, ko da ya kasance babu malami saɓanin ra'ayin mazhabar Isma'iliyya (daga Shi-a).

**15. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Yin Bincike Ta Hanyar Malaman Tauhidi Yana Wajaba A Kan Kowane Mukallafi, Wannan Shi Ma Ɓarna Ce Kuma Wahami Ne A Kan Haɗuwar Malamai."**

Sheikh Assunusi ya faɗa a cikin littafin Nur Assa'adah sharhin littafinsa na Assugra: "Ba a sharɗanta ba sanin bincike ta hanyar malaman tauhidi ba cewa a tace dalilai da tsara su da kuma kore shubuha wadda ta zo a kanta haka kuma rashin samun iko a kan bayani game da abin da ya faru a cikin zuciya."

Sheikh Assunusi ya sake faɗa a cikin sharhin Al-wusɗa: Ba a sharɗanta ba samun iko a kan jerantata yana nufin dalili ta fuskar da malamai suke tsara shi, haka kore shubuha wadda ta zo masa, haka (ba a sharɗanta) samun iko a kan yin bayani game da shi ba.

Sai kuma ya ce: "Domin wannan aikin malamai ne masu zurfin ilimi, kuma shi, farillar kifaya, ne duk wanda ya tsayu da shi daga cikin malamai a cikin kowane gari ya isar wa waninsa a cikin wannan garin."

Malam Halilu (Ahmad) ya ce: Malam ɗan Rushdi da waninsu sun nassanta a kan cewa: "Samun fahimta ba ya wajaba ta hanyar malaman tauhidi kuma duk wanda ya ƙudurta ta shi, jahili, ne."

**16 Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu A Kan Ittifaƙin Malaman Sunna A Kan Halaccin Ilimin Tauhidi.**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai.

Malam Abdulrahman Assuyuɗi ya faɗa a cikin littafin Addira'ya sharhin Anniƙayah a cikin bayanin ma'anarsa cewa: "Shi ne abin da ake jingina dalilai na hankali a cikinsa, kuma ana cirato maganganun malaman falsafa a cikinsa, wannan kuwa haramun ne a kan haɗuwar malamai magabata."

Malam Ahmad Zaruƙ ya faɗa a cikin Umdatul Mureed Assa'diƙ cewa: "Malamai sun yi saɓani cewa: Ko ba a gusar da ɓarna sai da gaskiya ko kuwa ana gusarwa da duk abin da ya sauƙaƙa a gusar ta hanyarsa?"

Wanda ya haramta ilimin tauhidi (falsafa) ya faɗi ra'ayin farko, wanda ya halatta shi, ya faɗi ra'ayi na biyu.

**Na ce:** Abin da ya kai su ga wannan wahami shi ne: rashin sanin bambanci tsakanin ilimin usuliddini da ilimul kalami. Haƙiƙa, bayanin ma'anar ilmul kalami ya gabata a cikin maganar Malam Abdulrahman Assuyudi ɗazu.

Amma ma'anar Usuluddini shi, ilimi, ne da ake bincike a cikinsa game da faruwar halitta da abin da ke wajaba ta gefen Ubangiji da abin da yake koruwa daga gare Shi da abin da ke halatta, a jingina maSa, da abin da ke wajaba ta gefen manzanni da abin da yake koruwa daga gare su da kuma abin da ke halatta a gare su. Haka kuma lamurra waɗanda ake ji (san-lyya'tu) ranar samuwar mala'iku da littattafan da aka saukar daga sama, da mutuwa ta hanyar cikar ajali, da lamurran Barzahu, da kuma Alƙiyama, duka waɗannan a kan tsari na Musulunci. Wannan shi ne ma'anar usuluddini, kuma shi abin yabawa ne. Kai shi ne mafifici daga kowane ilimi domin darajar kowane Ilimi tana daga gwargwadon abin da aka sani.

Amma shi, "Ilmul kalami," (tauhidi) abin yabawa ne ta hanyar lura da amfaninsa, shi ne tabbatar da tauhidi da kiyaye shi da bayyanar da abubuwa na gaskiya da kuma saninsu kamar yadda suke, kuma abin zargi ne ta hanyar lura da cutarwarsa shi ne tayar da abubuwa masu rikici da motsar da aƙidoji, saboda dalilin abin da muka ambata na kasancewar Ilmul kalami mai cutarwa mai kuma amfani. To, ya zama kuskure a rinƙa sakin magana da sukarsa ta kowane hali ba tare da rarrabewa ba.

Amma malaman Ilmul kalami kamar Malam Abul Hasan Al-ash'ari da jama'arsa da duk wanda ya bi su daga cikin Ahlissunnah waɗanda ake yaba musu ne kawai, amma waɗanda ake zargi daga malaman Ilmul kalami su ne Mu'utazilawa. Saboda haka Sheikh Assunusi ya ce a cikin sharhin Al-wusɗa: "Abin da sashen waɗanda Allah Maɗaukaki ya makantar da ganinsu suke dogara da shi a cikin da'awarsu ta haramcin yin bincike game da ilimin tauhidi na cewa Ashshafi'i Allah Maɗaukaki Shi yarda da shi, cewa game da ilimin tauhidi yana ganin a bugi masu shi da kankamen dabino, muna faɗa da irin hukuncinsa amma ga waɗanda suka zama ana kiransu da ma'abuta ilimin tauhidi a zamaninsa su ne: Amru bin Ubaid daga cikin Mu'utazilawa a zamaninsa da Hafs Al-fard daga cikin Kadariyya da ire-irensu."

Sai ya ce: "Wannan yin laƙabi da cewa ma'abuta Ilimin tauhidi a wancan zamani ya keɓanta ne da waɗancan." A nan ya tsaya.

Idan ka fahimci wannan dukansa za ka san cewa shi, ilimin tauhidi, abin yabawa ne ga kansa idan aka lura da wata fuska, kuma abin zargi ne ta lura da wata fuska, amma ma'abutansa wanda ya kasance daga cikin ahlissunna, to, abin yabawa ne, wanda ya zama cikin Mu'utazilawa daga cikin, to, wannan abin suka ne.

Amma zancen Malam Ahmad da ya ce: "Malaman Ilmul kalami, Zindiƙai ne ya keɓanta da waɗanda suke koyon daɗin magana don su karkato zukatan sarakuna da sauran mutane da wannan, kamar yadda sheikh Assunusi ya bayyana shi a cikin sharhin Kasida Aljaza-iriyya."

**17. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Sanin Salon Maganar Malaman Tauhidi (Almutakallimuna) Da Waɗanda Ake Kira(Assab'atu Almaɗa'libu) Da Kaifafa Magana A Kan Aƙidoji Da Jeranta Su Tare Da Laƙubbansu Da Kuma Sanin Yadda Ake Shigar Da Su A Karƙashin Kalma Maɗaukakiya (Kalmar Shahada) Da Rarrabe Bayanin Dangantakar Siffofi Da Nau'ukan Harhaɗuwar Dalilai, Cewa Duk Wannan Wajibi Ne A Kan Mukallafi(Baligi).**

Wannan shi ma ɓarna ne kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai."

Sheikh Assunusi ya faɗa a cikin Al-umdah sharhin Al-kubra cewa: "Wane mashiga ne ke ga lafuzzan da aka yi isɗilahi a kansu a cikin wani abu na dalilan aƙidoji har ya lizimta cewa jahiltar wani abu daga cikinta jahilta ne ga wani abu daga cikin dalilai."

Kuma ya faɗa a cikin Al-umdah a wani mahalli a cikin raddinsa a kan (Malam) Alfakhru lokacin da maganarsa ta zama wahami cewa dalilan malaman tauhidi, an sharɗanta su a babin ilimi. Wannan maganar tasa, an sharɗanta ta ne a cikin babin Ma'arifah (Ilimi) wannan magana tana nufin shi-Malam Alfakhru- Magana ce ta wanda ya yi wahami cewa ana sanin Aƙidoji ne ta hanyar cika baki wajen magana da kuma isɗila'hin da malaman zamanin ƙarshe suka ƙaga a cikin nau'ukan haɗa dalilai wadda su magabata ba su lisafta da ita ba. Manufa shi ne sanin gaskiya da abin da ke lizimtarta yanke, duk yadda abin ya tabbata da lafazi ko ba da lafazi ba da harhaɗa dalilai keɓance ko da waninsa, to, manufa dai ta tabbata, kuma babu buƙata zuwa ga wani ƙari.

Sai ya ce: "Bayan ya faɗi wata magana: Sai Malaman ƙarshe suka haddasa abin da suka haddasa na isɗila'hi domin wahala ta sauƙaƙa a gare su

a zamanin neman ilimi da koyarwa, ba a kan cewa sanin gaskiya ya dogara a kanta ba."

**18. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Wajabcin Yin Bincike Haƙiƙa Ya Zo Ne Nassance A Cikin Alƙur'ani Da Sunna.**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai, domin da a ce wannan ya zo nassance a cikin Alƙur'ani ko sunna da sashen malaman sunna kamar Gazali da ɗan Rushdi da ɗan Abi jamrah ba su tafi a kan cewa yin bincike ba wajibi ba ne, domin duk wanda ya ci karo da Alƙur'ani ko sunnar da ta tabbata, to, ya zama kafiri da haɗuwar malamai."

Sheikh Assunusi ya faɗa a cikin sharhin Alƙasidah Aljazairiyya cewa:

"Magana ta farko daga cikin maganganu guda huɗu tana nufin waɗanda aka ambata game da mukallidi haƙiƙa shi, taƙalidi yankakke, wanda ya dace a cikin aƙidun imani mai Isa ne, ko da ya tsiraita daga dalili, kuma haƙiƙa ɗan Rushdi ya rinjayar da wannan Magana." Ya kuma ƙara da cewa: "Shi, bincike, mustahabbi ne ba wajibi ba ne, kuma Hujjatul Islami Al-gazali da Waliyyi masanin Allah ta'ala ɗan Abi Jamrah sun karkata zuwa ga wannan ra'ayi."

**Na ce:** Saboda dalilin cewa babu nassi a cikin wannan shi ya sa Sheikh Assunusi ya yi bayani a cikin littafin Nur Assa'adah sharhinsa na Assugra da cewarsa: "Abin da yake gaskiya wadda Alƙur'ani da sunna suke nunawa shi ne wajibcin ingantaccen bincike tare da saɓani a kan Zamansa Sharaɗi a cikin ingancin imani, kuma bai faɗa ba, cewa: Gaskiya ita ce abin da Alƙur'ani da sunna suka zo da nassi a kansa," saboda haka Al-makarri ya faɗa a cikin littafin idha'atu Addujnah:

Shi (bincike) a kan wajibcinsa ya nuna kuma bai ce sun nassata ba.

**19. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Neman Ilimin Aƙidoji Ba Tare Da Sanin Lugar Larabci Ba Ba Ya Isar Ba'ajame (Wanda Ba Balarabe Ba).**

Wannan ɓarna ce kuma wahami ne a haɗuwar malamai, domin manufa shi ne fahimtar aƙidu a cikin zuciya, kuma wannan yana tabbata ta hanyar sauran harussa, da a ce suna da lura ko da mafi karamci da sun san cewa Ba'ajamen da ya haɗa musu aƙidu da lugar Ajamanci bai haɗa musu ita ba sai bayan fahimtarta tun farko da lugar Larabci gabanin haɗawa.

Muhammadu ɗan Umar ɗan Abdul'azizi ya faɗa a cikin littafin Alfaslil Auwali cewa: "Ka sani cewa duk wanda ke koyar da mutane yana buƙata zuwa ga kaifin basira domin gaskiya ta bayyana a gare su da abin da suke fahimtarsa ko da ta hanyar Ajamanci, domin abin da ake nema shi ne ɗan-ɗanon aƙidoji a cikin zuciya."

**20. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu A Cikin Ma'anar Maganar Muhammadu Salihu Ɗan Abdulrahman Ɗan Sulaimu Al-Aujali A Cikin Littafin Dalilil Ka'idi A Cikin Bayanin Alaƙar Gyara Da Samun Iko:**

Tun azal ta rataya da abin da yake yiwuwa irin ratayar gyara da zai bayyana. Haƙiƙa, aikata abin da ke yiwuwa tun azal halas ne domin samun iko ya dace da samar da shi, da a ce Maɗaukakin Sarki ya nufi bayyanar da shi a can sai dai wannan bai faru ba. Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai domin aikin korarre ne tun azal.

Muhammadu Aɗɗahir ɗan Sheikh Ibrahim ya faɗa a cikin sharhin Manzumatul kubra cewa: (Shi, Aikin, korarre ne tun azal). "Babu abin da ya kai su ga wancan wahami sai rashin sanin bambanci tsakanin samun iko na Zati da samun iko na aiwatarwa, kuma tun azal babu samun ikon aiwatar da abin da ke yiwuwa, a'a babu wani abu a can sai samun iko na Zati."

**21. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Iyakar Inda Jiki Yake Tarewa Shi Ne Ainihin Wurin Da Ba Komi.**

"Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a haɗuwar malamai, domin da ya kasance farfajiyar wuri shi ne inda jiki ya mamaye da wannan ya kai ga Ɗauri da Tasalsuli kuma wannan korarru ne domin shi wannan wurin shi ma yana neman wurin da zai shiga cikinsa ke nan don ya zama wata mamaya a gare shi, sai wannan ya kai ga abin da muka ambata, sai dai shi iyakar wurin da jiki ya mamaye ƙimarsa ne daga wurin ba haƙiƙanin wurin ba ne. Saboda haka Sheikh Assunusi ya ambata a cikin Ummul Baraeen cewa: "A cikin ƙaddarta kamannun Ubangijinmu Mai girma da buwaya shi ne ya zama jiki ai shi ne ZatinSa Maɗaukaki ya riƙi wani gwargwado na sashen wuri. Ka dubi faɗarSa cewa: (wani ƙima na wuri) "Don kasancewar shi jiki bai karɓar sashen wuri, sai dai yana karɓar gwargwadon kima daga gare shi, shi kuma abin da aka kimanta ba samammen abu ne ba sai dai jinginawa ne, kuma da yawa daga cikin malaman sunna sun faɗakar a kan wannan."

**22. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Abin Da Ake Nufi Da Al-Kha'riju Shi Ne Abin Da Ke Bayyana A Ganin Ido, "A Cikin Fassararsu Ga Maganar Malamai Cewa: "Su, Siffofi Na Ma'ani, Akwai Su A Sarari,"**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai, domin abin da ake nufi da zamansu samammu a sarari, shi ne ƙaruwar samun su a kan samuwar Zati, kamar yadda malaman sunna suka bayyana shi. Allah Maɗaukaki Shi yarda da su.

**23. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Haƙiƙa, Dalili Ya Zo A Kan Ganin Waɗancan Siffofi Saboda Jin Su Ga Abin Da Ake Faɗa A Kan Kaddartawa Cewa: "Da Dai An Kware Mana Shamaki Da Mun Gan Ta.**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai."

Sheikh Assunusi ya faɗa a cikin sharhin Al-wusɗa (faɗakarwa): "Masu faɗar ganin Allah Maɗaukaki sun yi saɓani a cikin cewa ko ganin siffofinSa Maɗaukaki yana inganta?"

Jamhurin malamai suka ce: "Na'am saboda samuwa tana hukunta ingancin ganin duk abin da yake samamme sai dai yadda lamarin yake babu dalili a kan aukuwa."

**24. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Dukan Lafazi Wanda Ma'anarsa Take Koruwa Ga Allah Yana Haramta A Faɗe Sa Gare Shi Ba Tare Da Rarrabewa Ba."**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai. A'a babu makawa a kan rarrabewa sai a ce: Sharia tana da hukunci in ya faɗa sai mu faɗa duk abin da shari'a ta faɗa na lafuzza ga Allah Maɗaukaki sai mu faɗe shi a gare Shi abin da kuma ba ta faɗa ba, to, ba za mu faɗa ba, kamar yadda malaman sunna suka bayyana, Allah Shi yarda da su.

**25. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Ga Fassarorin Malamai A Cikin Ayoyi Da Hadisai Masu Rikitarwa Sai Su Ɗauke Su A Matsayin Hukunci Da Aka Yanke:**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai, babu abin da ya kai su zuwa ga wancan wahami face rashin sanin bambanci tsakanin tafsiri da ta'wili.

Sheikh Abdulrahman Assuyuɗi ya faɗa a cikin Itma'mu Addirayah Sharhin Anniƙayah cewa: "Bambancin shi ne: Shi, Tafsiri, shi ne: Shaidawa ga Allah da yanke hukunci da cewa haka ake nufi da wannan lafazi."

Sai kuma ya ce: "Amma shi, ta'wili, shi ne: Rinjayar da ɗayan fassarar da abin ke iya ɗauka ba tare da yanke hukuncin ba da kafa shaida ga Allah, ka nemi gafara."

**Na ce:** "Duk abin da yake da rikitarwa a cikin Alƙur'ani da hadisi ba ya halatta a yi ijtihadi a wajen fassara shi, kuma babu wata hanya zuwa ga yin haka sai da tsayawa da nassi daga Alƙur'ani ko hadisi ko Ijma'in Al-Umma, kamar yadda malaman sunna suka bayyana, Allah Maɗaukaki ya yarda da su."

**26. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Mayarwar Sashensu: Ma'anar Musulmi Zuwa Ga Ma'anar Munafuki Saboda Haƙiƙanin Musulmi A Wurinsu Shi Ne Wanda Ke Bayyanar Da Musulunci Alhali Shi Ba Mai Imani Ba Ne A Cikin Zuciyarsa Kuma Wannan Shi Ne Haƙiƙanin Munafunci.**

Wannan shi ma ɓarna ne kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai. Haƙiƙanin Musulmi shi ne wanda ke bayyanar da Musulunci yana mai imani a cikin zuciyarsa domin imani sharaɗi ne a cikin haƙiƙanin Musulunci.

Sheikh Abdulrahman Assuyuɗi ya faɗa a cikin Al-kaukab Assaɗi-u cewa: "Aikin gaɓoɓi shi ne Musulunci * Sharaɗinsa da kammalarsa shi ne imani."

**27. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Ana Gane Mumini A Kan Ayyanawa Ba Tare Da Shaidar Mai Shari'a Ba Tsira Da Aminci Su Tabbata A Gare Shi."**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai Shi, imani, sirri ne daga cikin asirran Allah Maɗaukaki ba mu iya tsinkaya gare shi sai da shaidar mai shari'a, aminci ya tabbata a gare shi. Saboda haka ne mai tsira da aminci ya tsawatar da Sa'ad Allah shi yarda da shi a kan yanke hukuncinsa a cikin haƙƙin mutumin da Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya dakatar daga ba shi kyauta sai Sa'ad ya ce masa: "Me ya same ka game da sha'anin wane?" "Na rantse da Allah, ni ina ganinsa cewa Mumini ne da yin wasali sama ga Alhamzah ai ina saninsa a haka, sai Annabi tsirar Allah da aminci su tabbata a gare shi ya ce masa: "Ko dai Musulmi?" Da yi wa wawu ɗaurin wasali a kan kautarwa daga maganarsa

zuwa ga hukunci da abin da ke bayyane, Kamar dai ya ce: “A’a kana ganinsa dai Musulmi, me ya dame ka na yanke hukunci da imaninsa, saboda shi yana daga abin da ke ɓoye babu mai saninsa sai Allah Mai ɗaukaka da buwaya,” shi, wannan hadisi, Bukhari da Muslim da waninsu ne suka fitar da shi.

Sheikh Assunusi ya faɗa a cikin Al-umdah sharhin Alkubra bayan ya kawo wannan magana cewa: “Wannan dukansa ya rataya ne da haƙƙi, wani wanda ke bayyanar da imani amma shi, mutum, ga kansa shi ne mafi sani da halinsa in ya kasance mai hankali.”

## 28. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: “Da Masani Da Muƙallidi Da Wanda Bai Kai Ga Matsayin Taƙalidi Ba Sanannu Ne A Kan Ayyanawa.”

Wannan shi ma ɓarna ne kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai. Domin wannan ƙudurtawarsu, an gina ta ne a kan fassararsu ga ma’anar masani, da mukallidi da wanda bai kai matsayin taƙalidi ba, domin su suna riyanta cewa: “Shi, masani, shi ne wanda ke yawaita magana a kan aƙidoji tare da dalilanta, muƙalladi shi ne wanda ke yawaita magana a kan aƙidoji kawai amma ya kasa yawaita magana da dalilanta, shi kuwa wanda bai kai ga matsayin taƙalidi ba shi ne wanda ba shi iya yawaita magana a kan aƙidoji balle shi yawaita magana da dalilanta.” Wannan fassara ɓarna ce a kan haɗuwar malamai. Kuma bisa ga wannan fassara ake gane masani da muƙallidi da wanda bai kai matsayin taƙalidi ba a kan ayyanawa, wannan ɓarna ne domin masani shi ne wanda ke da abubuwa guda uku a cikin zuciyarsa:

**Na farko:** Ya kasance ya fahimci abin da aka sharɗanta fahimtarsa daga kalma Maɗaukakiya (kalmar shahada) a cikin babin imani.

**Na biyu:** Ya kasance akwai gaskata wannan a cikin zuciyarsa.

**Na uku:** Ya kasance ya yi amfani da tunani a cikin wannan har bincike ya tabbata gare shi irin wanda natsuwar zuciya ke tabbata da shi, domin ba a sharɗanta sanin bincike ba ta hanyar malaman tauhidi (Almutakallimuna) ba.

Muƙallidi shi ne wanda a cikin zuciyarsa akwai abubuwa guda biyu:

**Na ɗaya:** Ya kasance ya fahimci duk abin da aka sharɗanta fahimtarsa daga kalma maɗaukakiya a cikin babin imani.

**Na biyu:** Ya kasance akwai gaskata wannan a cikin zuciyarsa, kuma babu abin da ya yi saura gare shi a cikin wannan sai aiki da tunani wanda bincike yake tabbata da shi, wanda da shi ne natsuwar zuciya ke samuwa.

Shi kuma wanda bai kai ga matsayin taƙalidi ba shi ne wanda babu wani abu daga cikin waɗannan lamurra guda uku a cikin zuciyarsa. Haka nan wanda ya fahimci abin da aka sharɗanta fahimtarsa daga kalma Maɗaukakiya, a cikin babin imani sai dai shi babu gaskata wannan a cikin zuciyarsa. Idan ka fahimci wannan dukansa za ka san cewa shi masani da muƙallidi da wanda bai kai matsayin taƙalidi ba ba a saninsa a kan ayyanawa, domin haƙiƙaninsu yana ɓoye ba a bayyane yake ba, a'a sai dai a Jumlace yake.

Sheikh Assunusi ya bayyana a cikin Al-umdah: "Cewa shi, masani ba a san shi ba a kan ayyanawa da faɗarsa cewa: "Da za a ce mai bayyanar da Imani ya yi furuci da dalilansa kuma ya kyautata dalilan da ba mu yanke hukunci da imani ba a cikin haƙƙinsa haka nan ilimi domin zai yiwuwa ya kasance akwai shubuhohi a cikin zuciyarsa wadda ta tilasta masa yin kokwanto amma bai bayyanar da ita ba gare mu, ko kuma ya kiyaye waɗancan dalilan a kan taƙalidi amma bai tabbatar da ita ba, sai dai yanayin halaye suna rinjayar da zato da ɗayan lamari biyu."

Ya bayyana a cikin sharhin Al-wusɗa nasa cewa: "Shi, muƙallidi, ba a san shi ba a kan ayyanawa" da faɗarsa cewa: "Bai kasance a gare mu ba mu munana zato ga jahili ko waninsa, haka nan mu yanke hukunci da taƙalidi a cikin haƙƙinsa saboda kawai kasawar harshensa, ga tabbatar da dalilan aƙidojin imaninsa da dalilanta da kuma hujjojinta sai dai ta wata fuska wadda yin bayani a kanta yana da wahala a gare shi, kuma da yawa daga cikin malamai suna kasawa a kan bayani ga abin da ke cikin zukatansu na ilimummuka tabbatattu, balle Jahilai."

Kuma ya bayyana a cikin sharhinsa na Al-wusɗa a kan wanda bai kai matsayin taƙalidi ba ba a san shi ba a kan ayyanawa da cewarsa: "Amma shi, mutum, bisa ga lura da kansa shi, masani, ne da ita kuma ba a tambayar waninsa game da ita."

Sai kuma ya ce: "Amma shi, mutun, ta hanyar lura da waninsa abin da yake rabonsa shi ne jahiliyya da halin zuciyarsa da rashin yanke hukunci da wani abu a cikin haƙƙinsa ta hanyar lura da abin da ke cikin wannan lamarin, sai idan mai shari'a tsira da aminci su tabbata a gare shi ya yi shaida da wani

abu ga wani sai a yanke hukunci a gare shi da wannan a cikin wannan lamarin, domin Allah Maɗaukaki da ManzonSa su ne suka fi sani.”

Sannan kuma tare da wannan ba mu da damar munana zato ga imanin wani daga cikin Musulmi jahili ne ko waninsa sai ya ce: “Sai dai idan ya bayyana ga harshen wani mutum abin da ke nuna abin da yake ɓoye a cikin zuciyarsa na ɓatattar aƙida, abin da yake wajibi a lokacin shi ne ya tausasa a wajen koyar da shi ya magance cutarsa da abin da ya sauƙaƙa” Allah ne abin neman taimako.

**29. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: “Ijtiha'di, An Gina Shi Ne A Kan Yankakken Hukunci, Ba A Kan Zato Ba,” Saboda Haka Idan Aka Ce Musu: “Wane Ya Dawo Daga Maganarsa Ta Kaza, Suna Mamaki Ga Wannan Saboda Su Suna Kudurta Cewa Wannan Shi Ne Abin Da Allah Da Manzonsa Suke Nufi A Cikin Wannan Hukunci A Yanke.”**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai. Saboda shi, ijtihadi, kamar yadda malamai suka bayyana shi ne: “Sanya ƙoƙari don tabbatar zato ga wani hukunci daga cikin hukunce – hukunce na shari’a.” Amma ba dukan mai Ijtihadi ke dacewa ba sai dai ana ba shi lada saboda faɗarsa tsirar Allah da aminci su tabbata a gare shi:

(إذا اجتهد الحاكم فأصاب فله أجران وإن أخطأ فله أجر واحد)

*“Idan Alƙali ya yi ijtihadi Sai ya yi daidai yana da lada biyu, idan ya yi kuskure yana da lada ɗaya.”*

**30. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: “Dukan Saɓani Da Ya Auku Tsakanin Ahlu Assunnan Saɓani Ne Na Lafazi Ba Na Ma’ana Ba.”**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai. Saboda su suna faɗin maganganu waɗanda haɗuwarsu ba ta yiwuwa, abin da yake matuƙar lamari a cikin wannan shi ne a ce: “Su ba su saɓani a cikin manyan mas’aloli,” sai wannan ya kai zuwa kasancewar sashensu mai bidi’a, saboda haka (Malam)Muhammadu Aɗɗahir ɗan Ibrahim ya faɗa a cikin Manzumatul Kubra tasa a cikin bayanin mas’alolin da saɓani ya auku a cikinsu tsakanin Malam Al-ash’ari da Malam Al-maturidi, ya ce: “Dukansu ba su cikin manyan mas’aloli balle su kai ga warware hukunci.”

**31. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: Kuskuren Duk Wanda Ya Zamo Daga Cikin Ahlussunna Ba A Mayar Da Shi Da Cewa Wannan Ɓarna Ce,**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai. "Duk wanda ya faɗi wata magana da ta saɓa wa nassin Alƙur'ani ko nassin Sunna ko ƙa'idoji ko ijma'i ko ƙiyasi bayyananne ana mayar da ita, ana kuma cewa wannan ɓarna ne, duka ɗaya ne wannan mai faɗa ya kasance daga cikin Ahlissunna ko daga cikin ma'abuta bidi'a."

Haƙiƙa, Malam Abdul'aziz Al-andalusi ya yi magana a cikin talifinsa ya faɗi magana wadda ta kai matuƙa kuma gamsassa (ya ce): "Wanda Allah ya haskaka basirarsa yana gani a cikin lalacewar abin da suka riyanta."

**32. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: Annabci Wahayi Ne Kawai, Wannan Shi Ma Ɓarna Ce Kuma Wahami Ne A Kan Haɗuwar Malamai.**

Sheikh Assunusi ya faɗa a cikin sharhin Alwusɗa: ya ce: Al-ƙarrafi ya ce: "Mutane da yawa suna ƙudurta cewa Annabci, wahayi ne kawai, wannan ɓarna ne saboda tabbatarsa ga wanda ba Annabi ba kamar Maryam, ita ba Annabi ba ce a kan magana ingantatta tare da cewa Allah (Ta'ala)Yana cewa:

﴿ فَأَرْسَلْنَآ إِلَيْهَا رُوحَنَا ﴾ مريم: ١٧

*"Sai Muka aika ruhinMu zuwa gareta" Maryam: 17*

A cikin (Littafin) Muslim (ya ruwaito): Allah Maɗaukaki ya aika mala'iki ga wani mutun wanda ya kasance ya fita don ziyarar wani ɗan'uwansa ne don Allah Maɗaukaki, sai ya ce: *"Lallai Allah yana sanar da kai cewa Yana sonka saboda sonka ga ɗan'uwanka ne don Allah."*

Ba Annabci ba ne sai dai ita a wurin malamai masu tahƙiƙi wahayin Allah Maɗaukaki ne ga wasu, da wani ƙagaggen hukunci da ya keɓanta da shi,

Kamar faɗarSa Maɗaukaki:

﴿ ٱقْرَأْ بِٱسْمِ رَبِّكَ ٱلَّذِى خَلَقَ ۝١ ﴾ العلق: ١

*"Ka yi karatu da sunan Ubangijinka wanda Ya yi halitta" Alaƙ: 1*

Wannan kallafawa ne da ya keɓanta da shi a cikin lokaci, wannan Annabci ne ba Manzanci ba, amma lokacin da Aya:

﴿ قُمْ فَأَنذِرْ ۝٢ ﴾ المدثر: ٢

*"Tashi ka yi gargaɗi" Al-Muddaththir: 2*

Ta sauka sai ta kasance manzanci saboda ratayar wannan taka'lifi da waninsa kuma. Shi, Annabi, an kallafa masa ga abin da ya keɓance shi; shi kuma manzo (an kallafa masa) da wannan da kuma isarwa ga waninsa saboda haka shi, Manzo, shi ne mafi keɓanta. A nan maganar ta ƙare.

**33. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: Kafirta Musulmi Ga Wanda Ke Kafirta Shi Ko Ga Wanda Bai Kafirta Waninsa Ba Daga Cikin Musulmi Ba Tare Da Tawili Ba (Wannan) Ta'assubi Ne Kuma Kiyayya Ce.**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai. Saboda kafirta Musulmi ba tare da tawili ba (wannan) kafirci ne, Annawawi ya faɗa cikin (littafin) Arraudha: Mutawalli ya ce: "Da ya ce wa Musulmi: Ya kai kafiri ba tare da tawili ba" (wannan) Kafirci, (Malam) Annawawi ya faɗa cikin (littafin) Arraudhah: (Malam) Mutawilli ya ce: "Da ya ce wa Musulmi: Ya kai kafiri ba tare da tawili ba." To, (wannnan) kafirci ne saboda ya ambaci Musulunci da (cewa) kafirci ne.

Haƙiƙa, (imamu) Albukhari da Muslim da Abudawuda da Tirmithi da Ibnu Hibban da Aɗɗabrani da Albaihaƙi da Addailami da Alkhara'iɗi da Ibnu Annajjar sun ruwaito Manzon Allah tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(إذا كفر الرجل أخاه فقد باء به أحدهما)

*"Idan mutum ya kafirta ɗan'uwansa haƙiƙa ɗayansu ya dawo da ita."*

Kamar yadda Shihabuddini Ahmed ɗan Hijir Alhaitami ya bayyana a cikin littafin Azzawajir.

Malam Taƙiyyuddini ya ce: "Wannan ƙyacewa ce mai girma ga wanda ya kafirta wani daga cikin Musulmi sai ya zama ba haka abin yake ba."

Malam Abu Is'haƙ ya ce: 'Ina kafirta wanda ke kafirta ni."

Malam Takiyuddini ya ce: "Yana yiwuwa mafarin wannan magana ta ɓoyu daga sashen mutane sai ya aza shi ba a kan ingantaccen wurin aza shi ba, abin da ya kamata a aza a kansa haƙiƙa shi, wannan hadisi, ya haskaka abin da ke hukunta cewa duk wanda ya kira wani mutun da kafirci alhali ba haka yake ba, to, kafircin ya dawo a kansa, kuma wannan mai magana ya kasance yana cewa: Hadisin ya nuna a kan cewa kafirci yana tabbata ga ɗayan mutum biyu: Ko dai mai kafirtawa ko wanda ake kafirtawa. Idan sashen mutane suka kafirta ni, to, kafirci zai auku ga ɗayanmu, kuma ni na tabbatar cewa ba kafiri ba ne, saboda haka kafirci zai koma zuwa gare shi", A nan maganar ta ƙare.

Manjuri ya faɗa a cikin sharhin Al-muhassil, cewa ɗan Rushdi ya faɗa a lokacin bayar da amsarsa game da wata tambaya a cikinta cewa wasu jama'a daga cikin malaman tauhidi suna cewa: "Yana wajaba a kan malami da jahili su karanci mas'habobin malaman tauhidi daga cikin Asha'irah da farawa da wannan kafin neman sanin abin da zai tsayar da lamarin addininsa da shi kamar alwala da sallah da sauran Ibadun da aka farlanta a kansa, sai suna kafirta duk wanda ya saɓa wa wannan." Sai ya ce: "Ba kome ake cewa kafirci ba face ƙudurta abin da suka tafi zuwa gare shi na daga wannan, domin su idan ba su yi sallah ba ba su yi hajji ba, har sai sun san Allah Maɗaukaki ta waccan hanya mai wahalar fahimta manisanciya, mai yiwuwa ba za su kai ga sanin sa ba ta waccan hanya sai bayan lokaci mai tsawo, ko fahimtarsu ta kauce daga gare ta sai su hanu daga addini, su kuma fita daga jumlar Musulmi."

A nan magana ta ƙare.

Muna neman Allah tsari daga wannan, kai kana ganin abin da kafirta Musulmi ya kai gare shi, muna roƙon Allah aminci da lafiya.

Haƙiƙa, faɗarsu jama'a sun bayyana suna kafirta Musulmai a cikin waɗannan garuruwan namu na Sudan kamar waɗannan garuruwa namu na Sudan kamar wannan ƙungiyar jama'a wadda ambatonta ya gabata. Suna riyanta cewa kafirtawarsu shi ne hanyar Sunna saboda wahamin da ya kamanta musu a cikin littattafan ilimin tauhidi.

Yana daga cikin mahallin wahaminsu a cikin abin da suka riyanta, maganar Muhammadu ɗan Umar ɗan Abdul'aziz ɗan Abdulmalik a cikin Alfaslul Auwal daga littafinsa wanda ya tara shi a cikin fasulla biyu (ya ce): "Ka sani cewa kafirci ya bayyana a cikin jahilai da mata, wanda aka yi ijma'i a kansa har ma da mafi yawan ɗalibai, ba su yi tsinkaya ba cewa abin da maganarsa ke nufi shi ne ba da labari a kan bayyanar kafirci daga sashensu da magana ko da aiki, ba manufar maganarsa kafirta jahilan Musulmi ba."

Yana daga mahallin wahaminsu a cikin abin da suka riyanta, maganar Abubakar ɗan Muhammadu ɗan Abubakar a cikin littafinsa, Hujjatul Mas'uli Ala Ilimi Attauhidi, ya ce: "Misalin wanda ya faɗi La-ila'ha Illa Allah ba tare da sanin aƙidojin ba kamar mai jin ƙishin ruwa yana kiran ruwan. Ba su yi tsinkaya ba cewa abin da maganarsa ke nufi shi ne: Duk wanda ya faɗi La ila'ha Illa Allah ba tare da fahimtar ma'anar Aƙidojin ba ko da jumla ce wanda ke isarsa a babin imani, to, kamar mai jin ƙishin ruwa ne da yake kiran ruwa, a wajen rashin amfanin faɗar La'ila'ha Illa Allah a can lahira, amma a nan duniya, to, yana amfaninsa a wajen gudanar da hukunce – hukuncen Musulunci, a kansa, domin mu ba mu san shi ba a kan ayyanawa matuƙar kafircinsa bai bayyana ba a kan harshensa.

Yana daga cikin mahallin wahaminsu a cikin abin da suka riyanta kuma, maganar Muhammadu Salihu ɗan Abdulrahman ɗan Sulaimu Al'aujali a cikin mashahuriyar ƙasidarsa a kan jahilai: Idan ka kasance ka banzatar da abin da nake faɗa saboda rashin arziƙinka za a haramta maka saduwa, kana faɗar La-Ilaha Illa Allah, amma ba ka san abin da ke nan ba (to, ta zama) Ah-Ah.

Ba su yi tsinkaya ba cewa abin da maganarsa ke nufi shi ne: Idan ka bar abin da nake faɗa maka a kan nasiha da shiryarwa na sanin wannan kalma Maɗaukakiya ko da da ma'ana ta kusa kuma bayyananna, wanda zai ishe shi a babin imani, ana haramta saduwar alhairi da rabo da ni'ima a gidan dauwama (Lahira), domin kai kana cewa (La-Ila'ha illa Allah Muhammadun Rasu'lullah Sallallahu Alaihi Wa Sallam) ba ka san ma'anarta ba ko da a Jumla ce, amfanin furucinka ba zai dawo gare ka ba, kuma wani Alkhairi ba zai kasance ba a cikin rayuwarka, a ranar Lahira, amma a duniya amfanin furucinka da La-Ilaha illa Allah Muhammadun Rasulullah zai dawo a gare ka saboda gudanar hukunce – hukuncen Musulunci a kanka matuƙar kafircinka bai bayyana ba a harshenka.

Yana daga cikin mahallin wahaminsu a cikin abin da suka riyanta, faɗar Al-aujali kuma a cikin (Littafin) Dalilul Aƙa'idi cewa:- "Duk wanda ya rataya da waccan mazhaba, ya sha ruwa waɗanda suka gurɓata a cikin abin sha. Haka kuma wannan mutun shaiɗan ya ruɗe shi a cikin rai, babu abin da ke isa a cikinsa sai ilimi, wannan shi ne abin da jama'ar (malamai) suka tace."

Ba su yi tsinkaya ba cewa abin da maganarsa ke nufi shi ne: "Duk wanda ya yi taƙalidi a cikin fannin tauhidi ya sha ruwa mai gurɓata, domin abin da ake nema a cikin fannin tauhidi shi ne ilimi ta hanyar bincike mai inganci, taƙalidi ba ya isuwa da shi, ma'anar rashin isuwa da shi cewa: Shi, wajibcin bincike, ba ya faɗuwa ga mai shi, ko da ya kasance mumini domin shi yana saɓo a kan barinsa idan ya kasance a cikinsa akwai karɓuwa ga fahimtarsa, idan ba haka ba, to, babu saɓo." Wannan shi ne abin da Jamhurin malaman sunna suke a kansa.

Amma faɗar cewa shi, muƙallidi, kafiri ne, to, an san cewa (wannan magana)ta fito ne daga Abu Hashim Al-Jubba-ee daga cikin Mu'utazilawa. Kuma Imamul Haramaini ya tafi zuwa a kanta daga farko sai dai ya kuma dawo daga gare ta. Haka Sheikh Assunusi ya tafi zuwa gare ta sai kuma ya dawo daga gare ta. Wannan saɓani kuma a kan muƙallidi ya kasance ne ta wajen bincike a kan hukumce-hukuncen lahira amma a nan duniya imanin da ke isa a cikinta shi ne yin furuci da harshe kawai, duk wanda ya yi furuci da kalmomin shahada biyu duk hukunce – hukuncen Musulunci za su gudana a kansa, a kan ittifaƙin (malamai) kai har ma a kan haɗuwar malamai, matuƙar kafircinsa bai bayyana ba ta hanyar magana ko kuma aiki.

Yana daga cikin mahallin wahaminsu a cikin abin da suka riyanta kuma: Maganar Malam Muhammad Al-wa'li a cikin (littafin) Al-munhal cewa: Malam Assumusi ya ɓata (maganar) farko, ya kuma taimaki (Magana) ta biyu wadda ta biyo, ba su yi tsinkaya ba cewa abin da maganarsa ke nufi shi ne: Haƙiƙa, Malam Assunusi ya ɓata maganar da ke cewa shi, kafiri, ne, (ya faɗi wannan) a cikin Al-umdah sharhin Al-Kubra, sai kuma ya dawo daga wannan (ra'ayin) ya taimaki (ra'ayin da ke cewa) shi, mumini, ne mai saɓo, ko da babu yankakken hukunci a cikinsa saboda fahimtar bincike. (Ya faɗi wannan) a cikin sharhin Al-wusɗa, sai kuma ya dawo daga wannan (Ra'ayi) a cikin sharhin Al-muƙaddima'tu sharhin Sugrassugra, sa'annan kuma ita, wannan magana, dukkanta tana cikin abin da ke tsakanin bawa da tsakanin Ubangijinsa musamman abin da ke tsakanin bawa da ire-irensa.

Yana daga cikin mahallin wahaminsa a cikin abin da suka riyanta kuma maganar Malam Assunusi a cikin (littafin) Al-kubra cewa: “Ita (yana nufin sana’ar taƙlidi) a lahira ba mai kuɓutarwa ba ce, da kuma faɗarsa bayan wannan cewa: “Kada mukallidi ya ruɗu.” Da kuma faɗar Muhammadu Aɗɗahir ɗan Sheikh Ibrahim a cikin waƙarsa ( Ina nufin) Alkubra (ya ce):

“Mafi yawan (malamai sun ce) sana’ar taƙalidi ba ta kuɓutarwa daga a dauwama a wuta har abada a ranar sakamako.

Kuma ana ji masa kokwanto da darjewa a lokacin da manyan musibbu ke sauka.

Idan dogewa da kuma yawan ibada suka ruɗe shi, to, ka warware masa (wannan ra’ayi) domin malamai sun karkata zuwa ga ra’ayi na farko.”

Ba su yi tsinkaya ba cewa ma’anar wannan duka an gina ta ne a kan faɗar cewa shi, muƙallidi, kafiri ne. Wannan kuwa magana ce mai rauni domin abin da ke cikinta na saɓa wa abin da jamhurin malaman sunna ne suke a kansa kamar yadda (bayani) ya gabata, kuma haƙiƙa Malam Assunusi ya dawo daga wannan(ra’ayi) kamar yadda (bayani) ya gabata, sa’annan kuma ita, wannan magana dukanta, tana a kan abin da ke tsakanin bawa da Ubangijinsa ba abin da ke tsakanin bawa da ire-irensa ba.

Yana daga cikin mahallin wahaminsu a cikin abin da suka riyanta kuma: Maganar Ahmad Al-maƙarri a cikin (littafin) Idha’atu Addujnah (inda ya ce): Abin da ake nema ba ya kammala ga mai nema sai da ilimummuka guda bakwai da ake nema.

Ba su yi tsinkaya ba cewa abin da maganarsa take nufi shi ne cewa duk abin da ake nema ba zai cika ba a babin raddin malaman falsafa waɗanda suke riyanta cewa duniya ƙadimiyya ce (wannan raddi ba ya cika) sai da sanin abubuwa bakwai da ake nema a cikin babin imani ba ya cika sai da ita, da dai a ce lamarin ya kasance kamar yadda suka riyanta a kan ƙaddartawa ɓatatta, to, da wannan ya kasance ne a cikin abin da ke tsakanin bawa da Ubangijinsa ba abin da ke tsakanin bawa da ire-irensa ba.

Yana daga cikin mahallin wahaminsu a cikin abin da suka riyanta kuma: Maganar Ahmad ɗan Abdullahi Al-jaza’iri a cikin ƙasidarsa (inda ya ce): Domin Tauhidinmu shi ne asalin tsirarmu gobe (Lahira), kuma ga waɗanda suka rigaya suka shuɗe daga cikin Musulmi suna da addini.

Da kuma faɗarsa cewa: Haƙiƙa, dukan Annabawa da manzanni gaba ɗaya sun haɗu a kan cewa yin addini da tauhidi yana cikin addini.

Ba su yi tsinkaya ba cewa tauhidi da aka ambata a cikin waɗannan baituka (na waƙa) guda biyu ba manufa ce ba a kan ilimin tauhidi, a'a shi, wannan tauhidi, shi ne kaɗaita wanda ake bautawa, domin samun tsira bai dogara ba a kan ilimin tauhidi sai dai a kan fahimtar ma'ana Maɗaukakiya kuma a kan wannan tauhidi bayyananne makusanci ne ma'anar faɗar Allah take (da Ya ce):

﴿وَمَآ أَرۡسَلۡنَا مِن قَبۡلِكَ مِن رَّسُولٍ إِلَّا نُوحِيٓ إِلَيۡهِ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّآ أَنَا۠ فَٱعۡبُدُونِ ٢٥﴾

الأنبياء: ٢٥

***"Ba Mu aiko wani Manzo ba gabaninka face Muna yin wahayi (aike) zuwa gare shi cewa babu wanda ya cancanta a bautawa sai Ni saboda haka ku bauta miNi" Al-Anbiya'u: 25.***

Zuwa ga ma'anar wannan Aya ne ya yi ishara a cikin baiti na biyu.

Yana daga mahallin wahaminsu a cikin abin da suka riyanta kuma: Maganar mai (littafin) Jawa'hirul hisan, a cikinsa (yana cewa): "Wanda ya jahilci ɗaya daga cikin waɗannan rukunnai guda shida, to, ya zama kafiri wanda ake dauwamar da shi a cikin wuta, kuma an haramta masa shiga aljanna."

Ba su yi tsinkaya ba cewa manufar maganarsa shi ne; "Duk wanda ya jahilci waɗannan ƙa'idoji bayyanannu na larura waɗanda ingancin imani ke dogara a kan fahimtarsu ko da a kan jumla ce wanda ake isuwa da shi a cikin babin imani, to ya zama kafiri sai a cikin abin da ke tsakaninsa da Ubangijinsa, da kuma cikin hukuncin lahira, ba a cikin hukuncin duniya ba, wadda aka gina hukunce–hukuncenta a kan abubuwan da suke a bayyane. Haka kuma mu ba mu tsinkaya ga wanda ya jahilci abin da Ingancin imani yake dogara a kan fahimtarsa a kan ayyanawa; matuƙar kafircisa bai bayyana ba. Haka kuma ba a cewa: Lallai Imani ba ya tabbata ga mutum sai ya fahimci waɗannan ƙa'idoji bayyanannu na larura a rarrabe wanda yake a kan hanyar malaman tauhidi sai dai imani yana tabbata da fahimtarsa a jumlace. Wannan fahimta ta tabbata ne ta dalilin neman ilimi, ko ta dalilin cuɗanya ko da falalar Allah Maɗaukaki kawai ba tare da wani tsakani ba.

Yana daga cikin mahallin wahaminsu a cikin abin da suka riyanta: Maganar sashen malamai wadda (Malam) ɗan Imrana Al-jaura'i ya zo da ita a cikin littafinsa (mai suna) Aƙidatul Muwahhidina (in da ya ce): "Duk wanda bai tsayu ba a kan sanin tauhidi ba, wata shaida daga cikin shaidunsa haƙiƙa ƙafar ruɗuwa ta darje da shi a cikin ramin halaka, yana nufin cewa: "Duk wanda ya karkata zuwa ga taƙalidi bai lura da dalilin tauhidi ba, to, ya faɗo daga tudun tsira, kuma ya auka a cikin kamun halaka."

Ba su yi tsinkaya ba cewa manufar maganarsa an gina ta ne a kan maganar kafirta muƙallidi, wannan magana mai rauni ce saboda saɓawarta ga abin da Jamhurin malaman sunna suke a kansa, kamar yadda bayani ya gabata. Kuma haƙiƙa mun gabatar da bayani cewa Malam Assunusi ya tafi a kan wannan ra'ayi sai kuma ya dawo daga gare shi, sa'annan kuma wannan magana dukanta ga abin da ke tskanin bawa ne da Ubangijinsa ba abin da ke tsakanin bawa da ire-irensa ba.

Yana daga cikin mahallin wahaminsu a cikin abin da suka riynata: Kuma: Maganar Abu Hamid Algazali a cikin (littafinsa mai suna) Al-minhaju wadda kuma Abu Imrana Al-jaura'i ya zo da ita a cikin littafinsa mai suna Aƙidatul Muwahhidina (ya ce): "Farkon abin da ke wajaba a kansa shi ne sanin wanda ake bautawa, sa'annan ka bauta masa, ta yaya za ka bauta wa wanda ba ka san shi ba da sunayensa da siffofinsa, da abin da ke wajaba gare shi da abin da ke koruwa a kansa da abin da ke halatta a cikin haƙƙinsa mai yiwuwa ka ƙudurta wani abu a cikin siffofinsa daga cikin abin da yake saɓanin gaskiya ne sai ibadarka ta zama ƙura sheƙaƙƙiya, muna neman Allah tsari.

Ba su yi tsinkaya ba cewa maganar Gazali wannan ba a kan zahirinta take ba ga duk haɗuwar malamai, domin zahirinta shi ne cewa bawa ba ya bauta wa Ubnagijinsa sai bayan sanin abin da shahada biyu ke nunawa a rarrabe wanda yake a kan hanyar malaman tauhidi, wannan kuwa ɓarna ce a kan ijma'in malamai, a dalilin cewa shi, kafiiri, ana umurtarsa da yin Sallah idan ya musulunta lokacin halartowarta, haka da yin azumi idan ya musulunta lokacin halartowarsa, a kan Ijma'in malamai. Idan ka fahimta cewa wannan magana tasa tana kai zuwa ga ɓarna idan aka ɗaukaka a kan zahirinta, to, ka sani cewa abin da yake nufi shi ne ba da labari a kan cewa duk wanda bai yi ƙoƙari cikin abin da ba shi da komi (na lada) yana nufin: Idan Allah bai kiyaye ka ba. A nan maganar ta tsaya.

Yana daga cikin mahallin wahaminsu a cikin abin da suka riyanta kuma: Maganar sashen malamai wadda (Malam) Al-jaura'i ya zo da ita a cikin littafinsa mai suna Aƙidatul Muwahidina cewa: "Ibada ba ta inganta sai bayan sanin wanda ake bautawa, haka sanin shari'a (bai inganta) sai bayan sanin wanda Ya wajibta ta kuma Ya samar da ita. Haka kuma sanin Alƙur'ani (bai inganta) sai bayan sanin wanda Ya saukar da shi, haka sanin Manzo (bai inganta) sai bayan sanin Mai aikowa.

Ba su yi tsinkaya ba cewa ma'anar maganar sashen malamai wannan an gina ta ne a kan sanin abin da kalmomin shahada biyu suke nunawa, ko da a jumlace wanda ake isuwa da shi a babin imani (wannan) sharaɗi ne a cikin ingancin ibada, bai kamata a fahimta daga gare shi cewa ibada ba ta inganta sai bayan sanin abin da kalmomin shahada biyu suke nunawa a rarrabe wanda yake a kan hanyar malaman tauhidi.

Asalin wannan magana shi ne faɗar Mai tsira da amincin Allah ga Mu'azu ɗan Jabalu (Allah shi yarda da shi) lokacin da ya aike shi zuwa ga mutanen Yaman kamar yadda yake a cikin ruwayar Muslim:

(فليكن أول ما تدعوهم إليه معرفة الله، فإذا عرفوا الله فأخبرهم أن الله فرض عليهم خمس صلوات في يومهم وليلتهم ...)

***"Ya kasance farkon abin da za ka kira su zuwa gare shi sanin Allah, idan suka san Allah, to, ka ba su labari cewa Allah ya farlanta salloli biyar a kansu a cikin wuninsu da darensu."***

Har zuwa ƙarshen hadisi.

Wannan sanin (Allah) da aka ambata a cikin ruwayar Muslim shi ne sanin abin da (kalmomin) shahada biyu ke nunawa a jumlace wanda ake isuwa da shi a cikin babin imani ba a kan rarrabewa ba irin wanda yake a kan hanyar malaman tauhidi a kan ijma'in malamai.

Idan ka ce: Rikici ya gushe, gaskiya kuma ta bayyana da dalilanta a cikin duk abin da aka ambata, to, ka ba mu labari kuma game da haƙiƙanin Jahili wanda yake da Jahilci mai sauƙi da kuma haƙiƙanin Jahili wanda yake da Jahilci haɗaɗɗe, da haƙiƙanin mai kokwanto da mai zato da mai wahami domin lafuzzan waɗannan sunaye wurin wahami ne kuma.

**Na ce:** Amsa ita ce: "Shi, Jahili, wanda yake da jahilci mai sauƙi shi ne wanda yake da jahilci ɗaya shi ne rashin fahimtar kalma Maɗaukakiya (Kalmar shahada) ko da a jumlace wanda ake isuwa da shi a cikin babin imani.

Amma jahilin da ya kasance yana da jahilci haɗaɗɗe (murakkabi) shi ne wanda yake da jahilci biyu: Na farko, rashin fahimtar kalma maɗaukakiya. (Kalmar shahada) ko da a jumlace wanda ake isuwa da shi a cikin babin imani.

Haƙiƙa, Malam Assunusi ya faɗa kamar yadda Sayyid Mayyarah ya cirato a cikin (littafin) Adduraru Ath-thameen cewa: 'Duk wanda bai san ma'anar La-ilaha illa Allah ba" ba jumlace ba ba a rarrabe ba (wannan) yana da wahalar samu ƙwarai.

Amma mai kokwanto shi ne wanda gaskata abin da aka san zuwan manzanni ya zama lalura da ƙaryata wannan, duka wannan ya daidaita a zuciyarsa.

Amma mai zato shi ne wanda ɗayansu ya rinjaya a zuciyarsa. Amma mai wahami shi ne wanda akwai kishiyar abin da ke rinjayar da mai zato a cikin zuciyarsa.

Idan ka ce mene ne hukuncin waɗannan biyar? Shin su, muminai, ne ko kafirai ne?

**Sai na ce:** Su, kafirai, ne a kan ijma'in malamai sai dai a cikin abin da ke tsakaninsu da Ubangijinsu, da kuma cikin hukuncin lahira, ba a cikin hukuncin duniya ba wadda take an gina hukunce - hukuncenta a kan abubuwan da suke zahiri, domin mu ba mu sanin su a kan ayyanawa, domin jahilci mai sauƙi da jahilci murakkabi (Haɗaɗɗe) da kokwanto da zato da wahami siffofin zukata ne, su kuma siffofin zukata suna daga asirran gaibi sai dai idan wannan ya bayyana gare mu ta hanyar halussansu (maganarsu).

**34. Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Duk Wanda Ya Faɗi La Ila'ha Illa Allahu Muhammadun Rasulullahi, Zai Shiga Al-Janna, Ko Da Bai Fahimci Ma'anarta Ba Wanda Ingancin Imani Yake Dogara A Kan Fahimtarsa."**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai, domin tabbatar da (kalmomi) shahada biyu da harshe kawai, ba ya isa sai kawai a cikin hukunce – hukuncen duniya, amma shiga al-jannah babu

makawa a sharɗanta fahimtar ma'anarsu a cikinsa da kuma gasgatawarsa, sai dai ba a sharɗanta sanin wannan ba a rarrabe wanda ke a kan hanyar malaman tauhidi. Sai dai an sharɗanta sanin ma'ana ta fuskar da ta ƙunshi rarrabewa a cikin abin da Sheikh Assunusi ya ba da amsarsa. Kamar yadda Sayyadi Mayya'rah ya cirato a cikin (Littafin) Adduraru Ath-thameen wa mauridul ma-een, fee sharhi Almurshidil Mueen, Ala Al-dharuree min Ulumiddeeni na Al-Imam ɗan Ashir, Allah Maɗaukaki ya amfane mu da su da kuma ire-irensu, nassin tambayar da amsa shi ne:

An tambayi Sheikh Sayyid Muhammad Assunusi Allah Maɗaukaki ya amfane mu da shi cewa: "Ko an sharɗanta a cikin imanin mukallafi ya san ma'anar La Ila'ha Illa Allah Muhammadun Rasulullah, a kan rarrabe wanda ya ambata a cikin (littafin) Al-aƙidadu Assugra, ko a'a (ba a sharɗanta ba)?"

Sai ya ba da amsa da cewa: "Wannan ba a sharɗanta shi ba sai a cikin cikar imani." An sharɗanta ne kawai a cikin ingancin sanin ma'ana ta fuskar da ta ƙunshi rarrabewa, babu kokwanto cewa abin da yake mafi rinjaye a cikin muminai jahilansu da malamansu suna a kan sanin wannan, domin kowane ɗaya daga cikinsu ya san cewa Allah shi ne Mahalicci bai zama abin halitta ba, kuma Mai arzuttawa ba wanda ake arzurtawa ba. Wannan shi ne ma'anar wadatuwarSa Maɗaukaki Mabuwayi daga duk abin da yake waninSa da buƙatuwar duk wanda ba shi ba zuwa gare Shi, sun sani cewa Allah ba a yin sallah sai a gare Shi, ba a yin azumi sai a gare Shi, babu abin bautawa da cancanta waninSa, wannan shi ne ma'anar faɗarsu cewa: "Allah Shi ne wanda Ya cancanta da bautawa, kuma waninSa ba ya cancanta da ita. Jawabinsa ya ƙare."

## 35- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Ba A Samun Kafirai A Cikin Waɗannan Kasashe Na Sudan Tun Asali.

Wannan shi ma ɓarna ne kuma wahami ne a haɗuwar malamai domin a cikin waɗannan ƙasashe akwai wanda bai shiga a cikin Musulunci ba tun asali, kuma shi, kafiri, ne da Ijma'in dukan al-umma, a cikin waɗannan ƙasashe kuma akwai wanda ke girmama itatuwa da duwatsu da yin yanka a wurinta ko zuba gare ta a kanta, wannan shi ma kafiri ne da ijma'in al-umma. A cikin waɗannan ƙasashe kuma akwai wanda ke zagin Allah Maɗaukaki. Wannan shi ma kafiri ne a kan ijma'in al-umma."

Abin da ya kai su zuwa ga wannan wahami, shi ne waɗannan abubuwa da ambatonsu ya gabata, suna iƙrari da (samuwar) Allah Maɗaukaki, ba su yi tsinkaya ba cewa shi, kafirci, idan ya bayyana ta hanyar

magana ko aiki yana hana hukuncin Musulunci a bayyane da ɓoye, ba su yi tsinkaya ba kuma cewa shi, Abu Jahli, da ire-irensa daga cikin waɗanda suka yi zamani da Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, suna iƙrari da samuwar Allah, amma su tare da haka kafirai ne, ta wata fuska, (Allah) Maɗaukaki ya ce:

﴿وَلَئِن سَأَلْتَهُم مَّنْ خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ لَيَقُولُنَّ ٱللَّهُ﴾ لقمان: ٢٥

*"Idan ka tambaye su cewa wane ne ya halicci sammai da ƙasa wallahi lallai za su ce Allah ne" Lukman: 25*

﴿وَلَئِن سَأَلْتَهُم مَّنْ خَلَقَهُمْ لَيَقُولُنَّ ٱللَّهُ﴾ الزخرف: ٨٧

*"Idan ka tambaye su cewa wane ne ya halicce su wallahi za su ce Allah ne" Zukhruf: 87*

Idan suka ce: "Shi, Abu Jahli, da ire-irensa daga cikin waɗanda suka yi zamani da Annabi tsira da aminci su tabbata a gare shi ko da yake sun yi iƙirari da (samuwar) Allah Maɗaukaki, amma ba su cewa La-Ilaha Illa Allah. Muhammadun Rasulullah, Su kuwa waɗannan suna faɗarta.

Sai mu ce: Lallai su waɗannan ko da yake suna faɗar La-Ilaha Illa Allah Muhammadun Rasulullah, suna kasancewa Musulmi da faɗar wannan saboda su suna faɗarta ne ta hanyar abin da aka saba da shi a al'ada tare da tsayawarsa a kan bayyanannen kafircinsu, kuma kafiri ya zama Musulmi ne da faɗar: "La-Ilaha Illa Allah Muhammadun Rasulullah, idan ya faɗe ta da niyyar fita daga kafirci da shiga Musulunci."

A cikin (littafi) wallafar Abdul'aziz Al-andalusee (ya ce): "Lallai Yahudawan Bagadaza suna faɗar 'La-Ilaha Illa Allah Muhammadun Rasulullah." amma ba su zama Musulmi da (faɗar) wannan saboda suna faɗarta ne a kan abin da aka saba da shi da kuma al'ada tare da tsayawarsu a cikin bayyanannen kafircinsu, saɓanin Yahudawan Masar domin su ba su faɗarta sai lokacin fitar su daga kafirci da shigar su cikin Musulunci.

**36 – Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: Kowane Bafulatani Musulmi Ne.**

Wannan shi ma ɓarna ne kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai domin a cikinsu akwai wanda ke musun tayar da matattu, wannan kafirci ne a kan haɗuwar malamai, a cikinsu kuma akwai wanda ke izgili da addinin Allah, shi ma kafiri ne a kan haɗuwar malamai; a cikinsu akwai wanda ke zagin Allah Maɗaukaki, shi, kafiri, ne a kan haɗuwar Malamai. Idan lamarin ya kasance kamar haka ta yaya ake cewa: Kowane Bafulatani Musulmi ne, abin da ya kai su zuwa ga wannan shi ne kasancewar mafi rinjaye a cikin ƙabilar Fulani Musulunci ne, kuma darajar gamewar Musulunci ga dukan ƙabila Allah bai bayar da ita ba ga dukan ƙabilu da a ce waccan darajar ta kasance ana cimma ta ta hanyar dangataka kawai, to, da Larabawa sun kasance su ne mafi cancanta da wannan, domin su ne ƙabilar Muhammadu Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi kuma masoyinSa."

**37 – Yana daga cikin wancan wahami: Kudurtawar sashensu cewa: "Waɗansu jama'a sun tarar da iyayensu da shugabanninsu da malamansu a kan al'adu munana sai suka sanya samunsu a kanta (matsayin) hujja a kan sunna."**

Wannan shi ma ɓarna ne kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai.

Daga cikin waɗancan munanan al'adu akwai shiga gidan wani ba tare da neman izini ba, da rashin shamakancewar mace daga ɗan'uwan mijinta da ɗan amminta (ɗan ƙane ko wan babanta) da ɗan kawunta (ɗan ƙane ko wan mahaifiyarta) ko mijin yar'uwarta ko abokin mijinta. Haka kuma kaɗaitar namiji ba'ajnabi tare da mace ba'ajnaba, da tafiyarsa tare da ita babu waninsu tare da su (kamar) miji ko wani ɗan'uwa muharrami da fitar mata zuwa kasuwa suna turin juna tare da mazaje. Da fitarsu zuwa ga masu yawo a cikin alƙarya don sayen mundaye da 'yan hannu da tufafin ƙawa da auduga da wanin wannan daga cikin abin da ke cikin buƙatunsu, da rashin ba da gado a kan littafin Allah. Bugu da ƙari, walimar aure wadda ke haɗe da abubuwan munkari da walimar suna mai tattare da munkari da ruɗuwar miji ta hanyar amince wa matarsa saboda kasancewarta mai kamun kai sai ya bar ta tare da mazaje ajnabai da abin da suka sanya shi (a matsayin) ladabi ga manyansu a wajen gaisuwa kamar sunkuyar da kai da gurfani da abin da suke aikatawa a lokacin ambaton dalilan Raja'i (a wurin Allah) da dalilan samun rahama kawai ga jahilai domin su juyar da su daga wuraren wa'azi da wanin wannan

daga cikin al'adu munana wanda ijma'in malamai ya tabbata a kan haramcinsu.

Ahmad Zaruƙ ya faɗa a cikin (littafin) Umdatul Mureed Assadiƙ: Lallai sunna hujja ce a kan dukan al'umma, babu aikin wani daga cikin al'umma da yake hujja a kan sunna, domin ita, sunna, tsararra ce daga kuskure, mai ita shi ma tsararre ne amma sauran al'umma tsare su (daga kure) bai tabbata ba sai tare da ijma'insu a keɓance idan suka yi ijma'I, to, ijma'insu zai ƙunshi dalili na shari'a.

Sai kuma ya ce bayan ya yi wata magana: Abin da ya zo mana daga shugabannin malamai za mu aza shi ga Alƙur'ani da sunna, abin da suka karɓe shi sai mu karɓe shi, abin da kuma ba su karɓe shi ba sai mu bar shi. Idan sun kasance daga cikin nau'o'in waɗanda ake koyi da shi babu raddi a gare shi kuma babu gitta masa domin mu ba mu fahimci fuskar dawowarsa ba zuwa ga ƙa'idoji na shari'a, kamar yadda muka fahimci waninsa.

Ya zo a cikin (Littafin) Al-Madhal cewa: "Kana samun sashensu bai san sunna ba a'a ba ya bin kowa sai malaminsa; idan ka ce masa: "Abin da yake sunna shi ne kaza da kaza zai ce maka: Malamina ya kasance yana aikata kaza, kuma ita ce hanyar malamina, sai ya ci karo da sunna bayyananna ta irin wannan ra'ayi." A nan maganar ta ƙare.

**38 – Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Sunnar (Sanya) Rawani Ta Keɓanta Da Malamai Ne."**

Wannan shi ma ɓarna ne kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai, domin shi, rawani, shamaki ne tsakanin Musulmai da mushrikai, ba shamaki ba ne tsakanin malamai da waɗanda ba su kai matsayinsu ba.

Ya zo a cikin (Littafn) Al-Madkhal na Ibnul Haj cewa: "Shi (Manzon Allah) tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ɗaura wa Aliyu Rawani ya kuma sako gefensa a kan kafaɗunsa sai ya ce: *"Lallai rawani shamaki ne tsakanin Musulmai da mushrikai."*

**39 - Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Cewa Sashensu Ba Ya Umurni Da Alhairi, Ba Ya Hani Daga Munkari Saboda Galibin Mutane Ba Su Karɓar Wannan, Kuma Yana Sanya Wannan Cewa Uzuri Ne A Gare Shi A Cikin Barin Umurni Da Hani, Wannan Shi Ma Ɓarna Ne Kuma Wahami Ne A Kan Haɗuwar Malamai.**

Ya zo a cikin (Littafin) Al-Madkhal cewa: "Bai zama (wajibi ba) a kansa ya canza abin da aka umurce shi da canza shi sai dai abin da yake a kansa shi ne ya yi magana a cikin wannan ta hanyar zance, ya ambaci abin da yake hukunci a cikinsa. Idan ya saurare shi ya kuma dawo, to, abin da ake nufi ya tabbata. Idan kuma ya ƙi (saurare) haƙiƙa ya tsayar da uzurinsa a wurin Allah, kuma ya tsayu da abin da ya wajaba a kansa, kuma ya kuɓuta daga ya rataya a kansa (Ranar Kiyama)" domin haƙiƙa ya zo (a cikin nassi) cewa: "(A ranar alƙiyama mutun zai rataya da wani mutun wanda bai san shi ba, sai ya ce masa: Me ya same ka ni da ɗai ban taɓa ganin ka ba, sai ya ce: Haka ne ai ka gan ni wata rana a kan wani munkari sai ba ka canza shi ba gare ni." Wannan hari ne kuma kaɗan ne ake samun kuɓuta daga gare shi. Amma yana kuɓuta daga gare shi ta hanyar magana, kuma maganar babu wahala a cikinta, mafi yawan munkari a cikin zamaninmu babu wahala babu tsoro ga malami ga yin magana a cikinsa, sai dai yana barin ta tare da ganin ta saboda zukata suna ɗebe kewa da munanan al'adu waɗanda iyayensu suke a kansu. Wannan kuwa shi ne ya hallaka waɗanda suka shuɗe daga cikin al'ummomi.

**40 – Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Yin Kawaici Daga Magana Abin Da Ake Nema Ne A Cikin Kowane Hali, Suna Kafa Dalili Da Cewar (Manzon Allah) Tsira Da Amincin Allah Su Tabbata A Gare Shi "Duk Wanda Ya Yi Kawaici, To, Ya Kuɓuta."**

Wannan shi ma ɓarna ne kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai. Domin yin kawaici daga aikin alhairi da (yin kawaici) daga horo da Alhairi da hani daga munkari, ba abin godiya ba ne saboda faɗar (Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi kamar yadda yake a cikin sharhin Ibni Hibba'n: "Ka kame harshenka sai ga alhairi." Da faɗarsa tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi:

(كل كلام ابن آدم عليه لا له إلا أمرًا بمعروف أو نهيًا عن منكرٍ أو ذكرا لله)

*"Dukan maganar ɗan'adam tana a kansa ba shi da (La'danta) sai horo da Alhairi ko hani daga munkari ko ambaton Allah."*

**41 – Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kafa Dalilin Sashensu A Kan (Halaccin) Biyar Al'Adu Abin Zargi Da Maganar Da Ta Yaɗu A Cikin Garuruwa Cewa: "Al'adar Gari Kamar Sunna Ne."**

Wannan shi ma ɓarna ne kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai, domin al'ada ba a biyar ta idan ta saɓa wa sunna a kan haɗuwar malamai.

Haƙiƙa, sashen 'yan'uwa ya ambata mini cewa ya ji sashensu yana cewa: "Hani daga munkari a cikin garin da ake aikata munkari shi ma haƙiƙanin munkari ne saboda haka ba su hani daga munkari ba." Muna roƙon Allah Maɗaukaki tsari, kuma wannan yana daga cikin ɗabi'un Yahudawa kamar yadda (Allah) Maɗaukaki ya faɗa a cikin LittafinSa Mabuwayi:

﴿ كَانُوا لَا يَتَنَاهَوْنَ عَن مُّنكَرٍ فَعَلُوهُ ۚ لَبِئْسَ مَا كَانُوا يَفْعَلُونَ ﴿٧٩﴾ ﴾

المائدة: ٧٩

*"Sun kasance ba su hana junansu daga aikata munkari, Suna ma aikatawa, abin da suke aikatawa wallahi ya munana." Ma'idah: 79*

**42- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Wajibcin Umurni Da Alhairi Da Hani Daga Munkari Ya Dogara Ne A Kan Bayyanar Shugaba," Wannnan Shi Ma Ɓarna Ce Kuma Wahami Ne A Kan Haɗuwar Malamai.**

Sheikh Assunusi ya faɗa a cikin sharhin Al-wusɗa cewa: "Abin da ake nufi da al-ma'aruf shi ne Wajibi Munkari kuwa shi ne: Haram, babu kokwanto cewa shi, Umarni da Alkhairi da hani daga munkari, ga ma'anar da ta gabata a cikinsu wajibai ne ba tare da dogara da bayyanar shugaba ba kamar yadda Rafila'wa (Shi-a) suke riyantawa, kuma dalilin wajibcinsu shi ne Alƙur'ani da sunna da ijma'in (malamai)."

Sai kuma ya ce bayan magana: Har suka faɗa yana nufin malamai:- Umurni da alhairi da hani daga munkari suna halatta ko da yana zaton cewa shi za a kashe shi sai kuma ya ce: "An yi saɓani mene ne ya fi daga cikinsu a cikin wannan halayya, shin canzawar (ɓarna) ko kuma yin kawaici?"

Ra'ayin farko shi ne ra'ayin (Imamu) Malik da Ibnu Hibba'n da Sa'idu ɗan Jubair. Allah Maɗaukaki shi yarda da su sai kuma ya ce bayan wata magana: Umurni da alhairi da hani daga munkari bai keɓanta da shugabanni ba, domin su, Musulmai, a zamanin farko da bayansa sun kasance

suna umurtar shugabanni su kansu da alhairi kuma suna hana su daga munkari ba tare da samun musu daga wani ba bai dogara a kan izini ba, (da wannan ne) aka san cewa bai keɓanta da shugabanni ba, a'a sai dai ya halatta ga ɗaiɗaikun talakawa (su yi umurni da hani) ta hanyar magana da kuma aiki, sai dai idan lamari ya kai zuwa ga yaƙi da zare makami, to, sai a haɗa da shugaba don gudun fitina, haka Imamul Haramaini ya ambace shi Allah ya yi masa rahama.

**43- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Su, Jahilai, Babu Wajen Da Za Su Shiga A Cikin Umurtar Mutane Da Alhairi Da Hana Su Daga Munkari."**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai.

Sheikh Assunusi ya faɗa a cikin sharhin Al-wusɗa cewa: Imamul Haramani ya ce: "Hukunci na shari'a idan jahilai da malamai suka daidaita a cikin fahimtarsu, to, a cikinsa akwai umurni da alhairi da hani daga fahimtarsa suka keɓanta da ijtihadi da umarni da hani a cikinsa bai kasance ba ga jahilai shi ke nan an wakiltar da shi zuwa ga masu ijtihadi.

Ish-beelee ya faɗa a cikin sharhin Al-arba-ina Annawawiyyah cewa: "Wanda ke umurni da hani kawai shi ne wanda ya kasance masani da abin da yake umurni da shi da wanda yake hani daga gare shi. Idan ya kasance daga lamurran da suke bayyane kamar sallah da azumi da zina da shan giya da makamantansu, dukan Musulmi masana ne game da su. Idan ya kasance daga cikin ayyuka masu wahalar ganewa da matakai daban – daban da abinci ya rataya da ijtihadi babu mashiga a cikinta ga jahilai, kuma ba su da damar musun sa, wannan yana ga malamai."

**44- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: Wajibcin Umurni Da Alhairi Da Hani Daga Munkari Ya Keɓanta Ne Da Wanda Yake Da Tsentseni.**

Wannan shi ma ɓarna ne kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai.

Sheikh Assunusi ya faɗa a cikin sharhin Al-wusɗa cewa: "Wajibcin umurni da Alhairi da hani daga munkari bai keɓanta da wanda ke da tsentseni ba (wanda) ba ya aikata irin sa, a'a duk wanda ya ga munkari alhali yana aikata irin sa ya wajaba a kansa ya yi hani daga gare shi domin barinsa ga munkari da haninsa farillai ne masu bambanci, bai zama dole ba ga wanda ya bar ɗayansu a ce sai ya bar ɗayansu."

Idan suka kafa dalili da faɗar Allah Maɗaukaki:

﴿ أَتَأْمُرُونَ ٱلنَّاسَ بِٱلْبِرِّ وَتَنسَوْنَ أَنفُسَكُمْ ﴾ البقرة: ٤٤

***"Shin kuna umurtar mutane da alkhairi kuna kuma mantawa da kawunanku" Al-Baƙarah: 44***

Sai mu ce: Jumlar mantuwa duka shi ne mahallin tambaya ta musu, kamar yadda yake cikin tafsirin Abdulrahmani Assuyuɗi (mai suna): Attakmilah.

**45- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: Faɗar (Manzon Allah) Tsira Da Amincin Allah Su Tabbata Agare Shi Cewa: Addini Sauƙi Ne.**

Yana wajabta yin sakaci ko da a cikin wajibai da abubuwan da aka haramta, idan har suka ji wanda ke umurni da Alhairi yana kuma hani daga munkari a cikin gari, sai su ce: "Wannan mai tsanani ne ai addinin Allah sauƙi gare shi. Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai domin wannan sauƙi wanda aka ambata a cikin hadisi da waninsa yana shiga ne a cikin babin nafilfoli kawai, ba ya shiga a cikin babin wajibcin su. Haka kuma ba ya cikin haramce-haramce waɗanda dukan Musulmai suka haɗu a kan haramcin su, sai a kan lalura kamar taimama a lokacin rashin ruwa ko rashin samun dama a kan amfani da shi, haka kuma kamar cin mushe (matattar dabba) ga wanda ke cikin halin matsuwa.

**46- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: Masu Kissoshi Masu Kawatarwa Da Masu Wa'azi Waɗanda Ke Tunatarwa Dukansu Ɗaya Ne.**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne, a kan haɗuwar malamai, domin su, masu wa'azi masu tunatarwa, su ne waɗanda ba su ƙagen wani abu daga wurinsu a cikin babin tsoratarwa ko kwaɗaitarwa, kuma ba su tsoratar da mutane, ba su kwaɗaitar da su da abin da waɗansu suka ƙaga sai dai suna tsoratar da mutane suna kuma kwaɗaitar da su da littafin Allah da Sunnar ManzonSa tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, tare da koyarwarsu ga mutane ilimin hulɗa da Jama'a, ita kuma hanyar masu ƙissoshi masu ƙawatar da (Labari) suna akasin hanyar masu wa'azi masu tunatarwa.

Al-ghazali ya faɗa a cikin Ihya'u cewa: "Cirantar da wa'azi wanda ake godewa a shari'a cikin waɗannan zamunna, zuwa ga abin da sashen masu wa'azi ke gani a cikin waɗannan zamunna na ƙissoshi suna (kuma) nacewa a kansa yana daga cikin bidi'a, haƙiƙa, hanin (malamai) magabata ya zo a kan zaunawa ga masu ƙissoshi."

(Imamu) Ahmad Ya ce: "Waɗanda suka fi kowa ƙarya su ne masu ƙissoshi da maroƙa, (Sayyidina) Aliyu Allah shi yarda da shi ya fitar da masu ƙissoshi daga cikin masallacin Basarah amma yayin da ya saurari maganar Al-hasan Al-basari sai bai fitar da shi ba domin ya kasance yana magana a kan ilimin lahira da tunatarwa a kan mutuwa da faɗakarwa a kan aibobin rayuwa da aibobin ayyuka da haɗurran shaiɗan da kuma hanyar kariya daga gare su. Haka kuma yana kuma tunatarwa a kan ni'imomin Allah tsarki ya tabbatar maSa da sauran ni'imominSa da taƙaitawar bawa a wajen godiyarSa. Bugu da ƙari, yana kuma sanarwa (a kan) wulaƙantar duniya da ayubbanta da yankewarta da saɓawar alƙawarinta da haɗarin lahira da tsoron da ke cikinta. Haƙiƙa, masu ƙawata ƙissoshi sun riƙi hadisan da ke yabo a kan tunatarwa da wa'azi su zama hujja a kan tsarkake kawunansu, sai suka cirantar da sunan tunatarwa zawa ga ƙaryace-ƙaryacensu. A nan maganar ta ƙare.

Idan ka fahimci wannan dukansa za ka san cewa su ƙissoshi bidi'o'a ne.

Al-ghazali ya faɗa kuma a cikin (littafi) Ihya'u cewa: "Kissoshi da ake godewa suna komawa ne zuwa ga abin da Alƙur'ani ya tattara a kansa ko abin da ya inganta a cikin littattafai ingantattu na daga hadisai, cikin abin da Allah Maɗaukaki da ManzonSa suka ambata akwai wadatarwa daga ƙage a cikin wa'azi.

**47- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Barin Sanya Lulluɓi (Hijabi) Ga Mata Da Cuɗanyar Su Da Maza Da Riƙon Su Da Kabilanci Da Yin Kari A Kan Mata Huɗun Da Kore Maraya Daga Haƙƙinsa Da Wanin Wannan Daga Cikin Ayyukan Saɓo (Zunubi) Cikin Abin Da Malaminsu, Jibrilu, Ya Lisafta Shi A Cikin Ayyukan Kafirci.**

(Sun ce) kafirci ne a kan yankakken hukunci. Wannan shi ma ɓarna ne kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai."

Ya zo a cikin (Littafin) Risa'la ta Abu Muhammad cewa: "Babu wani daga cikin ma'abuta alƙibla (Mai Sallah) da zai kafirta saboda yin zunubi."

Ya zo a a cikin (littafin) Al-kifa'yah wadda Abul Hasan Al-sha'zili ya yi wa sharhin a cikin bayanin ma'anar wannan magana yana nufin Musulunci kamar yadda shi ya faɗa cewa wannan shi ne mazhabar ahlussunnah na farko da na baya.

Idan ka fahimci wannan dukansa, to, ka sani cewa shi, malaminmu Jibrilu, yana aza kafirci ne ga waɗannan ayyukan saɓo a kan babin tsanantawa ba bisa babin haƙƙi ba, abin da ke nuna muku haka shi ne mu'amalarsa tare da ma'abuta waɗancan ayyukan saɓo (zunubi) a cikin babin aure da cin yankansu da wanin wannan daga cikin mu'amaloli domin da ya kafirta su da wannan a kan haƙiƙa, to, da ya hanu daga yin mu'amala da su a cikin wannan. Idan ka fahimci wannan dukansa, to, ka sani cewa duk wanda ya doge a kan waɗannan ayyukan saɓo fasiƙi ne idan bai zama mai halartarwa ba a gare ta amma wanda ya zama mai halattawa a gare ta bayan saninsa da cewa an haramta ta a kan ijma'in (Malamai), to, shi kafiri ne.

Haka wanda ya yi wulakanci da ita shi ne ya aza ta matsayin abubuwan da aka halatta, kamar yadda ga wannan magudana akwai rabe bayani: Idan ya bi da ita mabiyar abubuwan da suke rabe bayani: Idan ya bi da ita mabiyar abubuwan da suke halas saboda wulaƙantar da hanin Allah tsarki ya tabbatar maSa wanda Ya yi a gare ta da kuma yin sassauci da umurninSa, to, shi, kafiri, ne, amma idan ya bi da ita mabiyar abubuwan da aka halatta ta hanyar lura da godewa saboda rinjayar sha'awar rayuwa ba domin wulakanci da hanin Allah ba kuma ba domin sassauci da umurnin Allah ba a'a shi mai girmama ɓangaren Ubangiji ne kuma mai tsoro ne da firgita sai dai shi mai dogewa ne a kanta. To, shi, fasiƙi, ne ke nan ba kafiri ba. Musulmi ba ya zama kafiri saboda saɓo kamar yadda muka gabatar da bayaninsa. Kafiri yana aikata abubuwan da aka hana tare da wulaƙanci da asalin addini da rashin kulawarsa tun asali. Shi, fasiƙi, yana aikata shi tare da wulaƙanci da asalin addini sai dai yana aikata shi aikatawar da take nuna ƙarancin kulawarsa da addini ba rashin wannan batun asali ba.

Haƙiƙa, Shihabuddini Ahmadu ɗan Hajar Al-haitami ya bayyanar da ma'anar abin da muka ambato shi da (bayani) filla – filla a cikin littafin Azzawajiru amma saboda rashin wannan bayani wanda ya yi wahami sai ya yi wahamin a cikin maganar malaminmu, Jibrilu Allah shi yarda da shi, a inda yake ambata kafirta ga wanda ya doge a kan ayyukan saɓo kuma ba ya tuba daga gare ta har abada.

Haƙiƙa, Abdulwahhabu Al-sha'arawi ya yi gaskiya inda ya ce a cikin (littafin) Minanu nasa: Yin (Magana) jumla ce ga mahallin da ke rarrabe kuskure ne.

**48- Yana Daga Cikin Wancan Wahami Cewa: Sashensu Yana Umurtar Yara Da Yin Sallah Amma Bai Umurtar Su Da Yin Alwala Kuma Yana Kudurta Cewa Shi Ya Aikata Alhairi.**

Wannan ɓarna ne kuma wahami ne, a kan haɗuwar malamai, domin umartar su da yin sallah ba tare da alwala ba munkari ne a kan ijma'in malamai.

**49- Yana Daga Cikin Wancan Wahami Cewa: Sashensu Yana Umurtar Bawansa Kafiri Da Yin Sallah Kafin: Ya Umurce Shi Da (Shiga) Musulunci, Kuma Shi Yana Kudurta Cewa Yana Aikata Alhairi Ne.**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai. Umurtar kafiri da yin ibada ba tare da umurtar sa da sharaɗinta ba wanda yake shi ne Musulunci (wannan) munkari ne a kan haɗuwar malami. Ibada ba ta inganta ba tare da shi ba haka kuma ba ta amfanarwa, Saɓanin haninsa daga munkari, cewa shi yana amfaninsa, domin shi (kafiri) idan ya bar aikin saɓo ba za a yi masa azaba ba a lahira kamar yadda (bayani) ya tabbata a cikin usulul fiƙhi.

**50- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Duk Wanda Ke Yin Sallah Ba Tare Da Tsarki Ba Kuma Ba Tare Da Wani Uzuri Na Shari'a Ba Ana Lisafta Shi Cikin Masu Sallah, Kuma Sallarsa Tana Daga Abin Da Ake Koyi Da Shi Domin Shi Yana Aikata Haka Saboda Allah."**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai. Abin da aka rasa a shari'ance kamar abin da aka rasa ne a bayyane (abin da idanu ke gani), kuma abin da ake gani daga gare su na siffar Sallah ba a koyi da shi kuma ba a karɓa domin rashin (cikar) sharaɗinta, *(Manzon Allah) tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:*

(لا تقبل صلاة بغير طهور)

***"Ba a karɓar sallah sai da tsarki"***

Haka kuma (Manzon Allah) tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(لا يقبل الله صلاة من أحدث حتى يتوضأ)

*"Allah ba ya karɓar sallar wanda ya yi hadasi har sai ya yi alwala."*

Haƙiƙa, ijma'in malamai ya haɗu a kan cewa sallolinsu waɗanda suke sallatarta haramun ce kuma ɓatatta ce. Saboda haka al-Akhdhari ya ce: "Sallah ba ta halatta ga wanda ba shi da alwala."

A wurin Sa'ad Attaftazanee a cikin sharhin Al'aƙa'idu cewa: "Yin sallah ba tare da alwala ba yana daga cikin ridda sai dai abin da jamhurin (malamai) suke a kansa shi ne yin ta ba tare da alwala ba saɓo ne, mai yin haka yana samun Zunubi a kan Ittifaƙin malamai kai har ma a ijma'in malamai, kamar yadda Annawawi ya yi hikayarsa."

**51- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Duk Wanda Ya Yi Wankan Janaba Kamar Yadda Allah Ya Umurce Shi Sai Dai Shi Bai Bambantawa Tsakanin Farillai Da Sunnoni Da Mustahabbai Daga Wannan Dukan Sa, Ko Wannan Dukan Sa Bai Inganta A Gare Shi A Kan Ijma'in Malamai."**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai sai dai ma abin da yake daidai kuma a wanda aka dogara a kansa shi ne ingancin wannan dukansa.

Ahmadu Zaruƙ ya faɗa a cikin sharhin Al-wagleesiyyah cewa: "Malamai sun yi saɓani a kan wanda ya zo da Ibada a kan fuska mafi kammala amma bai san farillanta ba daga waninsa ko (ibadar) tana isam masa? Sai (a wani ƙauli) aka ce tana isa domin Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi bai kasance yana tilasta Sahabbansa da wannan ba, a'a har ma ya ce: "*Ku yi sallah kamar yadda kuka ga ina sallah.*" Zuwa wanin wannan, (A wani ƙauli) an ce: Ba ta isar masa saboda Jahiltar sa ga aikinsa, (amma ra'ayi) na farko shi ya fi zama daidai. A nan maganar ta ƙare.

**Na ce:** Idan ka fahimci wannan za ka san cewa da'awar ijma'in malamai a kan lalacewar ibada saboda rashin rarrabewar abin da yake farilla a cikinta da abin da yake Sunna da abin da yake mustahabbi, to, wannan ɓarna ce.

**52- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Sashen Malamai Da Ke Jinkirtar Sallah Daga Lokutanta Da Aka Sani Cewa Suna A Kan Daidai."**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai domin mai shari'a shi ne wanda ya iyakance lokutan sallah, duk wanda ya tsallake iyakarsa, to, shi ɓarna ce kuma ba shi a kan daidai bisa ga ijma'in malamai.

**53- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu A Cikin Shigar Lokutan Sallah A Kan Hisabin Abee Miƙra'i A Cikin Cewarsa: *Dazhu-Jaba-Abadah-Hayyu.* Suna Kudurta Cewa Wannan Ya Game Dukkan Garuruwa Da Kuma Dukan Zamunna.**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai.

Abdulrahman Attajuri ya ce: "Duk wanda ya ayyana wani adadin takon ƙafafu don sanin karkatar rana a cikin kowane wata na Ajami kamar tako irin na Abu Miƙra'i ba ya inganta a yi aiki da wannan, a cikin kowane wuri, a'a wannan ya keɓanta da sashen ƙasashe kamar Marakish, amma Masar da Sham da Hij'az da Yaman da Indiya da Sudan hisabin Abu Miƙra'i wannan ba ya gudana a cikin su." A nan maganar ta ƙare.

**Na ce:** Lallai su zamunna kuma masu canzawa ne ba su dauwama a kan halayya ɗaya.

**54- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Sashen Malamai Wanda Ke Fatawa Da (Halaccin) Kome Ga Wanda Ya Saki Matarsa Saki Uku Kafin (Wani) Miji Cewa Yana Da Madogara Wadda Ake Lura Da Ita A Cikin Wannan Saboda Yawan Iliminsa.**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai."

An tambayi malaminmu, Muhammad ɗan Abdulkarim Attilimisa'nee, game da halatta wadda aka saki uku kafin wani miji sai ya ce: "Duk wanda ya yi fatawa da halaccin wadda aka sake ta saki uku gabanin wani miji, to, shi Jahili ne kuma Dujjal ne mai ɓatarwa, yana wajaba ga duk wanda yake da iko daga cikin Musulmi ya tsawace shi da duk abin da ya samu iko kamar bugu mai raunanarwa da ɗauri mai tsawo da duk abin da ya samu na tsawatarwa. "Duk wanda ya taƙaita a cikin wannan ko ya jawo shi zuwa gare shi ko ya ba shi kariya ta kowace fuska, to, yana tare da shi a cikin zunubi mai girma da azaba mai tsananin zafi. Haka kuma za a yi da matar da mijin wanda shi ne

ya yi saki uku, domin su sun aikata abin da bai, cikin addinin Musulunci, aurensu kuma ɓatacce ne, haddi kuma yana a kansu, sai idan sun kasance jahilai ne sun dogara a kan fatawar Dujjal daga cikin Dujjalai, kuma su ba su sani ba, (Wannan) Auren ana buɗe shi ta kowane hali ko da lokaci ya tsawaita, har ma an haifi 'ya'ya. Bugu da ƙari, mai fatawa da wannan shaiɗani ne mai mummunar manufa, ana neman ya tuba da zare masa takobi, idan har ya ƙi ya tuba sai a buge shi bugu mai raunatarwa a bar shi kuma a tsare har ya mutu. Idan tsare shi ba zai yiwuwa ba ya kasance da an bar shi, to, zai ci gaba a cikin cutarsa, to, kashe shi ya wajaba domin Musulmi su huta daga sharrinsa, addini kuma ya kuɓuta daga jahilcinsa da fasiƙancinsa."

Abul Hasan Karami ya ce: "Wanda duk ke mayar da wadda aka yi wa saki uku a cikin kalma ɗaya ko a cikin kalmomi daban-daban, to, limancinsa ba ya halatta haka shaidarsa kuma ya cancanci azabtarwa saboda abin da ya keta na alfarmar shari'a." A nan maganar ta ƙare.

**Na ce:** Labari ya sadu da mu cewa: (wani daga) sashen malamai ya kasance yana fatawa ga wanda ya saki matarsa saki uku daga cikin jahilai da (halaccin) mayar da ita kafin wani aure, idan aka ce masa; yaya kake aikata wannan alhali kuma ba ya halatta? Sai ya amsa da cewa: "Aurace-auracensu ɓatattu ne tun gabanin haka." Wannan yana daga cikin mafi mamakin abubuwan mamaki ta yaya yake tabbatar da su a kan ɓataccen(Aure) alhali bai umurce su da gyara lamarinsu su ba? A kan ƙaddarta ingancin abin da ya yi da'awar sa?

**55- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: Shi, Ilimin Sufanci, Ba Ya Daga Cikin Farillan Aini Sai Dai Shi Ya Keɓanta Ne Da Waliyyai Ba Tare Da Rarrabewar Bayani Ba.**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai domin Ilimin Sufanci yana a kan kashi biyu:

1- Ilimin sufanci don kyautata ɗabi'u. Wannan farilla ne a kan kowane mukallafi (baligi),
2- Ilimin sufanci don haƙiƙancewa, wannan shi ne wanda ya keɓanta da waliyyai. **Na farko** shi ne ya kasance a kan hanyar al-imam Abu Hamid (Al-Ghazali) da Al-Muha'sibee, da wanda ya tafi a kan wannan, kuma bai kamata a banzatar da shi ba ko kuma a taƙaita a kansa ba tare da aiki da shi ba. **Na biyu** Shi ne halaye da ilimummuka kuma su lamurra ne da suka keɓanta da waɗanda aka keɓance.

Sa'annan kuma kasancewar shi, ilimin sufanci, wanda yake don gyara ɗabi'u ya wajaba a bayar da shi ga kowane mutum amma ilimin sufanci wanda yake don haƙiƙancewa, to, ana taƙaitawa a cikinsa a kan muridai da masana ilimi sai dai (malamai) sun yi saɓani a cikin bayar da shi ga waɗanda ba ma'abutansa ba.

Sai shugaban jama'a (mai suna) Al-Junaidu Allah ya yi masa rahama ya ce: "Ana bayar da shi ga ma'abutansa da waɗanda ba ma'abutansa ba. Shi, Ilimi, shi ne mafi ba da kariyar sashe daga ya sadu da waɗanda ba ma'abutansa ba sai dai shi ya kasance yana amsa wa mai tambaya a bisa gwargwadon tambayarsa, kamar yadda (Malam) Assahrauradee ya ciranto daga gare shi."

**56- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: Yin Uzba (Barin Aure) Da Barin Abin Da Babu Makawa Gare Shi Na Mafarai (Hanyoyin Nema) Yana Daga Cikin Tsari Na Zuhudu (Gudun Duniya).**

Wannan shi ma ɓarna ne kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai.

Assuyuɗee ya ce a cikin sharhin Alkaukab: "Ba ya daga ciki zuhudu yin uzba (barin aure) da barin abin da babu makawa gare shi a'a har ma wannan yana daga cikin Zurfafawa wadda aka yi hani daga gare shi."

**57- Yana Daga Cikin Wancan Wahami; Kudurtawar Sashensu Cewa: "Abin Da Yake Daidai Shi Ne Haɗuwar Mutane Don Karatun Alƙur'ani A Cikin Daren Ashirin Da Bakwai Ga Ramadhan Ko Da Tare Da Abin Da Mutane Suka Saba Da Shi A Cikin Wannan Zamani A Cikin Wannan Daren Na Haɗuwar Maza Da Mata Da Murna Wadda Ta Wuce Wuri A Cikin Karatu Da Jayayya A Cikinta Ta Hanyar Wasa Saboda Kasancewar Wannan Yana Kwaɗaitar Da Yara Ga Yin Koƙari Wajen Haddar Alƙur'ani.**

"Wannan shi ma ɓarna ne kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai. Taruwarsu don karatun Alƙur'ani a kan wannan siffa da aka ambata munkari ne ko da ga haƙƙin yara ne, ko da wannan kuma yana kwaɗaitar da su ga haddar Alƙur'ani, domin su ke nan suna yin ƙoƙari ga haddar Alƙur'ani domin yin murna wadda ta wuce iyaka a cikin karatu da yin jayayya a cikinta ta fuskar alfahari. Wannan kuwa shi ne ainin munkari.

Ya zo a cikin sharhin Al'mufeed cewa: "Ya yi sauna daga abin da sashensu yake aikatawa a cikin daren ashirin da bakwai (ga Ramahan) na yanka kalmomin Alƙur'ani da munafasa da kuma shiga ƙunci irin wanda

tunani bai halartowa tare da shi." Sai kuma ya ce: "Wannan aiki muna neman tsarin Allah (daga gare shi) haramun ne ta fuskoki da yawa."

Ka duba yadda suka haramta wa kawunansu lada mai girma wanda ake neman Lailatul ƙadari saboda shi, wanda shi ne mafi Alhairi daga wata dubu sai suka sanya zunubbai da laifuffuka a wurin wannan Alhairi mai girma da dai waɗannan jahilan sun yi barci a cikin wancan daren da ya fi amintarwa kuma da ya fi kyau a gare su a kan waɗannan abubuwan haram. Maganarsa ta ƙare a taƙaice.

Ya zo a cikin Al-mad'khal cewa: "Ya kamata a gare shi ya nisanci abin da (mutane) suka ƙirƙira na bidi'oi a cikin ƙa'idojinsu don saukar Alƙur'ani su suna cewa: Wane yana saukar Alƙur'ani a cikin dare kaza, sai sashensu ya gitta wannan magana ga sashensu sai wannan ya zama yana zagayawa a tsakaninsu, har wannan ya kasance kamar walimomi ne ake yi, da waɗansu alamomin addini da ake bayyanarwa ba su gushewa suna kamar haka galibi tun daga rabin watan Ramadan har zuwa ƙarshen wata. To ya yi sauna daga irin wannan ga kansa kuma ya hana waninsa daga gare shi domin bai kasance daga cikin aikin waɗanda suka shuɗe ba." Maganarsa ta ƙare.

A cikinsa kuma (Al-madkhal): "Ya kamata a gare shi ya nisanta da kansa ya kuma hana waninsa daga abin da sashensu suka ƙirƙiro na halartowarsu da butoci da waninsu na daga ababen aje ruwa a cikin masallaci a lokacin saukar Alƙur'ani, idan mai karatu ya sauka sai su sha daga wannan ruwan, su kuma koma da su zuwa gidajensu su shayar da su ga iyalansu da wanda suka so domin neman albarka, wannan bidi'a ce ba a cirato ta ba daga wani daga cikin magabata Allah shi yarda da su. Wannan abin da aka ambata bai keɓanta da daren saukar Alƙur'ani ba a'a ya haɗe kowane dare wanda suka aikata haka a cikinsa."

**58- Yana Daga Cikin Wancan Wahami; Kudurtawar Sashensu Cewa: Lallai An Ruwaito Cewa; Annabi Tsira Da Amincin Allah Su Tabbata A Gare Shi Ya Sallaci Wata Salla Lokacin Da Ya Sallama Daga Gare Ta Sai Ya Shimfiɗa Hannuwansa Ya Yi Addu'a Sai Mamu Suka Ce "Ameen" A Kan Addu'arsa, Kuma Ya Jiyar Da Duk Mai Saurare A Kan Wannan Kamar Yadda Aka Sani Kuma Yadda Aka Saba A Yau A Cikin Waɗannan Zamunna.**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai, domin da an ruwaito cewa shi, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya aikata haka a yanke, to, da malaman sunna Allah shi yarda da su ba su yi

saɓani ba a cikin wannan. Sashensu ya ce “wannan bidi'a ce makaruhiya”, sashensu ya ce “mustahabbiya”, Sashensu ya ce “wadda aka kyutata.”

Ya zo a cikin Umdatul mureed Assa'diƙ: Sashen malamai sun ce “Bidi’a ce mustahabbiya, abin da yake asali shi ne kowane ɗaya ya yi addu’a ga kansa. Ya zo a cikin Al’minhaj Al’muntakhab:

### Faɗakarwa

Ka sani akwai saɓani wanda ake samu a cikin addu’a cikin jam’i a ƙarshen sallah.

An ce “An hana idan an jingina gare ta, haƙiƙa, an ji cewa wannan mai kyawo ne idan ba a jingina ba.”

Ya zo a cikin sharhinsa na Ahmad ɗan Aliyu ɗan Abdulrahman AlManjuree: An tambayi Izuddini game da addu’a a kan wannan siffa wadda aka saba da ita a yau bayan sallama, sai ya amsa da cewa: “Manzon Allah mai tsira da amincin Allah ya kasance yana zuwa da zikirori waɗanda aka shar’anta bayan sallama, sai kuma ya yi istigfa'ri sau uku sai ya juya ya fita. Alhairi dukansa yana a cikin biyar Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi.”

Ya zo kuma a cikin sharhin da aka ambata: An tambayi sashen waɗanda suka zo daga baya cikin malaman (ƙasar) Tunas, nassin tambayar shi ne: Me za ka ce game da yin addu’a bayan salla, jama’a suna cewa “Ameen” kamar yadda yake al’adar mutane a cikin garuruwa, ko sunna ne ko kuma bidi’a ce wadda aka kyautata?

Sai ya amsa wa mai tambaya da cewarsa: “Addu’a bayan sallah a kan fuskar da ka ambata bidi’a ce.”

Al-ƙarrafee ya ambata a cikin takardar ƙarshe daga (littafin) Al-ƙawa’idu cewa (imamu) Malik ya karhanta wannan, kuma haƙiƙa wannan mas’ala ta auku kamar yadda yake a cikin sharhin da ambatonsa ya gabata a ƙasar Fass kuma malamansu suka yi saɓani a cikinta.

Ya zo Kuma a cikin sharhin da ambatonsa ya gabata cewa wannan an yanke aikata shi a babban masallaci a ƙasar Tilimisana lokaci mai tsawo sai kuma sabawa ta rinjaya jama’a kuma suka aibanta wannan yankewa, sai lamari a cikin wannan ya sake dawowa zuwa ga al-a'da. A nan ya ƙare.

Sheikh Abu Is'haƙ Ashshaɗibee ya ce: Bidi'a ne lizimtar yin addu'a ƙarshen salla a kan siffar taron jama'a, har ta kai sashen waɗansu ma'abutanta zuwa cewa barinta mai wajabtar da kisa ne a wurinsa. A nan ya ƙare.

**Na ce:** Haƙiƙa Al-ƙadhee Abul Khaɗɗabi ya hakaito hikaya mai ban mamaki a cikin wannan daga Abu Abdullahi ɗan Mujahid Al'abid.

Ya zo a cikin Al'madhal na Ibnil Ha'jj cewa: "Ba a ruwaito ba cewa Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya sallaci wata salla ya sallama daga gareta ya shimfiɗa hannuwansa ya yi Addu'a mamu suka ce "amen" a kan addu'arsa, haka nan khulafa'u Arrashidina bayansa Allah shi yarda da su. Haka nan sauran Sahabbai Allah shi yarda da su gaba ɗaya, kuma duk wani abu wanda Annabi bai aikata ba haka ɗaya daga cikin Sahabbansa babu shakka cewa barinsa ya fi bisa ga aikata shi har ma shi bidi'a ne.

Idan ka fahimci wannan za ka salalewar abin da suka riyanta.

**59- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Mayarwar Sashensu Ma'anar Kasawa Daga Riƙon Sabubba(Hanyoyin Nema) Cewa Shi Ne Ma'anar Tawakkali.**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai, domin shi, tawakkali, shi ne amincewar zuciya da Allah saboda saninta a kan isarSa, da kyakkwan zaɓinSa ga bawanSa ko da tare da tsayuwarsa da mafarai (hanyoyin nema) wadda aka yi umurni da ita, da ƙoƙarinsa ga tabbatar da ita, kasawa kuwa ita ce watsi da lamurran biyu duka ko ɗayansu, ko dai ya yi watsi da mafari saboda kasawa daga gare shi sai ya riyanta cewa wannan tawakkali ne sai dai shi kasawa ne ko kuma ya tsayu da mafarai yana mai duba gare shi yana mai dogara a kansa ya zama marabkani daga Mai fararwa (Allah).

**60- Yana Daga Cikin Wancan Wahami; Mayarwar Sashensu Ma'anar Ta'anibi Zuwa Ga Ma'anar Nasiha.**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai domin abin da ake nufi da nasiha shi ne kyautatawa zuwa ga wanda ake yi wa nasiha, wanda ya fito ne daga tausayi da rahama da tausasawa, Shi kuma ta'anibi abin da ake nufi da shi shi ne: Aibantawa da wulaƙantawa da zagi cikin kama irin ta nasiha.

**61- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Mayarwar Sashensu Ma'anar Son Shugabanci Zuwa Ga Ma'anar Son Kira Zuwa Ga Allah.**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai, domin son kira zuwa ga Allah (da'awa) abin da ake nufi da shi shi ne: Girmama Allah da son yi maSa ɗa'a da kishi a kan addinin, shi kuma son shugabanci abin da ake nufi da shi shi ne: Ma'abucinsa ya kasance mai girma ga idanun jama'a kuma mai kwarjini a cikin zukatansa.

**62- Yana Daga Cikin Wancan Wahami; Mayarwar Sashensu Ma'anar Guluwwu(Wuce Wuri) Zuwa Ga Ma'anar Jjtihadi.**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai. Ijthadi shi ne: Sanya ƙoƙari a wajen dacewa da Umuwni. Guluwwi kuma shi ne: Tsallake umurni da wuce wuri.

**63- Yana Daga Cikin Wancan Wahami; Mayarwar Sashensu Ma'anar (Azzullu) Wulaƙanci Zuwa Ga Ma'anar Afuwa.**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai. Ita, afuwa, ita ce kayar da haƙƙi saboda baiwa da karimci tare da samun iko a kan ramuwa, shi kuma wulaƙanci shi ne barin ramuwa saboda kasawa da tsoro da wulaƙanci.

**64- Yana Daga Cikin Wancan Wahami; Mayarwar Sashensu Ma'anar Ɗemuwa (Teehu) Zuwa Ga Ma'anar Ɗaukakar Rayuwa.**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai, domin shi, ɗaukakar rayuwa, shi ne kiyaye ta daga wulaƙanta da munanan ɗabi'u da ƙwaɗayi wadda ke yankewa yayin mazaje, ita, ɗemuwa, tana komawa zuwa ga ji da kansa da wulaƙantar da waninsa.

**65- Yana Daga Cikin Wancan Wahami; Mayarwar Sashensu Ma'anar Kiyayya (Hiƙdu) Zuwa Ga Ma'anar Damuwa.**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai, domin shi, kaɗaitar rayuwa, don kawar da shi, kuma shi mai saurin gushewa ne, amma shi, hiƙidu (ƙiyayya), shi ne ɓoyewar sharri da hasashensa a cikin kowane lokaci, kuma shi mai jinkirin gushewa ne.

**66- Yana Daga Cikin Wancan Wahami; Mayarwar Sashensu Ma'anar Ɓarna (Assarfu) Zuwa Ga Ma'anar Kyauta (Al-Ju'd).**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai. Kyauta ita ce bayarwar mai bayarwa inda shari'a ta umurce shi, ɓarna kuwa ita ce bayarwarsa inda shari'a ta hana shi.

**67- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Mayarwar Sashensu Ma'anar Girman Kai (Al-Kibru) Zuwa Ga Ma'anar (Haiba) Kwarjini.**

Domin haiba ita ce: Kyawawan kawaici da natsuwa waɗanda suka sauka ga abin da ke bayyane saboda cikar abin da ke ɓoye da girman Allah da ƙaunarSa da girmama Shi. Shi, girman kai kuwa, yana faruwa ne daga ji-da-kai da zalunci da cikar zuciya da jahilci da kuma duhu.

**68- Yana Daga Cikin Wancan Wahami; Mayarwar Sashensu Ma'anar Wulaƙanci (Mahanah) Zuwa Ga Ma'anar Tawali'u (Kanƙan Da Kai).**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai, domin shi, tawali'u, yana faruwa ne daga sanin Allah da sanin siffofinSa da siffofin girmanSa da sanin bawa ga rayuwarsa da naƙasarta da aiboban aikinsa da ayubbansa suka haifar da karayar zuciya don Allah da sassauta fiffiken ƙasƙanta ga bayinSa ba ya ganin yana da fifiko a kan wani, ba ya ganin yana da haƙƙi a kan wani, shi, wulaƙanci (mahana), shi ne naƙasa da jefar da kai da ba da rayuwa wajen samun rabonta da sahawarta, da wulaƙantawar ga iya iyan duniya domin abin da yake nema gare su na Lisani ko biyan buƙata.

**69- Yana Daga Cikin Wancan Wahami; Mayarwar Sashensu Ma'anar Munanan Zato (Su'u Azzanni) Zuwa Ga Ma'anar Kariya (Al-Ihtizaz).**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai domin ita, kariya (Al-'ihtiraz), ita ce yin tanadi da tattali ta hanyar riƙo da mafarai wadda da ita yake kuɓuta daga abin ƙi. Shi kuma munanan zato shi ne cikar zuciya da munanan zato ga mutane har ya bayyana a kan harshensa ta hanyar sukar su.

**70- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Mayarwar Sashensu Ma'anar Haƙiƙanin Guri (Tamanni) Zuwa Ga Ma'anar Raja'i.**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai, domin shi, raja'i, shi ne abin da ake jinginawa zuwa ga mafari, shi kuwa tamanni (guri) ba ya jingina zuwa gare shi.

**71- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Mayarwar Sashensu Ma'anar (Al-Jaza'u) Raki Zuwa Ga Ma'anar (Arriƙƙah) Sassautawa.**

Wannan ita ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai domin sassautawa tana faruwa ne daga sauƙaƙawa da tausayi; shi kuma raki yana faruwa daga raunin zuciya da karayar zuciya wanda ke faruwa daga raunin imani da tsananin kwaɗayinsa da sha'awarsa.

**72- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Mayarwar Sashensu Ma'anar Bushewar Zuciya (Al'ƙasawah) Zuwa Ga Ma'anar Haƙuri.**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai, domin haƙuri shi ne kange zuciya daga raki da tsoro da yawan koke (kai ƙara) da tsayar da rayuwa a kan hukunce -hukuncen ƙaddara na shari'a kuma bushewar zuciya (ƙasawah) shi ne wani kaushin zuciya ne da yake hana zuciya tasiri ga abubuwan da ke sauka (na musiba) saboda kaushinta ba don haƙurinsa da jurewarsa ba.

**73- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Mayarwar Sashensu Ma'anar Rashawa Zuwa Ga Ma'anar Kyauta.**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai saboda kyauta ita ce: Abin da ake bayarwa da nufin jawo soyayya, ita, rashawa kuwa, ita ce abin da ake bayarwa da nufin lalata gaskiya ko tabbatar da ɓarna.

**74- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Mayarwar Sashensu Ma'anar Koke (Shakawa) Zuwa Ga Ma'anar Ambaton Halayya.**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai, domin ambaton halayya, ana yinsa da nufin kawar da shi ga wanda yake da iko a kansa, ko kafa uzuri daga wani lamari da aka nema daga gare shi ko tsawatarwa daga aukawa cikin irin abin da ya auka cikinsa, ko ɗauka a kan haƙuri ta hanyar koyi da shi, ita kuma shakawa ita ce abin da ake nufin a yi hushi da shi da kai ƙarar wanda Ya aza (musiba) zuwa ga waninSa.

**75- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Mayarwar Sashensu Ma'anar (Balaha Al-Kƙlbu) Shi Ne Zuciyar Da Babu Komi Cikinta Zuwa Ga Ma'anar Kuɓutarsa.**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai domin salamar zuciya shi ne barrantarsa daga nufin sharri bayan saninsa, shi kuma (balahu) shi ne jahilci da ƙarancin saninsa.

Haƙiƙa, malamai sun faɗa a cikin hadisin Albazzar "Mafi yawan 'yan aljanna su ne Al-Balah" Mai ƙarancin sani, suka ce wannan cikin lamurran duniya ba a cikin lamurran lahira ba, domin su kam a cikin (lamarinta) masu hankali ne.

**76- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Mayarwar Sashensu Ma'anar (Alfakharu) Zuwa Ga Ma'anar Godiya (Ash-Shukru).**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai, saboda godiya ana nufin ita ce bayyanar da falalar Allah da kyautatawarSa da yabonSa da kyautata yabo a gare Shi da tura zuciya a kan nema gare Shi ba ga waninSa ba da kuma a kan raja'inSa, sai ya kasance mai kira zuwa ga Allah da (yin) wannan, shi kuma (Alfakhariu) ana nufi da shi. "Nuna fifiko a kan mutane da bayyanawar cewa shi ya fi ɗaukaka bisa gare su kuma ya fi girma da bautar da zukatansu da karkatar da ita da girmamawa da yin hidima, a kan waɗannan lamurran da ambaton su ya gabata, Abdulrahman Assuyuɗee ya yi ishara cikin ƙarshen Al-kaukabu nasa da cewarsa:

Mutum mai buƙata ne ya san bambancin lamurra da suka ɓoyu cikin rarrabuwarsu. Kamar bambanci tsakanin kasawa da tawakkali da so ga Allah mai bayyana tare da shi da nasiha da komawa (ga Allah) da firasa da zato da da'awa da shugabanci da ƙarfi a cikin lamurran addini da nuna ɗaukaka da yin ƙoƙari a cikin biyar (sunna) da wuce iyaka da ƙasƙanci da yafewa da ɗimauta da ɗaukaka da godiya da damuwa da kyauta da ɓarna (Almubazzaranci) da girman kai da haiba, da wulakanta da tawali'u da girman kai da tsare mutumci, da kange rayuwa (taka-tsantsan) tare da mummunan zato. Haka ma raja'i da guri, da sauƙin hali da raki da bushewar zuciya da haƙuri da kyauta da rashawa, da ambatonsa ga halayya da kuma shakawa da kakkaɓewar zuciya da kuma aminta, da amincewa da kuma nuna ɗaukaka da godiya da alfahari ta hanya ambaton abin da Yake bayarwa kyauta.

**77- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Cewa: Sashensu Hasaɗa Tana Makantar Da Shi Sai Ya Ce: Abin Da Yake Daidai Shi Ne Barin Shagaltuwa Da Wallafa Littattafai A Yau Domin Wallafe – Wallafen Malamai Mashahurai Waɗanda Suka Gabata Ba Su Bar Komi Ba Wanda Ake Buƙata Zuwa Gare Shi, Kuma Su Ne Mafi Cikakken Ilimin A Kan Waɗanda Ke Wallafe-Wallafe A Yau.**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai domin kowane malami yana lura da himmomin mutanen zamaninsa a cikin wallafarsa da kuma manufofinsu domin shi ne masani ga wannan saboda haka wallafar kowane malami a zamaninsa ya kasance mafi amfani ga mutanen wannan zamani a kan wallafar waninsa. Saboda haka Muhammad Assalihu ɗan Abdulrahman ɗan Sulaim Al-aujali ya ce a cikin (littafin) Daleelul ƙa'idi:

“Ba mu samu wani (Mukhtasar) ba wanda ke rabbanta da abin da yake da wadatarwa wanda kuma ya tara komi.’

Ya kuma faɗa a cikin sharhin Mazeedul A-idi a cikin bayanin ma’anar wannan baiti cewa; “Mai son ya faɗa yana iya ya faɗa cewa (mukhtasirai) waɗanda suna wadatarwa daga wannan ƙage – ƙage suna da yawa daga cikin wallafe – wallafen manyan malamai wanda ba a daidaita ko da da sawun ƙafafunsu a cikin matsayin daraja.” To sai a ce masu: Naam! Lallai su Allah shi yarda da su Shi saka musu da alkhairi sun aikata abin da yake dacewa da zamunnansu da suka kai ƙoli (a wajen ɗaukaka).” A nan ya ƙare.

Madalla da mai magana da yake cewa:

“Kowane malami a cikin kowane zamani mai wallafawa da waninsa duka masu hankali ne.”

**78- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: “Barin Cuɗanya Da Mutane Shi Ne Ya Fi Ga Kowane Mutum Ɗaya.”**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai, domin cuɗanya da su ga wanda ke iya haƙuri a kan cutawarsu ya kuma kuɓuta daga aibobinsu ya fi alhairi a kan barin yin haka saboda faɗarsa tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi:

(المؤمن الذي يخالط الناس ويصبر على أذاهم خير من المؤمن الذي لا يخالط الناس ولا يصبر على أذاهم)

***"Mumini wanda ke cuɗanya da mutane yana kuma haƙuri a kan cutawarsu ya fi Alhairi a kan mumini wanda bai cuɗanya da mutane bai kuma haƙuri a kan cutawarsu."***

Amma wanda ke haƙuri a kan cutawarsu sai dai ba ya kuɓuta daga ayubbansu idan ya cuɗanya da su, to, abin da ya fi a gare shi shi ne ya nisanta, kuma a kan wannan ra'ayi ne ake ɗaukar faɗarsa tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ga Uƙubatu ɗan Amir bayan ya tambaye shi, sai ya ce: Mene ne mafita? Sai ya ce masa:

(أمسك عليك لسانك)

***"Ka kame harshenka gareka."***

Abdulrahman Assuyuɗi ne ya faɗe shi a cikin (Littafin) Itma'mu Addra'yah sharhin Anniƙa'yah.

A cikin sharhin Al-kaukabu na Assuyuɗee kuma Al-khaɗɗa'bee ya ce: "Da a ce babu abin da yake a cikin nisanta(uzulah) sai kuɓuta daga giba da ganin munkari wanda bai samun iko a kan kawar da shi da wannan ya zama alhairi mai yawa.

**79- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: Maganar (Imam) Ashshafi-I Allah Shi Yarda Da Shi Cewa: "Duk Wanda Aka Nemi A Fusatar Da Shi Sai Bai Yi Fushi Ba, To, Shi Jaki Ne)." Wannan Yabo Ne A Kan Kowane Irin Fushi.**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai, a'a sai dai maganarsa ta keɓanta ne da abin da ake gode wa yin fushi a cikinsa, kamar yin fushi a lokacin ganin ayyukan munkari da keta hurumi (tsallaka iyakokin Allah), bai kamata a ɗora maganarsa a kan abin da ba a gode wa yin fushi a cikinsa ba saboda kawai ƙiyayya ta jahiliyya da sauran buƙatun zuciya.

**80- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: Sharuɗɗan Fassara Alƙur'ani A Kan Hanyar Ijtihadi Ana Sharɗanta Su A Kan Wanda Ke Fassara Shi Ta Hanyar Hikaya.**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai, abin da ya kai su zuwa ga wannan wahami shi ne rashin sanin bambanci tsakanin mai fassara da mai hikaya. Sharuɗɗan mai fassara, ilimummuka goma sha biyar ne kamar yadda Abdulrahman Assuyuɗee ya faɗa a cikin Al'itƙa'nu su ne: Sanin Luga (Larabci) da nahawu da sarfu da al-ishtiƙa'ƙi da alma'aa'ni da al-bayan da albadi'u da ilimummukan ƙira'a da usuluddini da usulul fiƙhi da asbabu annuzul da ƙisas da nasikhu da mansukhi da fiƙhu da ilimin mauhiba. A nan ya ƙare.

Waɗannan sharuɗɗa na mai fassara ne ta hanyar ijtiha'di, ba a sharɗanta su ba ga wanda ke fassara shi ta hanyar hikaya.

Ya zo a cikin (Littafin) Unwanul Hikami cewa: "Ba ya halatta a fassara Alƙur'ani ga wani sai da (Ilimin) nahawu da luga, wannan hani ne ga wanda ke fassara shi ta hanyar ijtihadi, amma hana yin hikaya bidi'a ne." A nan ya ƙare.

**Na ce:** Ba malami ɗaya ba daga cikin malaman sunna sun ambata cewa: Hikaya ta halatta ba tare da saɓani ba, ko ga wanda bai san ilimin nahawu da luga ba idan mai fassara ya kasance mai tantancewa ne. Shi, ɗalibi, yana hikaya ne amma ba ya ƙara wani abu a kan gwargwadon abin da ya ji, abin da ake nufi da wancan ƙari wanda aka hana ga mai hikaya kamar yadda Abullaisi ya bayyana shi ne ya fitar da hukunci ko dalilin hukunci daga Aya ta hanyar ijtihadi da istimbaɗi kamar yadda mai fassara mujtahidi yake aikatawa.

Abullais ya ce: "Bai halatta ba yin tafsiri ga wanda bai zama hujja ba wadda ta kai matuƙa, idan kuwa har ya zama kamar haka nan, to, ya halatta ga wanda ya san Lugogin Larabawa, da dalilan saukar ayoyi ya fassara shi, amma wanda bai san fuskokin luga ba ba ya halatta ya fassara shi sai da gwargwadon abin da ya ji. Wannan ya zama ta fuskar hikaya ba ta fuskar tafsiri ba, da dai shi ya san tafisiri sai ya nufi ya fitar da hukunci daga Aya ko wani dalili, to, babu laifi a gare shi, da dai ya ce: "Manufa ita ce kaza ba tare da ya ji wani abu a cikinsa, to, ba ya halatta, kuma wannan shi ne aka yi hani daga gare shi." Maganar Abullaisi ta ƙare.

Haƙiƙa, Abdulrahman Assuyuɗi ya zo da ita a cikin Al'itƙan, a cikin nau'i na saba'in da takwas, ka duba a can.

### 81- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: Tafsirin Alƙur'ani Ba Ya Halatta Domin Shi Ne Dalilin Samun Fari Da Fitinoni.

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai. Haƙiƙa, ba malami ɗaya ba daga cikin malaman sunna sun bayyana cewa duk wanda ya ƙudurta wannan, to, shi, kafiri, ne wanda ya yi ridda daga addinin Musulunci, ana neman ya tuba idan har ya tuba (shi ke nan) amma idan bai tuba ba sai a kashe shi kuma ba a yi masa jinkiri ko da da ƙyaftawar idanu.

### 82- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: Fassara Alƙur'ani Ya Halatta Sai Dai Mu Ba Mu Cimma Fahimtar Haƙiƙaninsa.

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai.

Abdulrahman Assuyuɗee ya ce a cikin Al'itƙani: Ɗan Abbas ya ce: "Tafsiri fuska huɗu ce: Wata fuska Larabawa sun san ta daga maganarsu da tafsiri wanda ba a yi wa kowa uzuri a kan jahiltarsa da tafsirin da malamai su suka san shi da tafsirin da babu wanda ya san shi sai Allah."

### 83- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: Yana Halatta A Fassara Alƙur'ani Sai Dai A Cikin Daji Ba A Cikin Birane Ba.

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai, Shi, Alƙur'ani, ba a saukar da shi ba saboda dabbobin daji, kuma ya ce shi ba a fassara shi sai a cikin daji a'a lallai shi an saukar da shi saboda mutane, (Allah) Maɗaukaki ya ce:

﴿ إِنَّآ أَنزَلْنَآ إِلَيْكَ ٱلْكِتَٰبَ بِٱلْحَقِّ لِتَحْكُمَ بَيْنَ ٱلنَّاسِ بِمَآ أَرَىٰكَ ٱللَّهُ ﴾النساء: ١٠٥

***"Lallai Mu Mun saukar da littafi zuwa gare ka domin ka yi hukunci a tsakanin mutane da abin da Allah ya nuna maka" Annisa'u: 105***

Kuma (Allah) Maɗaukakin Sarki Ya ce:

﴿ وَمَآ أَنزَلْنَا عَلَيْكَ ٱلْكِتَٰبَ إِلَّا لِتُبَيِّنَ لَهُمُ ٱلَّذِى ٱخْتَلَفُوا۟ فِيهِ ﴾النحل: ٦٤

*"Ba Mu saukar da littafi a gare ka face sai don ka bayyana musu abin nan da suka yi saɓani a cikinsa" Annahli: 64.*

**84- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: Yana Halatta A Fassara Alƙur'ani Sai Dai Ga Tsoho Ba Ga Saurayi Ba.**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai domin fuskantar da hukunce – hukuncen Alƙur'ani ga tsoho da saurayi duka ɗaya ne.

**85- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa, Ba Ya Halatta Ga Mai Wa'azi Ya Tunatar Da Ayoyin Alƙur'ani.**

Wannan shi ma ɓarna ne kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai. Wannan yana daga cikin mafi ban mamakin abubuwan mamaki, domin shi akasi ne na abin da Allah Maɗaukaki ya yi umurni da shi a cikin Alƙur'ani, (Allah) Maɗaukaki ya ce:

﴿ فَذَكِّرْ بِالْقُرْآنِ مَن يَخَافُ وَعِيدِ ﴾ ق: ٤٥

*"Ka tunatar da Alƙur'ani ga wanda ke tsoron ƙyacewata" Ka'f: 45.*

Kuma (Allah) Maɗaukaki ya ce:

﴿ وَأَنذِرْ بِهِ الَّذِينَ يَخَافُونَ أَن يُحْشَرُوا إِلَىٰ رَبِّهِمْ ﴾ الأنعام: ٥١

*"Ka yi gargaɗi da shi ga waɗanda ke jin tsoron a tara su zuwa ga Ubangijinsu" Al'an'am: 51*

Idan sun ce lalle hukunce – hukuncen Alƙur'ani suna fuskanta ne zuwa ga mutanen zamaninsa tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi kaɗai, sai mu ce: "Wannan shi ma ɓarna ne yanke, domin shi, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, Manzo ne zuwa ga dukkan al'umma har zuwa ranar alƙiyama a kan ijma'in (Malamai). Hukunce – hukuncen Alƙur'ani masu fuskanta ne zuwa ga dukkanta. (Allah) Maɗaukaki Ya ce:

﴿ وَمَا أَرْسَلْنَاكَ إِلَّا كَافَّةً لِّلنَّاسِ ﴾ سبأ: ٢٨

*"Ba Mu aiko ka ba face ga mutane baki ɗaya" Saba'i 28.*

Kuma (Allah) Maɗaukaki Ya ce:

﴿ قُلْ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ إِنِّى رَسُولُ ٱللَّهِ إِلَيْكُمْ جَمِيعًا ﴾ الأعراف: ١٥٨

*"Ka ce ya ku mutane ni Manzon Allah ne zuwa gare ku baki ɗaya" Al'araf" 158.*

Kuma (Allah) Maɗaukaki Ya ce:

﴿ وَكَذَٰلِكَ أَوْحَيْنَآ إِلَيْكَ قُرْءَانًا عَرَبِيًّا لِّتُنذِرَ أُمَّ ٱلْقُرَىٰ وَمَنْ حَوْلَهَا ﴾ الشورى: ٧

*"Kamar haka Muka yi wahayi zuwa gare ka Alƙur'ani na Larabci domin ka yi gargaɗi ga uwar alƙaryu da waɗanda ke gefenta" Al'shura: 7*

Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿ قُلْ أَىُّ شَىْءٍ أَكْبَرُ شَهَٰدَةً ۖ قُلِ ٱللَّهُ ۖ شَهِيدٌۢ بَيْنِى وَبَيْنَكُمْ ۚ وَأُوحِىَ إِلَىَّ هَٰذَا ٱلْقُرْءَانُ لِأُنذِرَكُم بِهِۦ وَمَنۢ بَلَغَ ﴾ الأنعام: ١٩

*"Ka ce wane abu ne mafi girman shaida?" Ka ce "Allah ne, kuma Shi Mai shaida'ne a tsakanina da ku kuma an yi mini wahayin wannan Alƙur'ani domin in yi gargadi da shi da duk wanda wannan saƙo ya sadu da shi" Al-an'am:19*

Mu muna daga cikin waɗanda saƙo ya sadu da su.

Haƙiƙa, Al-ghazali ya lisafta nau'uka waɗanda mai wa'azi zai tunatar da su a cikin (littafinsa na) Ihya-u ya faɗa a farkonsu cewa: Ya tunatar a cikin abin da yake cikin Alƙur'ani na Ayoyi masu tsoratarwa da kuma hadisan Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ka dubi sauransu a can.

**86- Yana Daga Cikin Wancan Wahami Cewa: A Wajen Neman Shiriya, Sashensu Yana Kula Ne Da Maganar Malaman Tauhidi Kawai A Cikin Tauhidi, Amma A Cikin Wannan Ba Ya Kula Da Abin Da Ake Ambata Masa A Cikin Tafsirin Alƙur'ani.**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai saboda faɗar Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi:

(من تركه من جبار قصمه الله ومن ابتغى في غيره أضله الله)

***"Wanda ya bar shi saboda taurin kai Allah zai karya shi, kuma wanda ya nemi shiriya daga waninsa Allah zai ɓatar da shi."*** Har zuwa ƙarshen Hadisi.

Da kuma faɗarsa tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi.

(كفى بقوم حمقًا أو ضلالاً أن يرغبوا عما جاء به نبيهم إلى غير نبيهم أو كتاب غير كتابهم)

***"Ya isa ya zama wauta ko ɓata ga waɗansu mutane su yi ƙiyayya da abin da annabinsu ya zo da shi zuwa ga wanin annabinsu ko littafi wanin littafinsu."***

Ya zo a cikin (Littafin) Aƙeedatu Ashshaiba'ni: Sai dai Alƙur'ani ne muke shiryarwa kuma muke neman shiriya. Haƙiƙa, bawa wanda ya nemi shiriya da Alƙur'ani ya samu rabo.

Sheikh Assunusee ya ce a cikin sharhin Alƙasidah Aljaza'iriyya a cikin yabon bayyanar dalilan Alƙur'ani: Mene ne ya kai Albarkarsu ga hanya? Mene ne ya kai nasiharsu ga nunawarsu (ga gaskiya)? Saboda sun ƙunshi shiriya ta gaɓa ɗaya da samun abin nema ga dukan wanda aka yi wa muwafaƙa wanda yake neman saduwa zuwa ga gaskiya.

Ya kuma faɗa a cikin sharhin da aka ambata cewa: "Dalilan Alƙur'ani Maɗaukaka ne a kan mafi ɗaukakar darajar bayyana ta yadda makaho ya yi kusa ya gan su ba domin abin da ya rigaya ba na hukunci da kuma ƙudura."

Ya kuma faɗa a cikin sharhin da aka ambata a wurin faɗar mai tsara waƙa: Babu dalili a kan tauhidi wanda bai ambata ba (sai kuma ya ce): Babu wani dalili daga cikin dalilan aƙidojin tauhidi face an faɗe shi kuma an bayyana shi a cikin Alƙur'ani da Sunna ta fuskokin bayani masu yawa ta

yadda wawa da mai basira da mai ƙarfi da raunana za su daidaita a cikin fahimtarsu.

**87- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: Samun Izini (Ijaza) Daga Malamai Ba Sharaɗi Ba Ne A Cikin Halaccin Kafuwa Ga Aikin Karantarwa Da Fa'idantarwa Ta Hanyar Koyar Da Kowane Fanni Daga Cikin Fannonin Ilimi Da Yin Fatawa.**

Wannan shi ma ɓarna ne kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai.

Abdulrahman Assuyuɗi ya faɗa a cikin (littafin) Al-itƙanu cewa: "Samun izini (Ija'za) daga malami ba sharaɗi ba ne ga halaccin kafuwa don karantarwa da fa'idantarwa, duk wanda ya san cancanta ga kansa wannan ya halatta gare shi ko da wani bai ba shi izini ba (Ija'za), a kan wannan ne magabatan farko da zamanin salihai suke, haka nan a cikin kowane ilimi ga karantarwa da fatawa, saɓanin yadda wawaye suke yin wahami na ƙudurta kasancewarta sharaɗi. Mutane sun tafi a kan ijaza ne saboda cancantar mutum galibin wanda ke son a karɓa daga gare shi daga cikin 'yan bidi'ah da ire-irensu ba ya saninta saboda taƙaitar matsayinsu ga haka, yin bincike game da cancanta kafin a karɓa sharaɗi ne sai aka sanya ijaza ta zama kamar shaida daga malami wanda ke ba da izini (ijaza) a kan cancanta." A nan ya ƙare.

**88- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: Abin Da Aka Cirato Daga Malamansu Na Kuskure Bayyananne A Cikin Karatu (Na Alƙur'ani) Kamar Musanya Alif Da Ya'un A Wajen (Kalmar) {آمنتم} Da {آلهتنا} Da Wanin Wannan Daga Cikin Abin Da Suke Yin Kuskure A Cikin Karatu Cewa Daidai Ne Domin Sun Yi Kuskure Ne Don Suna Neman Dacewa Da Kira'ar Nafi'u.**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai, domin abin da aka cirato daga gare su na wannan kure bayyananne. Babu madogara gare shi a cikin maganar Larabawa, a'a da ma a ce wannan yana da madogara a cikin maganar Larabawa (duk da haka) da yin karatun Alƙur'ani da wannan bai halatta ba domin ita, ƙira'ah tauƙifiyya, ce (ta tsaya ne kawai daga abin da aka cirato daga mai shari'a (S.A.W.) hanyarta shi ne abin da aka cirato babu ƙofa ga maganar ra'ayi a cikinta.

**89- Yana Daga Cikin Wancan Wahami Cewa: Sashensu Yana Korewar Cewa: Allah Yana Buɗi (Fatahi) Ga Wani Daga Cikin Mutanen Karshe Irin Abin Da Bai Yi Buɗinsa Ba Ga Waɗanda Suka Gabata Daga Cikin Malamansu A Cikin Babin Ilimi.**

Wannnan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai, domin ba a faɗar irin wannan ga falalar Allah (wadda Ya yi) a gare ku, domin falalar Allah Maɗaukaki ba ta keɓantuwa da zamunna da kuma wurare, Shi, Maɗaukaki, Mai iko ne a kan komai ta yaya ake nisanta wannan.

Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿إِنَّ ٱلۡفَضۡلَ بِيَدِ ٱللَّهِ يُؤۡتِيهِ مَن يَشَآءُ﴾ آل عمران: ٧٣

*"Lallai falala tana hannun Allah Yana bayar da ita ga wanda Yake so" Ali-Imra'n: 73*

Kuma Allah Maɗaukaki ya ce:

﴿يَخۡتَصُّ بِرَحۡمَتِهِۦ مَن يَشَآءُ﴾ آل عمران: ٧٤

*"Yana keɓance wanda Ya so da rahamarSa kuma Allah Ma'abucin baiwa ne Mai girma" A-lu imran: 74.*

**90- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Barin Mu'ahadah (Yawan Maimaitawar) Karatun Lafuzzan Alƙur'ani Wanda Aka Haddace Saboda Neman Ilimin Farillan Aini Daga Ilimi (Suna Cewa Yin Haka) Daidai Ne Kuma Uzuri Ne Na Shari'a.**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai." Shihabuddini Ahmad ɗan Hajaril Haitami ya ce: "Al-ƙurɗubi ya ce: "Barin maimaita karatun Alƙur'ani yana kaiwa zuwa ga jahilci." A nan ya ƙare.

**Na ce:** Haƙiƙa, an lisafta mantawar lafuzzansa waɗanda aka haddace cewa kaba'ira ne ko da Ayah (ɗaya) a'a kai ko da harafi, kamar yadda Arra'fi'i ya tafi a kansa da Annawawi da waninsu.

Aljala'i Al-balƙeenee da Al-zarkashee da waninsu sun ce: "Wurin da kasancewar manta Alƙur'ani kaba'ira ko da da Ayah kai ko da harafi kamar

yadda Arrafi'i da Annawawee da waninsu suka tafi a kansa a wurin wanda ya faɗe shi shi ne idan ya kasance ta hanyar sakaci da wulakanci."

Shihabuddini Ahmad ɗan Hajar Al-haitamee ya faɗa a cikin litaffin Alzawajiru cewa: "Kama don su sun kange da wannan daga wanda ake ya shagala daga gare shi da (uzuri) kamar irin suma ko wata rashin lafiya mai hana shi daga yin karatu da waninsu daga cikin dukan abin da karatu ba shi samuwa tare da shi, to, rashin yin zunubi ta hanyar mantuwa a wannan lokaci bayyane yake domin shi an rinjaye shi kuma ba shi da zaɓi a cikinsa ta kowace fuska saɓanin idan ya shagala daga gare shi da abin da karatu ke yiwuwa tare da shi ko da abin da ya shagala da shi, shi ne mafi muhimmaci. Kuma mafi ƙarfi kamar neman ilimin(farillar) Aini domin shi shagaltuwa da shi ga barin Alƙur'ani wanda aka haddace ba ya cikin sha'anin neman iliminsa har a ce an manta. A nan ya ƙare.

**91- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: Dukkan Abin Da Suka Samu Cikin Littattafan Tafsiri Gaskiya Ne Domin Fassara Ce Ta Maganar Allah.**

Wannan shi ma ɓarna ne kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai, domin littattafan jahilan masu tafsiri suna cike da ɓarna da ababen da ba su cancanta ba ga Annabawa. Saboda haka Alƙali Iyal ya faɗa a cikin (littafin) Ashshifa-u cewa: "Ba za mu waiwaya ba zuwa ga abin da muke samu a cikin littattafan jahilan masu tafsiri da masu tarihi."

**92- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: Hadisai Ingatattu Suna Dacewa Da Mazhabobi Guda Huɗu Saboda Haka Yana Gaugawa Ga Aiki Da Kowane Hadisi Ingantacce Wanda Ya Ji.**

Wannan shi ma ɓarna ne kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai. Sashensu yana dacewa da mazhabar (Imamu) Maliki kawai; sashensu kuma yana dacewa da mazhabar (Imamu) Ashsha'fi-i kawai; sashensu kuma yana dacewa da mazahabar (imamu) Abu Hanifah kawai; sashensu kuma yana dacewa da mazhabar (Imamu) Ahmad kawai; sashensu kuwa yana dacewa da dukan waɗannan mazahabobi guda huɗu, idan ka san haka, to, za ka san cewa kowane ɗaya daga cikin masu waɗannan mazhabobi ya kula da abin da ya dace da mazhabarsa a cikinta.

**93- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: Faɗar Malamai Cewa, Wannan Hadisi Ne Ingantacce (Sahihi Ne), Wannan Hadisi Ne Mai Kyau (Hasan), Wannan Hadisi Ne Mai Runi (Dhaeefi), An Gina Wannan Magana A Kan Hukunci Yankakke.**

Wannan shi ma ɓarna ne kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai domin su suna faɗar wannan ne a kan dogaro da abin da yake a bayyane ba a kan dogaro da haƙiƙanin lamari ba, Saboda haka Al-iragee ya ce; "Sun yi nufin hukunci na zahiri a cikin (Hadisi) Sahihi da Dha'eefi ba a kan yanke ba."

**94- Tana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Manufar Gittawar Mujtahidi A Kan Mujtahidi (Irinsa) Shi Ne Nuna Kiyayya."**

Wannan shi ma ɓarna ne kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai. Ya koru ga amintattun Allah maganar Annabawa ya kasance akwai ƙiyayya a tsakaninsu, sai dai manufar gittawar mujtahidi a kan mujtahidi shi ne bayyanar da abin da yake shi ne gaskiya domin aiki da shi, domin kowane ɗaya daga cikinsu wanda ake amincewa ne shi kuma Shugaba ɗaya ne shi ne Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, saboda haka sashen magabata suka ce: "Duk abin da ya zo mana daga Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi sai mu karɓe shi kai tsaye, abin da kuma ya zo daga waninsa, to, su mazaje ne ko mu mazaje ne."

Ya zo a cikin Umdatul mureed Assa'di malamai sun ce. Dukan magana daga gare shi akwai abin karɓa da abin bari sai abin da ya kasance daga maganarsa. Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi.

**95- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Tsanance-Tsanancen Masu Ijtihadi A Cikin Babin Jayayya Da Waninsa, An Gina Shi Ne A Kan Yankakken Hukunci."**

Wannan shi ma ɓarna ne kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai. Misalin irin wannan kamar tsanantawar Sheikh Assunusi a kan Muƙallidi a cikin aƙidun tauhidi.

Al-manjuree ya ce: "Maganar Sheikh Assunusi Allah Ya yi masa rahama a cikin kafa hujja a kan kafirta muƙallidi akwai tsanantawa, ta dalilinsa ne jama'ar Tilmisana suka yi jayayya da shi suka yi masa musu a kan kafirta muƙallidi da kuma jingina wannan zuwa ga jamhurin malamai.

A cikin Takhleesul Ikhwa'ni haƙiƙa (Imamu) Al-ghazali ya soki malaman zamani suka irin wadda dukkan bayani yana taƙaita koma da bayan ta, wanda jahili yana zatonsa kamar kafirtawa ne, ya kuma zargi masu neman ilimi kuma da shi da waninsa sun hana karantar da su, suka ce: "Shi taimakawa ne a kan saɓo, taimakawa a kan saɓo shi ma saɓo ne ko da yankin kalma."

Yana daga cikin wannan faɗar sashensu cewa: "Haƙiƙa, hanyar sufanci ta yanke babu abin da ya yi saura sai riƙo da Zahiri duk wannan tsanantawa ne."

Yana daga cikin wannan faɗar Abulhasan Karami: "Babu malami yau sai a cikin lamari biyu": "A cikin karantar da ilimi da koyar da sana'a, babu wani."

Ya zo a cikin (Littafin) Talkhi'sul Ikhwani cewa: "Idan ya kasance nufinsa tsanantawa, to, (wannan) a bayyane yake, idan ba haka ba, to, ba za mu sallama ba."

Yana daga cikin wannan faɗar sashensu a cikin inkarinsa a kan Al-fakhari lokacin da yake riƙe da sanda: Da dai na gan shi da na buge shi da wannan sanda bisa kansa.

Yana daga cikin wannan faɗar sashensu ga sashe a cikin yi masa musu: Ban yanki kaza ba amma da na ga mai faɗar wannan magana da na yanka shi.

Ya zo kuma a cikin (Litttafin) Talkhi'sul Ikhwa'ni: Kada tsanantawar wani malami a kan wani malami ta ruɗe ka, kada ka kafa dalili a kan wani mutum da Mazhaba irin tasa. Haƙiƙa, Abu Muhammad ya yi musu a kan Imamu Ma'lik a cikin lalata (hukuncin) zaɓi (na ciniki) a cikin majlisi, inkari mai tsanani ya kuma kai matuƙa a cikinsa har ya ce: "Idan (Imamu) Malik bai dawo ba (daga ra'ayinsa), to, takobi zai sari wuyansa." Kuma ganin yin aiki saboda dalilin abin da ya musanta gare shi, kuma galibin maganganun malaman tauhidi a cikin ilimin tauhidi, an gina su ne a kan wannan babi kamar yadda Abdulwahhab ɗan Ahmad Al-shaara'wee ya faɗakar a kansa sai dai bai kamata ba a ce: Yana halatta a ba da tsoro da firgitarwa a cikin fatawowin malaman hukunce – hukunce.

Ya zo a cikin fatawa ta Al-bazzazee, an yi hikaya daga sashen wanda babu magabata a gare shi cewa: Ya kasance yana cewa: "Abin da aka ambata

na cewa ana kafirta da wannan da kaza, to, wannan don tsoratarwa ne da firgitarwa ba domin tabbatar da kafirci ba."

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne, kuma abu ne da ba zai kasance ba a ce amintattun Allah (ina nufin malamai masana hukunce-hukunce) a ce sun yi wasa da halal da haram da kafirci da Musulunci a'a ba su faɗa sai gaskiya. A nan ya ƙare.

**96- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Ba A Karɓa A Cikin Ilimin Tauhidi Sai Abin Da Sheikh Assunusi Ya Faɗa." "Ba A Karɓar Abin Da Waninsa Ya Faɗa Daga Cikin Malaman Sunna Idan Ya Saɓa Wa Maganarsa."**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai. Ya zo a cikin (Littafin) Talkhisul Ikhwa'n cewa: "Ba a rinjayar da malami a kan wani malami domin dukan mai faɗa yana faɗa ne da ijtihadi." A nan ya ƙare.

**Na ce:** Haƙiƙa (Bayani) ya gabata cewa: ijtiha'di shi ne: Sanya ƙoƙari saboda cimma fahimta ga wani hukunci daga cikin hukunce-hukuncen shari'ah, ba dukan mai ijtihadi yake dacewa ba sai dai ana ba shi lada, domin abin da yake daidai shi ne kamar abin da yake rufe ne duk wanda Allah yake so ya ci karo da shi, zai ci karo da shi.

**97- Yana Daga Cikin Wancan Wahami Cewa: Ana Mayar Da Magana Wadda Masu Shauƙi Suka Keɓanta Da Ita Ko Kuma A Yi Koyi Da Shi(Mai Shauƙi) Ba Tare Da Sanin Manufofinsa Ba Da Matsayinsa.**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai.

Al-ƙushairee ya ciranto a cikin (Littafin) Risalarsa, daga Abu Sa'id Al-abkaree cewa: "Wani tsuntsu ya yi nufin saduwa da wata tsuntsuwa a cikin ƙubbar (Annabi) Sulaiman ɗan Dawuda amincin Allah ya tabbata a gare su sai ta hanu daga gare shi, sai ya ce mata: "Kina hanawa alhali idan na so sai juye gubbar a kan Sulaiman amincin Allah ya tabbata a gare shi", sai ya ce masa: "Me ya ɗauke ka a kan abin da ka faɗa masa?" Sai ya ce masa "Ya kai Annabin Allah lallai masu shauƙi ba a kama su ta hanyar maganganunsu sai ya ce: Ka yi gaskiya ya kai khaɗɗa'f."

An yi hikaya daga sashen ma'abuta shauƙi ya kasance yana cewa: "Ina rantsuwa da Allah lallai kafaɗata za ta yi gogewa da kafaɗun sahabban

Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi a kan ƙofar aljanna har su san cewa su sun bar waɗansu mazaje a bayansu."

Al-imam Assahilee ya cirato a cikin littafinsa (mai suna) Bugyatul Assalikina daga Sheikh Sayyid ɗan Imrana cewa shi ya ce a cikin wata hikaya mai tsawo: "Shin sahabban Muhammadu tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi suna zaton cewa su ne kaɗai suka keɓanta da shi ba tare da mu ba? Ina rantsuwa da Allah za mu yi tarayya da su a cikinsa har su san cewa su sun bar mazaje a bayansu."

Abdullahi Al-khayyaɗ ɗan Muhammadu Al-harushi ya faɗa a cikin sharhinsa a kan littafin Kanzul Asrari fee Assalati ala Annabiyyi Al-mukhta'ri cewa: "Ka sani ya kai ɗan'uwa cewa ni bayan na kawo mafi yawan abubuwa a cikin wannan littafi sai tunani ya zo man na barin (wannan), na kuma yi shakka da yawa, na yi hasashen lamurra masu cutarwa a cikin addini da duniya, sai na shiga ina neman zaɓi ga Allah Subhanahu, sa'annan na shaida wa sashen 'yan'uwa masoya da abin da ya gudana sai ya faɗa man a kan gwargwadon ƙarfin soyayyarsa ga Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi: Ka kammala littafinka ni zan isar maka da dukan abin da zai riske ka a cikin addini da duniya da lahira kuma in ɗauki nauyinsa. Allah Shi ne Mai shaida a kaina, na ambaci wannan kuma a wurin wani sai ya faɗa man irin abin da na farko ya faɗa mani."

Ya faɗa a cikin sharhinsa wanda aka ambata a cikin wani mahalli: Wannan dukansa Ishara ne don tabbatar da saduwarsu da shi saboda yawan ambatonsa da kifuwa a kan son sa tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi.

Ya faɗa a wani mahalli a cikin sharhin da aka ambata cewa: "Ana faɗar irin wannan magana a matsayin yaranci." Kuma, sai dai Sayyidi Abdullahi ɗan Abbad ya faɗa a cikin Risalarsa Al-kubra: "Kar kuma ka yi zaton cewa kowa ne ɗaya ana ba shi dama sai ga wanda yake akwai tabbaci da sassauci a cikinsa ta yadda shi idan ya shiga tare da jama'a a cikin wuraren hutawarsu da mazaunensu inda suke ɗebe kewa da jin daɗinsu zuciya ba ta gurɓata da shi kuma hali ba ya canzawa saboda shi, domin haka idan wani ya gitta domin ya kore shi daga wannan gari ko majalisi ba zai samu dama a kansa ba. Kuma ba zai samu dalili zuwa ga yin haka ba. Idan har ya yi munazara da shi, zai rinjaye shi da hujja kuma zai toshe hujjarsa amma da dai wanda babu wannan siffa a cikinsa ya yi ƙarfin hali ya yi da'awarsa, to, wannan wuri ba zai ba shi dama ba. Farkon abin da zai cimma sa a lokacin da

yake yin wannan shi ne baƙuntar da shi a gefe kuma karnukan wannan wurin za su yi masa haushi idan har ya gitta masu gittawa kaɗan ba za su bar shi ya gurgusa ba ko da zambiya ɗaya har sai sun yaga fatarsa su kuma zubar da jininsa."

**98- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: Duk Wanda Yake Da Wani Rabo Daga Shugabancin Wani Abu Daga Cikin Siffofin Mutane Ba Zai Bayyana A Gare Shi Ba Ko Da A Kan Nadiri.**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai.

Ɗan Aɗa'ullahi ya faɗa a cikin Al-hikam cewa: Rashin siffantuwa ta ɗan'adan ba ya lizimta ga tabbata khususiyya, ya kuma faɗa a cikinsa cewa: "Ba duk wanda khususiyyarsa ta tabbata za a ce tsarkinsa ya tabbata ba."

Ya kuma faɗa a cikinsa cewa: "Zai yiwu wanda istiƙama ba ta kammala gare shi ba sai a arzutta shi da karama."

**Na ce:** Haƙiƙa, Ahmad Zaruƙ ya bayyana a cikin Umdatul Muridi Assadiƙi cewa: "Kuma sashen mutane sun hana neman albarka da sashen waɗanda ya yi zamani da su daga cikin Waliyyai saboda dalilin, bayyanar sashen waɗansu siffofi na ɗan'adam gare shi saboda zatonsa cewa wannan ba shi bayyana ba ga duk wanda yake da wani rabo na walittaka."

**99- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Duk Wanda Ya Kasance Daga Cikin Ma'abuta Kashfi Yana Inganta A Yi Koyi Da Shi A Cikin Hanyar Suluki Zuwa Ga Allah Maɗaukaki."**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai, domin abin da yake daidai shi ne cewa duk wanda ya kasance daga cikin ma'abuta kashfi idan ya kasance daga cikin waɗanda suka san hanyar sunna a bayyane da ɓoye yana inganta a yi koyi da shi a cikin hanyar suluki zuwa ga Allah. Idan kuma ba haka ba shi ne kamar idan ya zama daga cikin ma'abuta kashfi amma bai san hanyar sunna ba a cikin suluki zuwa ga Allah, to, girmama shi ya wajaba kawai amma ba ya inganta a yi koyi da shi a cikin wannan domin shi abu ne wanda aka so keɓantacce.

**100- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Duk Abin Da Ya Wuce Hankalinsa Na Ilimummukan Kashfi, To, Shi Abin Mayarwa Ne."**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai domin abin da yake daidai a cikin wannan shi ne kamar yadda Ahmad Zaruƙ ya ce: Malami ya yi riƙo da abin da shiriyarsa ta bayyana ya kuma bar duk abin da bai bayyana ba gare shi, yana mai miƙa wuya a gare shi, ba mai aiki da shi ba, ba domin wata naƙasa ga wanda ya faɗe shi ba, a'a sai dai domin rashin tsayuwa a kan iliminsa, domin ba a kallafa wa wani da abin da iliminsa bai farka zuwa gare shi ba a'a biyarsa ba ya halatta a gare shi.

﴿ وَلَا تَقْفُ مَا لَيْسَ لَكَ بِهِۦ عِلْمٌ ﴾الإسراء: ٣٦

*"Kar ka tsayar da abin da ba ka da ilimi a kansa" Al'isra'i 36*

(Imam) Al-ghazali ya ce: A cikin Ihya-u: Sashen masana sun ce: "Duk wanda ba shi da wani rabo daga wannan ilimi, ina ji masa tsoron mummunar makoma, rabon da ya fi kusa gare shi shi ne gaskatawa da shi da kuma miƙa shi ga ma'abutansa."

**101- Yana Daga Cikin Wancan Wahami: Kudurtawar Sashensu Cewa: "Duk Abin Da Ake Faɗa A Zahirin Hukuncin Shari'a Babu Wanda Ya San Haƙiƙaninsa Sai Allah, Kamar Yadda Ake Faɗa Ga Ayoyi Da Hadisai Masu Rikitarwa. Haka Kuma Kamar Misalin Mas'alar Haƙiƙanin Ruhi, Allah Bai Tsinkayar Da Wani A Kansa Kuma Dukan Mutane Daidai Suke A Cikin Wannan A Kan Haɗuwar Malamai.**

Wannan shi ma ɓarna ce kuma wahami ne a kan haɗuwar malamai, domin wannan ana faɗarsa ne a dangantaka zuwa ga fahimce – fahimcen ra'ayoyi ba a dangantaka zuwa ga kashfin Annabawa ba da waliyyai, domin Allah Maɗaukaki yana tsinkayar da su a kan sashen gaibobinSa.

(Imam) Alghazali ya ce a cikin littafin Ilja'mul Auwami an Ilimil kalami a cikin bayanin ma'anar miƙa wuya a cikin abubuwan da suka rikita: Shi ne mutum ya ƙudurta cewa duk abin da ya ɓoyu gare shi a cikin bayanin ma'anonin waɗannan abubuwa bayyanannu ba su kasance a ɓoye ba ga Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi da kuma (Abubakar) Assiddeeƙ. Haka ga manyan sahabbai da malamai waɗanda suka kafu. Yana nufin rayukansu sun kafu a cikin hadharatil ƙudusi. Su mutane an

halicce su daban-daban masu bambanci, bai kasance ba duk abin da jahilai da tsofaffi suke keɓanta da shi ya lizimta a ce waziran Sarki da keɓantattunsa suka keɓanta da shi.

Ya faɗa kuma a cikin Ihya'u cewa: "Abu yakan kasance a cikin ransa ɗan ƙarami har mafi yawan hankula su kasa fahimtarsa amma sai keɓantattu su keɓanta da shi fahimtarsa, ya wajaba a kansa kada su yaɗa shi zuwa ga wanda ba ma'abucinsa ba, domin wannan yana zama fitina a kansa inda hankulansu za su taƙaita, daga fahimta, da ɓoye asirran ruhi (rayuwa). Kamewar Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi daga yin bayaninsa yana cikin wannan sashe, domin duk wanda bai san ruhi ba, to, kamar shi bai san kansa ba. Wanda kuwa bai san kansa ba ta yaya yake sanin Ubangijinsa Maɗaukaki? Ba abu ne mai nisa ba wannan ya kasance a bayyane ga sashen waliyyai da malamai duk da cewa ba su zama Annabawa ba sai dai su suna ladaftuwa da ladubban shari'a sai su yi kawaici daga abin da ya yi kawaici daga gare shi. A nan ya ƙare.

**Na ce:** Waɗannan wahami gulbi ne babu gaɓa gare shi kuma ba a cimma zurfinsa, a cikin abin da muka ambata daga cikinta akwai isuwa a cikin faɗakarwa a kan abin da ba mu ambata ba daga cikinta wanda Allah Ya haskaka zuciyarsa.

A nan littafi (mai suna) *Kare Fahimta Daga Rundunar Wahami* ya ƙare.

Ya Ubangiji Ka fitar da mu daga duhun wahami kuma Ka girmama mu da hasken fahimta da ilimi.

Ya Ubangiji Ka nuna mana gaskiya, gaskiya ce Ka arzutta mu biyar ta; Ka nuna mana ƙarya, ƙarya ce Ka arzutta mu nisantar ta.

Godiya ta tabbata ga Allah wanda ya shiryar da mu daga wannan ba mu kasance muna shiriya ba ba domin Allah ya shiryar da mu ba.

Mafificin salati da mafi cikar aminci su tabbata ga shugabanmu, Muhamadu da Iyalansa da Sahabbansa baki ɗaya.

Allah Maɗaukaki ya yarda da shugabanni masu biya da shugabanni (malamai) huɗu masu ijtihadi da waɗanda suka rataya da su har zuwa ranar sakamako.

Karshen addu'armu shi ne godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, ya Ubangiji Ka yi rahama ga al'ummar Muhammadu rahama ta gaba ɗaya. Amin.

# تمييز المسلمين من الكافرين

## BAMBANTA MUSULMI DAGA KAFIRAI

Na

## Shehu Usmanu Ɗanfodiyo

**Mai Fassara**

**Muhammad Isa Talata Mafara**

## ABUBUWAN DA KE CIKI

**Shafi**

GABATARWAR MAWALLAFI............................................................ 165

Kungiya Ta Ɗaya: ................................................................................ 166

Kungiya Ta Biyu.......................................................................................... 167

Kungiya Ta Uku.......................................................................................... 168

Kungiya Ta Huɗu........................................................................................ 169

Kungiya Ta Biyar........................................................................................ 170

Kungiya Ta Shida........................................................................................ 171

Kungiya Ta Bakwai .................................................................................. 172

Kungiya Ta Takwas .................................................................................. 173

## GABATARWAR MAWALLAFI

*Da sunan Allah Mai rahama Mai jin-ƙai*

Bawa mai tsananin buƙata zuwa ga rahamar Ubangijinsa wanda yake shi ne Usmanu ɗan Muhammad ɗan Usmanu wanda aka fi sani da Ɗanfodiyo. Allah Ya yi masa kube da rahamarSa, amin, ya ce: Dukan godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai; kuma tsira da aminci su tabbata a bisa ga shugaban Manzanni; kuma da alayensa da sahabbansa gaba ɗaya. Yardar Allah Maɗaukaki ta tabbata a bisa ga shugabanni, tabi'ai kuma da malamai masu aiki da iliminsu kuma da shugabanni guda huɗu masu ijtihadi kuma da waɗanda suka bi hanyoyinsu da kyawawan ayyuka har ya zuwa ranar sakamako.

Bayan haka, wannan shi ne littafin TAMYIZUL MUSLIMINA MINAL-KAFIRINA (watau Bambanta Musulmi Daga Kafirai). A cikinsa na raba mutane zuwa ƙungiyoyi guda takwas domin kusantarwa ga zukata da hankulan marasa zurfin ilimi.

## KUNGIYA TA ƊAYA

Wannan ƙungiya ita ce ta Malamai waɗannan da suka inganta aƙidojinsu, kuma suna wankan janaba kuma suna alwala domin yin salla kuma ba su yin taimama face da larura, kuma suna aikata sauran ayyukan Musulunci kamar yadda aka shar'anta. Haka kuma ba a ganin aikata kafirci daga gare su kamar girmama duwatsu da itatuwa ta hanyar yin yanka a wajensu, ko kuwa zuba wani ɗan gari a kansu. Kuma ba a ji daga gare su, wani zance na kafirci kamar izgili da addinin Allah ko ƙaryata abin da aka san Manzo ya zo da shi a kan larura ba.

To, waɗannan su Musulmi ne a bisa ga haɗuwar Malamai.

## KUNGIYA TA BIYU

Wannan ƙungiya ita ce ta ɗalibai waɗanda suka inganta aƙidojinsu kuma ya kasance suna wanka daga janaba, kuma suna alwala domin salla, kuma ba su yin taimama face da uzuri, kuma suna aiwatar da sauran ayyukan Musulunci kamar yadda aka shar'anta, kuma ba a gani daga gare su wani aiki na kafirci kamar girmama duwatsu da itatuwa ta hanyar yanka a wajensu ko kuwa zuba wani ɗan gari a kansu ba. Haka har wa yau ba a ji daga gare su wani zance na kafirci ba. Wannan kamar izgili da addinin Allah ko ƙaryata abin da aka san Manzo ya zo da shi a kan Larura. To, waɗannan su ma Musulmi ne da ijma'i na Malamai.

## KUNGIYA TA UKU

Wannan ƙungiya ita ce ta masu saurare ga abin da Malamai ke faɗa kuma saurare na karɓa. Waɗannan su ne waɗanda suka inganta aƙidojinsu ta hanyar tambayar Malamai, kuma da halarto majalisunsu; haka kuma sun kasance suna wanka daga janaba, kuma suna alwala domin yin salla kuma ba su yin taimama face da uzuri, kuma suna aikata sauran ayyukan Musulunci kamar yadda aka shar'anta kuma ba a gani daga gare su wani aiki na kafirci tamkar girmama duwatsu da itatuwa ta hanyar yin yanka a wajensu ko zuba wani ɗan gari a kansu, kuma ba a ji daga gare su ba wani zance na kafirci kamar izgili da addinin Allah, kuma da ƙaryata abin da aka san Manzo ya zo da shi a kan Larura. To, waɗannan su ma Musulmi ne.

## KUNGIYA TA HUƊU

Wannan ita ce ƙungiya waɗanda ba su shiga a cikin Musulunci ba faufau. Waɗannan kafirai ne da ijma'i na malamai, kuma hukuncinsu ba zai rikita ba ga kowa.

## KUNGIYA TA BIYAR

Wannan ƙungiya ita ce wadda ke haɗa ayyukan kafirci da ayyukan Musulunci, watau dai su ne waɗanda suka shigo a cikin Musulunci amma kuma ba su bar ayyukan kafirci ba. Wannan kamar girmama duwatsu da itatuwa ta hanyar yin yanka a wajensu ko zuba wani ɗan gari a kansu.

Waɗannan kafirai ne da haɗuwa ta malamai.

## KUNGIYA TA SHIDA

Wannan ita ce ƙungiyar da ke haɗa zantuka na kafirci da ayyukan Musulunci; watau dai su ne waɗanda suka shiga a cikin Musulunci, amma ba su bar maganganu na kafirci ba. Wannan tamkar izgili da addinin Allah kuma da ƙaryata abin da aka san Manzo ya zo da shi a kan larura. Waɗannan kafirai ne da ijima'i na malamai.

## KUNGIYA TA BAKWAI

Wannan ita ce ƙungiyar ma'abuta hadasi. Waɗannan su ne waɗanda suka shiga a cikin Musulunci kuma suka inganta aƙidojinsu, sai dai sukan yi salla ba tare da alwala ba, kuma da ganganci.

Amma kuma ba a ji daga gare su wani zance na kafirci kamar musun wajabancin alwala ko musun wani abu da ka san Manzo (saw) ya zo da shi a kan Larura ba; haka kuma ba a gani daga gare su ba wani aiki na kafirci kamar girmama duwatsu da itatuwa ta hanyar yanka a wajensu ko kuwa zuba wani ɗan gari a kansu. Wannan ƙungiya, malamai sun yi saɓani a kansu. Duk ɗaya ne suna daga ƙungiyar masu saurare, ko kuwa suna daga ƙungiyar ɗalibai ko daɗa suna daga ƙungiyar malamai.

Mafi yawan Malamai sun tafi a kan cewa su, Musulmi, ne sai dai fasiƙai.

Waɗansu daga Malamai suka ce a'a waɗannan kafirai ne domin aikata salla ba tare da tsarki ba ridda ne a nasu ra'ayi. Malam Sa'ad Taftazani ya faɗa a cikin littafinsa mai suna Sharhul-Aƙa'id cewa: "Yana daga ridda aikata salla ba tare da tsarki ba."

Wannan kuwa shi ne zahirin zancen Malam Abdurrahman, mawallafin littafin Ahlari, a inda yake cewa "wanda ya yi salla ba tare da alwala ba kuma a kan ganganci, to, shi kafiri ne."

Amma zancen mafi yawan malamai da suka ce wannan aiki saɓo ne, to, shi ne zance sananne kuma wanda ake dogaro da shi, kuma shi ne malamai ke aiki da shi. Amma ko ta yaya bai kamata a yi saɓani a kan zaman wannan aikin saɓo ba, kuma irin wannan salla ɓatatta ce da haɗuwa ta malamai.

## KUNGIYA TA TAKWAS

Wannan ita ce ƙungiyar jahilai. Waɗannan su ne waɗanda suka shiga a cikin Musulunci amma ba su san abin da ke inganta imani ba, kuma ba su fahinci haka ba, kuma ba su shaƙi ko da ƙanshin koyi da magabata ba, ballantana sanin hujjoji. A'a, su dai suna furuci da kalmar shahada ba tare da aƙida ingantatta ba. Wannan kuwa saboda ba su neman ilimi, kuma ba su tambayar malamai, kuma ba su halarto majalisunsu; saboda rashin kulawarsu da haka. To, waɗannan kafirai ne ga abin da yake tsakaninsu da Ubangijinsu. Wannan kuwa da ijma'i na malamai. Duka ɗaya ne suna daga waɗanda ke yin wankan janaba, kuma suna alwala domin salla, ko kuwa ba su daga gare su. Waɗannan mutane ire-irensu ne Malam Sanusi ya tusgo da hukuncin su a cikin littafinsa mai suna Sharhul-Wusɗa. Wannan a inda ya ce:

An tambayi malaman garin Bujaya da wasunsu a farkon wannan ƙarni ko kuwa kafin haka da ɗan abu kaɗan a game da mutumin da ke furuci da kalmar Shahada kuma yana salla kuma yana hajji kuma yana aikata kaza da kaza. Amma duk yana zowa da waɗannan abubuwa a bisa gwargwardon abin da ya ga mutane suna faɗa ko kuwa suke aikatawa. Wannan har a matsayin yana furuci da kalmar shahada amma kuma bai fahinci ma'ana tata ba, kuma bai san ma'anar La'ilaha Illallah ba, kuma bai san ma'anar Manzo ba. A gaba ɗaya, bai san wani abu daga kalmar shahada ba na daga abin da aka tabbatar ko kuwa aka kore. A wani lokaci ma yakan zaci cewa Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi tamkar Ubangiji yake. Wannan kuwa saboda abin da yake gani na ambaton Manzo a cikin kalmar shahada da duk aka ambaci Allah sai an ambace shi; haka kuma da sauran wurare da haka ke aukuwa. Shin ko wannan mutum zai amfana da zantukansa da ayyukansa, kuma ko sunan imani zai gaskata a gare shi ga abin da ke tsakaninsa da Ubangijinsa, ko kuma haka ba za ta yiwu ba?

Sai Malaman suka ba da amsa gaba ɗaya da cewa: "irin wannan mutum ba ya da wani rabo daga imani."

Sa'annan Malam Sanusi ya ce: Na ce: "Wannan abu da suka yi fatawa da shi a game da wannan mutum kuma da ire-irensa abu ne da a bayyane, bayyana, wadda ta kai matuƙa; kuma bai kamata a sami saɓani a kansa ba.

Amma jayayya ta malamai a game da wanda ya san ma'anar kalmar Shahada kuma ya tabbatar da abin da ta ƙunsa na daga aƙidojin tauhidi ba tare da wata shakka ba, amma kuma wannan tabbatarwa tasa ta samo asali ne

daga tasawar da ya yi a tsakanin al'ummar Musulmi kawai ba tare da yana da wani dalili a kan haka ba gaba ɗaya, to, saɓanin da ke akwai a game da imanin wannan mutum shi ne wanda aka sani a game da imanin muƙallidi. A nan maganar Malam Sanusi ta tuƙe.

Na ce: A game da wannan ƙungiya ta takwas zancen ɗan Umar ke kai-da-komo da ya yi a cikin littafinsa mai suna Al-Fasalul-Awwal: Amma hukuncinsu a wajen mu'amala a zahirin shari'a kamar auratayya da su kuma da cin abin da suka yanka, kuma da salla a gare su idan suka mutu haka kuma da bizne su a cikin maƙabartar Musulmi, to, akwai bayanai a game da wannan.

Wanda kafircinsa ya bayyana daga cikinsu ta hanyar bincike, ko ta waninsa, to, sai mu umurce shi da ya tuba kuma ya nemi ilimi. Idan ya aikata haka, to, al'amarinsa a bayyane yake, amma idan ya ƙi, to, sai mu bar mu'amala da shi. Amma wanda kafircinsa bai bayyana ba daga cikinsu amma kuma sai ya bayyana a gare mu daga zantukansa da ayyukansa abin da ke nuna cewa jahilci ke tare da shi wanda ke kai zuwa ga kafirci, to, shi wannan mu'amalarmu da shi tana a kan zance biyu.

Zance na ɗaya, shi ne mu dogara a kan zahirin musuluncinsa sai mu yi mu'amala da shi. Wannan magana ita ce sananna wadda ake aiki da ita.

Zance na biyu, shi ne mu bincika. Yadda binciken zai kasance shi ne, mu bayyana masa rukunnan imani da Musulunci. Sai mu ce masa: "Ko kana a kan wannan?" ko kuwa, " ka gaskata wannan?" Idan ya ce , E. To, wannan ya isa: Abin da nake nufi watau, wannan ya gamsar ga mu yi hukunci da musuluncinsa, kuma mu yi mu'amala da shi. Wannan magana ita ce malamai na baya-baya suka tafi a kanta a waɗannan zamuna na baya-baya. Wannan kuwa saboda rinjayar jahilci a cikinsa. Wannan zance ba shi ne abin dogara ba, kuma ba shi ake aiki da shi ba, kuma ba a yi wa mutane fatawa da shi ba.

Domin zance ne na 'yan kaɗan. Amma kuma wanda ke aiki da shi a ƙashin kansa, kuma bai kasance mai yi wa mutane fatawa da shi ba, to, ba za a yi masa musu ba; wannan idan binciken nasa ya kasance kamar yadda muka siffanta. Amma idan a cikin binciken nasa ya kasance yana cewa: mene ne imani, kuma mene ne Musulunci? Idan ya kasa siffantawa, to, sai ya yi hukunci da kafircinsa, wai saboda kawai ya kasa yin bayani, to, wannan gaba ɗaya ba daidai ne ba.

Amma wanda bincikensa da jarrabawarsa suka kasance a kan fuska ta karantar da aƙidoji, a kan hanya ta nasiha; wannan kamar yadda Malam ɗan Umar da waninsa ke yi na daga malamai masu nasiha, to, wannan bai kamata a yi saɓani ba a kan zaman binciken daidai kuma alheri.

Amma idan ya bayyana a gare mu na daga zantukan da ayyukansa, abin da ke nuna cewa ba ya tare da jahilci mai kaiwa zuwa ga kafirci, to, shi wannan zahirin musuluncinsa ya isar muna ga mu'amala da shi.

Idan wani abu kuwa bai bayyana a gare mu ba na daga zantukansa da ayyukansa, amma kuma sai ya kasance zato ya nuna yana daga wannan ƙungiya ta takwas, to, shi wannan Malam ɗan Umar ya tafi a kan cewa za mu dakatar da mu'amala da shi a kan hanya ta kewayewa; a'a ba wai a kan hanya ta yanke hukunci ba. Wannan kuwa har halayyarsa ta bayyana a gare mu. Ya faɗi wannan magana a ƙarshen littafinsa na Alfasalul-Awwal a inda ya ce: "Kuma mutanen zamanin da ya gabata wanda kafircinsa bai bayyana ba, to, aurensa da yankansa sun halatta. Ba za a yi ƙiyasin zamaninmu da nasu ba. Wannan saboda yawaitar kafirci da ƙaruwarsa a cikinsa (namu zamani). A dalilin haka na dakatar da mu'amala da wanda halinsa ya ɓoyu. Shin ko yana daga waɗanda ake gabatar da galibi – watau abu mafi rinjaye – ko kuwa yana daga abin da ake gabatar da nadiri watau abin da yake kaɗan. Idan aka yi la'akari da abu mafi rinjaye, to, auratayya da shi da kuma yankansa ba su halatta ba. Amma idan aka gabatar da abin da yake nadiri, to, sai a ce a'a. Amma tare da haka mun kasance muna sayen nama ga waɗanda muka karantar da su aƙidoji. Zancenmu bai kasance a game da wanda kafircinsa ya tabbata ba. A'a wannan zaɓi yana kasancewa a game da wanda halayyarsa ba ta bayyana ba." A nan maganar ɗan Umar ta ƙare.

Abin da a tabbatattar magana tasa a cikin littafin Al-Fasalul-Awwal shi ne, duk wanda ke bayyana Musulunci amma kuma bai fahinci abin da ke inganta imaninsa ba, to, wannan za a ce kafiri ne ga abin da ke tsakaninsa da Ubangijinsa. Wannan kuwa da ijma'i na malamai. A gare mu idan kafircinsa ya bayyana sai mu umurce shi da ya tuba kuma ya je ya nemi ilimi. Idan ya yi haka al'amarinsa ya zama bayyane, watau shi, Musulmi, ne. Amma idan ba haka ba, to, ya kafirta ta kowace irin fuska. Abin da nake nufi da wannan, ya zama kafiri ga abin da ke tsakaninsa da Ubangijinsa, kuma da abin da ke tsakaninsa da mutane.

Amma idan babu wani abu da ya bayyana na daga halayyarsa, amma kuma yana daga wannan ƙungiya ta takwas a mafi rinjayen zato, to, sai mu

dakatar da mu'amala da shi har halayyarsa ta bayyana. Wannan shi ne haƙiƙar abin da ke cikin littafin Alfasalul-Awwal.

Wannan magana ta ɗan Umar da ya nuna wanda ke faɗar kalmar shahada amma kuma bai fahinci abin da ke ingantar da imani ba, da cewa kafiri ne, ga abin da tsakaninsa da Ubangijinsa kuma da haɗuwa ta malamai, to, lalle wannan magana haka take babu wata jayayya. Amma kuma a game da dakatar da mu'amala da wanda halayyarsa ba ta bayyana ba, amma a galibin zato yana daga ƙungiya ta takwas, wannan dakatarwar an yi ta ne a kan hanya ta kewayewa. To, wannan ra'ayi ba abin dogaro ba ne, kuma ba shi ake aiki da shi ba, kuma ba a fatawa da shi, ko da yake ita dakatarwar a kan sawaba take. Amma kuma mutumin da ke aiki da wannan ra'ayi shi kaɗai ba tare da yin fatawa ga mutane da shi ba, to, ba za a yi masa inkari ba, idan ya yi haka a kan hanya ta kewayewa ba, a kan kafirtawa ba. Wannan kamar yadda shi ɗan Umar ya aikata.

Amma abin da a magana sananna kuma wadda ake dogaro a kanta game da wannan mas'ala ita ce, duk wanda ke bayyanar da Musulunci, to, mu'amala da shi ta halatta sai fa idan kafircinsa ya bayyana. Daɗa shi wannan halayyarsa ta bayyana a gare mu ko ba ta bayyana ba. A game da zamunan da suka gabata, wannan ya kasance da ijma'i na malamai, saboda nasu zamuna akwai yawaitar ilimi a ciki. Amma a zamuna na baya-baya waɗanda ilimi ya ƙaranta a cikinsu, to, wannan mas'ala tana daga abin da ake gabatar da abin da a kaɗan a kan mai yawa. Wannan kuwa shi ne ra'ayin mafi yawan malamai. Dalili a kan wannan shi ne rahama ga al'umma. Wannan abu kuwa tabbatacce ne a cikin ilimin aƙidoji.

Idan ka ce wannan magana da ta gabata na cewa mutanen wannan ƙungiyar ta takwas Musulmi ne ga zahirin hukunci na shari'a idan dai kafircinsu bai bayyana ba, kuma lalle su kafirai ne ga abin da ke tsakaninsu da Ubangijinsu da ijma'i na malamai, to, wannan zai sanya mu riƙa munana zato ga aƙidojin da yawa daga jama'ar Musulmi, waɗanda muke kiransu Musulmi, kuma muminai, a bisa ga zahirin shari'a, wannan kuwa saboda rashin neman ilimi. To, mene ne zai kuɓutar da mu daga wannan matsala? Kuma mene ne madogararka a kan cewa mutum yana iya zama kafiri ga abin da ke tsakaninsa da Ubangijinsa, sa'annan kuwa mu ce masa Musulmi, ko mai imani idan kafircinsa bai bayyana ba, kuma mu yi mu'amala da shi?

Jawabi ga wannan su ne hujjoji masu yawa:

Wannan kuwa domin dukan zancen malaman sunna yana a kan haka. Abu ne da babu saɓani cewa Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya kasance yana gamsuwa da Musuluncin duk wanda ya yi furuci da kalmar shahada a game da hukunce-hukunce na zahiri; amma ban da hukunce-hukunce na tsakanin mutum da Ubangijinsa, na daga imanin da ke kuɓutarwa daga wuta. Wannan ya isa ya kasance abin dogaro. Kuma wannnan ra'ayi shi ne Malam Sanusi ya bayyanar a cikin littafinsa na Al-Umda Sharhin aƙida Al-Kubra. Wannan kuwa a wurin da ya ce: "Amma gamsuwar Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi da kuwa gamsuwar Sahabbansa Allah ya yarda da su na gudanar da hukunce-hukuncen Musulunci, ga wanda ya faɗi kalmar shahada kuma da hani ga a yaƙe shi, kuma ba tare da sun yi bincike ga abin da yake ɓoye ba, to, wannan ba yana nuna abin haka yake har a lahira ba. A'a wancan yana daga babin gudanar da hukunce-hukunce a kan zato da zahiri – kuma wannan ba a kansa zancenmu yake ba. A'a, zancenmu ya kasance ga abin da ke tsakanin bawa da Ubangijinsa, na daga abin da ke hana masa dawwama a wuta tare da sauran kafirai.

Sa'annan Malam Sanusi ya faɗi cewa: "Hukunce-Hukuncen duniya, an gina su a kan zahiri. A bisa ga wannan ne Gazali ya ce: "Kada ku motsar da aƙidojin jahilai, a'a ana barinsu a kan abin da suke a kai." Abin da yake nufi da wannan shi ne, sunna ta gabata da rashin bincike daga abin da ke cikin zukata, a'a abin da suke a kai." Abin da yake nufi da wannan shi ne, sunna ta gabata da rashin bincike daga abin da ke cikin zukata, a'a abin da ke cikin zukata zai bayyana ne a ranar Kiyama ranar da ake jarraba asirai.

Abin da a wajibi shi ne yaɗa ilimi ga wanda ya tambaya, ko kuwa ya kasance ya cancanta da shi. A'a ban da wanda ya kawar da kai daga gare shi, ya kasance bai cancanta da shi ba. Abin da yake nufi da wannan Allah ne Masani, watau idan munkari bai bayyana ba ga aƙidojinsu kamar a wannan zamani namu. Idan haka ta faru, to, kawar da munkari yana wajaba, kuma da karantarwa a gare su karantarwa mai taushi a bisa gwargwadon yadda hankulansu ke ɗauka. Haƙiƙa, Allah Maɗaukakin Sarki ya yalwata ga lafuza da dalilai. Da wannan za a yi zance da kowane mutum a bisa ga fahimta tasa. A nan maganar da ƙare.

Abin da ke da ma'anar wannan shi ne abin da har wa yau Malam Sanusi ya bayyana a cikin littafinsa na Al-Umdah a wani muhalli a inda ya ce:

"Amma zancen Alƙali (Abubakar Ibnu Ɗayyib) da ya ce: "Ba za a sami mumini ba face masani ne ga Allah." To, wannan ba yana nufi da mumini wanda muke faɗar lafazin imani a gare shi a bisa ga zahiri ba. A'a abin da yake nufi da mumini, shi ne wanda ya ke mumini a wajen Allah Maɗaukakin Sarki ga haƙiƙanin al'amari." A nan maganar ta ƙare.

Haka har wa yau ya ambata a cikin littafin na al-Umda a wani muhalli dangane da wannan zance na Alƙali a kan siga ta tambaya ya ce:

"Idan aka ce an cirato daga Alƙali Abubakar Ibnu Ɗayyib Allah ya yarda da shi cewa, ba za a sami mumini ba face masani ga Allah Maɗaukakin Sarki, sai dai halaye su saɓa dangane da wannan. Domin daga cikinsu akwai mai kaifin hankali wanda ke da ikon bayyanar da abin da ke cikin zuciya tasa kuma ya kafa hujja a kai. Daga cikinsu akwai wanda ya san Allah a kan yaƙini, amma kuma ba ya iya bayani a game da abin da ke cikin zuciya tasa".

To, sai ya karɓa wannan tambaya ya ce: "Amma zancen Alƙali da ya ce daga cikinsu akwai mai kaifin hankali wanda ke da ikon bayyana abin da ke cikin zuciya tasa har zuwa ƙarshen maganar. To, wannan a bayyane yake domin sanin Allah Muhallinsa shi ne zuciya. Dalilinsa kuwa na al'ada ne, watau dai nazari da hankali. Shi, furuci da harshe, ba ya da ta'asiri a gare su. A dalilin haka ya kasance bai zama sharaɗi a gare su ba. A'a abin da a manufa tabbatar da aƙida a cikin zuciya da hujjojinta. Daɗa mai wannan aƙida ya sami ikon bayaninta ko kuwa a'a. Abu ne da ba shakka ga cewa akwai samuwar imani ga kwatankwacin wannan, kuma ba a kansa ne muke jayayya ba. A'a, jayayyarmu ita ce, shin wannan sanin Allah da Alƙali ke magana a kansa, shin yana nufin abu ne samamme ga dukan wanda ke ɗauke da sunan imani a kan zahiri nasa, ko kuwa a'a? Abu ne da yake sananne da cewa lalle Alƙali ba ya nufin haka daɗa ko shi ko kuwa waninsa.

A'a abu ne da yake tabbatacce cewa, duk wani mai hankali yana iya nuna yiwuwar kasancewar duk wani mai bayyana imani da ya kasance Muƙallidi, ko mai zato, ko kuwa mai shakka ko mai wahami kai ko kuwa kafiri, ko kuwa daɗa zindiƙi. Kai ko da mai bayyanar da imanin nasa ya furta muna dalilai nasa, kuma ya inganta su, to, da ba za mu yi yanke da imani ko sanin Allah a game da shi ba. Domin zai yiwu ya kasance akwai wata shubha a cikin zuciyarsa, wadda za ta sanya kokanto a gare shi amma ya zama bai bayyana ta a gare mu ba. Ko kuma ya zama ya kiyaye waɗannan hujjoji nasa a kan kwaikwayo ba tare da tabbaci ba, amma dai ko ta yaya alamomi na rinjayar da ɗaya daga abubuwan biyu.

Sa'annan bayan haka Malam Sanusi ya ce a game da wanda ke bayyanar da imani: "Amma shi mutum a game da kansa shi ne mafi sani ga halayyarsa idan dai ya kasance mai hankali. Wannan kuwa domin daga jahilai akwai wanda bai san halayyar kansa ba."

Wani abu mai kama da haka shi ne abin da Malam Abdulsalami ɗan Ibrahim Allaƙani ya bayyana a cikin sharhin littafin Jauharatul-tauhidi a inda ya ce: "Lalle imanin da ake gamsuwa da shi a cikin hukunce-hukunce na duniya shi ne furci, shi kaɗai. Wanda ya furta kalmar shahada za a gudanar da hukunce-hukuncen Musulunci a kansa, kuma ba za a yi hukunci da kafircinsa ba, face sai an sami wata alama da ke nuna kafirci nasa kamar yin sujada ga gunki."

Wani abu kuma mai kama da wannan shi ne abin da Alƙali Abul-Falali ya ambata a cikin littafin Ashafa a inda ya yi magana a game da hukuncin waɗanda ke furuci da kalmar shahada ba tare da aƙida ta zuciya mai inganci ba, kuma kafircinsu bai bayyana ba, sai ya ce: "Waɗannan a ranar Alƙiyama ba su kasance daga muminai ba, amma a nan duniya suna daga cikin masu imani a dalilin abin da ya bayyana na shaidar harsunansu. Za a gudanar da hukunce-hukuncen duniya a kansu waɗanda ke da dangantaka da shugabannin da mahukunta na Musulmi. Wannan domin suna aiki da zahiri na daga alamomin Musulunci, domin shi mutum ba ya da wata hanya ta sanin abin da yake ɓoye, kuma ba a yi umurni da binciken wannan ba. A'a har ma Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya yi hani haka, kuma ya zargi mai aikata haka. Wannan a lokacin da ya ce :

"Me ya hana ka tsaga zuciyarsa."

A nan ne amsata ta ƙare a game da madogarata a kan cewa duk wanda ke bayyanar da Musulunci, to, za mu kira shi, Musulmi kuma mai imani, kuma mu yi mu'amala da shi a kan haka idan dai ba kafircinsa ya bayyana ba.

Amma a game da mafita daga munanan zato ga aƙidojin da yawa daga jama'ar Musulmi waɗannan da muke ambatonsu, masu imani kuma Musulmi a bisa abin da ya bayyana a gare mu, idan dai ba kafircinsu ya bayyana ba, to, lalle Malam Sanusi ya yi bayanin wannan a cikin littafinsa na Sharhin (Aƙida) Al-Wusɗa a inda ya ce, Amma shi muutum shi ya fi kowa sanin kansa ba zai tambayi wani ba a game da kansa. Amma a game da

waninsa, to, lalle ba ya da wani rabo ga sanin abin da ke cikin zuciyar wani, kuma ba ya da ikon ya yi yanke a game da wani a bisa ga gaskiyar al'amari.

Wannan sai idan Manzo ma'abucin shari'a tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya shaida a game da wani a kan wani abu, to, lalle dole ne a yi yanke da wannan al'amari a bisa gaskiya tasa.

Wannan kuwa domin Allah da ManzonSa su suka sani. Tare da wannan kuma bai halatta a gare mu da mu munana zato ga imanin wani daga cikin Musulmi daɗa masani ne ko ba masani ba; domin sanin Allah Muhallinsa shi ne zuciya, kuma ba sharɗi ne ba a ce sai idan yana iya faɗar hujjojinsa ta irin yadda malamai ke yi ba. A'a idan ya fahinci imani ta hanyar da aka saba fahimta tasa, kuma ya zama ya fita daga zama muƙallidi, to, za a ɗauki cewa shi masanin Allah, ko da kuwa ba ya iya bayani mai gamsarwa a game da abin da ke cikin zuciyarsa."

To, idan ka san cewa samun iko ga tabbatar da dalilai, kuma da bayani a game da abin da ke zuciya ba sharaɗi ne ba ga sanin Allah ko kuwa fita daga kasancewa muƙallidi, a'a fahimta ta zuciya shi ne sharaɗi, to, lalle, ba ya halatta da mu munana zato ga imanin wani, masani ne ko ba masani ba; haka kuma ba ya halatta ga mu yi yanke da cewa wane muƙallidi ne domin ya kasa bayani da harshensa a game da tabbatar da dalilai na aƙida. Wannan kuwa domin zai yiwu ya zama ya san aƙidojin imaninsa ta hanyar nazari na zuciya, amma kuma da fuska wadda ba ya iya yin bayaninsu. Akwai da yawa daga malamai waɗanda ba su iya yin bayanin abubuwan da ke cikin zukatansu na daga fannonin ilimi tabbatattu, to, daɗa ballantana jahilai. Wannan sai idan wani abu ya bayyana a harshen muutm wanda ke nuna wani abu da ke ɓoye a cikin zuciya tasa na aƙida ɓatatta. To, ko shi abin da yake wajibi shi ne a koyar da shi koyarwa mai taushi, kuma a yi maganin cutar da ke tare da shi da abin da ya sauƙaƙa. Allah ne ake neman taimakonSa. Abu ne kuma da ke yiwuwa wanda ba ya da ilimi ya furta hujjoji kuma ya yi raddi ga shubhohi, kai zai yiwu haka ta faru ga wanda yake mai shakku ne amma kuma wani mai ilimi ya kasa aikata haka. A nan maganar Malam Sanusi ta ƙare.

Idan ka ce, to, bayyana muna madogara ta kafirtawa, domin mu san wanda ake kafirtawa da wanda ba a kafirtawa. Sai in ce: to, ka sani shi, kafirci, shi ne kishiyar imani. Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce:

﴿فَمِنْهُم مَّنْ ءَامَنَ وَمِنْهُم مَّن كَفَرَ﴾البقرة: ٢٥٣

*"Kuma daga gare su akwai waɗanda suka yi imani kuma daga cikinsu akwai waɗanda suka kafirta." Baƙara:253*

Imani shi ne gaskata Manzo kuma da gaskata abin da ya zo da shi. Shi kuwa kafirci shi ne ƙaryata haka. A cikin gaskata Manzo akwai gaskata Allah. A cikin ƙaryata shi kuwa akwai kishiyar haka.

﴿مَّن يُطِعِ ٱلرَّسُولَ فَقَدْ أَطَاعَ ٱللَّهَ﴾النساء: ٨٠

*"Wanda ya yi wa Manzo ɗa'a, to, lalle ya yi wa Allah ɗa'a" Nisa'i:80*

To, idan ka fahinci wannan za ka san cewa abin da a madogara ga kafirtawa shi ne ƙaryata Manzo. Bayanin wannan shi ne ka san cewa kafirci shi ne saɓa wa nassi yankakke, ko saɓa wa ijma'i na gaba ɗaya a game da wani al'amari na addini, to, a cikin waɗannan biyu akwai ƙaryata Manzo. Wannan matsala ce ta fiƙihu wadda hankali da nazari ba su da abin cewa a ciki.

To, idan ka ce: ƙara muna bayani dangane da wannan, sai in ce: ka sani sharhin wannan al'amari na abin da ake kafirta mutum da shi da wanda ba a kafirtawa, to, abu ne da ke neman bayani mai tsawo. Amma sai ka gamsu da wata wasiyya kuma da wata doka. A cikinsu akwai gamsuwa a game da wannan manufar.

Ita dai wasiyya ita ce ka kame kanka daga kafirta ma'abuta addinin Musulunci gaba ɗaya idan dai suna furta kalmar shahada kuma ba su warware ta ba. Warware ta na kasancewa ta zahiri da wani abu da muke iya tsinkaya a gare shi a zahiri ta hanyar bayyanar da kafirci a aikace. Wannan kamar girmama waɗansu duwatsu da itatuwa ta hanyar yin yanka a gare su ko zuba wani ɗan gari a gare su. (Ko kuwa kafircin) ya bayyana ta hanyar zance, kamar izgili da addinin Allah da ƙaryata abin da aka san Manzo ya zo da shi a kan Larura.

Amma a game da warwarewa ta baɗini, to, wannan ba mu kasance masu iko ga haka ba.

Amma a game da doka, to, yana kasancewa ka san cewa addini ya rabu zuwa gida biyu. Wani yanki ya rataya ne da asalin aƙidoji. Shi kuwa ɗayan yana da dangantaka ne da rassa.

A koyaushe aka sami ƙaryatawa, to, kafirtawa ta wajaba. Daɗa wannan duk ɗaya ne a wajen asali ne ƙaryatawar ta auku ko kuwa ga reshe ne, idan dai abin da aka ƙaryata ya kasance abin da aka san Manzo ne ya zo da shi a kan larura.

Malam Nawawi ya ce: Wanda ya yi musun abin da aka sani a cikin addinin Musulunci wanda yake a kan larura, to, za a yi hukunci da ridda tasa kuma da kafirci nasa, face wanda ya kasance sabon shiga ne a Musulunci, ko kuma ya kasance ya taso a cikin daji mai nisa (daga inda ake samun koyarwa ta Musulunci) da wanda yake makamancinsa wanda yake irin wannan abu na ɓoyuwa a gare shi. To, shi kuwa sai a karantar da shi. Idan kuwa ya ci gaba da ƙaryatawa, to, sai a yi hukunci da kafircinsa. Wannan kamar hukunci (ga kafircin) wanda ya halattar da zina ko giya ko kisan kai ko waninsu na daga abubuwan da aka san haramcinsu a kan larura.

Tabbatattar maganar da ya ambata (watau Nawawi) a cikin littafinsa na ***Raula*** shi ne duk wanda ya yi musun wani abu da aka yi ijma'i a kansa kuma abin da yake sananne a kan larura, to, ya kafirta. Duk ɗaya ne abin akwai nassi a kansa ko kuwa babu. Abin da ake nufi da abin da aka sani a kan larura shi ne, abu ya kasance daga al'amura na Musulunci kuma na zahiri wanda malami da wanda ba malami ba sun yi tarewa ga saninsa aka san Manzo ya zo da shi a kan Larura.

Amma a game da warwarewa ta baɗini, to, wannan ba mu kasance masu iko ga haka ba.

Amma a game da doka, to, yana kasancewa ka san cewa addini ya rabu zuwa gida biyu. Wani yanki ya rataya ne da asalin aƙidoji. Shi kuwa ɗayan yana da dangantaka ne da rassa.

A koyaushe aka sami ƙaryatawa, to, kafirtawa ta wajaba. Daɗa wannan duk ɗaya ne a wajen asali ne ƙaryatawar ta auku ko kuwa ga reshe ne, idan dai abin da aka ƙaryata ya kasance abin da aka san Manzo ne ya zo da shi a kan larura.

Malam Nawawi ya ce: "Wanda ya yi musun abin da aka sani a cikin addinin Musulunci wanda yake a kan larura, to, za a yi hukunci da ridda tasa kuma da kafirci nasa, face wanda ya kasance sabon shiga ne a Musulunci, ko kuma ya kasance ya tasa a cikin daji mai nisa (daga inda ake samun koyarwa ta musulunci) da wanda yake makamancinsa wanda yake irin wannan abu na ɓoyuwa a gare shi. To, shi kuwa sai a karantar da shi. Idan kuwa ya ci gaba da ƙaryatawa, to, sai a yi hukunci da kafircinsa. Wannan kamar hukunci (ga kafircin) wanda ya halattar da zina ko giya ko kisan kai ko waninsu na daga abubuwan da aka san haramcinsu a kan larura."

Tabbatattar maganar da ya ambata (watau Nawawi) a cikin littafinsa na Raula shi ne, duk wanda ya yi musun wani abu da aka yi ijma'i a kansa kuma abin da yake sananne a kan larura, to, ya kafirta. Duk ɗaya ne abin akwai nassi a kansa ko kuwa babu. Abin da ake nufi da abin da aka sani a kan larura shi ne, abu ya kasance daga al'amura na Musulunci kuma na zahiri wanda malami da wanda ba malami ba sun yi tarewa ga saninsa.

# هداية الطالبين

# SHIRYAR DA ƊALIBAI

Na

Shehu Usmanu Ɗanfodiyo

Mai Fassara:
Muhammad Isa Talata Mafara

## ABUBUWAN DA KE CIKI

**Shafi**


GABATARWAR MAWALLAFI........................................................ 193

SASHI NA ƊAYA: Ilimin Asalin Addini ................................................194

Mu'ujizar Annabawa................................................................ 198

Karamar Waliyyai .................................................................... 198

Azabar Kabari Da Tambaya A Cikinsa..................................................... 199

Tara Talikai Gaba Ɗaya A Wuri Ɗaya..................................................... 200

Tafkin Alkausara........................................................................ 201

Siraɗi ........................................................................................ 202

Sikeli ........................................................................................ 203

Ceto ......................................................................................... 204

Ganin Muminai Ga Allah Maɗaukakin Sarki ........................................ 206

Mi'iraji, Shin Da Jikinsa Da Ruhinsa Ko A'a Ko Kuwa A Cikin Barci? .. 207

Saukar Isa Ɗan Maryam Amincin Allah Ya Tabbata A Gare Shi ............ 209

Ɗauke Alƙur'ani ......................................................................... 212

Aljanna Da Wuta An Riga An Halitta Su ............................................... 213

Aljanna A Sama Take ................................................................. 214

Ko A Ina Ne Wuta Take?........................................................................ 215

Rai Mai Wanzuwa Ne Bayan Mutuwa .................................................... 216

Ba A Mutuwa Sai Kwana Sun Ƙare........................................................ 216

Fasicci Ba Ya Kawar Da Imani ................................................................ 216

Mafificin Talikai Shi Ne Annabi Mu-Hammad Sa'annan Annabawa Ulul Azmi, Sa'annan Sauran Annabawa ........................................................ 217

Mala'iku Ke Biye Da Annabawa ........................................................ 219

Fifiko A Tsakanin Sahabbai ........................................................ 219

Fifikon Daraja A Tsakanin Mata ........................................................ 222

Mafificiya Daga Matan Annabi ........................................................ 223

Annabawa Abin Tsarewa Ne Daga Kowane Zunubi ................................ 224

Dukan Sahabbai Adilai Ne ........................................................ 224

Shugabanni Ma'abuta Mazhabobi Da Wasunsu Suna A Kan Shiriya ....... 225

SASHI NA BIYU: Ilimin Sufanci ………………..…………………....227

Mumini Kammalalle ........................................................ 232

Rassan Imani ........................................................ 233

(1-6) Imani Da Allah Da Mala'iku Da Littattafai Da Manzanni Da Kaddara Da Ranar Alƙiyama ........................................................ 233

(7-9) Son Allah Da So Da Ki Dominsa Kuma Da Son Annabi ................ 233

(10) Girmama Annabi ........................................................ 234

(11) Iƙhlasi (Tsarkake Aiki Domin Allah) ........................................ 235

(12) Tsoro (Tsoron Azabar Allah) ........................................................ 236

(13) Fatar Rahamar Allah ........................................................ 237

(14) Godiyar Allah ........................................................ 237

(15) Cika Alƙawari ........................................................ 238

(16-17) Haƙuri Da Yarda Da Hukuncin Allah.......................................... 239

(18) Jin Kunya.............................................................................. 239

(19) Dogara Ga Allah.................................................................... 240

(20) Rahama.................................................................................. 241

(21-22) Tawali'u, Barin Girman Kai Da Ji-Da-Kai.................................. 241

(23) Barin Hasada Da Jiyewa.......................................................... 243

(24) Barin Fushi............................................................................ 244

(25) Furuci Da Kalmar Shahada...................................................... 245

(26) Karatun Alƙur'ani.................................................................. 245

(27-28) Neman Ilimi Da Sanar Da Shi.............................................. 246

(29) Addu'a.................................................................................. 247

(30-31) Zikiri Da Nisantar Yasassar Magana........................................ 247

(32) Tsarki Na Bayyane Da Na Hukunce.......................................... 249

(33) Suturce Al'aura....................................................................... 250

(34-35) Sallar Farilla Da Ta Nafila Da Zakka....................................... 251

(36) Fansar Bayi Da 'Yanta Su........................................................ 252

(37) Kyauta.................................................................................. 253

(38) Azumi Na Farilla Da Na Taɗawwa'i.......................................... 253

(39) Yin I'itikafi............................................................................ 255

(40) Neman Lailatul Kadri.............................................................. 255

(41) Hajji Da Umra........................................................................ 255

(42) Ɗawafi ........................................................................................ 256

(43) Gudu Domin Kubutar Da Addini ...................................................... 256

(44-45) Cika Alwashi Da Kiyaye Rantsuwa ............................................. 257

(46) Ba Da Kaffara ..................................................................................... 257

(47) Kame Kai Ta Hanyar Yin Aure .......................................................... 258

(48) Tsayuwa Da Hakkokin Iyali .............................................................. 258

(49) Biyayya Ga Iyaye ................................................................................ 259

(50) Tarbiyyar 'Ya'ya .................................................................................. 260

(51) Sadar Da Zumunta .............................................................................. 261

(52) Biyayya Ga Uwayengiji Da Tausaya Wa Waɗanda Aka Mallaka..... 261

(53) Tsayuwa Da Shugabanci Tare Da Yin Adalci .................................. 262

(54) Hukunci Da Littafin Allah Ɗa Da'a Ga Annabi Da Rashin Jayayya Da 'Yan'adam Da Lizimtar Jama'a .................................................................. 263

(55) Biyayya Ga Ma'abuta Umarni ........................................................... 263

(56) Sulhi A Tsakanin Mutane ................................................................... 264

(57) Taimaka Wa Juna A Bisa Ga Alheri Da Taƙawa .............................. 265

(58) Tsayar Da Haddi .................................................................................. 265

(59) Jihadi A Kan Hanyar Allah ................................................................ 266

(60) Bayar Da Amana ................................................................................. 266

(61) Ba Da Rance ........................................................................................ 267

(62) Girmama Makwabci ........................................................................... 267

(63) Kyakkyawar Mu'amala ...................................................................... 268

(64) Ciyar Da Dukiya A Wurin Da Ya Cancanta ...................................... 268

(65) Mayar Da Sallama ............................................................................ 269

(66) Gayar Da Mai Atishawa .................................................................... 270

(67) Kame Cutarka Daga Mutane ............................................................ 270

(68) Nisantar Wasanni ............................................................................... 271

(69) Gusar Da Abin Da Ke Cutarwa Daga Hanya ................................... 271

Kammalawa ................................................................................................ 272

Matakan Fannonin Ilimi ............................................................................ 274

Salla Ita Ce Mafificiya Daga Dukan Ibada ............................................... 275

Yin Nafila A Gida Shi Ya Fi A Bisa Ga Wajensa .................................... 276

Nafilar Dare Ta Fi A Bisa Ga Ta Rana ..................................................... 277

Karatun Alƙur'ani Da Fahimta Shi Ne Ya Fi Dukan Zikiri ...................... 278

KARANTA ALKUR'ANI DA LITTAFI YA FI A BISA GA YI DA KA 280

Yin Kawaici Shi Ya Fi A Bisa Ga Yin Magana Face A Kan Hakki.......... 281

Cuɗanya Da Mutane Da Jure Wa Cutarsu Ya Fi Daga Nisantarsu ........... 283

Samun Gwargwadon Buƙata Shi Ne Ya Fi A Bisa Ga Talauci Da Tara Dukiya .................................................................................................... 284

SASHI NA UKU: A Game Da Waɗansu Hadisai Daga Cikin Buhari Da Muslimu Da Suka Kamata Mai Hankali Ya San Su........................................289

Zikirorin Dare Da Yini ................................................................................ 289

Zikirori A Cikin Salla Da Bayan Kare Salla ............................................. 292

Zikiri Bayan Kare Alwala Kuma Da Yadda Ake Karba Wa Mai Kiran Salla ................................................................................................................ 294

SHIRYAR DA ƊALIBAI

Zikiri A Wajen Kwanciya ........................................................ 296

Zikiri Ga Wanda Ke A Cikin Damuwa .................................................... 297

Zikiri A Lokacin Shiga Gida Kuma Da Lokacin Cin Abinci ................... 298

Zikiri Domin Samun Shiga Aljanna ........................................................ 299

Zikiri Domin Kariya Daga Shaiɗan ........................................................ 300

Sa'ar Da Ake Karba Addu'a A Cikin Dare .............................................. 303

Neman Tsari Kuma Da Yin Tofi A Lokacin Kwanciya ........................... 304

Falalar Sunayen Allah Casa'in Da Tara .................................................... 305

Nau'o'in Sadaka ........................................................................................ 305

Falalar Karatun Alƙur'ani Da Falalar Waɗansu Surori ............................ 307

Falalar Azumin Ranar Arfa Da Ashura Kuma Da Azumin Kwana Uku A Kowane Wata ........................................................................................ 307

Falalar Sadaka Kuma Da Falalar Sauƙaƙe Wa Matsattse.......................... 308

Falalar Istigfari ......................................................................................... 309

Falalar Salla A Cikin Yini Da Dare ......................................................... 310

Yi Wa Ɗan'uwa Musulmi Addu'a A Lokacin Da Ba Ya Nan.................. 311

Kammalawa .............................................................................................. 312

Bayanin Baƙin Kalmomi .......................................................................... 314

## GABATARWAR MAWALLAFI

**Da sunan Allah Mai rahama Mai jin-ƙai**

Allah ya daɗa tsira a bisa ga shugabanmu, Muhammad da iyalan gidansa da sahabbansa kuma Ya yi aminci a gare su aminci mai yawa.

Bawa, mabuƙaci, matsattse, kuma mai zunubi, mai rauni kuma wanda aikinsa ya munana, wanda yake shi ne Usmanu ɗan Muhammad ɗan Usmanu Bafulatani ga nasaba, Bamalike ga mazhaba, kuma Ba'ash'are ga aƙida; Allah ya amfane mu da shi kuma Ya albarkace mu da iliminsa, amin. Kuma Ya gafarta zunubansa da alfarmar shugaban mutanen farko da na ƙarshe ya ce: Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, kuma tsira da amincin Allah su tabbata a bisa ga masoyinSa, Muhammad da Sahabbansa da jama'arsa har ya zuwa ranar sakamako.

Bayan haka: Wannan shi ne littafin HIDA'YATU AL-ƊALIBINA watau Shiryar Da Ɗalibai, mai amfani ne in Allah Maɗaukakin Sarki ya so ga wanda ya dogara gare shi.

Littafin yana da sassa uku:

**Sashi na ɗaya** a game da ilimin asalin addini (Tauhidi).

**Sashi na biyu** a game da ilimin Sufanci.

**Sashi na uku** a game da waɗansu hadisai da aka cirato daga littafin Buhari da Muslimu ko kuwa daga ɗayansu waɗanda ma'abucin hankali ba zai rafkana daga saninsu ba.

Allah ne nake roƙo daidaito da taimako da kiyayewa da shiriya.

## SASHI NA ƊAYA

### Ilimin Asalin Addini

Sashi na ɗaya, shi ne ilimin asalin addini. Abin da ake nufi da shi kamar yadda Malam Abdulrahman Suyuɗi ya sanar da shi, shi ne: "Ilimi ne da ake bincike a cikinsa a game da abin da ya wajaba a ƙudurta shi." Kuma ya rabu zuwa gida biyu: Akwai wanda jahiltarsa aibi ne ga imani; wannan kamar sanin Allah da siffofi naSa na daga abin tabbatarwa a gare Shi, kuma da waɗanda suke abin korewa; haka kuma da manzanci da annabci da al'amuran lahira. Wani yanki kuwa jahiltarsa ba ya da ta'asiri ga imani, wannan kamar fifikon mala'iku. Lalle, Malam Subki ya ambata a cikin wani littafi nasa cewa, idan mutum ya kasance a tsawon rayuwarsa bai taɓa tunanin fifita wanda yake annabi ne a kan mala'iki ba, Allah ba zai tambaye shi a game da haka ba.

**Talikai**: Su ne duk abin da ba Allah Maɗaukakin Sarki ba. Kuma su, fararru, ne, ma'ana halitta su aka yi watau dai an samar da su bayan da babu su. Abin da ke ma'anar zamansu fararru saboda su masu sauyawa ne, to, duk kuwa abin da ke sauyawa fararre ne; domin an same shi ne bayan da can a da babu shi. Wanda ya farar da su shi ne Allah Makaɗaici wanda babu kama a gare Shi ga ZatinSa ko ga siffofi naSa.

Allah daɗaɗɗe ne, ana nufin babu farko ga samuwarSa kuma babu ƙarewa ga ƙarshenSa. Domin da Ya kasance fararre, to, da Ya yi buƙata zuwa ga mai samarwa, Allah ya ɗaukaka daga haka. Faɗar Kalmar fararwa (Sani'i) ga Allah abu ne da ya watsu a wajen malaman tauhidi. Amma waɗansu suka ce a'a, bai dace ba, domin bai tusgo ba, alhali kuwa sunayen Allah ba a ƙiyasinsu. Sai aka ba da amsa da cewa, ai sunan yana da asali daga zancen Allah a cikin Alƙur'ani da ya ce: "Sun'allah" watau aikin Allah.

Kuma an karanta shi "Sana'allah"; watau Allah ya aikata, da lafazi na aikatau da ya shuɗe. Wannan an faɗe shi ne a bisa gamsuwa da tusgowarsa da lafazi na suna da aikatau da suka tusgo.

Malam Abdulrahman Suyuɗi ya ce: "Faɗar wannan suna (Sa'ni'u) ga Allah Maɗaukakin Sarki ya tusgo a cikin wani hadisi ingantacce, wanda da shi wanda ya ce ana faɗar haka da wanda ya ce a'a, ba su zo da shi ba. Hadisin kuwa Hakimu ya ruwaito shi kuma ya inganta shi, haka kuma

Baihaƙi ya ruwaito shi daga Huzaifa yana mai jingina shi ga Annabi cewa: "Allah ne ya aikata (Sana'a) kowane mai aiki da abin da ya aikata."

**ZATINSA:** Ya saɓa wa zantukan talikai, Allah ya girma kuma Ya ɗaukaka. Malam Suyuɗi ya faɗa a game da zancen Malam Subki a cikin littafin Jam'ul-Jawa'mi'i da ya ce: "HaƙiƙarSa ta saɓa wa sauran nau'o'in haƙiƙa" domin Malam ɗan Azzamlaka'ni ya ce: "Ba ya halatta a faɗi lafazin haƙiƙa ga Allah". Malam Ibnu Jama'a ya ce: "Domin bai tusgo ba. Amma faɗar kalmar zati a gare Shi ta tusgo." Ya zo a cikin Buhari ga ƙissar Khubaibu daga zancensa da ya ce: "Wannan a cikin Zatin Ubangiji."

**SIFFOFINSA:** Rayuwa, ita, wannan, siffa ce, wacce ke nuna ingancin ilimin wanda ya siffantu da ita.

Irada, watau nufi, ita kuwa siffa ce da ke keɓance ɓangarori biyu na faruwar abu ko rashin faruwarsa.

Ilimi, ita, wannan siffa, abubuwa na kuranyewa da ita a bisa ga ratayuwarta da su.

Kudura, watau iko, ita siffa ce da ke da ta'asiri da abubuwa a bisa ratayuwarta da su.

Ji da gani, waɗannan siffofi ne guda biyu da suke ƙara bayyanar da al'amura a bisa ga abin da siffar ilimi ta bayyanar.

Zance, zancenSa wanda ya tsayu da ZatinSa Maɗaukakin Sarki, watau dai abin da aka sani da Alƙur'ani, abin rubutawa a cikin takarda da nau'o'i na rubutu daban-daban da harufa masu nuni zuwa gare Shi, kuma abin haddacewa a cikin zukata da lafuza nasa abin kamantawa, kuma abin karantawa da harsuna da harufa da ake faɗa kuma ake ji.

To, duk waɗannan siffofi daɗaɗɗu ne.

Shi, Allah Maɗaukaki, abin tsarkakewa ne daga jiki da launi da ɗanɗano da Arlu da sauka. Ma'ana Ya tsarkaka ga a ce Ya sauka a cikin wani abu (Ya haɗe da shi). Wannan kuwa saboda kasancewar waɗannan abubuwa fararru ne alhali Shi kuwa Maɗaukakin Sarki ya tsarkaka daga faruwa. Abin da ake kira jiki shi ne abin da kasancewarsa ta dogara ga wani abu. Launi da

ɗanɗano suna daga cikin Arlu. Allah yana nan kamar yadda Ya faɗa a cikin littafinSa Mabuwayi:

﴿لَيْسَ كَمِثْلِهِۦ شَىْءٌ ۖ وَهُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلْبَصِيرُ ﴿١١﴾﴾ الشورى: ١١

***"Wani abu bai zama kamar tamkarSa ba, kuma Shi ne Mai ji, Mai gani." Shurah:11***

Abin da ya tusgo a cikin Alƙur'ani da Sunna na daga siffofi muna imani da zahirinSa, kuma mu tsarkake Shi daga haƙiƙa taSa; wannan kamar faɗarSa Maɗaukakin Sarki:

﴿ٱلرَّحْمَٰنُ عَلَى ٱلْعَرْشِ ٱسْتَوَىٰ ﴿٥﴾﴾ طه: ٥

***"Mai rahama Ya daidaita a kan Al'arshi." Daha:5***

﴿وَيَبْقَىٰ وَجْهُ رَبِّكَ ذُو ٱلْجَلَٰلِ وَٱلْإِكْرَامِ ﴿٢٧﴾﴾ الرحمن: ٢٧

***"Kuma fuskar Ubangijinka ke wanzuwa." Arrahman:27***

﴿وَلِتُصْنَعَ عَلَىٰ عَيْنِىٓ ﴿٣٩﴾﴾ طه: ٣٩

***"Kuma domin a riƙe ka da kyau a kan ganiNa." Daha:39***

﴿يَدُ ٱللَّهِ فَوْقَ أَيْدِيهِمْ﴾ الفتح: ١٠

***"Hannun Allah na bisa hannayensu." Fathi:10***

Haka har wa yau da faɗarsa tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi.

(إن قلوب بني آدم كلها بين أصبعين من أصابع الرحمن كقلب واحد يصرفه كيف يشاء)

***"Lalle zukatan 'yan'adam suna a tsakanin yatsu biyu na daga yatsun Mai rahama kamar zuciya ɗaya Yana juyar da su yadda Ya so."*** Muslimu ne ya ruwaito hadisin.

Sa'annan sai mu fawalla sanin ma'anarsa (watau nassin da ya zo da siffa) zuwa ga Allah Maɗaukakin Sarki, wanda wannan ita ce mazhaba ta magabata, kuma ita ce hanya mafi aminci. Ko kuwa mu yi ta'wili kamar yadda abin yake a mazhaba ta malamai da suka biyo a baya. A bisa ga

wannan sai mu yi ta'wilin daidaita da rinjaya; ita kuwa fuska sai ta zama da ma'anar zati; shi kuwa gani ya zama da ma'anar tausasawa; a lokacin da hannu yake da ma'anar iko. Abin da ke manufa ga hadisin da ya gabata shi ne zukatan bayi a gaba ɗayansu idan aka danganta su ga ƙudura taSa, to, ba wani abu suke ba, Yana juyar da su yadda Ya so, kamar yadda ɗaya daga bayi naSa ke sarrafa wani abu kaɗan a tsakanin yatsu biyu daga yatsunsa.

Kudura, wannan shi ne abin da ke aukuwa na daga abin da aka ƙaddarta tun azal na daga alheri da sharri. Dukan biyun daga Allah suke Maɗaukaki suna daga halittarSa da nufinSa. Abin da Ya so shi ke kasancewa, kuma abin da Bai so ba, to, ba ya kasancewa. Allah ba ya gafarta shirka idan an mutu ana yinta, amma yana gafarta abin da bai kai gare ta ba idan Ya so.

Allah Maɗaukakin Sarki ya ce:

﴿ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَغْفِرُ أَن يُشْرَكَ بِهِۦ وَيَغْفِرُ مَا دُونَ ذَٰلِكَ لِمَن يَشَآءُ ﴾ النساء: ٤٨

***"Lalle ne, Allah ba ya gafarta a yi shirki game da Shi, kuma Yana gafarta abin da yake bayan wannan ga wanda Yake so." Nisa'i:48***

Babu wani abu da yake wajaba a kanSa Maɗaukakin Sarki; domin Shi ne wanda ya halitta talikai. Ta yaya ne wani abu zai wajaba a kanSa ta ɓangarensu?

Allah Maɗaukakin Sarki ya aiko ManzanninSa suna abin ƙarfafawa da mu'jizoji marinjaya kuma bayyanannu, kuma Ya cika manzancinsu da Annabi Muhammad tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi. Wannan kamar yadda Maɗaukakin Sarki ya faɗa:

﴿ وَلَٰكِن رَّسُولَ ٱللَّهِ وَخَاتَمَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ ﴾ الأحزاب: ٤٠

***"Kuma amma shi ya kasance Manzon Allah kuma cikon Annabawa." Ahzaf:40***

A cikin wannan bayani na (Alƙur'ani) akwai nau'i na ilimin Balaga na juyar da abu. Domin asalin abin shi ne Ya cika annabcinsu da Muhammad. Fa'idar da ke akwai ita ce nuni da cewa a haƙiƙa shi ne farko (ko da yake ya zo a ƙarshe). A cikin hadisi na Isra'i ya ce:

(جعلتك أول النبين خلقا وآخرهم بعثا)

*"Na sanya ka farkon annabawa ga halitta, kuma ƙarshensu ga aikowa."*

Wannan hadisi Bazzaru ne ya ruwaito shi daga hadisin Abuhuraira.

## MU'UJIZAR ANNABAWA

Mu'ujiza da aka ƙarfafa manzanni da ita, wani abu ne da ya saɓa wa al'ada. Watau dai al'amari ya gudana a bisa ga saɓanin abin da aka sani. Wannan kamar rayar da matacce, ko halaka dutse ko ɓuɓɓugowar ruwa a tsakanin yatsu a bisa ga ƙalubalanta ta da'awar Manzanci. Da haka sai aka fitar da abin da bai saɓa wa al'ada ba, kamar ɓullowar rana a kowace safiya, haka kuma aka fitar da abin da ya saɓa wa al'ada amma ba tare da ƙalubalanta ba. Wannan an san shi da sunan karama ta Waliyyai. Haka kuma aka fitar da abin da ya saɓa wa al'ada da ya auku saɓanin abin da shi mai da'awa ke da'awa a kansa. Wannan kamar ya yi da'awar cewa, gaskiyarsa shi ne jariri ya yi magana da gaskata shi, to, amma sai jaririn ya yi magana da ƙaryata shi.

## KARAMAR WALIYYAI

Karama tana kasancewa ga waliyyi a bisa gwargwado. Wannan kuwa shi ne mutumin da ya lizimci yin ɗa'a ga Allah, kuma ya nisanci saɓa maSa, kuma ya kawar da kai ga kutsawa a cikin abubuwan jin daɗi da sha'awoyi. Misali a gare ta gudanar Kogin Nil da takardar Umar yardar Allah ta tabbata a gare shi, haka kuma da ganinsa ga wata runduna ta yaƙi da ya tura zuwa Nahawanda alhali yana a kan minbarinsa a garin Madina har ya ce ga kwamandan wannan rundunar (mai suna Sariya): Ya kai Sariya dutsi (dutsi); watau yana mai yi masa kashedi da bayan dutsi a dalilin kasancewar abokan gaba sun yi kwanto a wurin; haka kuma da cewa shi, Sariya, ya ji sautin Umar, duk da kasancewa akwai fage mai nisa a tsakaninsu. Wannan dai da ire-irensa na daga abubuwan da suka auku ga sahabbai da waninsu. Amma samuwar ɗa ba tare da mahaifi ba, ko juyar da wani abu sandararre ya koma dabba, wannan ba zai kasance karama ga waliyyi ba. Wannan shi ne ra'ayin Malam Kushairi da ya shiga tsaka-tsaki.

Malam Ibnus Subki ya faɗa a cikin littafin Jam'ul Jawa'mi'i: Wannan magana ce ta gaskiya wacce ke keɓance zancen waninsa da ya ce: abin da ya

kasance mu'ujiza ga wani annabi, to, yana kasancewa karama ga waliyyi ba tare da wani bambanci ba sai ƙalubalanta.

## AZABAR KABARI DA TAMBAYA A CIKINSA

Muna ƙudurta cewa azabar ƙabari gaskiya ce. Wannan ga kafiri da fasiƙin da aka nufi azabtarwa a gare shi. Wannan ta hanyar mayar da rayuwa a jikinsa, ko wani abu da ya rage na jiki. Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(عذاب القبر حق)

***"Azabar ƙabari gaskiya ce."***

Wata rana Manzo ya wuce ga wasu kaburbura biyu sai ya ce:

(إنهما يعذبان)

***"Lalle, su, ana yi musu azaba."*** Buhari da Muslimu suka ruwaito waɗannan hadisan guda biyu.

Tambayar mala'iku biyu, watau Munkar da Nakir ga wanda aka sanya a cikin ƙabari gaskiya ne. Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(إن العبد إذا وضع في قبره وتولى عنه أصحابه أتاه ملكان فيقعدانه فيقولان له ما كنت تقول في هذا النبى محمد –صلى الله عليه وسلم– فأما المؤمن فيقول أشهد أنه عبدالله ورسوله وأما الكافر أوالمنافق فيقولان لا أدرى)

***"Lalle bawa, idan aka sanya shi a cikin ƙabari kuma jama'a suka juya, to, mala'iku biyu za su zo a gare shi, kuma su zaunar da shi, sai su ce a gare shi: Me ne ka kasance kana faɗa a game da wannan Annabi Muhammad tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi? Wanda yake mumini zai ce: "Ina sheda cewa, shi, bawan Allah, ne kuma manzonSa ne. Amma shi kafiri da munafiki za su ce ba mu sani ba."*** Buhari da Muslimu suka ruwaito.

A wata ruwaya ta Abudawuda, mala'ikun za su ce a gare shi,

(فيقولان له من ربك وما دينك وما هذا الرجل الذي بعث فيكم فيقول المؤمن ربى الله وديني الإسلام والرجل المبعوث رسول الله صلى الله عليه وسلم- ويقول الكافر في الثلاث لا أدري)

***"Wane ne Ubangijinka, kuma mene ne addininka, kuma mene ne wannan namiji da aka aiko a cikinku? Mumini zai ce: "Ubangijina Allah, kuma addinina Musulunci, kuma namijin da aka aiko a cikinmu Manzon Allah ne, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi."***

Shi kuwa kafiri zai ce bai sani ba, ga dukan waɗannan (tambayoyi) uku.

A wata ruwaya ta Tirmizi: ana ce da gudansu, Munkaru; guda kuwa Nakiru.

Malam Abdulrahman Suyuɗi ya ce: "Ibnu Yunusa daga malamanmu ya ambata cewa, mala'ikun da ke zo wa mumini Mubasshiru da Bashiru ne sunayensu."

## TARA TALIKAI GABA ƊAYA A WURI ƊAYA

Tara talikai gaba ɗaya gaskiya ne. Wannan shi ne, Allah ya raya su bayan ƙarewarsu, kuma Ya tara su domin bincike da hisabi. Mayar da jiki bayan an rasa shi da sassansa da halayyarsa (ta motsi da natsuwa) tamkar yadda yake can farko gaskiya ne. Allah Maɗaukakin Sarki ya ce:

﴿وَحَشَرْنَٰهُمْ فَلَمْ نُغَادِرْ مِنْهُمْ أَحَدًا ﴿٤٧﴾﴾ الكهف: ٤٧

***"Kuma Mu tara su har ba Mu bar kowa ba daga gare su". Kahfi:47***

﴿وَإِذَا ٱلْوُحُوشُ حُشِرَتْ ﴿٥﴾﴾ التكوير: ٥

***"Kuma idan dabbobin daji aka tattara su" Kausar:5***

﴿وَهُوَ ٱلَّذِى يَبْدَؤُا۟ ٱلْخَلْقَ ثُمَّ يُعِيدُهُۥ﴾ الروم: ٢٧

***"Kuma Shi ne wanda Ya fara halitta, sa'annan Ya sake ta". Rum:27***

﴿كَمَا بَدَأْنَآ أَوَّلَ خَلْقٍ نُّعِيدُهُۥ﴾ الأنبياء: ١٠٤

*"Kamar yadda Muka fara a farkon halitta Muke mayar da ita." Al-Anbiya'i:104*

## TAFKIN ALKAUSARA

Lalle Tabkin Alkausara, gaskiya ne. Malam Kurɗubi ya ce: Su, tafuka, ne guda biyu: Ɗayan a gabanin Siraɗi kuma gabanin auna sikeli a bisa ga mafi ingancin zance. Wannan kuwa domin mutane za su fito daga cikin ƙaburbura suna masu ƙishi sai su tusgo masa gabanin a auna ayyukansu kuma gabanin su hau siraɗi.

Na biyu shi kuwa a cikin Aljanna yake. Kuma dukan tafukan biyu ana kiransu da sunan Alkausara.

Muslimu ya ruwaito daga Anas, ya ce:

(بينما رسول الله صلى الله عليه وسلم- ذات يوم بين أظهرنا إذ اغفى إغفاءة ثم رفع رأسه متبسما فقلنا ما أضحكك يارسول الله قال –صلى الله عليه وسلم- (أنزلت على آنفا سورة فقرأنا إنا أعطيناك الكوثر ثم قال أتدرون ما الكوثر فقلنا الله ورسوله أعلم قال فإنه نهر وعدنيه ربي عليه خير كثير وهو حوض ترد عليه أمتي يوم القيامة آنيته عدد نجوم السماء يختلج العبد منهم فأقول يارب إنه من أمتي فيقال ما تدري ماأحدث بعدك)

***"Wata rana Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi yana a cikinmu, sai ya yi wata 'yar runtsawa sai kuma ya ɗaga kansa yana mai murmushi; sai muka ce: Me ya sanya ka dariya ya Manzon Allah? Sai Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: "Ba" da jimawa ba aka saukar da wata sura a gare ni." Sai ya karanta aya ta ɗaya daga Suratul-Kausar. Sa'annan sai ya ce: "Ko kun san abin da ake ce wa Alkausar? "Sai muka ce: Allah da ManzonSa suka sani. Sai ya ce: "Lalle shi, wata ƙorama ce da Ubangijina ya yi mini alƙawari da ita, tare da ita akwai alheri mai yawa. Ita,wani tafki, ne da al'ummata za su tusgo a gare shi a ranar Alƙiyama, ƙoransa (na sha) kamar yawan taurarin sama. Ana kore wani daga gare shi, sai in ce: "Ya Ubangiji lalle, shi yana daga al'ummata! Sai a ce, ba ka san abin da ya haddasa a bayanka ba."***

Ya zo a cikin Buhari:

(حوضي مسيرة شهر ماؤه أبيض من الورق وريحه أطيب من المسك وكيزانه كنجوم السماء من شرب منه لم يظمأ بعده أبدا، وفي رواية مسلم: (يشخب فيه ميزابان من الجنة)

***"Tafkina tafiyar wata ɗaya ne. Ruwansa suna da fari fiye da azurfa, kuma ƙanshinsu ya fi almiski, kuma ƙoransa tamkar taurarin sama ne, wanda ya sha daga gare shi ba zai yi ƙishi ba har abada."***

A wata ruwaya ta Muslimu:

(يشخب فيه ميزابان من الجنة)

***"Akwai magudanan ruwa guda biyu a cikinsa da suka fito daga Aljanna."***

A wani lafazi daga waninsa:

(غيره يغت فيه ميزابان من الكوثر)

***"Waɗansu magudanan ruwa biyu suna zuba a cikinsa (daga Aljanna).***

Ibnu Maja ya ruwaito hadisi:

(الكوثر نهر في الجنة حافتاه الذهب مجراه على الدر والياقوت تربته أطيب من المسك وأشد بياضا من الثلج)

***"Kausara, Korama, ce a cikin Aljanna, gaɓarta biyu zinari ne, magudanarta a bisa ga Lu'lu'i ne da yaƙuti, turɓayarta ita ce mafi ƙanshi daga almiski, kuma ruwanta su ne mafi fari daga ƙanƙara."***

## SIRAƊI

Siraɗi lalle gaskiya ne. Wannan kamar yadda ya zo a cikin hadisin Muslimu:

(جسر ممدود على ظهر جهنم أدق من الشعر وأحد من السيف حق)

***"Wata gada ce da aka shimfiɗa a kan Jahannama. Shi ne mafi ƙanƙanta daga gashi kuma mafi kaifi daga takobi."***

Ya zo a cikin Buhari:

(يضرب الصراط بين ظهراني جهنم ويمر المؤمنون عليه فأولهم كالبرق الخاطف ثم كمر الريح ثم كمر الطير وأشد الرجال حتى يجيء الرجل ولا يستطيع سيرا إلا زحفا وفي حافتيه كلاليب معلقة مأمورة بأخذ من أمرت بأخذه فمخدوش ناج ومكدوس في النار وأن الميزان حق وله لسان وكفتان تعرف به مقادير الأعمال بأن يوزن صحفها به)

***"Za a buga siraɗi a kan Jahannama, kuma muminai za su shuɗe a kansa: Na farkonsu tamkar walƙiya mai fisge ido; sa'annan kuma tamkar iska; sa'annan kamar shuɗewar tsuntsaye, haka kuma da kamar zambiyar namiji (majiyin ƙarfi); har a sami wani mutum ya zo ba ya iya tafiya face jan gindi. A sassansa guda biyu akwai waɗansu ƙugiyoyi da aka rataye, an umurce su da su kama wanda aka umurta da su kama shi. Akwai wanda aka yi wa rauni, kuma ya tsira, akwai kuma wanda ake jefawa a cikin wuta."***

SIKELI

Lalle ma'auni, watau sikeli gaskiya ne. Kuma shi yana da harshe da ɓangarori biyu; wanda da shi ne ake sanin gwargwadon ayyuka; watau dai a auna littattafan ayyuka. Allah Maɗaukakin Sarki ya faɗa:

﴿ وَنَضَعُ ٱلْمَوَٰزِينَ ٱلْقِسْطَ لِيَوْمِ ٱلْقِيَـٰمَةِ ﴾ الأنبياء: ٤٧

***"Kuma Muna aza ma'aunan adalci ga Ranar Kiyama." Al-Anbiya'i:47***

Tirimizi ya ruwaito hadisi kuma ya kyautatar da shi cewa:

(يصاح برجل من أمتي على رءوس الخلائق وينشر عليه تسعة وتسعون سجلا كل سجل مثل مدالبصر ثم يقول أتنكر من هذا شيئا أظلمك كتبتي الحافظون فيقول لا يارب فيقول أفلك عذر فيقول لا يا رب فيقول بلى إن لك عندنا حسنة وإنه لا ظلم عليك اليوم فتخرج له بطاقة فيها أشهد أن لا إله إلا الله وأشهد أن محمد عبده ورسوله فيقول له أحضر وزنك فيقول يارب ما فائدة البطاقة مع هذه السجلات فيقول إنك لا تظلم

فتوضع السجلات في كفة والبطاقة في كفة فطاشت السجلات فثقلت البطاقة ولا يثقل مع اسم الله شيء)

***"Za a yi kururuwa da wani mutum daga al'ummata a bisa ga kawunan talikai; sai a buɗe masa takardu casa'in da tara (na ayyukansa) kowace takarda iyakar ganin mutum; sa'annan Ya ce masa: "Ko akwai abin da kake musu daga wannan? Shin ko masu rubutu, masu tsaro sun zalunce ka? Sai ya ce: a'a, ya Ubangiji! Sai Allah ya ce: "To, kana da wani uzuri? Sai shi kuwa ya ce: a'a, ya Ubangiji! Sai Allah ya ce: "Gaskiya ne. lalle akwai gare ka a wajenmu aiki kyakkyawa, kuma lalle, babu zalunci a gare ka a yau.Daga nan sai a fitar da wata 'yar takarda a gare shi, a cikinta akwai: Ina shedar babu abin bauta da gaskiya face Allah, kuma ina shedar Muhammadu bawanSa ne kuma ManzonSa ne. Sai Ya ce masa: kawo abin awonka. Sai shi kuwa ya ce: Ya Ubangiji! Mece ce fa'idar wannan 'yar takarda tare da waɗanan takardu! Sai Ya ce: Lalle kai ba za a zalunce ka ba. Sai a ɗora waɗannan takardu a ɓangare ɗaya (na sikeli) ita kuwa wannan 'yar takarda a ɗayan ɓangaren; ta haka sai wannan 'yar takarda ta rinjayi waɗannan takardu; domin babu wani abu da zai kasance mai nauyi tare da sunan Allah."***

Gazali da Kurɗubi sun ce: Sikeli ba zai kasance ga kowa da kowa ba, domin mutanen nan dubu saba'in waɗanda ke shiga Aljanna ba tare da hisabi ba ba za a ɗora sikeli a gare su ba, kuma ba za su karɓi takardu ba.

## CETO

Ceto lalle gaskiya ne. Kuma shi nau'i-nau'i ne. Mafi girmansu shi ne ceto a wajen rarrabe hukunci da hutar da mutane daga tsawaitar tsayuwa. Wannan ya keɓanta da Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi. Wannan zai kasance bayan kai da komon talikai daga wannan Annabi zuwa ga wancan.

Ceto na biyu shi ne na shigar da waɗansu mutanen Aljanna ba tare da hisabi ba. Nawawi ya ce wannan ya keɓanta da Annabi. Malamai biyu watau Ibnu Daƙiƙil Idi da Subki sun yi shakka a game da wannan (magana ta Nawawi).

Ceto na uku shi ne a game da wanda ya cancanci shiga wuta sai ya zama bai shige ta ba. Alƙali Iyal ya ce wannan bai keɓanta da Manzon Allah

ba. Amma Nawawi ya yi shakku a game da haka. Subki ya ce, “ba a sami wani abu bayyananne ba a game da tabbatar da haka ko kuwa kore shi”.

Ceto na huɗu shi ne a game da fitar da waɗanda aka sanya a wuta na daga muminai. A nan Annabawa da mala’iku da Muminai suna tarewa da shi (Manzon Allah).

Ceto na biyar shi ne a game da ƙarin darajoji a cikin Aljanna ga waɗanda suka shige ta. Nawawi ya nuna yiwuwar keɓantar wannan da Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi.

Ceto na shida shi ne a game da sauƙaƙe azaba ga wanda ya cancanci dauwama a cikin wuta. Wannan kamar yadda yake ga Abu’ɗalib.

Ya zo a cikin Buhari cewa:

(أنه أول شافع وأول مشفع )

***“Ni ne farkon mai ceto kuma farkon wanda ake bai wa ceto.”***

Haka kuma an ambata masa amminsa, Abu’ɗalib, sai ya ce:

(لعله ينفعه شفاعتي فيجعل في ضحضاح من نار)

***“La’alla cetona zai amfane shi sai a sanya shi a wani wuri marashin zurfi daga wuta.”***

Baihaƙi ya ruwaito hadisi:

(خيرت بين الشفاعة وبين أن يدخل شطر أمتي الجنة فاخترت الشفاعة لأنها أعم وأكفي أترونها للمتقين لا ولكنها للمذنبين المتلوثين الخاطئين)

***“An ba ni zaɓi tsakanin ceto da rabi na daga al’ummata su shiga Aljanna, to, sai na zaɓi ceto, saboda kasancewarsa mafi gamewa kuma mafi zama isasshe. Shin kuna ganin ceto ga masu tsoron Allah yake kawai? A’a, lalle ceto ga masu zunubi yake waɗanda suka gauraya (ayyuka) kuma suka yi laifi?”***

## GANIN MUMINAI GA ALLAH MAƊAUKAKIN SARKI

Ganin muminai ga Allah Maɗaukakin Sarki gabanin shiga Aljanna da bayan an shige ta gaskiya ne. Allah Maɗaukakin Sarki ya ce:

﴿ وُجُوهٌ يَوْمَئِذٍ نَّاضِرَةٌ (٢٢) إِلَىٰ رَبِّهَا نَاظِرَةٌ (٢٣) ﴾ القيامة: ٢٢ – ٢٣

***"Wasu fuskoki a ranar nan masu annuri ne. Zuwa ga Ubangijinsu masu kallo ne." Al-Kiyamah:22-23***

Ya zo a cikin Buhari da Muslimu cewa:

(إن الناس قالوا يارسول الله هل نرى ربنا يوم القيامة فقال رسول الله –صلى الله عليه وسلم–: ((هل تضارون في القمر ليلة البدر قالوا لا يارسول الله قال فهل تضارون في الشمس ليس دونها سحاب قالوا لا يارسول الله قال فإنكم ترونه كذلك)

***"Waɗansu mutane sun ce, ya Manzon Allah! Shin muna ganin Ubangijinmu ranar Alƙiyama? Sai Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: "Ko kuna cutuwa ga ganin wata a daren goma sha huɗu?" Sai suka ce a'a ya Manzon Allah. Sai ya ce: "Ko kuna cutuwa ga ganin rana alhali babu wani girgije da ya shamakace ta? Sai suka ce, a'a, ya Manzon Allah! Sai ya ce: "To, lalle, kuna ganinSa kamar haka……"***

Har zuwa ƙarshen hadisi. A cikinsa (watau hadisin) wannan na kasancewa kafin shiga Aljanna.

Muslimu ya ruwaito hadisi:

(إذا دخل أهل الجنة الجنة يقول الله أتريدون شيئا أزيدكم فيقولون ألم تبيض وجوهنا ألم تدخلنا الجنة وتنجنا من النار فيكشف الحجاب فما أعطوا شيئا أحب إليهم من النظر إلى ربهم)

***"Idan 'yan Aljanna suka shiga Aljanna, Allah zai ce a gare su: Ko kuna son wani abu da Zan ƙara muku? Sai su kuwa su ce: Ashe ba Ka haskaka fuskokinmu ba? Ashe ba Ka shigar da mu Aljanna ba kuma Ka kuɓutar da mu daga wuta? Sai a kware shamaki. Ba a ba su wani abu mafi zama abin so a gare su ba kamar kallo zuwa ga Ubangijinsu".***

A wata ruwaya: Sa’annan ya karanta wannan ayar:

﴿ ۞ لِّلَّذِينَ أَحْسَنُوا الْحُسْنَىٰ وَزِيَادَةٌ ﴾ يونس: ٢٦

***“Waɗanda suka kyautata yi, suna da abu mai kyawo kuma da ƙari” Yunus:26***

Abu mai kyawo shi ne Aljanna; ƙari kuwa shi ne kallo zuwa ga Allah Maɗaukakin Sarki.

Wannan yana faruwa da kwarewa wadda take bayyananna Yana abin tsarkakewa daga fuskanta da kuma jiha.

Amma su, kafirai, ba su ganinSa. Wannan kuwa saboda faɗarSa Maɗaukakin Sarki:

﴿ كَلَّا إِنَّهُمْ عَن رَّبِّهِمْ يَوْمَئِذٍ لَّمَحْجُوبُونَ ﴿١٥﴾ ﴾ المطففين: ١٥

***“A’aha! Haƙiƙa, lalle ne su, daga Ubangijinsu a ranar nan waɗanda ake shamakacewa ne.” Al-Mudaffin:15***

Wannan ya dace da zancenSa Maɗaukakin Sarki:

﴿ لَّا تُدْرِكُهُ الْأَبْصَارُ ﴾ الأنعام: ١٠٣

***“Gannai ba su iya riskuwarSa.” Al-An’am:103***

Ana nufin waɗanda suka keɓanta da abin da ya gabata ba su ganinSa.

## MI’IRAJI, SHIN DA JIKINSA DA RUHINSA KO A’A KO KUWA A CIKIN BARCI?

Lalle Mi’iraji da jikin Annabi abin zaɓi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi zuwa sammai gaskiya ne. Wannan kuwa bayan da aka yi Isra’i da shi zuwa Baitil Miƙdasi alhali kuwa yana farke. Allah Maɗaukakin Sarki ya ce:

﴿ سُبْحَانَ الَّذِي أَسْرَىٰ بِعَبْدِهِ ﴾ الإسراء: ١

***“Tsarki ya tabbata ga wanda Ya yi tafiyar dare da bawanSa”. Isra’i:1***

Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(أتيت بالبراق وهو دآبة أبيض طويل فوق الحمار دون البغل يضع حافره عند منتهى طرفه فركبته حتى أتيت البيت المقدس إلى أن قال ثم عرج بنا إلى السماء)

***"An zo min da Buraka, ita, wata dabba, ce fara mai tsawo, sama da jaki koma da bayan alfadari. Tana aza ƙafafuwanta a matuƙar ganinta. Sai na hau samanta har na zo Baitil Miƙdasi."*** Wannan har zuwa inda ya ce: ***"Sa'annan aka hau da mu zuwa sama."*** Har zuwa ƙarshen hadisi. Muslimu ne ya ruwaito shi.

A wani zance cewa aka yi da Isra'i da Mi'raji sun kasance da ruhi ne kawai. Wannan saboda zancenSa Maɗaukakin Sarki.

﴿ وَمَا جَعَلْنَا ٱلرُّءْيَا ٱلَّتِىٓ أَرَيْنَٰكَ إِلَّا فِتْنَةً لِّلنَّاسِ ﴾ الإسراء: ٦٠

***"Kuma ba Mu sanya mafarki wanda Muka nuna maka ba face domin fitina ga mutane." Isra'i:60***

Haka kuma da abin da Ibnu Is'haƙa ya ruwaito a cikin siyar cewa: "Mu'awiya idan aka tambaye shi a game da Isra'i ya kasance yana cewa: mafarki ne na gaskiya daga Allah."

Haka kuma A'isha ta ce: "Ban rasa jikin Manzon Allah ba tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi (a wannan dare). A'a an dai yi Isra'i ne da ruhinsa."

An ba da amsa a game da aya ta (60) da ke cikin sura ta Isra'i da cewa faɗarSa" Fitina ga mutane" yana ƙarfafa cewa gani ne na ido. Domin ai shi, mafarki, babu wata fitina a game da shi, kuma babu wani mai ƙaryata shi.

Haka kuma ya inganta daga Ibnu Abbas na ya kasance yana cewa, gani ne na ido da aka nuna wa Manzon Allah.

Waɗansu kuma sun ce wannan ayar ba ta sauka ne a game da ƙissa ta Isra'i ba.

Haka kuma sun ba da amsa a game da zancen A'isha (Ban rasa jikinsa ba) da cewa a lokacin ai bai aure ta ba. Domin Isra'i ya kasance gabanin

hijira alhali kuwa ita ba ta tare a gidan Manzon Allah ba face sai a bayan hijira.

A wani zance cewa aka yi an yi Isra'i da shi alhali yana farke, shi kuwa Mi'raji a cikin barci.

A wani zancen an ce an yi Mi'rji da shi sau biyu: ɗaya a farke ɗaya kuwa a cikin barci.

Abdulrahman Suyuɗi ya ce: "Haƙiƙa, mun yi bayani na sosai da sosai a game da wannan (a littafin da muka yi) sharhin sunayen Annabi".

Ka'abu ya ruwaito cewa, matakan abin hawa na Mi'raji matakai ne na azurfa kuma da na zinari.

Ibnu Sa'ad ya ruwaito cewa matakan an laƙa musu lu'lu'i?.

## SAUKAR ISA ƊAN MARYAM AMINCIN ALLAH YA TABBATA A GARE SHI

Saukar Isa ɗan Maryam amincin Allah ya tabbata a gare shi lalle gaskiya ne. Ya zo a cikin ingantaccen hadisi daga Buhari cewa:

(لينزلن ابن مريم حكما عدلا فليكسرن الصليب وليقتلن الخنزير وليضعن الجزية)

***"Lalle ɗan Maryam zai sauka yana mai hukunci, adali; lalle zai karya kuros, kuma lalle zai kashe alade, kuma lalle zai kayar da ba da jiziya."*** Har zuwa ƙarshen hadisin.

Dayyalisi ya ruwaito hadisi a cikin Musnad nasa, Manzon Allah ya ce:

(أنا أولى الناس بعيسى ابن مريم فإذا رأيتموه فاعرفوه فإنه رجل مربوع إلى الحمرة والبياض كأن رأسه يقطر ماء ولم يصبه بلل وأنه يكسر الصليب ويقتل الخنزير ويفيض المال حتى يهلك الله الملل كلها إلا الإسلام وحتى يهلك الله زمانه مسيح الضلالة الأعور الكذاب وتقع الأمانة في الأرض حتى يرعى الأسد مع الإبل والنمر مع البقر

والذئاب مع الغنم وتلعب الصبيان بالحيات فلا يضر بعضهم بعضا يبقى في الأرض أربعين سنة ثم يموت ويصلي عليه المسلمون ويدفنوه)

***"Ni ne mafi cancantar mutane da Isa ɗan Maryam, to, idan kuka gan shi, ku san shi, lalle shi, murabba'i, ne kuma (jikinsa) yana da launin ja da fari; kansa yana ɗiga da ruwa alhali ruwa ba su taɓa shi ba. Lalle ne shi, zai karya kuros, kuma zai kashe alade, kuma dukiya za ta yawaita (a zamaninsa). Wannan har Allah ya halakar da dukan addinai face Musulunci. Kuma har Allah ya halakar a zamaninsa (Dujjal) mai kira zuwa ga ɓata, mai ido ɗaya, maƙaryaci. Amana za ta auku a cikin ƙasa har zaki ya yi kiyo tare da raƙumi, haka kuma damisa tare da shanu, kuma kuraye tare da awaki; kuma yara su riƙa wasa da macizai, sashi ba zai cuta wa sashi ba. Zai kasance a cikin duniya shekaru arba'in; sa'annan ya mutu, kuma Musulmi su yi salla a gare shi, kuma su turbuɗe shi."***

A wata ruwaya cewa aka yi:

(أنه يمكث سبع سنين في الأرض)

***"Lalle shi, zai zauna shekara bakwai a bayan ƙasa."***

An ce wannan ruwaya ita ce, mafi zama daidai. Abin da ake nufi da arba'in ga ruwaya ta farko tsawon zamansa a duniya kafin ɗauke shi kuma da bayan saukarsa. Domin an ɗauke shi zuwa sama yana ɗan shekaru talatin da uku.

A cikin ingantaccen hadisi da Muslimu ya ruwaito an ce:

(ما بين خلق آدم إلى قيام الساعة خلق)

***"A tsakanin halittar Adam zuwa tashin Alƙiyama babu wata halayya."***

A wata ruwaya:

(امر أكبر من الدجال)

***"Babu wani al'amari mai girma da ya kai Dujjal."***

A cikiin Musnad na Ahmad daga hadisin Jabir:

(يخرج الدجال في حفقة من الدين وإدبار من العلم وله أربعون ليلة يسيحها في الأرض اليوم كالسنة واليوم منها كالشهر واليوم منها كالجمعة ثم سائر أيامه كأيامكم هذه وله حمار يركبه عرض ما بين أذنيه أربعون ذراعا فيقول للناس أنا ربكم وهو أعور وأن ربكم ليس بأعور مكتوب بين عينيه كافر يقرؤه كل مؤمن كاتب وغير كاتب يرد كل ماء ومنهل إلا المدينة ومكة حرمهما الله عليه وقامت الملائكة لأبوابهما ومعه جبال من خبز والناس في جهد إلا من اتبعه ومعه نهران أنا أعلم بهما منه نهر يقول له الجنة ونهر يقول له النار فمن أدخل الذي يسميه الجنة فهو في النار ومن أدخل الذي يسميه النار فهو في الجنة قال ويبعث معه شياطين تكلم الناس ومعه فتنة عظيمة يأمر السماء فتمطر فيما يرى الناس ويقتل نفسا ثم يحييها فيما يرى الناس أيها الناس هل يفعل مثل هذا إلا الرب فيفر الناس إلي جبل الدخان بالشام فيأتيهم فيحاصرهم يشتد حصارهم ويجهدهم جهدا شديدا ثم ينزل عيسى –عليه السلام– فيأتي في السحر فيقول أيها الناس ما منعكم أن تخرجوا إلى الكذاب الخبيث فينطلقون فإذا هم بعيسى فتقام الصلاة فيقال تقدم يا روح الله فيقول فليتقدم إمامكم فليصل بكم فإذا صلوا صلاة الصبح خرجوا إليه فحين يراه الكذاب ينماع أى يذوب كالملح في الماء فيقتله حتى أن الشجر والحجر ينادى يا روح الله هذا يهودي فلا يترك ممن كان يتبعه أحد إلا قتله)

*"Dujjal zai bayyana a lokacin girgizar addinai da ba da baya na ilimi. Yana da kwanaki arba'in da zai yawata a cikin ƙasa: Wani yini daga cikinsu tamkar shekara ne, wani kuwa tamkar wata ɗaya, wani kuwa tamkar mako ɗaya; sa'annan sauran ranaku tamkar ranakun da kuka saba da su. Yana da wani jaki da yake hawa: daga wannan kunne nasa zuwa wancan zira'i arba'in ne. Zai ce ga mutane: Ni ne Ubangijinku. To, shi yana da ido ɗaya, to, lalle Ubangijinku bai kasance mai ido ɗaya ba. An rubuta a tsakanin idanuwansa" "kafir" "kuma kowane mumini yana iya karanta shi, wanda ya san karatu da wanda bai sani ba. Zai tusgo wa kowaɗanne ruwa, kuma da kowace mashaya face Madina da Makka, su kuwa Allah ya haramta su a gare shi, domin Mala'iku suna a tsaye ga ƙofofinsu. Tare da shi akwai duwatsu na waina, kuma mutane suna a cikin tsanani face wanda ya bi shi. Tare da shi akwai ƙoramu biyu. Ni ne mafi sani da su. Korama ɗaya yana ce da ita, Aljanna,*

***ɗayar kuwa yana ce da ita wuta. Wanda ya shigar a cikin wannan da yake ce da ita, Aljanna, to, shi yana a cikin wuta; wanda kuwa ya shiga a cikin wadda ya ke ce da ita, wuta, to, shi yana Aljanna." Ya ce: "Za a tayar da sheɗanu tare da shi da suke magana da mutane. Akwai fitina mai girma tare da shi. Zai umarci sama da ta yi ruwa sai kuma ta yi a bisa ga abin da mutane ke gani. Zai kashe rai, sa'annan kuma ya rayar da wanda ya kashen a bisa ga ganin mutane. Sai ya ce ga mutane: Ya ku mutane! Akwai mai iya aiwatar da haka ban da Ubangiji? Mutane za su gudu zuwa ga wani dutsi mai hayaƙi da ke a can Sham. Sai kuma ya bi su a can ya kewaye su kuma ya tsanantar da ƙangi a kansu; kuma ya shigar da su a cikin wahala mai tsanani. Daga nan sai Isa amincin Allah ya tabbata a gare shi ya sauko. Zai sauko ne a lokacin jijjifi. Sai ya ce: Ya ku mutane! Me ya hana ku fita zuwa ga wannan maƙaryaci mummuna? Sai kuma su tafi. Ana haka sai ga Isa. Sai a yi iƙama domin salla. Sai a ce da Isa: Sai ka gabata ya kai Ruhullahi, sai shi kuma ya ce: a'a, limaminku ya gabata, kuma ya jagorance ku. Idan suka sallaci sallar Asuba sai su fita zuwa gare shi (Dujjal). Idan maƙaryacin ya gan shi (Isa) sai ya narke tamkar yadda gishiri kan narke a cikin ruwa. Daga nan sai (Isa) ya kashe shi. Itatuwa da duwatsu za su riƙa kira suna cewa, ya kai Ruhullah ga wani Bayahude a nan! Ba zai bar wani wanda ke biyar sa ba face sai ya kashe shi."*** A cikin Buhari akwai hadisai masu irin wannan ma'ana.

## ƊAUKE ALKUR'ANI

Lalle ɗauke Alƙur'ani gaskiya ne. Ibnu Maja ya ruwaito daga hadisin Huzaifa:

**(يدرس الإسلام كما يدرس وشى الثوب حتى لا يدرى ما صيام ولا صلاة ولا نسك ويسرى على كتاب الله في ليلة فلا يبقى في الأرض منه آية)**

***"Musulunci zai tsufa tamkar yadda zanen tufa ke tsufa har ya kai ba a sanin me ne azumi kuma mece ce salla, kuma mece ce ibada (ta yanka) kuma mece ce sadaka. Wannan zai shafi littafin Allah a cikin dare har ya kasance babu wata aya tasa da za ta rage a bayan ƙasa."***

Baihaƙi ya ruwaito a cikin littafin Shu'abul Imani daga Ibnu Mas'udu cewa, ya ce: "Ku karanci Alƙur'ani gabanin a ɗauke shi. Lalle, Alƙiyama ba za ta tsayu ba face sai an ɗauke shi. Sai suka ce, idan an ɗauke littattafai, to, yaya za a yi da abin da ke a cikin zukatan jama'a? Sai ya ce: Za a auka masa

dare ɗaya a ɗauke shi daga zukatansu! Sai su wayi gari ba su san kome ba. Daga nan sai su auka a cikin waƙa."

Malam Kurɗubi ya ce: "Wannan zai kasance bayan rasuwar Annabi Isa kuma bayan mutanen Habasha sun rusa Ka'aba".

## ALJANNA DA WUTA AN RIGA AN HALITTA SU

Muna masu aƙidar cewa: Aljanna da wuta halittattu ne a halin yanzu gabanin ranar sakamako. Wannan saboda nassoshi da ke nuna haka. Wannan kamar:

﴿أُعِدَّتْ لِلْمُتَّقِينَ ﴿١٣٣﴾﴾ آل عمران: ١٣٣

***"An yi tattalinta domin masu taƙawa" Ali-Imrana:133***

﴿أُعِدَّتْ لِلْكَٰفِرِينَ ﴿٢٤﴾﴾ البقرة: ٢٤

***An yi tattalinta domin kafirai." Baƙara:24***

Haka har wa yau da ƙissar Adamu da Hawwa'u a game da zaunar da su a cikin Aljanna kuma da fitar da su daga gare ta.

Haka kuma da hadisan Isra'i. Domin a cikinsu akwai:

(أدخلت الجنة وأريت النار)

***"An shigar da ni Aljanna, kuma an nuna min wuta."***

A cikin hadisin ceto:

( وهل أخرجكم من الجنة إلا خطيئة أبيكم)

***"Adamu zai ce: Shin me ya fitar da ku daga Aljanna face kuskuren babanku."***

Wannan da sauran ire-irensu.

## ALJANNA A SAMA TAKE

Mun kasance masu aƙidar cewar Aljanna na a cikin sama. A wani zance aka ce a ƙasa take; a wani kuwa aka yi waƙafi da cewa, babu wanda ya san haƙiƙanin al'amarin sai Allah.

Malam Abdurrahman Suyuɗi ya ce: "Abin da na zaɓa shi ne abin da ake fahimta daga ayoyin Alƙur'ani da hadisai".

Wannan kamar faɗarSa a game da ƙissar Adamu:

﴿قُلْنَا ٱهْبِطُوا۟ مِنْهَا﴾ البقرة: ٣٨

***"Muka ce: "Ku sauka daga gare ta." Baƙara:38***

A cikin Buhari akwai hadisin:

(سلوا الله الفردوس فإنه أعلى الجنة وفوقه عرش الرحمن ومنه تفجر أنهار الجنة)

***"Ku roƙi Allah Firdausi domin ita ce mafi ɗaukakar Aljanna; a sama gare ta Al'arshin Mai rahama yake; kuma daga gare ta ne ƙoramun Aljanna ke ɓuɓɓugowa."***

A cikin ingantaccen hadisi da Muslimu ya ruwaito:

(أروح الشهداء في حواصل طيور خضر تسرح في الجنة حيث شائت ثم تأوى إلى قناديل معلقة بالعرش)

***"Rayukan shahidai suna a cikin buliƙoton tsuntsaye, masu kore-kore suna kai da komo a cikin Aljanna a duk inda suka so; sa'annan sai su zo ga wata fitila da aka rataya ga Al'arshi."***

Abu Nu'aimi ya ruwaito a cikin littafinsa na tarihin Asbahan daga hanyar Ubaidu ɗan Mujahid daga Ibnu Amiru yana ɗaga hadisin (zuwa ga Manzon Allah) cewa:

(أن جهنم محيطة بالدنيا وإن الجنة من ورائها فلذلك كان الصراط على جهنم طريقا إلى الجنة ونقف عن النار أى نقول فيها بالوقف عن محلها حيث لا يعلمه إلا الله)

***"Lalle Jahannama tana kewaye da duniya, ita kuma Aljanna tana bayanta. A bisa ga wannan dalili ne Siraɗi ya kasance a saman Jahannama a kan hanya ta zuwa Aljanna."***

KO A INA NE WUTA TAKE?

Ita, wuta, za mu yi waƙafi a game da ita. Ma'ana za mu yi waƙafi ga faɗin bagiren da take domin ba wanda ya san takamaiman haka face Allah.

Malam Abdulrahman Suyuɗi ya ce: "Babu wani hadisi da ya tabbata a wajena da zan dogara da shi a game da wannan".

A wani zance, an ce a ƙarƙashin ƙasa wuta take. Wannan saboda wani hadisi da Ibnu Abdulbarri ya ruwaito kuma ya raunanar da shi na daga hadisin Abdullah ɗan Umar yana mai ɗaukaka shi zuwa ga Manzon Allah:

(لا يركب البحر إلا غاز أو حاج أو معتمر فإن تحت البحر نارا)

***"Babu mai hawa a cikin teku face mai yaƙi, ko mai zuwa hajji ko mai Umra, domin a ƙarƙashin teku akwai wuta."***

Haka kuma an ruwaito daga gare shi kwatankwacin haka:

(لا يتوضأ بماء البحر لأنه طبق جهنم)

***"Ba a alwala da ruwan Teku, domin ita, marufin Jahannama, ce."***

Ya zo a cikin littafin Shu'abul Imani na Baihaƙi daga Wahab ɗan Munabbah cewa: "Idan ranar Alƙiyama ta tsayu za a umarci Teku da ta yanke, to, sai ta yanke daga wuta. Tekun, ita ce marufi nata sai wuta ta fito daga gare ta, idan ta sadu da Teku wacce take marufi a bisa gaɓar Jahannama watau dai Teku babba, to, sai ta tsotse (ruwan) na Teku mafi gaggawa daga ƙiftawar ido. Waɗannan ruwan su ne shamaki a tsakanin Jahannama da ƙasa bakwai.

To, idan ta tsotse Tekun sai ta buru a can cikin ƙassai bakwai sai ta bar su (ƙassai bakwai) garwashi ɗaya.

A wani ƙauli cewa aka yi wuta a bayan ƙasa take. Wannan saboda har wa yau abin da aka ruwaito daga Wahabu ɗan Munabbah ya ce: "Zulƙarnaini ya je a wajen da dutsin Ka'f yake sai ya ga waɗansu duwatsu 'yan ƙanana a

ƙarƙashinsa. Wannan dai har zuwa inda ya ce da dutsin. "Ya kai Ka'f! Ba ni labari a game da girman Allah Maɗaukakin Sarki! Sai Kaf ya ce: Idan Ubangijinmu Mai girma Ya So: Lalle, bayana akwai wata ƙasa wacce tsawon tafiyarta shekaru ɗari biyar ne, haka kuma faɗinta. Ita tana daga duwatsun ƙanƙarar sanyi, sashinsu na rufe sashi wanda ba dominsu ba da na ƙone a dalilin zafin Jahannama."

Harisu ɗan Usama ya ruwaito a cikin Musnad nasa daga Abdullah ɗan Salam cewa: "Aljanna a cikin sama take; ita kuwa wuta a ƙasa. A wani ƙauli aka ce dukan biyun a sama suke".

## RAI MAI WANZUWA NE BAYAN MUTUWA

Muna masu aƙidar cewa, lalle, ruhi mai wanzuwa ne bayan mutuwar jiki. Zai kasance (ruhi) abin yi wa ni'ima ko abin yi wa azaba. Bai kasance mai ƙarewa ba. Amma a game da bagirensu bayani ya gabata a game da bagiren rayukan Shahidai. Amma bagiren waninsu, kamar rayukan muminai, to, suna a cikin ***ILLIYINA.*** Su kuma rayukan kafirai suna a cikin Sijjin. Kowace rai yana da alaƙa da jiki nasa alaƙa ta ma'ana.

Malam Kurɗubi ya ce: Rayukan shahidai suna a cikin Aljanna, rayukan waɗanda ba haka ba, a wani lokacin suna kasancewa a cikin ƙasa a bisa farfajiyar ƙaburbura. Wani lokacin kuwa sukan kasance a cikin sama. A wani ƙauli cewa aka yi, rayuka sukan ziyarci ma'abutansu a cikin ƙaburbura a kowace Juma'a. A wani zance cewa aka yi, rayukan muminai gaba ɗaya suna a cikin Aljanna.

## BA A MUTUWA SAI KWANA SUN KARE

Muna masu aƙidar cewa, ba a mutuwa sai ajali ya yi. Wannan da Allah ya rubuta ƙarewar rayuwa tun azal. Babu wanda zai mutu face sai kwanakinsa sun ƙare. Daɗa kashe shi aka yi ko kuwa mutuwa ya yi.

## FASICCI BA YA KAWAR DA IMANI

Muna masu aƙidar cewa fasiƙanci ba ya kawar da imani, a ce mutum ya koma kafiri kuma babu wani abu a tsakaninsu. Haka kuma bidi'a ba ta kawar da imani. Wannan kamar musun siffofi na Allah da halittarSa ga ayyukan bayi naSa, kuma da musun halacin gani naSa a lahira. Wannan saboda an gina waɗannan matsaloli a kan ta'awili. Amma siffanta Allah da

jiki da musun saninSa ga ƙananan abubuwa, to, wannan kafirci ne ba tare da wata jayayya ba.

Ba Mu kasance masu yin yanke da azaba ga wanda ya kasance bai tuba ba kuma ya mutu yana fasicci.

Wannan saboda zancenSa Maɗaukakin Sarki:

﴿ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَغۡفِرُ أَن يُشۡرَكَ بِهِۦ وَيَغۡفِرُ مَا دُونَ ذَٰلِكَ لِمَن يَشَآءُ ﴾ النساء: ٤٨

***"Lalle ne, Allah ba ya gafarta a yi shirki game da Shi, kuma Yana gafarta abin da yake bayan wannan ga wanda yake so." Nisa'i:48***

Wannan aya mai keɓancewa ce ga (ayoyin da) ke nuna gamewar azaba.

Haka kuma muna imani da cewa ba a dauwamar da shi a cikin azaba idan aka azabtar da shi; a'a muna masu yin yanke da fitar da shi kuma da shigar da shi Aljanna.

Bazzaru da Ɗabarani sun ruwaito hadisi cewa:

(من قال لا إله إلا الله نفعته يوما من دهره يصيبه قبل ذلك ما أصابه)

***"Wanda ya faɗi babu abin bautawa da gaskiya sai Allah, to, za ta amfane shi a wata rana daga zamaninsa; abin da zai faru a gare shi kafin haka zai faru a gare shi."*** Isnadin wannan hadisi yana da inganci.

## MAFIFICIN TALIKAI SHI NE ANNABI MU-HAMMAD SA'ANNAN ANNABAWA ULUL AZMI, SA'ANNAN SAURAN ANNABAWA

Muna masu aƙidar cewa mafificin talikai a gaba ɗaya shi ne masoyin Allah zaɓaɓɓe, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi. Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(أنا سيد ولد آدم ولافخر)

***"Ni ne shugaban 'yan'adam ba alfahari nake yi ba."*** Muslimu ya ruwaito hadisin.

Ibnu Abbas ya ce: "Allah Maɗaukakin Sarki ya fifita Annabi Muhammad a bisa ga 'yan sama kuma a bisa ga Annabawa." Baihaƙi da waninsa suka ruwaito.

Amma a game da hadisin da Buhari da Muslimu suka ruwaito inda Manzo ya ce:

(لا تخيروني على موسى وما ينبغي لعبد أن يقول أنا خير من يونس بن متى)

***"Kada ku fifita ni a kan Musa, kuma ba ya kamata ga wani bawa da ya ce, ni ne mafifici ga Yunusa ɗan Matta."***

Wannan hadisin an ɗauki cewa Manzon Allah ya faɗi haka ne a bisa ga tawali'u. Ko kuwa gabanin a sanar da shi cewa shi ne mafificin talikai.

Siffanta shi (Manzon Allah) da mafi girman siffofinsa na samo shi daga wani hadisi da Tirmizi ya ruwaito inda Manzo ya ce:

(إبراهيم خليل الله وأنا حبيب الله)

***"Ibrahim Badaɗayi ne na Allah; ni kuwa masoyin Allah ne."***

Ibrahim yana biye da shi ga fifiko: Ibrahim shi ne mafificin talikai gaba ɗaya bayan Annabi Muhammad.

Wani sashi na malamai ya ciranto ijma'i a kan wannan.

Ya zo a cikin Buhari cewa:

(خير البرية إبراهيم)

***"Fiyayyen talikai shi ne Annabi Ibrahim".***

An keɓance Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi da cewa bai shigo a cikin wannan ba. A dalilin haka hadisin yana nan a bisa gamewarsa. Annabi Musa da Isa da Nuhu su waɗannan ukun su ne mafifita daga sauran Annabawa.

Abdulrahman Suyuɗi ya ce: "Ban tsayu ba a kan cewa ga wanda a mafifici a cikinsu;" watau dai waɗannan guda biyar ma'abuta himma

waɗanda aka ambata a cikin surar Ahƙaf. Waɗannan da suke ma'abuta gaskiya da ƙoƙari.

Su kuwa sauran annabawa su ne mafifita a bisa ga sauran mutane tare da cewa su ma sun bambanta ga daraja a tsakaninsu na daga abin da aka keɓance kowane ɗaya daga cikinsu.

## MALA'IKU KE BIYE DA ANNABAWA

Su kuwa Mala'iku su ne ke biye da Annabawa ga fifiko a bisa ga sauran mutane. Mafifici daga cikin Mala'iku shi ne Jibril kamar yadda yake a cikin wani hadisi da Ɗabarani ya ruwaito.

## FIFIKO A TSAKANIN SAHABBAI

Abubakar Sadiƙ shi ne mafifici daga cikin 'yan'adam bayan Annabawa. Sa'annan Umar ɗan Haɗɗabi na biye da shi. Daga shi sai Usman ɗan Affan sa'annan Aliyu ɗan Abuɗalib.

Abdullahi ɗan Umar ya ce: "Mun kasance muna fifitawa a tsakanin mutane a zamanin Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi. Mun kasance muna fifita Abubakar, sa'annan Umar, sa'annan Usman, da Aliyu."

Buhari ya ruwaito shi. Ɗabarani ya ƙara a tasa ruwaya cewa: Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya san da wannan amma ba ya musantawa.

Tirmizi ya ruwaito hadisi kuma ya kyautata shi daga Anas ya ce: Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya faɗa a game da Abubakar da Umar cewa:

(هذان سيدا كهول أهل الجنة من الأولين والآخرين إلا النبيين والمرسلين)

***"Waɗannan biyu su ne shugabannin gwarzayen 'yan Aljanna na daga mutanen farko da ƙarshe ban da Annabawa da Manzanni."***

Daga waɗannan sai sauran cikon goma na daga waɗanda aka yi wa albishir da Aljanna. Wannan ana nufin sauran mutanen nan guda shida. Malam Abu Mansuru Attamimi ya cirato ijma'i a game da haka. Waɗannan kuwa su ne: Ɗalha da Zubairu da Sa'ad ɗan Abu Waƙƙas da Sa'idu ɗan

Zaidu ɗan Amru ɗan Nufailu da Abdurrahman ɗan Aufu haka kuma da Abu'ubaida ɗan Jarrahi.

Ma'abuta sunnoni sun ruwaito kuma Tirmizi ya inganta hadisin daga Sa'idu cewa, Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: "Mutum goma suna a cikin Aljanna: Abubakar yana Aljanna, Umar yana Aljanna, Usmanu yana Aljanna, Aliyu yana Aljanna haka kuma da Zubairu da Ɗalha da Abdurrahman ɗan Aufu da Abu'ubaida da Sa'ad ɗan Abu Waƙƙas da Sa'idu ɗan Zaidu."

Waɗanda suka halarci yaƙin Badar su ne mafifitan al'umma. Adadinsu ɗari uku ne da goma sha uku.

Ya zo a cikin Buhari:

(لعل الله اطلع على أهل بدر فقال اعملوا ما شئتم قد غفرت لكم)

***"Mai yiwuwa ne Allah ya yi tsinkaya ga ma'abuta yaƙin Badar ya ce: "Ku aikata abin da kuke so, lalle Na gafarta muku."***

Ibnu Maja ya ruwaito daga Rafi'u ɗan Khadiji ya ce Jibrilu ya zo ko kuwa wani mala'ika zuwa ga Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(ما تعدون من شهداء بدر فيكم قال خيارنا قال كذلك عند خيار الملائكة)

***"Me ne matsayin Shahidan Badar a wajenku? Sai Manzon Allah ya ce: "(Suna daga) zaɓaɓɓunmu." Sai Mala'ikan ya ce: "Haka suke a wajen zaɓaɓɓun Mala'iku."***

Sai waɗanda suka halarci yaƙin Uhudu su ne masu biya ga ma'abuta yaƙin Badar ga daraja.

Daga su sai ma'abuta mubaya'ar nan ta yarda a can Hudaibiyya, watau dai su ke biye da ma'abuta yaƙin Uhudu.

Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(لا يدخل النار أحد ممن بايع تحت الشجرة)

*"Babu ɗaya da zai shiga wuta na daga waɗanda suka yi mubaya'a a ƙarƙashin Itaciya."*

Abu'dawuda ne ya ruwaito shi. Haka kuma Tirmizi ya ruwaito shi kuma ya inganta shi. Malam Tamimi ya ruwaito ijma'i a bisa ga wannan tsari. Su kuwa sauran sahabbai su ne mafifita daga sauran jama'a.

Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(لا تسبوا أصحابي فو الذي نفسي بيده لو أنفق أحدكم مثل أحد ذهبا ما بلغ مد أحدهم ولا نصفه)

*"Kada ku zagi sahabbaina, da ɗaya daga cikinku ya ciyar da kwantankwacin Uhudu na zinari da bai kai (darajar) mudu ɗaya ko rabin mudu nasu ba."*
Muslim ne ya ruwaito shi.

Su kuwa sauran wannan al'umma su ne mafifita daga sauran al'ummomi. Allah Maɗaukain Sarki ya ce:

﴿كُنتُمْ خَيْرَ أُمَّةٍ أُخْرِجَتْ لِلنَّاسِ﴾ آل عمران: ١١٠

*"Kun kasance mafi alherin al'umma wadda aka fitar ga mutane". Ali-Imrana:110*

Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(أنتم توفون سبعين أمة أنتم خيرها وأكرمها على الله)

*"Ku, za ku zo kuna ciko na al'umma saba'in amma ku ne mafi alheri kuma mafi girma a wajen Allah a bisa dukansu."*

Ma'abuta sunnoni suka ruwaito shi. Wannan a bisa ga bambancin siffofin wannan al'umma. Daga cikinsu akwai malami da mai ibada da wanda yake da gabata (ta samun tsira) da mai bi masa da wanda ya daidaita a kan hanya da kuma wanda ya zalunci kansa.

## FIFIKON DARAJA A TSAKANIN MATA

Muna masu aƙidar cewa mafifita daga cikin mata su ne Maryam ɗiyar Imrana da Faɗima 'yar Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi.

Tirmizi ya ruwaito hadisi kuma ya inganta shi cewa:

(حسبك من نساء العالمين مريم بنت عمران وخديجة بنت خويلد وفاطمة بنت محمد —صلى الله عليه وسلم— وآسية امرأة فرعون)

***"Ya isar maka (daraja) daga matan talikai Maryam 'yar Imran da Khadija 'yar Khuwailid da Faɗima 'yar Muhammad tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi; haka kuma da Asiya, matar Fir'auna."***

Ya zo a cikin Buhari da Muslimu daga hadisin Aliyu cewa:

(خير نسائها مريم بنت عمران وخير نسائها خديجة بنت خويلد)

***"Mafificiya daga matan (zamaninta) Maryam 'yar Imran, kuma mafificiya daga matan (zamaninta) Khadija 'yar Khuwailid".***

Ya zo a cikin Buhari:

(فاطمة سيدة نساء هذه الأمة)

***"Faɗima ita ce shugabar matan wannan al'umma."***

Nasa'i ya ruwaito daga Huzaifa cewa Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(هذا ملك من الملائكة استأذن ربه ليسلم علي وبشرني أن حسنا وحسينا سيدا شباب أهل الجنة وأن أمهما سيدة نساء أهل الجنة)

***"Wannan mala'ika ne daga cikin mala'iku ya nemi izinin Ubangijinsa domin ya zo ya yi sallama a gare ni, kuma ya yi min albishir da cewa Hasan da Husaini su ne shugabannin samarin Aljanna. Haka kuma mahaifiyarsu ita ce shugabar matan Aljanna."***

Ɗabarani ya ruwaito cewa:

(إذا كان يوم القيامة قيل لأهل الجمع غضوا أبصاركم متي تمر فاطمة بنت محمد صلي الله عليه وسلم)

***"Idan ranar Alƙiyama ta zo za a ce wa ma'abuta taro: Ku runtse idanunku har sai Faɗima 'yar Muhammad tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ta wuce."***

A cikin waɗannan hadisai akwai nuni ga fifikon darajarta a kan Maryam. Wannan tun ma ba a ce idan muka tafi a kan magana mafi inganci na cewa ita, Maryam, ba ba'annabiya ba ce. Abu ne tabbatacce cewa, wannan al'umma ita ce mafi daraja a bisa ga waɗanda ba su ba.

Harisu ɗan Usama ya ruwaito a cikin Musnad nasa da isnadi mai inganci ga hadisi wanda yake MURSALI cewa:

(مريم خير نساء عالمها وفاطمة خير نساء عالمها)

***"Maryam ita ce mafificiyar matan lokacinta, Faɗima kuwa ita ce mafificiyar matan lokacinta."***

Tirmizi ya ruwaito hadisin MAUSULI daga hadisin Aliyu da lafazin:

(خير نسائها مريم وخير نسائها فاطمة)

***"Mafificiyar matanta ita ce Maryam kuma mafificyar matanta ita ce Faɗima."***

Malami masanin hadisi watau Abulfadli Ibnu Hajri ya ce hadisi Mursali yana bayanin wanda yake Mausuli ne.

**MAFIFICIYA DAGA MATAN ANNABI**

Mafificiya daga cikin uwayen muminai, watau matan Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi – wannan kamar yadda Maɗaukakin Sarki ya ce:

﴿وَأَزْوَٰجُهُۥٓ أُمَّهَٰتُهُمْ﴾ الأحزاب: ٦

***"Kuma matansa uwayensu ne." Ahzaf:6***

Ita ce, Khadija 'yar Khuwalid, mata ta farko ga Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, sa'annan A'isha Siddiƙa.

Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(كمل من الرجال كثير ولم يكمل من النساء إلا مريم وآسية وفضل عائشة على النساء كفضل الثريد على سائر الطعام)

***"Da yawa daga maza akwai waɗanda suka kammala, babu waɗanda suka kammala daga mata face Maryam da Asiya, kuma fifikon A'isha a bisa ga mata tamkar fifikon kaɓaki a bisa ga sauran nau'o'in abinci."***

A wani lafazi:

(لا ثلاثة مريم وآسية وخديجة)

***"Babu (waɗanda suka kammala) face uku: Maryam da A'siya da Khadija."***

A wajen ko wace ce ta fi daga su biyun (Khadija da A'isha) akwai maganganu. A ra'ayina uku aka ce a yi waƙafi. (Ma'ana kada a shiga a cikin wannan matsala).

## ANNABAWA ABIN TSAREWA NE DAGA KOWANE ZUNUBI

Muna masu aƙidar cewa Annabawa tsira da amincin Allah su tabbata a gare su tsararru ne. Babu wani laifi da ke faruwa daga gare su, babba ko ƙanƙane, ko da ganganci ko da rafkanuwa. Wannan a dalilin kasancewarsu masu girma a wajen Allah Maɗaukakin Sarki. Ma'ana su abin tsarewa ne daga aikata makaruhi. Domin aukuwar makaruhi daga mai tsoron Allah abu ne da ba a cika samu ba, to, ballantana ga wanda yake Annabi ne.

## DUKAN SAHABBAI ADILAI NE

Muna masu aƙidar cewa, Sahabbai (yardar Allah ta tabbata a gare su) dukansu adilai ne. Wannan saboda kasancewarsu su ne mafifitan wannan al'umma. Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(خير أمتي قرني)

***"Mafificiyar al'ummata su ne tsarata."*** Buhari da Muslimu ne suka ruwaito shi.

## SHUGABANNI MA'ABUTA MAZHABOBI DA WASUNSU SUNA A KAN SHIRIYA

Muna masu aƙidar cewa, Imamu Maliki da Shafi'i da Abuhanifa (da Ahmad Ibnu Hambali) da sauran limamai suna a kan shiriya daga Ubangijinsu. Wannan kuwa ta sashin aƙida da waninta. Ba za mu waiwaya ga wanda ya yi suka a gare su ba da abin da suke sun barranta daga gare shi. Albishir da Imamu Shafi'i da Maliki ya tusgo a cikin hadisi. Dayyalisi ya ruwaito a cikin Musnad nasa kuma da Baihaƙi a cikin littafin al-Ma'rifah hadisin da ya ce:

(لا تسبوا قريشا فإن عالمها يملأ الأرض علما)

***"Kada ku zagi Kuraishawa lalle ne, wani malami daga cikinsu zai cika ƙasa da ilimi."***

Imam Ahmad ya ce: Wannan malami shi ne Sha'fi'i. Domin a cikin sassa na duniya babu ilimin wani malami daga Kuraishawa tun daga Sahabbai da waɗanda ba su ba da iliminsa ya watsu kamar na (Imam) Shafi'i).

Hakimu ya ruwaito hadisi a cikin littafinsa na Al-Mustadrak cewa:

(تضربون أكباد الإبل فلا تجدون عالما أعلم من عالم المدينة)

***"Za ku hau raƙuma (zuwa neman ilimi) kuma ba za ku sami malamin da ya kai malamin Madina ba."***

Sufyanu ya ce: Muna ganin wannan malami shi ne Maliki.

Abin da ake zuwa da shi na hadisai a game da Abu'hanifa, to, wannan ƙarya ce kuma abin ba ya da asali.

Muna ƙudurta cewa shugaba Abulhassan Al'ash'ari; yana daga zuri'ar Abu Musa al'ash'ari shugaba ne a cikin sunna; ma'ana hanyar da ta gabata. Kuma shi abin gabatarwa ne a bisa ga waninsa. Babu waiwaye zuwa ga wanda ya yi magana a game da shi ga abin da yake shi barrantacce ne a gare shi.

Kuma muna ƙudurta cewa hanyar Abulƙasim Junaid, shugaban sufaye ta ilimi da aiki kuma da abota, hanyarsa abin gabatarwa ce. Domin

hanya ce da ta kuɓuta daga bidi'a; kuma tana kewaya a kan fawwala al'amari da miƙa shi zuwa ga Allah. Haka kuma ta dogara a kan barranta daga (son) rai kuma an gina ta a kan biyar Alƙur'ani da sunna.

Wannan shi ne ƙarshen abin da muka nufi mu tusgo da shi na daga abin da ya shafi asalin addini. Kuma shi ne ɓangare na farko daga littafin.

## SASHI NA BIYU

### Ilimin Sufanci

Abin da ake nufi da shi kamar yadda Gazali ya sanar da shi: "Tsiraitar da zuciya ga Allah Maɗaukakin Sarki kuma da wulaƙanta abin da ba Shi ba. A dalilin haka aka ambace Shi da wannan sunan. An samo wannan suna ne daga kalmar "Safa'u" wacce ke da ma'anar tsarkakewa. Wannan a dalilin tsarkakewarsa ga zukata. Wannan kamar yadda aka ce: Babu wanda ke shahara da sunan "Sufi" face wanda yake mai tsarkin zuciya; watau dai ya tsarkaka har aka ambace shi da tsarkakakke.

Da haka idan ka san manufa ga sufanci, to, sai ka kiyayi Allah Maɗaukakin Sarki ga dukan halayenka. Ma'ana ka kiyaye Shi tamkar kana kallo zuwa gare Shi. Domin idan ka kasance ba ka ganinSa, to, Shi yana ganinka. Wannan zai kasance da ka soma da aikata farillai waɗanda Allah ya farlanta a kanka; kuma ka bar abin da aka haramta a kanka, manya da ƙanana. Sa'annan sai aiwatar da nafiloli da barin abubuwan da suke makaruhai ne.

Ya zo a cikin hadisi daga Allah Maɗaukakin Sarki:

(ما تقرب إلى عبدي بشيء أحب إلى مما افترضته عليه وما يزال عبدى يتقرب إلى بالنوافل حتى أحبه فإذا أحببته كنت سمعه الذي يسمع به وبصره الذي يبصر به ويده التي يبطش بها ورجله التي يمشي بها ولئن استعاذلي لأعيذنه)

***"BawaNa da ɗai bai kusanta a gare Ni da wani abu mafi zama abin so a gare Ni ba kamar da abin da Na farlanta a kansa. Kuma bawaNa ba zai gushe ba yana kusanta zuwa gare Ni da nafiloli har in so shi. To, idan Na so shi sai In kasance jinsa wannan da yake ji da shj, kuma ganinsa wannan da yake gani da shi, kuma hannunsa wannan da yake jimƙa da shi, kuma ƙafarsa wannan da yake tafiya da ita. Lalle, idan ya roƙe Ni tsari Zan tsare shi."*** Hadisin Buhari ya ruwaito shi.

Ka kasance mai tsananin himmatuwa da barin abin da aka hane ka fiye da ƙoƙari wajen aikata abin da aka umurta, domin shi na farko kamewa ne, kuma shi ne mafi sauƙi daga aikatawa. Yana daga ƙa'idojin shari'a cewa, tunkuɗe ɓarna shi ya fi a bisa ga jawo maslaha. A dalilin haka aka ce idan ba ka sami ikon bauta wa Allah ba, to, kada ka saɓa maSa.

Ya zo a cikin Buhari da Muslimu daga hadisin Abu'huraira cewa:

(ما نهيتكم عنه فاجتنبوه وما أمرتكم به فافعلوا منه ماااستطعتم)

***"Abin da na hane ku a kai, to, ku nisance shi, kuma abin da na umurce ku da shi, to, ku aikata shi gwargwadon ikonku."***

A nan an rataya samun iko a kan abin da aka umurta, amma ba a yi haka ba ga abin da aka hana; wannan ya faru ne a dalilin cewa, nisanta abu ne mai sauƙi. Amma a cikin Mu'jamu na Ɗabarani an ruwaito hadisin.

(إذا أمرتكم بشيء فأتوه وإذا نهيتكم عن شيء فاجتنبوه ما استطعتم)

***"Idan na umurce ku da wani abu, to, ku aikata shi, kuma idan na hane ku daga wani abu, to, ku nisance shi a bisa gwargwadon ikonku."***

Abdulrahman Suyuɗi ya ce: "A wajena wannan ruwaya ce da aka juyar." Ruwayar da ke a cikin Buhari da Muslimu (wadda ta gabata) daga Abu'huraira ta fi zama tabbatatta.

Amma a game da abin da yake ***MUBA'HI,*** to, kana da zaɓi, a tsakanin aikatawa da bari. Idan ka nufi ɗa'a da shi, wannan kamar zaunawa a cikin masallaci domin hutawa kuma da haɗa shi da niyyar Itikafi; ko ka nufi cimma wata ibada ta hanyar cin abinci domin samun ƙarfi a gare ta; ko ka nufi kange kanka daga haram ta hanyar jima'i da iyali domin karya sha'awa, kuma da guje wa aukawa a cikin zina, to, abu ne mai kyau da za a ba ka lada a kansa. A game da jima'i akwai hadisin da Muslimu ya ruwaito; cewa

(وفي بضع أحدكم صدقة فقيل أيأتي أحدنا شهوته وله فيها أجر فقال أرأيتم لو وضعها في حرام أكان له وزر فكذلك إذا وضعها في الحلال كان له أجر)

***"A saduwar ɗaya daga gare ku da iyalinsa sadaka."*** Aka ce ɗaya daga gare mu zai zo wa sha'awarsa kuma ya kasance yana da lada? Sai ya ce: ***"Ku ba ni labari, shin da ya sanya ta (sha'awar) ga haram, shin akwai zunubi a kansa? To, haka ne idan ya sanya ta ga halal, ya kasance yana da lada."***

Ka ƙudurta, bayan ka kiyaye abubuwan da suka gabata cewa akwai kasawa a gare ka a game da abubuwan da ka zo da su, kuma lalle ba ka ba da haƙƙoƙin Allah da ke a kanka ba ko da gwargwadon nauyin zarra. Ta yaya?

Alhali ba da ikon da ya yi a gare ka na daga abin da ka aikata wata ni'ima ce daga gare Shi wadda gode mata ya wajaba a kanka.

Ya zo a cikin Musnad na Ahmad hadisin da ya ce:

(لو أن رجلا يخر على وجهه من يوم ولد إلى يوم يموت في مرضات الله لحقره يوم القيامة)

***"Da a ce mutum yana faɗuwa (sujada) a kan fuskarsa tun ranar da aka haife shi har zuwa ranar mutuwarsa yana a kan abin da Allah ya yarda da shi, to, da ya ga wannan ba kome ba ne a ranar Alƙiyama."***

Ka ƙudurta cewa kai ba ka fi wani ba, ko da kuwa a bisa ga zahiri kana ganin haka. Saboda lalle kai ba ka san mene ne ƙarshe a gare ka ba da kuma shi. Haƙiƙa, Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(إن أحدكم ليعمل بعمل أهل الجنة حتى ما يكون بينه وبينها إلا ذراع فيسبق عليه الكتاب فيعمل بعمل أهل النار فيدخل النار وإن أحدكم ليعمل بعمل أهل النار حتى ما يكون بينه وبينها إلا ذراع فيسبق عليه الكتاب فيعمل بعمل أهل الجنة فيدخل الجنة)

***"Lalle, ɗayanku yana aiki da aikin 'yan Aljanna har babu abin da zai kasance a tsakaninsa da ita face zira'i, to, sai littafi ya rigaya a gare shi sai ya yi aiki da aikin 'yan wuta sai ya shiga wuta. Kuma lalle, ɗayanku yana aiki da aiki 'yan wuta har babu abin da zai kasance tsakaninsa da ita face zira'i, to, sai littafi ya rigaya a gare shi sai ya yi aiki da aikin 'yan Aljanna sai ya shiga Aljanna".*** Buhari da Muslimu suka ruwaito.

Ka miƙa wuya ga al'amarin Allah Maɗaukakin Sarki kuma da hukuncinSa, kana mai ƙudurta cewa, babu wani abu da ke kasancewa face sai abin da Shi yake nufi, a'a'ba abin da kai kake nufi ba ko da kuwa ka yi kwaɗayin haka.

Ya zo a cikin ingantaccen hadisi da Muslimu ya ruwaito daga Abu'huraira: "Ka nemi taimakon Allah, kuma kada ka nuna kasawa; idan wani abu ya same ka, kada ka ce: "Da na yi kaza da kaza, to, da kaza da kaza ya kasance. A'a, sai ka ce: "Kadarar Allah ce, abin da Ya so Shi yake aikatawa." Domin cewa, "Da na yi kaza" tana buɗa aikin Shaiɗan."

Ina yi maka kashedi da duba ga halayen mutane ko kuma neman dubansu a gare ka. Wannan zai toshe ƙofofi na alheri masu yawa a gare ka. Wannan sai fa da abin da shari'a ta zo da shi na nuna ***MUDARATI*** da zance wanda ya kuɓuta daga sharri tare da nuna albishir da kawar da kai (daga abubuwan da ba na ƙwarai ba). Ka halarto da abubuwa uku a cikin rayuwarka waɗanda suke su ne tushe da za su taimake ka a bisa ga wasiyyoyin da suka gabata.

Na ɗaya: Ka san cewa amfani da cuta ba su kasancewa face daga gare Shi Maɗaukakin Sarki. Kuma lalle, Ya ƙaddarta a gare ka arziki da amfani da tsanani da cuta tun azal. Kuma su masu saduwa ne da kai babu ƙarya. Idan wani abu ya gudana ta hannun wani, to, a bisa ga ƙaddartawarSa Maɗaukakin Sarki. Wannan kamar yadda ya faɗa a cikin littafinSa Mabuwayi:

﴿وَإِن يَمْسَسْكَ ٱللَّهُ بِضُرٍّ فَلَا كَاشِفَ لَهُۥٓ إِلَّا هُوَ ۖ وَإِن يُرِدْكَ بِخَيْرٍ فَلَا رَآدَّ لِفَضْلِهِۦ ﴾

يونس: ١٠٧

***"Kuma idan Allah ya shafe ka da wata cuta, to, babu mai yaye ta face Shi, kuma idan Yana nufinka da wani alheri, to, babu mai mayar da falalarSa." Yunus:107***

﴿وَإِن تُصِبْهُمْ حَسَنَةٌ يَقُولُوا۟ هَٰذِهِۦ مِنْ عِندِ ٱللَّهِ ۖ وَإِن تُصِبْهُمْ سَيِّئَةٌ يَقُولُوا۟ هَٰذِهِۦ مِنْ عِندِكَ ۚ قُلْ كُلٌّ مِّنْ عِندِ ٱللَّهِ ﴾ النساء: ٧٨

***"Kuma idan wani alheri ya same su sai su ce: "Wannan daga wurin Allah ne," kuma idan wata cuta ta same su sai su ce: Wannan daga gare ka ne." Ka ce: "Dukkansu daga Allah ne". Nisa'i:78***

Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(احفظ الله تجده أمامك وإذا سألت فاسأل الله وإذا استعنت فاستعن بالله واعلم أن الأمة لو اجتمعوا على أن ينفعوك لم ينفعوك إلا بشيء قد كتبه الله لك ولو اجتمعوا على أن يضروك بشيء لم يضروك إلا بشيء قد كتبه الله عليك رفعت الأقلام وجفت الصحف)

***"Ka kiyayi Allah sai Allah ya kiyaye ka. Ka kiyayi Allah sai ka same ta (kiyayewar Allah) a gabanka. Idan za ka roƙo, to, ka roƙi Allah; kuma idan za ka nemi taimako, to, ka nemi taimako daga Allah. Kuma ka sani cewa da al'umma sun haɗu a bisa ga su amfane ka da wani abu, to, ba za su amfane ka ba face da abin da Allah ya rubuta a gare ka. Kuma da sun haɗu a bisa ga su cuta maka da wani abu, to, ba za su cuta maka ba face da abin da Allah ya rubuta a kanka. An ɗauke alƙaluma, kuma takardu sun bushe."*** Tirmizi ya ruwaito hadisin kuma ya inganta shi.

Idan ka halarto da wannan asali, to, zai sauƙaƙa a gare ka barin kiyayewar mutane a gare ka domin babu wata ma'ana a gare shi a lokacin.

Na biyu: Ka san cewa, kai bawa kake da aka yi waƙafinka babu wata gudanarwa a gare ka ga kanka. A'a Ubangijinka, kuma wanda Ya mallake ka Shi ke da gudanarwa a gare ka ta yadda ya so; wannan dai kamar yadda al'amarin mai mallaka yake a bisa ga abin da ya mallaka. Lalle, abu ne mai muni a ce kana ƙin abin da Ubangijinka yake aikatawa a gare ka, wanda yake Shi ne mafi tausayi a gare ka kuma Mafi jin-ƙayi a gare ka a bisa ga kanka da iyayenka. Ya zo a cikin hadisi:

(الله أرحم بالمؤمن من المرأة بولدها)

***"Allah ne mafi jin-ƙai ga mumini a bisa ga uwa da ɗanta."***

Kuma Allah Shi ne Mai hukunci a bisa ga masu hukunci a cikin ayyukansa. Wannan kamar yadda Ya labarta da haka a cikin littafinSa. Kuma ka san cewa, ba Ya nufi da wancan abu da Ya sadar a gare ka na cutarwa face don gyaranka da amfaninka na daga karkare kurakuranka da ɗaukaka darajajojinka. Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(لا يصيب المؤمن من نصب ولا وصب ولا سقم ولا حزن حتى الهم يهمه إلا كفر الله به من سيئاته)

***"Babu wani abu da zai sami mumini na daga wahala ko cuta ko rashin lafiya ko baƙin ciki. Kai hatta da damuwa face Allah ya karkare masa miyagun ayyukansa a dalilinsu."*** Ɓuhari da Muslimu suka ruwaito hadisin.

Idan ka halarto da wannan asali, to, miƙa wuya ga hukuncin Allah zai sauƙaƙa a gare ka.

Na uku: Ka san cewa, duniya mai gushewa ce kuma mai ƙarewa ce kuma lahira mai zuwa ce kuma wanzazza ce. Kuma lalle kai a nan duniya matafiyi kake kuma babu makawa tafiyarka ta kasance ƙararra, ka sadu da gida ka zauna a can sai ya kasance ka sami hutu da jin daɗi da haɗuwa da masoya waɗanda suka gabace ka ga wannan tafiya. A dalilin haka sai ka jure wa wahalhalun tafiya waɗanda za su yanke ba da daɗewa ba. Wannan ta hanyar juriya ga yi wa Allah ɗa'a da barin saɓa maSa, kuma da haƙuri da tsanance-tsanancen rayuwa da ire-irensu.

Ka kasance mai ƙoƙari ga raya gidanka wanda yake shi ne mazauninka na gaskiya. Gyaransa da ƙawata shi yana kasancewa da yawaita ibada a cikin wannan fage ƙanƙane domin jin daɗi da ita (ibadar) a zamani mai tsawo ba tare da wata wahala ba.

Idan ka halarto da wannan asali; kallon mutane da dubansu zai zamo ba kome ba a gare ka. Kamanta duniya da tafiya da aka yi an samo haka ne daga hadisin Ibnu Mas'udu da ya ce: "Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya yi barci a kan tabarma, to, sai ya tashi alhali akwai gurbin kwanciyar tabarmar a sashin jikinsa, sai muka ce: Ya Manzon Allah! Ai da mun samar da shimfiɗu a gare ka! Sai ya ce:

(مالي والدنيا ما أنا في الدنيا إلا كراكب استظل تحت الشجرة ثم راح وتركها)

***"Me ya haɗa ni da duniya! Ai ni ban kasance a cikin duniya ba face kamar wanda ke saman dabba (matafiyi) da ya tsaya a ƙarƙashin inuwar wata itaciya sa'annan ya tafi ya bar ta."*** Tirmizi ne ya ruwaito hadisin.

## MUMINI KAMMALALLE

Mumini na gaskiya wanda yake mai kammalallen imani shi ne wanda rassan imani suka kammala a gare shi. Wanda kuwa reshe ɗaya ya rage a gare shi, to, wani abu ya ragu daga imaninsa a bisa gwargwadon raguwar reshen.

Haƙiƙa, magabata sun haɗu a bisa ga cewa, imani yana ƙaruwa kuma yana raguwa. Karuwarsa tana kasancewa da yi wa Allah ɗa'a; raguwarsa kuwa tana kasancewa da saɓa wa Allah. Su, rassan imani, kamar yadda suka zo a cikin hadisi: "Sittin da wani abu ne ko saba'in da wani abu." Buhari da Muslimu suka ruwaito hadisin da wannan siga ta kokwanto daga hadisin Abu'huraira. Amma uku daga ma'abuta littattafan Sunanu sun ruwaito shi da

lafazin sittin da shida ko saba'in da bakwai. Shi kuwa Tirmizi ya ruwaito shi da lafazin sittin da huɗu. Waɗansu daga malamai sun kallafa wa kansu fitar da adadinsu a bisa ga hanya ta ijtihadi. Mafi kusantarsu ga ƙidaya shi ne Ibnu Hibbana. Domin ya ambaci duk wata halayya (ta ƙwarai) da aka ambata a cikin Alƙur'ani da sunna da sunan imani. Malamin Musulunci, Abulfadli Ibnu Hajar ya bi shi a kan haka ga sharhinsa na Buhari. Malam Abdulrahman Suyuɗi a cikin littafinsa na Niƙaya ya ce: "Mu kuma mun bi su." (Shehu Usmanu Ɗanfodiyo) ya ce: "Ni kuma na bi su a nan".

## RASSAN IMANI

### (1-6) Imani Da Allah Da Mala'iku Da Littattafai Da Manzanni Da Kaddara Da Ranar Alƙiyama

Wancan shi ne imani da Allah da siffofinSa da kasancewar abin da ba shi ba fararre ne. Kuma da imani da mala'ikunSa da littattafanSa da manzanninSa kuma da ƙaddara. Kuma da imani da ranar lahira da alƙiyama. Wannan kuwa saboda kasancewarsa ƙarshen ranaku. Kuma ya game tayar da halitta da hisabi da Aljanna da wuta da tabkin Alkausara da siraɗi kuma da ma'auni.

### (7-9) Son Allah Da So Da Ki Dominsa Kuma Da Son Annabi

Kuma da son Allah kuma da so da ƙi dominSa, kuma da son Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi.

Buhari da Muslimu sun ruwaito daga Anas cewa, Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(ثلاث من كن فيه وجد حلاوة الإيمان أن يكون الله ورسوله أحب إليه مما سواهما وأن يحب المرء لا يحبه إلا لله)

***"Abu uku waɗanda suka kasance a gare shi, to, ya sami ɗanɗanon imani: Allah da Manzo su kasance mafi zama abin so a gare shi a bisa ga abin da ba su ba; kuma ya so mutum ba yana sonsa domin wani abu ba face don Allah".***
Wannan har zuwa ƙarshen hadisi.

Abu'dawuda da Tirmizi sun ruwaito hadisin da ya ce:

(الحب لله والبغض في الله من الإيمان)

*"So domin Allah, kuma da ƙi dominSa suna daga imani."*

Ya zo a cikin Musnad na Ahmad cewa:

(أوثق عري الإيمان أن تحب في الله واعتقاد تعظيمه)

*"Mafi amincin igiyoyin imani: Ka yi so domin Allah, kuma ka ƙi dominSa."*

**(10) Girmama Annabi**

Kuma da ƙudurta girmama Annabi. Wannan ya ƙunshi yin salati a gare shi. Haƙiƙa, Allah ya nemi muminai da su yi salati a gare shi (a cikin Alƙur'ani); haka kuma a cikinsa akwai abin da ya ƙunshi girmama shi. Allah Maɗaukakin Sarki ya ce:

﴿يَا أَيُّهَا الَّذِينَ آمَنُوا صَلُّوا عَلَيْهِ وَسَلِّمُوا تَسْلِيمًا ﴿٥٦﴾﴾ الأحزاب: ٥٦

*"Ya ku waɗanda suka yi imani! Ku yi salati a gare shi." Ahzaf:56*

Ya kuma ce:

﴿يَا أَيُّهَا الَّذِينَ آمَنُوا لَا تُقَدِّمُوا بَيْنَ يَدَيِ اللَّهِ وَرَسُولِهِ﴾ الحجرات: ١

*"Ya ku waɗanda suka yi imani! Kada ku gabata (ga kome) gaba ga Allah da ManzonSa." Hujurat:1*

Ya kuma ce:

﴿يَا أَيُّهَا الَّذِينَ آمَنُوا لَا تَرْفَعُوا أَصْوَاتَكُمْ فَوْقَ صَوْتِ النَّبِيِّ﴾ الحجرات: ٢

*"Ya ku waɗanda suka yi imani! Kada ku ɗaukaka saututtukanku bisa sautin Annabi." Hujurat:2*

Wannan girmamawa ne a gare shi.

(Daga ciki akwai) biyar sunnarsa tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi.

(لن يستكمل مؤمن إيمان حتى يكون هواه تبعا لما جئتكم به)

***"Mumini ba zai cika imaninsa ba har sai abin da yake so ya kasance mai biya ga abin da na zo da shi."***

Asbahani ya ruwaito shi a cikin littafin Al-Targib. Hasan Ibnu Sufyan ya ruwaito shi da lafazin:

( لا يؤمن أحدكم حتى يكون هواه تبعا لما جئت به)

***"Ɗayanku ba zai kasance mai imani ba face abin da yake so ya kasance mai biya ga abin da na zo da shi."*** Isnadin hadisin mai kyau ne.

Kuma Manzo tsira da amicin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(عليكم بسنتي وسنة الخلفاء الراشدين عضوا عليها بالنواجذ وإياكم ومحدثات الأمور فإن كل محدثة بدعة وكل بدعة ضلالة)

***"Ina umartarku da biyar sunnata kuma da sunnar halifofi shiryayyu, ku yi cizo a gare ta da gaɓoɓin haƙora; kuma ina yi muku kashedi da al'amurran da aka haddasa; domin kowane abu da aka haddasa bidi'a ne kuma dukan bidi'a ɓata ce."*** Tirmizi ya ruwaito shi kuma da Ibnu Majah.

**(11) Iƙhlasi (Tsarkake Aiki Domin Allah)**

Kuma da Ikhlasi, Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(ثلاث لا يغل عليهن قلب المؤمن إخلاص العمل وطاعة ذوي الأمر ولزوم الجماعة)

***"Abubuwa uku zuciyar mumini ba ta ƙiyayya da su: Tsarkake aiki (domin Allah), kuma da biyayya ga ma'abuta al'amari, kuma da lizimtar jama'ar Musulmi."***

Ahmad ne ya ruwaito shi, kuma Hakimu da Waninsa suka inganta shi. Abin da ake nufi da ƙiyayya, ai ba zai zama mai jiyewa da hasada da nuna gaba a gare su ba.

Daga cikin wannan akwai barin riya da munafunci. Ibnu Majah ya ruwaito daga Shaddad ɗan Ausu yana mai ɗaga hadisin zuwa ga Annabi cewa:

(أن أخوف ما أخاف على أمتي الإشراك بالله أما أني لست أقول يعبدون شمسا ولا قمرا ولا وثنا ولكن أعمالا لغير الله وشهوة خفية)

***"Lalle mafi girman abin da nake ji wa al'ummata tsoro a kansa shi ne shirka da Allah, sai dai ni ban kasance ina cewa, suna bauta wa rana ko wata ko gunki ba, a'a' sai dai ayyuka domin wanin Allah, haka kuma da sha'awa ɓoyayya."***

A wani lafazi daga gare shi a wajen waninsa: "Mun kasance muna ƙidayar riya a zamanin Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi a matsayin shirka ƙarama."

Haƙiƙa, an fassara (kalmar) shirka da ta zo a cikin zancenSa Maɗaukakin Sarki

﴿ وَلَا يُشْرِكْ بِعِبَادَةِ رَبِّهِۦٓ أَحَدًۢا ﴾ الكهف: ١١٠

***"Kuma kada ya haɗa kowa ga bauta wa Ubangijinsa." Kahfi:110***

An fassara ta da riya.

Munafunci shi ne ɓoye kafirci da bayyanar da Musulunci. Allah Maɗaukakin Sarki ya ce:

﴿ وَتُوبُوٓاْ إِلَى ٱللَّهِ جَمِيعًا أَيُّهَ ٱلْمُؤْمِنُونَ لَعَلَّكُمْ تُفْلِحُونَ ﴾ النور: ٣١

***"Kuma ku tuba zuwa ga Allah gaba ɗaya, ya ku muminai! Tsammaninku, ku sami babban rabo." An-Nur:31***

**(12) Tsoro (Tsoron Azabar Allah)**

Kuma da tsoro, Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(إن من أفضل إيمان العبد أن يعلم أن الله معه حيث كان)

***"Yana daga mafificin imanin bawa, ya san cewa, Allah yana tare da shi a duk wurin da yake."***

Baihaƙi ya ruwaito shi a cikin littafin Shu'abul Imani a wannan babi kuma da Ɗabarani a cikin littafin Mu'jumul Ausaɗi.

Asbahani ya ruwaito a cikin littafinsa na Al-Targib daga hadisin Mu'azu cewa:

***"Lalle, mumini zuciyarsa ba za ta aminta ba, kuma tsoronsa ba zai natsu ba."***

### (13) Fatar Rahamar Allah

Kuma da fata, domin Allah ya siffanta kishiyarta da kafirci. Allah Maɗaukakin Sarki ya ce:

﴿ إِنَّهُۥ لَا يَاْيْـَٔسُ مِن رَّوْحِ ٱللَّهِ إِلَّا ٱلْقَوْمُ ٱلْكَٰفِرُونَ ﴿٨٧﴾ ﴾ يوسف: ٨٧

***"Lalle ne, babu mai yanke tsammani daga rahamar Allah face mutane kafirai". Yusuf:87***

Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(حسن الظن من حسن العبادة)

***"Kyakkyawan zato yana daga kyakkyawar ibada."*** Abu'dawuda da Tirmizi suka ruwaito.

Haka kuma ya ce:

(أفضل العبادة انتظار الفرج)

***"Mafificiyar ibada ita ce sauraren yayewar damuwa".*** Baihaƙi ya ruwaito shi.

### (14) Godiyar Allah

Kuma da godiyar Allah, domin Allah ya ambaci kishiyarsa da kafirci, wannan a inda Ya ce:

﴿ وَمَن يَشْكُرْ فَإِنَّمَا يَشْكُرُ لِنَفْسِهِۦ ۖ وَمَن كَفَرَ فَإِنَّ ٱللَّهَ غَنِىٌّ حَمِيدٌ ﴿١٢﴾ ﴾ لقمان: ١٢

***"Kuma wanda ya gode, to, yana godewa ne domin kansa kawai, kuma wanda ya kafirta, to, lalle Allah Mawadaci ne, Godadde." Luƙman:12***

Abu'dawuda ya ruwaito hadisi:

(من أعطى عطاء فوجد فليجز به وإن لم يجد فليثن به فمن أثنى به فقد شكره ومن كتمه فقد كفره)

***"Wanda aka bai wa wata kyauta, kuma ya sami abin da zai yi sakayya da shi, to, ya yi sakayyar, kuma wanda bai samu ba, to, ya yi yabo da ita, kuma wanda ya yi yabo da ita, to, lalle ya yi godiya a gare ta, kuma wanda ya ɓoye ta, to, ya kafirta da ita."***

Hadisi ya tusgo a cikin littafin Musnadul Firdausi cewa:

(الإيمان نصفان نصف في الصبر ونصف في الشكر)

***"Imani an raba shi zuwa gida biyu: rabi yana a cikin haƙuri, rabi kuwa yana a cikin godiya".***

**(15) Cika Alƙawari**

Kuma da cika alƙawari, Allah Maɗaukakin Sarki ya ce:

﴿يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَوۡفُواْ بِٱلۡعُقُودِ﴾ المائدة: ١

***"Ya ku waɗanda suka yi imani! Ku cika alƙawurra." Ma'idah:1***

Kuma Allah Mai tsarki da ɗaukaka ya ce:

﴿وَأَوۡفُواْ بِعَهۡدِ ٱللَّهِ إِذَا عَٰهَدتُّمۡ﴾ النحل: ٩١

***"Kuma ku cika da alƙawarin Allah idan kun yi alƙawari." Nahli:91***

Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(حسن العهد من الإيمان)

***"Kyakkyawan alƙawari yana daga imani."*** Tirmizi da waninsa suka ruwaito.

## (16-17) Haƙuri Da Yarda Da Hukuncin Allah

Kuma da haƙuri da yarda da hukuncin Allah. Daga ciki akwai yaƙini. Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(الصبر نصف الإيمان واليقين الإيمان كله)

***"Haƙuri shi ne rabin imani, shi kuwa yaƙini shi ne imani dukansa."*** Baihaƙi ya ruwaito shi a cikin littafin Al-Zuhdu.

Haka wasu ma sun ruwaito shi. Amma sun inganta tsayar da hadisin ga Abdullahi ɗan Mas'udu.

Bazzaru ya ruwaito hadisin da ya ce:

(خمس ومن الإيمان من لم يكن له فيه شيء منهن فلا إيمان له التسليم لأمر الله والرضى بقضاء الله والتفويض إلي الله والتوكل علي الله والصبر عند الصدمة الأولى)

***"Abubuwa biyar suna daga imani, wanda ba ya da wani abu daga cikinsu, to, ba ya da imani: miƙa wuya ga al'amarin Allah; kuma da yarda da hukuncin Allah; kuma da fawwala al'amura ga Allah; kuma da dogara ga Allah; haka kuma da haƙuri da musifa idan ta auku."***

Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(من سعادة ابن آدم استخارته الله ورضاه بما قضى الله ومن شفاوته تركه استخارة الله وسخطه بما قضى الله)

***"Yana daga arzikin ɗan'adam ya zama mai bai wa Allah zaɓi, kuma mai yarda da abin da Allah ya hukunta; kuma yana daga taɓewar ɗan'adam ya kasance ba mai bai wa Allah zaɓi ba; kuma mai fushi da abin da Allah ya hukunta."*** Tirmizi ne ya ruwaito shi.

## (18) Jin Kunya

Kuma da jin kunya, Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(الحياء شعبة من الإيمان)

*"Kunya reshe ce na imani."* Buhari da Muslim suka ruwaito.

### (19) Dogara Ga Allah

Kuma da dogara ga Allah; Allah Maɗaukakin Sarki ya ce:

﴿ وَعَلَى ٱللَّهِ فَلْيَتَوَكَّلِ ٱلْمُؤْمِنُونَ ﴿١٢٢﴾ ﴾ آل عمران: ١٢٢

*"Ga Allah muminai sai su dogara." Ali-Imrana:122*

Haƙiƙa, an ƙidaya dogara ga Allah a cikin abubuwan imani a cikin hadisin Bazzaru wanda aka ambata a nan kusa. (Watau a cikin reshe na 16-17).

Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(الطيرة شرك ومامنا إلا أن الله يذهبه بالتوكل)

*"Shu'umci, shirka ne, babu wani daga cikinmu face yana tare da shi sai fa idan Allah ya kawar masa da shi da dogaro a gare Shi."*

Haka kuma ya ce:

(الرقى والتمائم والتولة شرك)

*"Tofi da layu da Tiu'la shirka ne."*

Haka kuma ya ce:

(العيافة والطيرة والطرق من الجبت)

*"Bokanci da shu'umci da bugun tsakuwa suna daga sihiri."* Waɗannan hadisai Abu'dawuda ne ya ruwaito su, haka kuma da waninsa.

Laya ita ce abin da ake rataya wa ƙaramin yaro. Tiula kuwa shi ne abin da ke jawo soyayya a tsakanin miji da mata. Bugun tsakuwa kuwa shi ne duba ta hanyar zane ga ƙasa.

## (20) Rahama

Rahama tana daga rassan imani. Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(لا تنزع الرحمة إلا من شقى)

***"Ba za a cire rahama ba face daga taɓaɓɓe."***

Buhari ya ruwaito shi a cikin littafinsa na Al-Adab; haka kuma waninsa ya ruwaito shi.

Ya kuma ce (tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi):

(من لا يرحم الناس لا يرحمه الله)

***"Wanda ba ya rahama ga mutane, Allah ba ya rahama a gare shi."*** Buhari da Muslimu suka ruwaito.

Haka kuma ya faɗa (tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi).

(لا يدخل الجنة إلا رحيم) قيل يا رسول الله كلنا نرحم قال (ليس أن يرحم أحدكم صاحبه إنما الرحمة أن يرحم الناس)

***"Ba mai shiga Aljanna face wanda yake mai rahama ne."*** Sai aka ce: Ya Manzon Allah! Dukanmu masu rahama ne. Sai ya ce: ***"A'a, ba ita ce rahama ba, ɗayanku ya tausaya wa abokinsa; abin da yake rahama shi ne ya tausaya wa mutane."*** Bazzaru ne ya ruwaito.

## (21-22) Tawali'u, Barin Girman Kai Da Ji-Da-Kai

Kuma da tawali'u; a cikinsa akwai girmama babba da rahama ga ƙanana; haka kuma da barin girman kai da ji-da-kai. Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(لا يدخل النار من كان في قلبه مثقال ذرة من الإيمان)

***"Ba ya shiga wuta wanda ya kasance a cikin zuciyarsa akwai kwatankwacin nauyin zarra na imani."*** Muslimu ne ya ruwaito shi.

Kuma ya faɗa tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi:

(ومن لم يرحم صغيرنا ويعرف حق كبيرنا فليس منا)

***"Wanda bai yi rahama ga ƙananamu ba, kuma ya san haƙƙin manyanmu, to, ba ya daga gare mu."***

Buhari ne ya ruwaito shi a cikin littafinsa na Al-Adab, kuma Abudawuda da Tirmizi sun ruwaito shi.

A wani lafazi na Tirmizi:

(ويوقر كبيرنا ويأمر بالمعروف وينهى عن المنكر)

***"Kuma ya girmama manyanmu, kuma ya yi umarni da alheri, kuma ya yi hani daga abin da aka ƙi."***

A wani lafazi a wajen Ahmad:

(ليس من أمتي من لم يجل كبيرنا ويرحم صغيرنا ويعرف لعالمنا حقه)

***"Bai zamo a cikin al'ummata ba, wannan da bai girmama manyanmu, kuma ya yi rahama ga ƙananmu, kuma ya san haƙƙoƙin malamanmu."***

Ɗabarani ya ruwaito hadisi:

(ثلاثة لا يستخف بهم إلا منافق ذو الشبية في الإسلام وذو العلم وإمام مقسط)

***"Mutane uku ba mai wulaƙanta su face munafuki: Wanda ya yi furfura a cikin Musulunci, da malami kuma da shugaba adali."***

Ɗabarani ya ruwaito har wa yau:

(ثلاث مهلكات شح مطاع وهوى متبع وإعجاب المرء لنفسه)

***"Abubuwa uku masu halakarwa ne: Rowa wacce ake biya da son rai shi ma wanda ake biya, da mutum ya riƙa ji-da-kansa."***

Hakimu da waninsa sun ruwaito hadisai:

(أهل النار كل جواظ مستكبر)

***"'Yan-wuta su ne: Kowane mai taƙama, mai girman kai."***

*"Babu wani mutum da ke girmama kansa kuma ya yi taƙama a wajen tafiyarsa face ya haɗu da Allah yana mai fushi da shi."*

Allah yana cewa:

(ويقول الله: الكبرياء ردائ والعظمة إزارى فمن نازعني في واحد منهما أدخلته جهنم)

*"Girmame-girmame mayafiNa ne, kuma girma gyautoNa ne, wanda ya yi jayayya da Ni ga ɗaya daga gare su, zan shigar da shi a cikin Jahannama."*

A wani lafazi:

(قصمته)

*"Zan karya shi."*

**(23) Barin Hasada Da Jiyewa**

Haka kuma da barin hasada kuma da barin jiyewa. Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(الحسد يأكل الحسنات كما تأكل النار الحطب)

*"Hasada tana cin kyawawan ayyuka tamkar yadda wuta ke cin itatuwa."*

Abu'dawuda ne ya ruwaito.

Haka kuma ya ce:

(لا تدخلوا الجنة حتى تؤمنوا ولا تؤمنوا حتى تحابوا)

*"Ba za ku shiga Aljanna ba face sai kun yi imani, kuma ba za ku yi imani ba face sai kun yi soyayya."* Muslimu ne ya ruwaito shi.

Haka kuma ya ce:

(دب إليكم داء الأمم قبلكم الحسد والبغضاء هى الحالقة حالقة الدين لا حالقة الشعر)

***"Cutar al'ummomin da suka gabace ku ta yi rarrafe zuwa gare ku, watau dai hasada da ƙiyayya. Ita mai aske addini ce, a'a, ba mai aske gashi ba."*** Tirmizi ne ya ruwaito shi.

Haka kuma ya ce:

(إن النميمة والحقد في النار لا يجتمعان في قلب مسلم)

***"Annamimanci da jiyewa suna a cikin wuta, kuma ba su haɗuwa a cikin zuciyar Musulmi."*** Ɗabarani ya ruwaito shi.

Haka kuma ya faɗi cewa:

(لا يستقيم إيمان عبد حتى يستقيم قلبه)

***"Imanin bawa ba zai daidaita ba har sai zuciyarsa ta daidaita."*** Ahmad ne ya ruwaito shi.

**(24) Barin Fushi**

Kuma da barin fushi, Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(أكمل المؤمنين إيمانا أحسنهم خلقا)

***"Mafi cikar muminai ga imani shi ne mafi kyawonsu ga halaye."*** Hakimu ya inganta hadisin.

Asbahani ya ruwaito hadisi a cikin littafin Al-Targib:

(لا يستكمل العبد الإيمان حتى يحسن خلقه ولا يشفى غيظه)

***"Imanin bawa ba zai cika ba face sai ya kyautata halayensa kuma ya zama ba ya warkar da fushinsa."***

Haƙiƙa, Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(لمن قال له أوصني لا تغضب)

***"Ga wannan da ya nemi da ya yi masa wasicci: "Kada ka yi fushi."*** Buhari ya ruwaito shi.

### (25) Furuci Da Kalmar Shahada

Kuma da furuci da kalmar shahada. Ya zo a cikin hadisin rassan imani da ya gabata:

(أر فعها قول لا إله إلا الله)

*"Mafi ɗaukakarsu (rassan imani) shi ne zancen La'Ilaha Illallah."*

Ahmad da waninsa sun ruwaito hadisin da ya ce:

(جددوا إيمانكم قيل يارسول الله كيف تجدد إيماننا قال أكثروا من قول لا إله إلا الله)

*"Ku sabunta imaninku! Sai aka ce: ya Manzon Allah! Yaya za mu sabunta imaninmu? Sai ya ce: "Ku yawaita daga zancen LA'ILAHA ILLALLAH."*

### (26) Karatun Alƙur'ani

Kuma da karantun Alƙur'ani, Allah Maɗaukakin Sarki ya ce:

﴿ ثُمَّ أَوْرَثْنَا ٱلْكِتَٰبَ ٱلَّذِينَ ٱصْطَفَيْنَا مِنْ عِبَادِنَا ﴾فاطر: ٣٢

*"Sa'annan Mun gadar da Littafin ga waɗanda Muka zaɓa daga bayinMu." Faɗir:32*

Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(اقرءوا القرآن فإنه يأتي يوم القيامة شفيعا لأصحابه)

*"Ku karanta Alƙur'ani, lalle ne shi zai zo ranar Alƙiyama yana mai ceto ga ma'abutansa."* Muslimu ne ya ruwaito shi.

An tambaye shi: a cikin ayyuka wane ne mafifici? Sai ya ce:

(الحال المرتحل)

*"Mai sauka mai tafiya."*

Sai aka ce: Mene ne shi? Sai ya ce:

(صاحب القرآن يضرب في أوله حتى يبلغ آخره وفي آخره حتى يبلغ أوله)

***"Makarancin Alƙur'ani da ya soma daga farkonsa har ya zuwa ƙarshensa, sa'annan kuma daga ƙarshensa har ya zuwa farkonsa".***

Haka kuma ya ce:

(أفضل عبادة أمتي قراءة القرآن)

***"Mafificiyar ibadar al'ummata ita ce, karatun Alƙur'ani."***

Waɗannan hadisai biyu da suka gabata Baihaƙi ne ya ruwaito su.

Ahmad da waninsa sun ruwaito hadisi:

(أهل القرآن هم أهل الله وخاصته)

***"Ma'abuta Alƙur'ani su ne mutanen Allah kuma keɓantattu a wurinSa."***

**(27-28) Neman Ilimi Da Sanar Da Shi**

Kuma da neman ilimi da sanar da shi. Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(من يرد الله به خيرا يفقهه في الدين)

***"Wanda Allah ya nufi alheri a gare shi, to, Yana fahimtar da shi a cikin addini."*** Buhari da Muslimu suka ruwaito shi.

Haka kuma ya ce:

(خصلتان لا يجتمعان في منافق حسن سمت وفقه في الدين)

***"Halayya biyu ba su haɗuwa ga munafiƙi: Siffar mutanen ƙwarai da fahimtar addini."*** Tirmizi ne ya ruwaito shi.

Haka kuma ya faɗi cewa:

(لكل شيء عماد وعماد هذا الدين الفقه)

***"Kome yana da gimshiƙi, abin da yake gimshiƙin wannan addini, shi ne fahimta a cikinsa."*** Dabarani ne ya ruwaito shi.

Haka kuma ya ce:

(طلب العلم فريضة على كل مسلم)

*"Neman ilimi farilla ne a kan kowane Musulmi."*

Haka kuma ya ce:

(تكون فتن يصبح الرجل فيها مؤمنا ويمسي كافرا إلا من أحيا الله قلبه بالعلم)

*"Fitintinu za su kasance waɗanda mutum zai wayi gari a cikinsu yana mumini kuma ya yi marece yana kafiri face sai wanda Allah ya rayar da zuciyarsa da ilimi."* Waɗannan hadisai biyu Ibnu Maja ne ya ruwaito su.

Haka kuma ya ce:

(من سئل عن علم فكتمه ألجمه الله بلجام من نار يوم القيامة)

*"Wanda aka tambaya daga wani ilimi, kuma ya ɓoye shi, to, Allah zai yi masa lizzame na wuta a ranar Alƙiyama."* Tirmizi ne ya ruwaito shi, Hakimu kuma ya inganta shi.

### (29) Addu'a

Kuma da yin addu'a, Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: "Du'a'i shi ne ibada;" sa'annan sai ya karanta wannan aya:

(الدعاء هو العبادة)

*"Ku kira Ni in karɓa muku."* Buhari da Muslimu ne suka ruwaito shi.

﴿إِنَّ ٱلَّذِينَ يَسْتَكْبِرُونَ عَنْ عِبَادَتِي سَيَدْخُلُونَ جَهَنَّمَ دَاخِرِينَ ﴿٦٠﴾﴾ غافر: ٦٠

*"Lalle waɗannan da ke kangara daga barin bauta Mini, za su shiga Jahannama suna ƙasƙantattu." Gafir:60*

### (30-31) Zikiri Da Nisantar Yasassar Magana

Kuma da zikiri, a cikinsa akwai istigfari; haka kuma da nisantar yasassar magana. Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(أفضل الإيمان أن تحب لله وتبغض لله وتعمل لسانك في ذكر الله)

***"Mafificin imani shi ne ka yi soyayya domin Allah, kuma ka yi ƙi domin Allah, kuma ka aiwatar da harshenka a cikin ambaton Allah."*** Ahmad da Baihaƙi suka ruwaito shi.

Allah Maɗaukakin Sarki ya faɗa a wajen siffanta muminai ya ce:

(إذا سمعوا اللغو أعرضوا عنه)

***"Idan suka ji yasassar magana suna kawar da kai a gare ta."***

Wannan ya haɗe dukan zance mai muni kamar annamimanci da gulma da ƙarya da soke soke da alfasha ta magana. Lalle, hadisin da Ɗabarani da ya ruwaito a game da annamimanci ya gabata.

Ya zo a cikin Buhari da Muslim cewa;

(لا يدخل الجنة نمام)

***"Annamimi ba ya shiga Aljanna."***

Allah ya faɗa a game da gulma (giba):

﴿وَلَا يَغْتَب بَّعْضُكُم بَعْضًا﴾ الحجرات: ١٢

***"Kada sashenku ya yi gibar sashe." Hujurat:12***

Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(يطبع المؤمن على الخصال كلها إلا الخيانة والكذب)

***"Ana ɗabi'antar mumini da dukan ɗabi'u amma ban da ha'inci da ƙarya."*** Ahmad ne ya ruwaito shi.

Haka kuma ya ce:

(المؤمن ليس بالطعان ولا اللعان ولا الفاحش ولا البذى)

***"Mumini bai kasance mai suka ba, ko mai la'anta, ko mai alfasha, ko mai miyagun maganganu ba."***

Ya kuma faɗi cewa:

(الحياء والعى شعبتان من الإيمان البذاء والبيان شعبتان من النفاق)

*"Kunya da kame harshe rassa ne biyu na imani, alfasha da bayani (maganar da ta yi zurfi har a kai ga ƙarya) rassa biyu ne na munafunci."*

Tirmizi ya ruwaito waɗannan hadisan guda biyu; haka ma wani daga masu ruwaya ya ruwaito su; Hakimu kuma ya inganta su.

Ya zo a cikin Buhari da Muslimu:

(من كان يؤمن بالله واليوم الآخر فليقل خيرا أو ليصمت)

*"Wanda ya yi imani da Allah da ranar Lahira, to, ya faɗi alheri ko kuma ya yi kawaici".*

**(32) Tsarki Na Bayyane Da Na Hukunce**

Kuma da tsarki na bayyane ta hanyar alwala da wanka da gusar da najasa; haka kuma da a hukunce ta gusar da gashi da ɗebe akaifa da gusar da abin da ke jawo iska mai wari kuma da yin kaciya. A cikin wannan akwai nisantar najasa. Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(الطهر شطر الإيمان)

*"Tsarki rabi ne na imani."* Muslimu ne ya ruwaito shi.

A wani lafazi a wajen Nasa'i da Ibnu Maja:

(إسباغ الوضوء)

*"Cika alwala."*

Haka kuma ya faɗi cewa:

(لا يحافظ على الوضوء إلا مؤمن)

*"Babu mai kiyayewa a kan alwala face mai imani."* Ibnu Hibbana ya inganta shi.

Haka kuma ya faɗa:

(الفطرة خمس الختان وحلق العانة والاستحداد وقص الشارب وتقليم الأظفار ونتف الإبط)

***"Abubuwan halitta guda biyar ne: "Kaciya da aske gashin mara da rage gashin baki da ɗebe akaifa kuma da cirar gashin hamata."*** Buhari da Muslimu suka ruwaito.

Haka kuma ya faɗi cewa:

(إن الله طيب نظيف يحب النظافة فنظفوا أفنيتكم)

***"Lalle, Allah Mai tsarki ne kuma Mai tsafta ne, Yana son tsafta, to, ku tsaftace farfajiyar gidajenku."*** Tirmizi da Ibnu Maja suka ruwaito shi.

A wani lafazi:

(تنظفوا فإن الإسلام نظيف)

***"Ku yi tsafta, lalle Musulunci mai tsafta ne."***

**(33) Suturce Al'aura**

Kuma da suturce al'aura, Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(من كان يؤمن بالله واليوم الآخر فلايدخل الحمام بغير إزار)

***"Wanda ya kasance ya yi imani da Allah da ranar Lahira, to, kada ya shiga a gidan wanka face da gyauto."*** Tirmizi da waninsa suka ruwaito.

Haka kuma ya ruwaito (Tirmizi) daga Mu'awiya ɗan Haida ya ce na ce: Ya Manzon Allah! Al'aurarmu, me ke akwai a game da ita kuma me za mu bari? Ya ce:

(احفظ عورتك إلا من زوجتك أو ما ملكت يمينك) فقال الرجل يكون مع الرجل قال (إن استطعت أن لا يراها أحد فافعل) قال فالرجل يكون خاليا قال (الله أحق أن يستحيا منه)

***"Ka kiyaye al'aurarka face daga matarka ko abin da damarka ta mallaka." Sai ya ce: namijin da ke tare da namiji? Sai ya ce: "Idan ka sami ikon kada wani ya ga al'aurarka, to, ka aikata haka." Sai ya ce: "Idan mutum yana shi kaɗai? Sai ya ce: "Allah ne mafi cancantar a ji kunya daga gare shi."***

**(34-35) Sallar Farilla Da Ta Nafila Da Zakka**

Haka da salla ta farilla da ta nafila haka kuma da zakka ta farilla da ta nafila. Buhari da Muslimu da waɗansu sun ruwaito daga Ibnu Abbas Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya faɗa ga wakilan jama'ar Abdulƙaisi:

(أتدرون ما الإيمان بالله شهادة أن لا إله إلا الله وإني رسول الله وإقام الصلاة وإيتاء الزكاة وأن تود واخمس ما غنمتم)

***"Shin ko kun san mene ne imani da Allah? "Shaidar: Ba abin bautawa da gaskiya face Allah, kuma ni, Manzon Allah, ne, kuma da tsayar da salla, kuma da ba da zakka, kuma ku ba da kashi ɗaya daga biyar na ganimar da kuka samo."***

Buhari da Muslimu sun ruwaito daga Ibnu Umar cewa, Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(أمرت أن أقاتل الناس حتى يشهدوا أن لا إله إلا الله وأن محمدا رسول الله ويقيموا الصلاة ويؤتوا الزكاة فإذا قالوا ذلك عصموا مني دماءهم وأموالهم)

***"An umarce ni da in yaƙi mutane har sai sun shaida: Ba abin bautawa da gaskiya face Allah, kuma Muhammad Manzon Allah ne, kuma su tsayar da salla, kuma su ba da zakka, to, idan suka aikata haka sun tsare daga gare ni jininsu da dukiyarsu."***

Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(إن بين الرجل وبين الشرك والكفر ترك الصلاة)

***"Lalle abin da ke tsakanin mutum da shirka kuma da kafirci shi ne barin salla."*** Muslimu ne ya ruwaito shi.

A wani lafazi:

(العهد الذي بيننا وبينهم الصلاة فمن تركها فقد كفر)

***"Alƙawarin da ke tsakaninmu da su ita ce salla, wanda ya bar ta, to, lalle ya kafirta,"*** Hakimu ya inganta hadisin.

Ɗabarani ya ruwaito hadisi:

(إن الإسلام ضواى أو علامات كمنار الطريق ورأسه وجماعه شهادة أن لا إله إلا الله وأن محمدا عبده ورسوله وإقام الصلاة وإيتاء الزكاة وتمام الوضوء)

***"Lalle Musulunci yana da alamomi kamar alamomin hanya; abin da a kansa kuma da matattararsa, shi ne shaidar: ba abin (bautawa da gaskiya face Allah; kuma Annabi Muhammad tsira da aminci su tabbata a gare shi)bawanSa ne kuma ManzonSa, kuma da tsayar da salla kuma da ba da zakka; haka kuma da cika alwala."***

Ya zo a cikin ingantaccen hadisi daga Muslimu:

(الصلاة نور والصدقة برهان)

***"Salla haske ce, sadaka kuwa hujja ce."***

Ana nufin hujja ce a bisa ga imanin mai yinta.

**(36) Fansar Bayi Da 'Yanta Su**

Kuma da fansar wuyaye, Allah Maɗaukakin Sarki ya ce:

﴿وَلَٰكِنَّ ٱلۡبِرَّ مَنۡ ءَامَنَ بِٱللَّهِ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِ﴾ إلى قوله ﴿وَفِي ٱلرِّقَابِ﴾ البقرة: ١٧٧

***"Amma addini shi ne ga wanda ya yi imani da Allah da ranar Lahira."*** Har zuwa faɗarSa: ***"Kuma a cikin fansar Wuya." Baƙara:177***

Buhari da Muslimu sun ruwaito hadisin da ya ce:

(من أعتق رقبه أعتق الله بكل عصو منها عضوا منه من النار حتى فرجها بفرجه)

***"Wanda ya 'yanta bawa, to, Allah zai 'yantar da kowace gaɓa tashi (bawan) da gaɓa tasa (wanda ya 'yanta shi) har farjinsa da nasa farji."***

## (37) Kyauta

Kuma da yin kyauta. Ahmad ya ruwaito daga Amru ɗan Absah ya ce na ce: "Ya Manzon Allah! Mene ne imani? Ya ce:

(الصبر والسماحة)

*"Haƙuri da kyauta."* Abu'ya'ala ya ruwaito kwatankwacinsa daga Jabir.

Haka kuma ya ruwaito daga hadisin Anas cewa:

(ما محق الإسلام محق الشح شيء)

***"Babu wani abu da ke shafe Musulunci da ya kai ga rowa."***

Tirmizi ya ruwaito hadisi cewa:

(خصلتان لا يجتمعان في مؤمن االبخل وسوء الخلق)

***"Halayya biyu ba su haɗuwa ga mumini: rowa da mugun hali."***

Yana daga kyauta, ciyar da abinci da yi wa baƙi liyafa. Ya zo a cikin Buhari da Muslimu: Cewa wani mutum ya tambayi Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi: Mene ne mafifici a cikin Musulunci? Sai ya ce masa:

(تطعم الطعام وتقرء السلام على من عرفت ومن لم تعرف)

***"Ka ciyar da abinci, kuma ka yi sallama ga wanda ka sani da wanda ba ka sani ba."***

Ya zo a cikin hadisi:

(من كان يؤمن بالله واليوم الآخر فليكرم ضيفه)

***"Wanda ya kasance yana imani da Allah da ranar Lahira, to, ya girmama baƙonsa."***

## (38) Azumi Na Farilla Da Na Taɗawwa'i

Kuma da azumi na farilla da na nafila. Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(بنى الإسلام على خمس شهادة أن لا إله إلا الله وأني رسول الله –صلى الله عليه وسلم– وإقام الصلاة وإيتاء الزكاة وصوم رمضان وحج بيت الله الحرام)

***"An gina Musulunci a bisa ga abubuwa biyar: Shaidar: ba abin bautawa da gaskiya face Allah, kuma ni, Manzon Allah ne (tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi); kuma da tsayar da salla, kuma da ba da zakka, kuma da azumin watan Ramalan; haka kuma da hajji ga ɗakin Allah mai alfarma."*** Buhari da Muslimu suka ruwaito shi.

Haka kuma ya ce:

(الإسلام ثلاث الصلاة والصوم والزكاة)

***"Rabe-raben Musulunci uku ne: Salla da azumi da zakka."*** Ahmad ne ya ruwaito.

Haka har wa yau Ahmad ya ruwaito daga hadisin Jabir cewa, wani mutum ya ce: Ya Manzon Allah! Shin mene ne imani? Sai ya ce:

(أن تشهد أن لا إله إلا الله وأن محمدا رسول الله والصلاة وتؤتي الزكاة وتصوم رمضان وتحج البيت)

***"Ka shaida; Ba abin bautawa da gaskiya sai Allah, kuma Muhammad Manzon Allah ne, kuma da salla, kuma ka ba da zakka, kuma ka yi azumin watan Ramalan kuma ka yi hajji ga ɗakin Allah."***

Abu'ya'ala ya ruwaito hadisi:

(عرى الإسلام وقواعد الدين ثلاثة من ترك واحدة منهن فهو كافر حلال الدم شهادة أن لا إله إلا الله والصلاة المكتوبة وصوم رمضان)

***"Igiyoyin Musulunci da gimshiƙan addini uku ne, wanda ya bar ɗaya daga gare su, to, shi kafiri ne wanda jininsa ya halatta: shaidar ba abin bautawa da gaskiya face Allah, kuma da salla wadda a farilla, kuma da azumin watan Ramalan."***

Ya zo a cikin ingantaccen hadisi daga Muslimu cewa:

(الصيام جنة أو وقاية من النار )

***"Azumi garkuwa ne, ko kuwa kariya ne daga wuta."***

**(39) Yin I'itikafi**

Kuma da yin i'tikafi. Ibnu Hibbana ya ruwaito a cikin ingantaccen littafinsa haka kuma waninsa ya ruwaito hadisi:

(إذا رأيتم الرجل يعتاد المسجد فاشهدوا له بالإيمان فإن الله يقول: ﴿إِنَّمَا يَعْمُرُ مَسَٰجِدَ ٱللَّهِ مَنْ ءَامَنَ بِٱللَّهِ وَٱلْيَوْمِ ٱلْءَاخِرِ﴾ التوبة: ١٨)

***"Idan kuka ga mutum ya saba da masallaci, to, ku shaida a gare shi da imani. Lalle Allah yana cewa: "Abin sani kawai, mai raya masallatan Allah, shi ne wanda ya yi imani da Allah da ranar Lahira" Taubah:18***

Wannan dai har zuwa ƙarshen aya.

**(40) Neman Lailatul Kadri**

Kuma da neman Lailatul Kadri; watau dai biɗarta a cikin dare na Ramalan tare da raya daren. Umarni da haka ya zo a cikin hadisai masu inganci. Ya zo a cikin Buhari da Muslimu cewa:

(من قام ليلة القدر إيمانا واحتسابا غفر له ما تقدم من ذنبه)

***"Wanda ya tsayu a daren Lailatul Kadari yana mai imani kuma yana fatar lada, to, an gafarta a gare shi, abin da ya gabata na zunubansa".***

Abdurrahman Suyuɗi ya ce: Mazhabarmu ita ce ta keɓanta da kwana goma na ƙarshe kuma a cikin darairen da suke mara.

**(41) Hajji Da Umra**

Kuma da Hajji da Umra watau hajjin farilla da na nafila. Allah Maɗaukakin Sarki ya ce:

﴿وَأَتِمُّوا۟ ٱلْحَجَّ وَٱلْعُمْرَةَ لِلَّهِ﴾ البقرة: ١٩٦

***"Kuma ku cika Hajji da Umra" Baƙara:196***

Ya gabata a cikin hadisin: "An gina Musulunci a kan abubuwa biyar ƙirga hajji a cikinsu".

Bazzaru da waninsa sun ruwaito hadisi;

(الإسلام ثمانية أسهم الإسلام سهم الصلاة سهم الزكاة سهم وحج البيت سهم والصيام سهم والأمر بالمعروف سهم والنهى عن المنكر سهم والجهاد في سبيل الله سهم وقد خاب من لا سهم له منها)

***"Musulunci rabo takwas ne: Musulunci rabo ne, salla rabo ce, zakka rabo ce, hajji ga gidan Allah rabo ne, azumi rabo ne, umarni da alheri rabo ne, hani daga abin da ake ƙi rabo ne, jihadi a kan hanyar Allah rabo ne, to, lalle ya taɓe wanda babu rabo gare shi a cikinsu."***

Ibnu Hibbana ya ruwaito a cikin ingantaccen littafinsa daga hadisin Abu Sa'id Al-Khudri cewa, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa:

(إن عبدا صححت له جسمه ووسعت عليه في المعيشة يمضى عليه خمسة أعوام لا يفد إلى محروم)

***"Lalle, bawan da Na ba shi lafiyar jiki, kuma Na yalwata masa a rayuwa, shekaru biyar su wuce bai zo a wajeNa ba, to, shi abin haramta wa (alheri) ne."***

**(42) Ɗawafi**

Kuma da dawafi domin yana da matsayin salla har ma waɗansu sun fifita shi a kanta. Hadisi ya zo a cikin littafin Al-Mustadrak:

(الطواف بالبيت صلاة)

***"Dawafi ga Ka'aba salla ne."***

**(43) Gudu Domin Kubutar Da Addini**

Kuma da gudu da addininsa, a cikin wannan akwai yin hijira daga ƙasar kafirci da fasicci. Ahmad ya ruwaito daga Amru ɗan Absah ya ce:

(الهجرة قال وما الهجرة قال أن تهجر السوء قال: فأي الهجرة أفضل قال الجهاد.)

***"Wani mutum ya ce: Ya Manzon Allah! Wane imani ne mafifici? Ya ce: "Hijira". Ya ce: Me ake kira hijira? Ya ce: "Ka ƙaurarce wa mummunan aiki." Ya ce: Wace hijira ce ta fi? Ya ce: "Yin Jihadi."***

**(44-45) Cika Alwashi Da Kiyaye Rantsuwa**

Kuma da cika alwashi, Allah Maɗaukakin Sarki ya ce:

﴿يُوفُونَ بِالنَّذْرِ﴾ الإنسان: ٧

***"Suna cikawa da alwashin (da suka bakanta)." Insan:7***

Haka kuma da hasashe a wajen rantse-rantse ta hanyar kiyaye ratsuwa kuma da rantsuwa da abin da ya halatta a yi rantsuwa da shi. Allah Maɗaukakin Sarki ya ce:

﴿وَاحْفَظُوا أَيْمَانَكُمْ﴾ المائدة: ٨٩

***"Kuma ku kiyaye rantsuwoyinku." Ma'idah:89***

(من حلف على يمين صبر يقتطع لها مال امرء مسلم لقى الله وهو عليه غضبان)

***"Wanda ya yi rantsuwa ta haƙuri domin ya karɓi dukiyar wani Musulmi da ita, to, zai haɗu da Allah yana mai fushi da shi."*** Buhari da Muslimu suka ruwaito.

Haka kuma ya ce:

(من حلف بغير الله فقد كفر وأشرك)

***"Wanda ya yi rantsuwa da wanin Allah, to, haƙiƙa ya kafirta ko kuwa ya yi shirka."*** Abu'dawuda da Tirmizi suka ruwaito kuma Hakimu ya inganta shi.

**(46) Ba Da Kaffara**

Kuma da ba da kaffara domin tana daga amanoni; wannan saboda kasancewarta daga haƙƙoƙin Allah Maɗaukakin Sarki.

Ya zo a cikin hadisi da Buhari da Muslimu suka ruwaito

(وأداء الكفارة لأنها من الأمانة إذ هى حقوق الله تعالى)

*"Bashin Allah ne mafi cancanta da a biya."*

### (47) Kame Kai Ta Hanyar Yin Aure

Kuma da kame kai ta hanyar yin aure. Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(يا معشر الشباب من استطاع منكم الباءة فليتزوج فإنه أغض للبصر وأحصن للفرج)

*"Ya ku jama'ar samari, wanda ya sami ikon abin da zai ciyar da iyali, to, ya yi aure domin shi ne mafi kangewa ga duba kuma mafi tsarewa ga farji."*

Haka kuma ya ce:

(إني أنام وأقوم وأصوم وأفطر وأتزوج النساء فمن رغب عن سنتي فليس مني)

*"Lalle ni, ina barci kuma ina tsayuwa (sallar dare) kuma ina azumi, kuma ina shan ruwa (rashin yin azumi) kuma ina auren mata; to, wanda ya yi ƙyama daga sunnata, to, bai kasance daga gare ni ba."* Buhari da Muslimu suka ruwaito su.

Tirmizi da waninsa sun ruwaito hadisi:

(أربع من سنن المرسلين الحياء والتعطر والسواك والنكاح)

*"Abubuwa huɗu suna daga sunnonin manzanni: Kunya da shafa turare da aswaki kuma da aure."*

### (48) Tsayuwa Da Hakkokin Iyali

Kuma da tsayuwa da haƙƙoƙin iyali. Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(ابدأ بمن تعول)

*"Ka soma da wanda kake ciyarwa."* Buhari da Muslimu suka ruwaito.

Haka har wa yau ya ce:

(أفضل الدينار دينار ينفقه الرجل على عياله)

***"Mafificin dinari shi ne wanda mutum ke kashewa ga iyalansa."*** Muslimu ne ya ruwaito shi.

Haka har wa yau ya ce:

(كفى بالمرء إثما أن يضيع من يعول)

***"Ya ishi mutum zunubi, ya zama ya tozartar da wanda yake ciyarwa."*** Abudawuda ya ruwaito shi".

A wajen Muslimu kuwa ya ruwaito ma'ana tasa.

**(49) Biyayya Ga Iyaye**

Kuma da biyayya ga iyaye. Allah Maɗaukakin Sarki ya ce:

﴿ وَقَضَىٰ رَبُّكَ أَلَّا تَعْبُدُوٓاْ إِلَّآ إِيَّاهُ وَبِٱلْوَٰلِدَيْنِ إِحْسَٰنًا ﴾الإسراء: ٢٣

***"Kuma Ubangijinka Ya hukunta kada ku bauta wa kowa face Shi, kuma game da mahaifa biyu, ku kyautata kyautatawa." Isra'i:23***

Buhari da Muslimu sun ruwaito daga Ibnu Mas'udu ya ce: Na ce: Ya Manzon Allah! (tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi):

((أى الأعمال أفضل قال الصلاة لوقتها قال قلت ثم أى قال بر الوالدين قلت ثم أى قال الجهاد في سبيل الله)

***"Waɗanne ayyuka ne a mafifita? Sai ya ce: "Salla a cikin lokacinta." Na ce: Sa'annan me? Ya ce: "Jihadi a kan hanyar Allah."***

Tirmizi da waninsa sun ruwaito hadisin:

(رضى الرب في رضى الوالد وسخطه في سخط الوالد)

***"Yardar Ubangiji tana a cikin yardar mahaifi, kuma fushin Ubangiji yana cikin fushin mahaifi."***

## (50) Tarbiyyar 'Ya'ya

Kuma da tarbiyyar 'ya'ya, Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(من كان له ثلاث بنات يؤدبهن ويكفهن ويرحمهن فقد وجبت له لجنة البتة)

***"Wanda ke da 'ya'ya mata guda uku, ya tarbiyyantar da su, kuma ya kange su; haka kuma ya nuna rahama a gare su, to, lalle Aljanna ta wajaba a gare shi yanke."*** Buhari ya ruwaito shi a cikin littafinsa na Al-Adab.

Abu'dawuda da Tirmizi sun ruwaito hadisi:

(من كان له ثلاث بنات أو ثلاث أخوات أو بنتان أو أختان فاحسن صحبتهن واتقي الله فيهن فله الجنة)

***"Wanda ke da 'ya'ya mata uku, ko 'yan'uwa mata uku, ko 'ya'ya mata biyu, ko 'yan'uwa mata biyu, kuma ya kyautata zamantakewa da su, kuma ya ji tsoron Allah a game da su, to, Aljanna ta tabbata a gare shi."***

Tirmizi ya ruwaito hadisi:

(لأن يؤدب الرجل ولده خير له من أن يتصدق بصاع)

***"Lalle mutum ya tarbiyyantar da ɗansa ya fi zama alheri a bisa ga ya yi sadaka da sa'i."***

Haka kuma da hadisin da ya ce:

(ما نحل والد ولدا أفضل من أدب حسن)

***"Mahaifi bai bai wa ɗansa wata kyauta ba wadda ta fi kamar tarbiyya kyakkyawa,"***

Buhari ya ruwaito a cikin littafinsa na Al-Adab daga Ibnu Umar cewa shi ya ce: "Allah ya ambaci barrantattu da wannan suna domin alherinsu ga iyaye da 'ya'ya, domin kamar yadda mahaifinka yake da haƙƙi a kanka, haka ne ɗanka yake da haƙƙi a kanka."

**BAYANI:** Daga ƙa'idojin shari'a shi ne cewa, abin da ke tsawatarwa na ɗabi'a yana wadatarwa ga abin da ke tsawatarwa na shari'a. Misali ga

wannan, shan bawali haramun ne, haka kuma shan giya. To, sai aka shata yin haddi a game da shan giya amma ba a yi haka ba ga bawali; wannan domin rayuwa tana ƙyama a gare shi, to, sai aka bar ta da ɗabi'a. A dalilin haka mahaifi da ɗa sun yi tarewa ga haƙƙi, to, sai Allah Maɗaukakin Sarki a cikin littafinSa Mabuwayi ya kai matuƙa a wajen wasiyya da mahaifa a wurare daban-daban; amma ba a yi haka ba a wajen ɗa sai aka bar shi ga ɗabi'a; domin a bisa larura ɗabi'a tana hukunta tausayawa a gare shi.

## (51) Sadar Da Zumunta

Kuma da sadar da zumunta. Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(لا يدخل الجنة قاطع الرحم)

***"Mai yanke zumunta ba ya shiga Aljanna."*** Buhari da Muslimu suka ruwaito shi.

## (52) Biyayya Ga Uwayengiji Da Tausaya Wa Waɗanda Aka Mallaka

Kuma da ɗa'a ga Uwayengiji. Buhari da waninsa sun ruwaito hadisi:

(إن العبد إذا نصح لسيده وأحسن عبادة ربه فله الأجر مرتين)

***"Lalle, bawa idan ya tsarkake biyayya ga shugabansa, kuma ya kyautata bautar Ubangijinsa, to, yana da sakamako biyu."***

Kuma da tausaya wa waɗanda aka mallaka kuma da bayi. Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(إخوانكم جعلهم الله تحت أيديكم فمن كان أخوه تحت يده فليطعمه من طعامه
وليلبسه من لباسه ولا يكلفه ما يغلبه فإن كلفه ما يغلبه فليعنه)

***" 'Yan'uwanku ne (watau bayi) Allah ya sanya su a hannuwanku, to, wanda ɗan'uwansa ke ƙarƙashinsa ya ciyar da shi daga abin da yake ci, kuma ya tufayar da shi daga abin da yake tufatar da kansa, kuma kada ya ɗora masa (aiki) wanda ya rinjaye shi; kuma idan ya ɗora masa abin da ya fi ƙarfinsa, to, ya taimaka masa a kansa."*** Buhari da Muslimu suka ruwaito shi.

Kuma Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(لا يدخل الجنة سيئ المملكة)

***"Mai mummunar mallaka ba ya shiga Aljanna."***

Wani mutum ya tambaye shi, har sau nawa zan yafe wa mai yi min hidima? Sai ya ce:

(كل يوم سبعين مرة)

***"Sau saba'in a kowane yini."***

Waɗannan hadisai guda biyu Tirmizi da waninsa suka ruwaito su.

An karɓo daga Aliyu cewa: ƙarshen maganar Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ita ce:

(الصلاة الصلاة واتقوا الله فيما ملكت أيمانكم)

***"Ku tsare salla! Ku tsare salla!! Kuma ku ji tsoron Allah ga abin da damarku ta mallaka."***

Hakimu da waninsa sun ruwaito hadisi

(أكمل المؤمنين إيمانا أحسنهم خلقا وألطفهم لأهله)

***"Mafi cikar muminai ga imani shi ne mafi kyawonsu ga ɗabi'u, kuma mafi taushinsu ga iyalinsa."***

**(53) Tsayuwa Da Shugabanci Tare Da Yin Adalci**

Kuma da tsayuwa da shugabanci tare da yin adalci domin shugabanci yana daga masalahar al'umma. Allah Maɗaukakin Sarki ya ce:

﴿وَإِذَا حَكَمْتُم بَيْنَ ٱلنَّاسِ أَن تَحْكُمُوا۟ بِٱلْعَدْلِ﴾ النساء: ٥٨

***"Kuma idan kun yi hukunci a tsakanin mutane, ku yi hukunci da adalci." Nisa'i:58***

Hadisi ya zo a cikin Buhari da Muslimu cewa:

(سبعة يظلهم الله في ظل عرشه إمام عادل)

***"Mutane bakwai Allah yana yi musu inuwa a cikin inuwar al'arshinSa: Shugaba adali ….."*** Har zuwa ƙarshen hadisin.

Bazzaru ya ruwaito hadisin da ya ce:

(الإسلام علامات كمنار الطريق شهادة أن لا إله إلا الله وإقام الصلاة وإيتاء الزكاة والحكم بكتاب الله وطاعة النبى –صلى الله عليه وسلم– والتسليم على بني آدم)

***"Musulunci yana da alamomi kamar alamomin hanya: Shaidar: ba abin bautawa da gaskiya face Allah kuma da tsayar da salla kuma da ba da zakka."***

**(54) Hukunci Da Littafin Allah Ɗa Da'a Ga Annabi Da Rashin Jayayya Da 'Yan'adam Da Lizimtar Jama'a**

Kuma da hukunci da littafin Allah da ɗa'a ga Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi da nisantar jayayya da 'yan'adam da biyar jama'a (ta sunna).

A cikin hadisin da ya gabata an ce: "Da lizimtar jama'a." Tirmizi da Nasa'i sun ruwaito hadisi."

(آمركم بخمس، الله أمرني بهن السمع والطاعة والجهاد والهجرة والجماعة فإنه من فارق الجماعة قيد شبر فقد خلع ربقة الإسلام في عنقه إلا أن يرجع)

***"Ina umartar ku da abubuwa guda biyar waɗanda Allah ya umarce ni da su: Saurare (ga shugaba) da ɗa'a da jihadi da hijira kuma da lizimtar jama'a; domin wanda ya rabu da jama'a gwargwadon taƙa ɗaya, to, ya tuɓe igiyar Musulunci daga wuyansa face sai idan ya komo."***

**(55) Biyayya Ga Ma'abuta Umarni**

Kuma da biyayya ga ma'abuta umarni. Allah Maɗaukakin Sarki ya ce:

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَطِيعُواْ ٱللَّهَ وَأَطِيعُواْ ٱلرَّسُولَ وَأُوْلِي ٱلۡأَمۡرِ مِنكُمۡ ﴾ النساء: ٥٩

***"Ya ku waɗanda suka yi imani.! Ku yi ɗa'a ga Allah, kuma ku yi ɗa'a ga ManzonSa da ma'abuta al'amari daga cikinku." Nisa'i:59***

A cikin hadisin da ya gabata an ce:

(وطاعة ذوى الأمر)

*"Da ɗa'a ga ma'abuta daga cikinku."*

Abu'dawuda da waninsa sun ruwaito hadisi:

(أو صيكم بتقوي الله والسمع والطاعة ولو بعبد حبشي)

*"Ina yi muku wasiyya da tsoron Allah kuma da saurare kuma da ɗa'a ko da ga bawa ne daga Habasha."* Dabarani ya ruwaito da dangane mai rauni.

(الإسلام عشرة أسهم شهادة أن لا إله إلا الله وهى الملة والثانية الصلاة وهي الفطرة والثالثة الزكاة وهى الطهرة والرابعة الصوم وهى الجنة والخامسة الحج وهى الشريعة والسادسة الجهاد وهى الغزوة السابعة الأمر بالمعروف وهى الوفاء والثامنة النهى عن المنكر وهى الحجة والتاسعة الجماعة وهى الألفة والعاشرة الطاعة وهى العصمة)

*"Musulunci kaso goma ne: Shaidar ba abin bautawa da gaskiya face Allah; wannan kuwa shi ne addini; na biyu ita ce salla, kuma ita ce halitta; na uku zakka, kuma ita ce tsarki; na huɗu azumi kuma shi ne garkuwa; na biyar hajji; shi ne shari'a; na shida jihadi, shi ne kai hari; na bakwai umarni da alheri, shi ne cika (alƙawari); na takwas hani daga abin da ake ƙi, kuma shi ne hujja; na tara lizimtar jama'a kuma shi ne haɗin kai; na goma ɗa'a; wannan kuma shi ne tsari."*

**(56) Sulhi A Tsakanin Mutane**

Kuma da sulhi a tsakanin mutane a cikinsa akwai yaƙi da waɗanda suka yi bore suka fita daga ɗa'ar shugaba.

Allah Maɗaukakin Sarki ya ce:

﴿ وَإِن طَآئِفَتَانِ مِنَ ٱلْمُؤْمِنِينَ ٱقْتَتَلُوا۟ فَأَصْلِحُوا۟ بَيْنَهُمَا ﴾ الحجرات: ٩

*"Kuma idan jama'a biyu ta muminai suka yi yaƙi, to, ku yi sulhu, a tsakaninsu." Hujurat:9* Wannan har zuwa ƙarshen aya.

## (57) Taimaka Wa Juna A Bisa Ga Alheri Da Taƙawa

Kuma da taimakekeniya a kan aikin alheri da taƙawa. Umarni da alheri da hani daga abin da ake ƙi yana daga gare shi. Wannan kuwa ya shuɗe a cikin hadisai daban-daban.

Muslimu ya ruwaito:

(من رأى منكم منكرا فليغيره بيده فإن لم يستطع فبلسانه فإن لم يستطع فبقلبه وذلك أضعف الإيمان)

***"Wanda ya ga abin ƙi daga cikinku, to, ya sauya shi da hannunsa; idan bai sami iko ba, to, da harshensa; idan bai sami iko ba, to, da zuciyarsa; wancan shi ne mafi raunin imani."***

## (58) Tsayar Da Haddi

Kuma da tsayar da haddi. Allah Maɗaukakin Sarki ya ce:

﴿ وَلَا تَأْخُذْكُم بِهِمَا رَأْفَةٌ فِي دِينِ ٱللَّهِ ﴾ النور: ٢

***"Kuma kada tausayi ya kama ku game da su a cikin addinin Allah." An-Nur:2***

Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(إنما هلك الذين من قبلكم أنهم كانوا إذا سرق فيهم الشريف تركوه وإذا سرق فيهم الضعيف أقاموا عليه الحد)

***"Lalle abin da ya halakar da waɗanda suka gabace ku shi ne sun kasance idan wanda yake maɗaukaki a cikinsu ya yi sata sai su bar shi; kuma idan wanda yake mai rauni a cikinsu ya yi sata, to, sai su tsayar da haddi a gare shi."*** Buhari da Muslimu suka ruwaito shi.

Haka kuma ya ce:

(إقامة حد من حدود الله خير من مطر أربعين ليلة في بلاد الله)

***"Tsayar da haddi daga haddohin Allah ya fi a yi ruwan sama kwana arba'in a cikin garuruwan Allah."***

Haka kuma ya ce:

(أقيموا حدود الله في القريب والبعيد ولا تأخذكم في الله لومة لائم)

***"Ku tsayar da haddodin Allah ga na kusa da na nesa, kuma kada zargin mai zargi ya kama ku ga al'amarin Allah."***

Waɗannan hadisai guda biyu Ibnu Maja ne ya ruwaito su.

**(59) Jihadi A Kan Hanyar Allah**

Kuma da jihadi, bayani a kansa ya gabata a cikin hadisai daban daban. Ribaɗi yana daga cikinsa.

Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(كل ميت يختم على عمله إلا الذي مات مرابطا في سبيل الله فإنه يزاد عمله إلى يوم القيامة ويأمن فتنة القبر)

***"Dukan matacce an rufe (littafin) aikinsa face wanda ya mutu yana ribaɗi a kan hanyar Allah, to, lalle shi ana ƙari ga aikinsa har ya zuwa ranar Alƙiyama, kuma yana aminta daga fitinar ƙabari."***

**(60) Bayar Da Amana**

Kuma da bayar da amana. Allah Maɗaukakin Sarki, ya ce:

﴿ ۞ إِنَّ ٱللَّهَ يَأۡمُرُكُمۡ أَن تُؤَدُّواْ ٱلۡأَمَٰنَٰتِ إِلَىٰٓ أَهۡلِهَا ﴾ النساء: ٥٨

***"Lalle ne Allah yana umarninku ku bayar da amanoni zuwa ga masu su." Nisa'i:58***

Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(لا إيمان لمن لا أمانة له)

***"Babu imani ga wanda babu amana a gare shi."*** Ahmad ne ya ruwaito.

Haka kuma ya ce:

(المؤمن من أمنه الناس على دمائهم وأموالهم)

***"Mumini shi ne wanda mutane suka aminta da shi a bisa jininsu da dukiyarsu."*** Hakimu ya inganta wannan hadisi.

Hadisi ya gabata na cewa:

(يطبع المؤمن على الخلال كلها إلا الخيانة والكذب)

***"Ana ɗabi'antar mumini da kowace irin halayya face ha'inci (da ƙarya)."***

Ɗabarani ya ruwaito hadisi:

((ناصحوا في العلم فإن خيانة أحدكم في علمه أشد من خيانته في ماله))

***"Ku tsarkake nasiha a game da ilimi, lalle ha'incin ɗayanku a wajen ilimi ya fi tsanani a bisa ha'incinsa ga dukiya."***

Yana daga amana ba da humusi (ɗaya a cikin biyar) na ganima. Wannan kamar yadda bayani ya gabata ga hadisin da Buhari da Muslimu suka ruwaito.

### (61) Ba Da Rance

Kuma da ba da rance domin lalle shi, taimako, ne a bisa ga yaye damuwa. Wannan tare da biyansa, domin shi yana daga amana. Ya zo a cikin hadisi da Muslimu ya ruwaito cewa:

(خياركم أحسنكم قضاء)

***"Zaɓaɓɓenku shi ne mafi kyautatawarku a wajen biyan bashi."***

### (62) Girmama Makwabci

Kuma da girmama maƙwabci. Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(من كان يؤمن بالله واليوم الآخر فلا يؤذي جاره)

***"Wanda ya kasance yana imani da Allah da ranar Lahira kada ya cuta wa maƙwabcinsa."***Buhari da Muslimu suka ruwaito.

Tirmizi ya ruwaito hadisi:

( أحسن إلى جارك تكن مؤمنا)

***"Kyautata zuwa ga maƙwabcinka ka zama mumini."***

**(63) Kyakkyawar Mu'amala**

Kuma da kyakkyawar mu'amala. Wannan ya gabata ga hadisin:

(المؤمن من أمنه الناس على أموالهم)

***"Mumini shi ne wanda mutane suka aminta da shi a bisa ga (jininsu) da dukiyoyinsu."***

Yana daga mu'amala tara dukiya daga halas:

Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(إن التجار يبعثون يوم القيامة فجارا إلا من اتقى الله وبر وصدق)

***"'Yan kasuwa ana tayar da su ranar Alƙiyama suna fajirai face wanda ya ji tsoron Allah ya aikata alheri kuma ya yi gaskiya."*** Tirmizi ya ruwaito shi kuma ya inganta shi, haka kuma Ibnu Maja ya ruwaito shi.

Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(أيها الناس إن أحدكم لن يموت حتى يستكمل رزقة فاتقوا الله وأجملوا في الطلب خذوا ماحل ودعو ما حرم)

***"Ya ku mutane! Lalle ɗayanku ba zai mutu ba face ya cika arzikinsa, to, ku ji tsoron Allah kuma ku kyautata a wajen neman (arziki). Ku riƙi abin da Ya halatta, kuma ku bar abin da Ya haramta."*** Ibnu Maja ne ya ruwaito shi.

**(64) Ciyar Da Dukiya A Wurin Da Ya Cancanta**

Kuma da ciyar da dukiya ga haƙƙinta. Barin almubazzaranci da wuce iyaka na daga cikin haka. Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(إن الله كره لكم إضاعة المال)

*"Lalle, Allah ya ƙi a gare ku da ku tozarta dukiya."* Buhari da Muslimu suka ruwaito.

Ibnu Abbas ya faɗa a game da zancenSa Maɗaukakin Sarki:

﴿وَمَآ أَنفَقْتُم مِّن شَيْءٍ فَهُوَ يُخْلِفُهُۥ﴾ سبأ: ٣٩

***"Kuma abin da kuka ciyar daga wani abu, to, Shi ne Zai musanya shi." Saba'i:39***

Ya ce: "Ba a cikin wuce iyaka ba kuma ba da ƙwauro ba."

Haka kuma ya faɗa a game da zancenSa Maɗaukakin Sarki:

﴿وَلَا تُبَذِّرْ تَبْذِيرًا ٢٦﴾ الإسراء: ٢٦

***"Kuma kada ka bazzara dukiyarka bazzarawa." Isra'i:26***

Ya ce:

(التبذير الإنفاق في غير حق الله)

*"Mubazzaranci shi ne ciyarwa ba a cikin haƙƙin Allah ba."* Buhari ya ruwaito shi a cikin littafin Al-Adab.

**(65) Mayar Da Sallama**

Kuma da mayar da sallama. Allah Maɗaukakin Sarki ya ce:

﴿وَإِذَا حُيِّيتُم بِتَحِيَّةٍ فَحَيُّوا بِأَحْسَنَ مِنْهَآ أَوْ رُدُّوهَآ﴾ النساء: ٨٦

***"Kuma idan aka gaishe ku da wata gaisuwa, to, ku yi gaisuwa da abin da yake mafi kyau daga gare ta, ko kuwa ku mayar da ita." Nisa'i:86***

Kuma umarni da a yi haka ya zo a cikin hadisai ingantattu. Haka kuma ƙyarga yin haka daga cikin imani ya zo a cikin hadisin da Bazzarau ya ruwaito, a inda aka ce:

(ثلاث من الإيمان: (الإنفاق بغير إقتار وبذل السلام والإنصاف من نفسك)

***"Abu uku suna daga imani: Ciyarwa ba tare da ƙwauro ba, kuma da watsa sallama, haka kuma da ba da haƙƙi ko da abu ya shafe ka."***

Ɗabarani ya ruwaito hadisi da lafazin:

(من جمعهن فقد جمع الإيمان)

***"Wanda ya tara su (abubuwan uku), to, lalle ya tara imani."***

**(66) Gayar Da Mai Atishawa**

Kuma da gayar da mai atishawa. Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(حق المسلم على المسلم ست: إذا لقيته فسلم عليه وإذا عطس وحمد فشمته)

***"Haƙƙin Musulmi ga Musulmi shida ne: "Idan ya haɗu da shi, to, ka yi sallama a gare shi; kuma idan ya yi atishawa kuma ya gode wa Allah, to, ka gayar da shi."*** Wannan har zuwa ƙarshen hadisin.

Buhari ya ruwaito hadisi cewa:

(إذا عطس أحدكم وحمد الله كان حقا على كل مسلم سمعه أن يقول له يرحمك الله)

***"Idan ɗayanku ya yi atishawa kuma ya gode wa Allah, to, ya kasance haƙƙi a kan duk Musulmin da ya ji shi da ya ce: "Allah ya yi rahama a gare ka."***

**(67) Kame Cutarka Daga Mutane**

Kuma da kame cutarka daga barin mutane. Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(لا ضر ولا ضرار)

***"Babu cutarwa kuma babu riskar da cuta ga wani."*** Daru-Kuɗuni ne ya ruwaito shi da kuma waninsa.

**(68) Nisantar Wasanni**

Kuma da nisantar wasanni. Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(لست من دد ولا الدد مني)

***"Ban kasance daga wasa ba, kuma wasa ba ya kasance daga gare ni ba."***

Haka kuma ya ce: "Wasa sharri ne."

Ibnu Abbas ya faɗa a game da zancen Allah Maɗaukakin Sarki.

﴿ وَمِنَ ٱلنَّاسِ مَن يَشۡتَرِي لَهۡوَ ٱلۡحَدِيثِ ﴾ لقمان: ٦

***"Kuma akwai daga mutane wanda ke sayen tatsuniyoyi". Luƙman:6***

Ya ce: Abin da ake nufi waƙa da makamantanta. Buhari ne ya ruwaito haka a cikin littafin Al-Adab a babin wasa.

Ibnu Abid-Dunya ya ruwaito hadisi a cikin littafinsa na Zammul-Mala'hi cewa:

(العناء ينبت النفاق في القلب)

***"Waƙa tana tsirar da munafunci a cikin zuciya."***

Ya zo a cikin Musnad na Bazzaru da isnadi ingantacce cewa:

(كل شيء ليس فيه ذكر الله فهو سهو ولغو إلا الأربع مشى الرجل بين العرضتين وتأديبه فرسه وملاعبته أهله وتعليمه السباحة)

***"Kowane abu wanda babu ambaton Allah a ciki, to, ya kasance rafkana da wasa face abubuwa huɗu: tafiyar mutum a tsakanin cicita biyu; kuma da ladabtar da dokinsa; kuma da wasansa da matarsa; haka kuma da koyon ninƙaya."*** Ibnu Maja ya ruwaito kwatankwacinsa.

**(69) Gusar Da Abin Da Ke Cutarwa Daga Hanya**

Haka kuma da gusar da abin da ke cutarwa daga hanya. Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(الإيمان بضع وستون أو سبعون شعبة وأرفعها قول لا إله إلا الله وأدناها إماطة الأذى عن الطريق)

***"Imani yana da rassa sittin da wani abu ko saba'in da wani abu; mafi ɗaukakarsu shi ne zancen La'ilaha Illallah; kuma mafi ƙanƙantarsu shi ne gusar da abin da ke cutarwa daga hanya."*** Muslimu ne ya ruwaito.

## KAMMALAWA

### Ilimi Shi Ne Tushen Aiki

Ilimi shi ne tushen aiki, kuma aiki ba ya inganta sai da shi. Ma'ana aiki shi ne fa'idar ilimi. Ilimi ba ya da amfani matsawar babu aiki, a'a, har ma yana cutarwa. Kaɗan daga aiki tare da ilimi shi ya fi a bisa ga aiki mai yawa tare da jahilci. Domin wanda ya yi aiki ba tare da ilimi ba, ɓarnarsa za ta fi gyaransa yawa. Daga wannan ne ilimi ya kasance mafi fifiko a bisa ga sallar nafila, kamar dai yadda Imamu Shafi'i yardar Allah ta tabbata a gare shi ya faɗa. Wannan kuwa saboda kasancewarsa ko dai farlu aini ko kuwa farlu kifaya. Farilla kuwa ita ce mafificiya a bisa ga nafila.

Wannan saboda hadisin da Buhari ya ruwaito wanda ya gabata a farkon babin Sufanci.

Haƙiƙa mai tsira da amincin Allah ya ce:

(فضل العالم على العابد كفضلي على أدناكم)

***"Fifikon malami a kan mai ibada kamar fifikona a kan mafi zama ƙasa ƙasanku."***

Haka kuma ya faɗi cewa:

(فقيه واحد أشد على الشيطان من ألف عابد)

***"Malami ɗaya shi ne mafi tsanani ga shaiɗan a bisa ga mai ibada dubu."***
Hakimu ne ya ruwaito shi.

A wani lafazi ga ruwaya ta Ɗabarani:

(قليل العلم خير من كثير العبادة وكفى بالمرء فقها إذا عبد الله وكفى بالمرء جهلا إذا أعجب برأيه)

*"Kaɗan nan ilimi ya fi daga yawan ibada. Ya isa fahimta ga mutum idan ya bauta wa Allah, kuma ya isa jahilci ga mutum idan ra'ayinsa ya ba shi sha'awa."*

A wani lafazi a wajensa:

(فضل العلم أحب إلى من فضل العبادة)

*"Kaɗan nan ilimi ya fi daga yawan ibada."*

Ya zo a cikin ingantaccen hadisi da Muslimu ya ruwaito:

(إذا مات ابن آدم انقطع عمله إلا من ثلاث صدقة جارية وعلم ينتفع به)

*"Idan ɗan'adam ya mutu, to, aikinsa ya yanke face daga abubuwa uku: Sadaka mai gudana, da ilimin da ake amfani da shi...."* Har zuwa ƙarshen hadisin.

A wani lafazi na ruwayar Ibnu Maja:

(إن مما يلحق المؤمن من عمله وحسناته بعد موته علما نشره)

*"Daga abin da ke riskar mumini daga aikinsa kuma da kyawawan abubuwa nasa bayan mutuwarsa shi ne ilimin da ya yaɗa."*

Manzon Allah ya kasance yana addu'a:

(اللهم إني أعوذبك من علم لا ينفع)

*"Ya Allah, ni ina neman ka kiyaye ni daga ilimin da ba ya da amfani."* Hakimu da waninsa suka ruwaito shi.

Haka kuma ya faɗa:

(كل علم وبال علي صاحبه يوم القيامة إلا من عمل به)

*"Kowane ilimi musifa ne ga ma'abucinsa a ranar Alƙiyama face wanda ya yi aiki da shi."* Dabarani ya ruwaito shi.

## MATAKAN FANNONIN ILIMI

Mafifici daga fannonin ilimi shi ne ilimin tauhidi. Wannan saboda tsayuwar asalin addini a kansa ko kuwa kammaluwarsa.

Bayan haka sai ilimin tafsiri, saboda ratayuwarsa da zancen Allah (Alƙur'ani) wanda yake shi ne mafi ɗaukakar zance.

Daga nan sai hadisi, shi kuwa saboda ratayuwarsa da maganar Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi.

Daga wannan sai ilimin *USULUL* Fiƙihi. An gabatar da shi a kan ilimin Fiƙihu saboda ɗaukakar tushe a bisa ga reshe. Shi kuwa ilimin Fiƙihu shi ne mafi ɗaukaka a bisa ga waninsa. Wannan kuwa saboda hadisan da suka gabata a game da shi.

Bayan haka sai rassan ilimi masu taimakawa na daga nahawu da sarfu da harshe da ilimin ma'anoni da sauransu. Wannan kuwa kowane a bisa gwargwadon buƙatar da ake da ita a kansa.

Ilimin likitanci shi ke biye da wannan. Shi kuwa yana daga farilla ta kifaya. Mai littafin Raudah da waninsa ya bayyanar da haka.

Fannonin ilimin Falsafa suna haramta kamar irin su, ilimin Manɗiƙi. Wannan da ijima'i na magabata kuma da mafi yawan waɗanda ake lura da ra'ayinsu daga mabiyansu. Daga cikinsu akwai Ibnus-Salah da Nawawi da jama'a waɗanda ba su ƙidayuwa. Malam Abdurrahman Suyuɗi ya ce: "Lalle na wallafa littafi a game da haramcinsa (Manɗiƙ). A cikinsa na cirato nassoshin malamai a game da haramcinsa."

Malamin nan masanin hadisi, Sirajud-Dini Alƙazwini daga malaman Hanafiyyah, ya ambaci cewa, lalle Gazali ya koma zuwa ga haramcinsa bayan a can baya ya yi yabo a gare shi a farkon littafinsa na Al-Mustasfa.

Abdulrahman Suyuɗi ya ce: "Malam Salafi daga Shafi'awa da Ibnu Rushdi daga Malikawa sun tafi a kan cewa, wanda ya shagaltu da shi (Manɗiƙ) ba a karɓar ruwaya tasa".

## SALLA ITA CE MAFIFICIYA DAGA DUKAN IBADA

Salla ita ta fi daga ɗawafi haka kuma daga dukan ibada a bisa zance mafi inganci. Wannan saboda hadisin da ya ce:

(خير أعمالكم الصلاة)

***"Salla ita ce mafificiya daga ayyukanku."***

Hadisin, Hakimu da waninsa suka ruwaito shi. Haka kuma domin kasancewar ta ƙunshi nau'o'in ibada da waninta bai ƙunsa ba; watau na daga tsarki da fuskantar Alƙibla da karantun Alƙur'ani da ambaton Allah da salati a bisa ga ManzonSa. Haka kuma an hana a cikinta duk abin da aka hana ga sauran ibadodi; wannan tare da cewa ta keɓanta da hanin yin magana da tafiya da ire-irensu.

A wani zance an ce azumi ne mafifici, saboda hadisin da Buhari da Muslimu suka ruwaito:

(كل عمل ابن آدم له إلا الصوم فإنه لي وأنا أجزى به)

***"Dukan aikin ɗan'adam nasa ne face azumi, to, lalle shi Nawa ne, kuma Ni zan saka da shi."***

A wani zance aka ce ɗawafi ne mafifici daga salla.

A wani ƙauli aka ce ɗawafi ne ya fi ga waɗanda suke baƙi ne a can Makka.

A wani ƙauli aka ce hajji ne mafifici daga salla; wannan saboda akwai wahalar da jiki a cikinsa, kuma da amfani da dukiya; haka kuma da kasancewar an kira mu zuwa gare shi tun a cikin tsatson iyaye, sai ya kasance ya yi kama da imani; haka kuma da kasancewar ba a kamanta aukuwarsa a bisa ga nafila, domin rayar da Ka'aba da shi farilla ne ta kifaya; a dalilin haka duk wanda ya tsayu da shi, to, aikinsa an tsayar da shi a bisa matsayi na farilla.

A wani zance cewa aka yi salla ce mafificiya a Makka, shi kuwa azumi shi ne mafifici a Madina.

Shi kuwa ɗawafi shi ya fi daga sauran ibadodi, wannan kuwa har da Umra. Malam Azraƙi ya ruwaito cewa, Anas ɗan Malik ya zo a garin

Madina, sai Umar ɗan Abdul'aziz ya hau zuwa gare shi, kuma ya tambaye shi, wane ne ya fi: ɗawafi ko umra? Sai ya karɓa masa da cewa ɗawafi ne ya fi.

A wani zance aka ce umra ce ta fi daga ɗawafi. Malam Muhibbu Al-Dabari ya faɗa a cikin wani daga littattafansa a game da wannan matsala. Ya ce, wannan kuskure ne bayyananne (watau fifita umra a kan ɗawafi). Babban dalili a kan haka shi ne saɓa wa magabata; domin ba a cirato kwankoma ta ba daga Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi; haka kuma da waɗanda suka biyo bayansa. A'a har ma Imam Maliki da Ahmad sun ƙi a kwankoma umra a cikin shekara ɗaya; amma kuma malamai sun haɗu a kan yawaitar da ɗawafi.

Zance a game da yawaitawa; ma'ana ga wanda ya nufi ya yawaita abu ɗaya, kuma ya zama shi ne galibi a gare shi, watau dai ya kasance ya taƙaita a kan wani abu ɗaya, to, a bisa ga magana mafi ƙarfi, abin da ya fi shi ne yawaita salla, sa'annan ɗawafi. Amma idan ba haka ba azumin yini ɗaya shi ne mafifici a bisa raka'a biyu na nafila. Wannan babu saɓani a kan haka. Haka kuma umra ɗaya ita ce ta fi daga ɗawafi ɗaya, domin ta ƙunshi ɗawafi; ma'ana tana da ƙari a bisa ɗawafi. Nawawi ne ya farkar a kan haka a cikin littafinsa na Sharhin Muhazzab kuma da Muhibbu Al-Dabari a cikin littafinsa da aka ambata.

## YIN NAFILA A GIDA SHI YA FI A BISA GA WAJENSA

Yin nafila a gida shi ya fi a bisa ga yinta a wajensa, wannan kuwa har da masallacin Makka da Madina.

Wannan saboda hadisin da Buhari da Muslimu suka ruwaito:

(أيها الناس صلوا في بيوتكم فإن أفضل الصلاة صلاة المرء في بيته إلا المكتوبة)

***"Ya ku mutane! Ku yi salla a cikin gidajenku domin mafificiyar sallar mutum ita ce wadda ya yi a gida face sallar farilla."***

Malam, mawallafin littafin Muhazzab, ya ƙayyade wannan da nafilar rana. Imam Nawawi ya yi sha'awar wannan ra'ayi nasa ga sharhinsa ga littafin na Muhazzab.

Malam Ibnu Subki ya faɗa a cikin littafin Al'Ashbahu Wal Al-Naza'iru cewa: Zai yiwu ya yi ishara da haka da cewa yinta a gida ya fi a

dalilin ɓoyuwarta, a lokacin da a masallaci za ta bayyana; amma da ba haka ba yinta a masallaci ya fi. Ya ce wannan ra'ayi yana da kyau.

## NAFILAR DARE TA FI A BISA GA TA RANA

Nafilar dare ita ce mafificiya a bisa ga nafilar rana; a dalilin hadisin da Muslimu ya ruwaito:

(أفضل الصلاة بعد الفريضة صلاة الليل)

***"Mafificiyar salla bayan sallar farilla ita ce sallar dare."***

Sa'annan tsakiyar dare; watau sulusinsa na ƙarshe bayan da ya raba shi kuma ya fi a bisa ga sauran sassansa. Shi kuwa ƙarshen dare ya fi sashi na farko, watau dai rabi na ƙarshe. An tambayi Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi cewa:

(أى الصلاة أفضل بعد المكتوبة فقال ((جوف الليل)

***"Wace salla ce ta fi bayan sallar farilla? Sai ya amsa" sallar cikin dare."*** Muslimu ne ya ruwaito shi.

Haka kuma ya faɗi cewa:

(أحب الصلاة إلى الله صلاة داود كان ينام نصف الليل ويقوم ثلثه وينام سدسه)

***"Salla mafi zama abin so a wajen Allah ita ce sallar (Annabi) Dawuda: Ya kasance yana barcin rabin dare, kuma yana tsayuwa sulusinsa, kuma yana barcin sudusinsa."***

Haka kuma ya ce:

(ينزل ربنا كل ليلة إلى السماء الدنيا حين يبقى ثلث الليل الآخر فيقول من يدعوني فأستجيب له من يسألني فأعطيه من يستغفرني فأغفر له)

***"Ubangijinmu yana sauka a kowane dare a sama ta duniya a lokacin da sulusi na ƙarshe na dare ya rage yana cewa: "Wane ne ke kiraNa in karɓa masa; kuma wane ne ke roƙoNa in ba shi; kuma wane ne ke roƙoNa gafara sai In gafarta masa."*** Buhari da Muslimu suka ruwaito.

## KARATUN ALKUR'ANI DA FAHIMTA SHI NE YA FI DUKAN ZIKIRI

Alƙur'ani shi ya fi kowane zikiri, wannan saboda hadisin da zai zo a nan gaba. Su kuwa biyun watau zikiri da karatun Alƙur'ani sun fi daga addu'a a inda ba a shar'anta ta ba. Tirmizi ya ruwaito hadisi kuma ya kyautata shi daga Abu Sa'id Al-Khudri. Ya ce Mai tsira da amincin Allah ya ce:

(يقول الرب من شغله القرآن وذكرى عن مسألتي أعطيته أفضل ماأعطى السائلين وفضل كلام الله على سائر الكلام كفضل الله على خلقه)

***"Ubangiji yana cewa: "Wanda Alƙur'ani da ambatoNa suka shagaltar da shi daga roƙoNa, to, zan ba shi fiye da abin da Nake bai wa masu roƙo." "Kuma fifikon zancen Allah a bisa ga sauran zantuka tamkar fifikon Allah ne a bisa ga halittarsa."***

A lafazin Musnad na Bazzaru Allah yana cewa:

(من شغله قراءة القرآن عن دعائي أعطيته أفضل ثواب الشاكرين)

***"Wanda karatun Alƙur'ani ya shagaltar da shi daga roƙoNa, to, zan ba shi mafificiyar ladan da nake bai wa masu godiya."***

Tirmizi ya ruwaito hadisi:

(ما تقرب العباد إلى الله بمثل ما خرج منه)

***"Bayi ba su bauta wa Allah da wani abu ba kamar abin nan da ya fito daga gare Shi".***

Baihaƙi ya ruwaito hadisi a cikin littafinsa na Shu'abul-Imani:

(قراءة القرآن في الصلاة أفضل من التسبيح والتكبير)

***"Karatun Alƙur'ni a cikin salla ya fi karantun Alƙur'ani ba a cikin salla ba, karatunsa ba a cikin salla ba ya fi daga tasbihi da takbir".***

Amma shi kuwa du'a'i a inda aka shar'anta shi shi ne mafifici. Harafi ɗaya da lura da shi ya fi a bisa ga haruffa biyu da aka karanta ba tare da lura ba. Allah Maɗaukakin Sarki ya ce:

﴿ كِتَٰبٌ أَنزَلۡنَٰهُ إِلَيۡكَ مُبَٰرَكٞ لِّيَدَّبَّرُوٓاْ ءَايَٰتِهِۦ ﴾ ص: ٢٩

***"(Wannan) littafi ne, Mun saukar da shi zuwa gare ka, yana mai albarka, domin su lura da ayoyinsa." Sad:29***

Haka kuma Maɗaukakin Sarki ya faɗa:

﴿ وَرَتِّلِ ٱلۡقُرۡءَانَ تَرۡتِيلًا ﴿٤﴾ ﴾ المزمل: ٤

***"Kuma ka kyautata karatun Alƙur'ani daki-daki." Muzzammil:4***

Buhari da Muslim sun ruwaito daga Abu Wa'ili ya ce: "Mun tafi zuwa ga Abdullahi sai wani mutum ya ce: "Na karanta surorin Mufassal a jiya." Sai Abdullahi ya ce: "Katsewa tamkar katsewar waƙa."!

Ahmad ya ruwaito daga A'isha yardar Allah ta tabbata a gare ta cewa, an ambata a wajenta waɗansu mutane suna karance Alƙur'ani sau ɗaya ko sau biyu a cikin dare ɗaya sai ta ce: "Waɗannan sun yi karatu amma ba su karanta kome ba. Na kasance ina tsayuwa tare da Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi dare ɗaya cikakke, ya kasance yana karanta Suratul Baƙara da Ali Imrana da Nisa'i; ba ya wucewa ga aya wadda akwai gargaɗi a cikinta face ya roƙi Allah, kuma ya nemi tsari; kuma ba ya wucewa ga aya wadda a cikinta akwai albishir face ya roƙi Allah, kuma ya yi kwaɗayi zuwa gare Shi".

Tirmizi da waninsa sun ruwaito hadisi:

(يقال لصاحب القرآن اقرأ وارق ورتل كما كنت ترتل فإن منزلتك عند آخر آية تقرأها)

***"Za a ce ga ma'abucin Alƙur'ani: "Karanta kuma taka ka hau, kuma karanta daki-daki kamar yadda ka kasance kana karantawa daki-daki, lalle matsayinka yana a ƙarshen ayar da kake karantawa."***

Abu'ubaida ya ruwaito daga Abu'hamza ya ce na ce ga ɗan Abbas: Ni mai saurin karatu ne. Sai ya ce: "In karanta Suratul Baƙarah a dare ɗaya in fahimce ta, ya fi a gare ni a bisa ga in karance Alƙur'ani gaba ɗaya a cikin sauri."

Ma'abuta Sunanu sun ruwaito hadisi:

(لا يفقه من قرأ القرآن في أقل من ثلاث)

***"Bai fahimta ba wanda ya karance Alƙur'ani a ƙasa da kwanaki uku."***

Buhari ya ruwaito hadisi daga Anas ya ce: "Karatun Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya kasance abin jan MADDA a cikinsa."

Abu'dawuda da Tirmizi da Nasa'i sun ruwaito daga Ummu Salma cewa ta siffanta ƙira'ar Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi da cewa ƙira'a ce mai bayani, harafi harafi.

## KARANTA ALKUR'ANI DA LITTAFI YA FI A BISA GA YI DA KA

Karatun Alƙur'ani da littafi shi ya fi a bisa ga yi da ka. Domin duba ga littafi ibada ne. Wannan har ya kai ga cewa, wasu daga cikin magabata sun ƙi a ce rana ta zo kuma ta wuce ga mutum ba tare da ya yi nazari a cikin Alƙur'ani ba.

Abu'ubaida ya ruwaito hadisi:

(فضل قراءة القرآن نظرا على من يقرؤوه ظهرا كفضل الفريضة على النافلة)

***"Falalar karatun Alƙur'ani ta hanyar nazari ta fi ta wanda ke karantunsa da ka, wannan kamar yadda sallar farilla ta fi ta nafila."*** Wannan hadisi isnadinsa yana da rauni.

Hadisi ya zo a cikin littafin Shu'abu na Baihaƙi da isnadi mai rauni:

(لقراءة القرآن في غير المصحف ألف درجة وقراءته في المصحف تضعف على ذلك إلى ألفى درجة)

***"Lalle karatun Alƙur'ani ba a cikin littafi ba yana da daraja dubu, kuma karatunsa a cikin littafi yana ninkawa har zuwa daraja dubu biyu."***

Haka kuma da hadisin da ya ce:

(أعطوا أعينكم حظها من العبادة قالوا وما هو قال النظر في المصحف)

***"Ku bai wa idonku rabonsu daga ibada! Sai suka ce: "Mene ne shi? Sai ya ce: "Duba a cikin Alƙur'ani."***

Har wa yau ya zo a cikin Shu'abu da isnadi ingantacce ga hadisin da aka tsayar ga Ibnu Mas'ud ya ce: "Ku dauwamar da duba a cikin Alƙur'ani."

Bayyana karatun Alƙur'ani shi ya fi daga asirta shi idan aka aminta daga riya. Domin amfaninsa yana ƙetare mai karatu zuwa ga mai saurare.

Amma idan aka ji tsoron riya, to, sai a asirta. A bisa ga wannan ne ake ɗaukar hadisin da Tirmizi ya ruwaito:

(الجاهر بالقرآن كالجاهر بالصدقة)

*"Mai bayyanar da karatun Alƙur'ani tamkar mai bayyanar da sadaka ne."*

YIN KAWAICI SHI YA FI A BISA GA YIN MAGANA FACE A KAN HAKKI

Kuma kawaici shi ne ya fi daga yin magana ko da maslaharsu ta daidaita face sai ga haƙƙi. Wannan kamar yadda mai tsira da amincin Allah ya faɗa:

(كل كلام ابن آدم عليه لا له إلا أمر بالمعروف ونهى عن المنكر أو ذكر الله –تعالى)

*"Dukan zancen ɗan'adam hujja ne a kansa ba hujja a gare shi ba face umarni da alheri, kuma da hani daga abin da ake ƙi, ko ambaton Allah Maɗaukakin Sarki."*

Ya kuma ce:

(لا تكثروا الكلام بغير ذكر الله فإن الكلام بغير ذكر الله قسوة للقلب وإن أبعد الناس من الله القلب القاسي)

*"Kada ku yawaita magana ba da ambaton Allah ba, domin magana ba da ambaton Allah ba, bushewa ce ga zuciya, kuma lalle mafi nisantar mutane daga Allah, ita ce zuciyar da ta bushe."*

Haka kuma ya faɗa:

(إذا أصبح ابن آدم فإن الأعضاء كلها تكفر من اللسان فتقول له اتق الله فينا فإنما نحن بك فإن استقمت استقمنا وإن اعوجت اعوججنا)

***"Idan ɗan'adam ya wayi gari, to, gaɓoɓi dukansu suna koke ga harshe suna cewa a gare shi: Ka ji tsoron Allah a game da mu, domin mu, talakawa ne a gare ka; idan ka daidaita, sai mu daidaita, kuma idan ka karkace sai mu karkace,"***

Haka ya faɗa ga Uƙubatu ɗan Amir alhali ya tambaye shi: Mene ne tsira:

(أمسك عليك لسانك وليسعك بيتك)

***"Ka kame harshenka, kuma gidanka ya yalwata a gare ka."***

Haka kuma ya faɗa ga Sufyanu a lokacin da ya tambaye shi: Mene ne mafi girman abin da kake tsoro a gare ni? Sai ya ce: "Wannan." Sai ya kama harshensa ya riƙe.

Anas ya ce wani mutum ya cika sai wani ya yi masa albishir da Aljanna sai Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(أولا تدري فلعله تكلم فيما لا يعنيه)

***"Ai ba ka sani ba mai yiwuwa ne yana magana a game da abin da ba ya amfaninsa."***

Duk waɗannan hadisan Tirmizi ne da waninsa suka ruwaito su.

Ya zo a cikin Buhari da Muslimu cewa:

(إن العبد يتكلم بكلمة ما يتبتن فيها ينزل بها إلى النار أبعد ما بين المشرق والمغرب)

***"Lalle ne bawa yana magana da kalima ba tare da ya yi tunani da ita ba sai ya zama ya abka wuta a dalilinta ga abin da yake mafi nisan abin da ke tsakanin gabas da yamma."***

Buhari ya ruwaito hadisi:

(من يضمن لي ما بين لحييه ورجليه أضمن له الجنة)

***"Wane ne zai lamunce a gare ni ga abin da ke tsakanin gaɓoɓinsa da abin da ke tsakanin ƙafafuwansa, Ni kuwa In lamunce masa Aljanna."***

Kalmar “Ya tabayyanu” ta Larabci ita ce ke da ma’anar tunani. Shi kuwa faɗar da aka yi na cewa sai ga haƙƙi, shi ne abin da aka toge na cewa: “Sai umarni da alheri” har zuwa ƙarshe.

## CUƊANYA DA MUTANE DA JURE WA CUTARSU YA FI DAGA NISANTARSU

Kuma da cuɗanya da mutane da jure wa cutarsu ya fi a bisa ga nisantarsu. Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(المؤمن الذي يخالط الناس ويصبر على أذاهم خير من الذى يخالط الناس ولا يصبر على أذاهم)

***“Mumini wanda ke hulɗa da mutane kuma yana jure wa cutarsu ya fi a bisa ga wanda ba ya cuɗanya da mutane kuma ba ya jure wa cutawarsu.”*** Buhari ya ruwaito shi a cikin littafin Al-Adab da waninsa.

Nisantarsu shi ya fi idan ya ji tsoron fitina ga addininsa a bisa ga ya bi su ga abin da suke a kai (na ɓarna). A kan wannan ne ake ɗaukar hadisin Uƙuba da ya gabata: “Gidanka ya yalwace ka” (ka tsaya a gidanka). Haka kuma a kansa ne ake ɗaukar hadisin da Buhari ya ruwaito:

(يوشك أن يكون خير مال المسلم غنم يتبع به شعف الجبال ومواقع القطر يفر بدينه من الفتن)

***“Ya kusanta ya kasance mafificiyar dukiyar Musulmi: Awaki da zai bibiyi ƙolin duwatsu da su kuma da mafaɗar ruwan sama yana mai gudu da addininsa daga fitina.”***

Haka kuma da hadisin da Buhari da Muslimu suka ruwaito:

(أى الناس أفضل قالوا من جاهد بماله ونفسه وقال ثم مه فقالوا الله ورسوله أعلم قال ثم مؤمن يعتزل الناس في شعب يتقى ربه ويدع الناس من شره)

***“Daga mutane wane ne mafifici? Sai suka ce: Wanda ya yi jihadi da dukiyarsa da kansa. Sai ya ce: “Sa’annan me”? Sai suka ce: Allah da ManzonSa suka sani. Sai ya ce: “Sa’annan muminin da ke nisantar mutane a cikin rafuka yana jin tsoron Ubangijinsa, kuma yana nisantar da mutane daga sharrinsa.”***

Ibnu Abid-dunya ya ruwaito hadisi a cikin littafinsa na Al-Uzlah cewa:

(إن أعجب الناس إلى رجل يؤمن بالله ورسوله ويقيم الصلاة ويؤتي الزكاة ويحفظ دينه ويعتزل الناس)

*"Mafi ban sha'awar mutane a wajena, shi ne mutum wanda ya yi imani da Allah da ManzonSa kuma yana tsayar da salla, kuma yana ba da zakka kuma yana kiyaye addininsa; kuma yana nisantar mutane".*

Baihaƙi ya ruwaito a cikin littafin Al-Zuhdu hadisi wanda ya sadar da shi ga Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi:

(يأتي على الناس زمان لا يسلم لذي دين دينه إلا من هرب بدينه من واد إلى واد ومن شاهق إلي شاهق ومن حجر إلي حجر فإذا كان ذلك الزمان لم تنل المعيشة إلا بسخط الله فإذا كان ذلك كان هلاك الرجل على يدى زوجته وولده فإن لم يكن له زوجة ولا ولد كان هلاكه على يدي أبويه وإن لم يكن له أبوان كان هلاكه على يدى قرابته أو الجيران)) قالوا كيف ذلك يا رسول الله قال يعيرونه بضيق المعيشة فعند ذلك يورد نفسه الموارد التى يهلك نفسه فيها)

*"Zamani zai zo ga mutane wanda addini ba zai kuɓuta ga ma'abucinsa ba face wanda ya gudu daga wannan rafi zuwa ga wancan, daga wannan ƙoli na dutsi zuwa ga wancan, daga wannan dutsi zuwa ga wancan. Idan wancan zamani ya kasance ba za a samu a rayu ba face da fushin Allah. Idan al'amari ya kasance haka halakar mutum tana kasancewa a hannun matarsa da ɗansa; idan ba ya da mata ko ɗa, to, halakarsa za ta kasance a hannun iyayensa; idan kuwa ba ya da iyaye, to, halakarsa za ta kasance a hannun 'yan'uwan zumunta nasa ko maƙwabta nasa." Sai suka ce: yaya ne wancan abu ya Manzon Allah! Sai ya ce: "Za su zarge shi da ƙuncin rayuwa; a lokacin nan sai ya jefa kansa a wuraren halaka waɗanda zai halakar da kansa a cikinsu."*

## SAMUN GWARGWADON BUKATA SHI NE YA FI A BISA GA TALAUCI DA TARA DUKIYA

Kuma samun abin da yake gwargwadon buƙata shi ne mafifici a bisa ga talauci da tara dukiya. Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(قد أفلح من أسلم ورزق كفافا وقنعه الله بما رزقه)

***"Haƙiƙa ya rabbanta wannan da ya musulunta kuma aka uzurta shi da gwargwadon buƙata kuma Allah ya gamsar da shi da abin da Ya azurta shi da shi."***

Haka kuma ya ce:

(طوبى لمن هدى للإسلام وكان عيشة كفافا وقنع)

***"Farin ciki ya tabbata ga wanda aka shiryar da shi zuwa ga Musulunci kuma rayuwarsa ta kasance a bisa gwargwadon buƙata kuma ya gamsu da haka."***

Haka kuma ya ce:

(لهم اجعل رزق آل محمد كفافا)

***"Ya Allah Ka sanya arzikin iyalan Muhammad a bisa gwargwadon buƙata."***

Hadisi na farko da na ƙarshe Muslimu ne ya ruwaito su; shi kuwa na biyu Tirmizi ne ya ruwaito shi.

Haka kuma Tirmizi ya ruwaito:

(أن أغبط أوليائي عندي المؤمن خفيف الحاذ ذو حظ من الصلاة أحسن عبادة ربه وأطاعه في السر وكان غامضا في الناس لا يشار إليه بالأصابع وكان رزقه كفافا فصبر على ذلك)

***"Mafi ban sha'awar masoyaNa a wajenNa shi ne mumini mai kaɗan na abin hannunsa, kuma mai rabo ga salla, wanda ya kyautata bautar Ubangijinsa, kuma ya yi maSa ɗa'a a ɓoye, kuma shi ya kasance a ɓoye a cikin mutane, ba a nuna shi da yatsu; kuma arzikinsa ya kasance a bisa gwargwadon buƙata kuma ya yi haƙuri a kan haka."***

Muslimu ya ruwaito hadisi:

(يا ابن آدم إن تبذل الفضل خير لك وأن تمسكه شرلك ولا تلام على كفاف)

***“Ya kai ɗan’adam! Ka ba da abin da ya yi saura (a bisa buƙatarka) shi ne mafi alheri a gare ka, kuma ka kame shi sharri ne a gare ka, kuma ba a zarginka a bisa gwargwadon buƙata.”***

Waɗansu daga malamai sun ce talauci tare da haƙuri shi ya fi saboda hadisin da Buhari da Muslimu suka ruwaito:

(يدخل فقراء المؤمنين الجنة قبل أغنيائهم بنصف يوم وهو خمس مائة عام)

***“Talakawan muminai za su shiga Aljanna gabanin mawadata da rabin yini.”***
Wannan kuwa su ne shekaru ɗari biyar.

A wajen Tirmizi:

(اللهم أحيني مسكينا واحشرني في زمرة المساكين يوم القيامة)

***“Ya Allah! Ka rayar da ni ina miskini, kuma ka cika min ina miskini, kuma Ka tara ni a cikin jama’ar miskinai a ranar Alƙiyama.”***

Waɗansu suka ce wadata tare da godiya ita ce ta fi saboda hadisin da Buhari da Muslimu suka ruwaito:

“Ma’abuta dukiya sun tafi da lada.”

Waɗansu mutane sun fifita dogara ga Allah a bisa ga yin sana’a; watau dai kawar da kai daga dalilan sana’a da dogarar zuciya ga Allah Maɗaukakin Sarki.

Waɗansu kuwa suka zo da saɓanin haka, watau suka fifita yin sana’a a bisa ga barinta.

Waɗansu kuwa rarrabewa suka yi a bisa gwargwadon halayyar mutane. Wanda ya kasance mai dogara ga Allah kuma ba ya fushi idan aka ƙuntata arzikinsa, kuma ba ya tsinkaya zuwa ga roƙon wani daga cikin talikai, to, wannan tawakkali a wajensa shi ya fi. Wannan saboda abin da ke cikinsa na haƙuri da yaƙi da rai.

Amma wanda tawakkalinsa yake saɓanin abin da aka ambata, to, sana’a a wajensa ita ce ta fi; wannan domin tsoron faɗawa a cikin fushin Allah kuma da roƙon mutane.

Malam Abdurrahman Suyuɗi ya ce: Abin da yake zaɓaɓɓe a wajena: Sana'a ba ta kore tawakkali, a'a yana iya kasancewa mai sana'a kuma mai tawakkali. Wannan ta hanyar yarda da abin da Allah ya raba Ya ba shi, ya kasance ba mai tsinkaya ga sama da haka ba.

Haƙiƙa, Umar yardar Allah ta tabbata a gare shi ya faɗa ga waɗansu mutane da suka zauna (ba su sana'a) suka yi da'awar tawakkali ga Allah, ya ce: "Waɗannan ci-ma-kwance ne. Lalle, wanda ake kira mai tawakkali shi ne mai shuka irinsa a cikin ƙasa sa'annan ya dogara (ga Allah)." Baihaƙi ya ruwaito shi.

Ya zo a cikin littafin Risala ta Kushairi daga Sahlu ɗan Abdullahi: "Tawakkali shi ne halayya ta Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, sana'a kuwa ita ce sunnarsa. Wanda ya ƙarfafa a bisa ga halayya tasa, to, kada ya bar sunna tasa." Abin da ke kusa ga wannan hadisin shi ne abin da wani ya ce (ga Annabi):

(أدع ناقتي وأتوكل فقال (إعقلها وتوكل)

***"Zan bar raƙuma ta in dogara ga Allah! Sai Manzo ya ce a gare shi: "Ka yi mata dabaibaya ka dogara."***

Ajiye abincin shekara ba ya kore tawakkali. Lalle Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya kasance yana ajiye abincin shekara ga iyalinsa kamar yadda maganar ta tusgo a cikin Buhari da Muslimu. Wannan kuwa tare da cewa shi, Manzo, shi ne shugaban masu dogara ga Allah.

Kowane daga cikin talikan Allah, tsarki ya tabbatar maSa ya tsayar da shi a bisa ga abin da yake nufi na daga halayyar da mutum yake a kanta; watau dai na daga ilimi da aiki da ɗaukaka da ƙasƙantarwa da sauran ire-irensu.

An yi haka ne domin tsarin rayuwa ya gudana. Domin da a ce mutane gaba ɗaya sun bar yin sana'a, to, da masalaha da rayuwa sun lalace, haka kuma da ba a sami bambanci a matakai duniya da lahira ba. Wannan (haka Allah ya hukunta) kuma babu mai mayarwa ga hukuncinSa ta tunkuɗewa ko kuwa mai bin hukuncinSa da warwarewa; tsarki ya tabbatar maSa kumaYa ɗaukaka.

## SHIRYAR DA ƊALIBAI

Wannan shi ne ƙarshen abin da muka tusgo da shi a game da ilimin sufanci, wanda yake shi ne sashi na biyu na wannan littafi.

## SASHI NA UKU

### A Game Da Waɗansu Hadisai Daga Cikin Buhari Da Muslimu Da Suka Kamata Mai Hankali Ya San Su

Wannan sashi na uku na magana ne a game da waɗansu hadisai da aka tsamo daga cikin Buhari da Muslim ko daga cikin ɗaya daga gare su waɗanda ba ya kamata a ce mutum mai hankali ya rafkana ga saninsu. Da kammala bayani a kansu littafin ya cika. Muna roƙon Allah daidaita da sawaba a wajen aiwatar da su a bisa ga baiwarSa da karimcinSa.

### ZIKIRORIN DARE DA YINI

Ya zo a cikin Buhari da Muslimu daga Abu'huraira yardar Allah ta tabbata a gare shi cewa, Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(من قال لا إله إلا الله وحده لا شريك له له الملك وله الحمد وهو على كل شى قدير في يوم مائة مرة كانت له كعدل عشر رقاب وكتبن له مائة حسنة ومحيت عنه مائة سيئة وكانت له حرزا من الشياطين يومه ذلك حتى يمسي ولم يأت أحد بأفضل مما جاء إلا رجل عمل أكثر منه)

***"Wanda ya faɗi: Babu abin bautawa da gaskiya face Allah, shi kaɗai, babu abokin tarayya a gare shi, dukkan mulki da dukkan yabo nasa ne, kuma shi mai iko ne bisa komai. To, wannan ya kasance daidai da 'yanta bayi goma, kuma za a rubuta masa kyawawan ayyuka ɗari, kuma a shafe a gare shi miyagun ayyuka ɗari, kuma wannan ya kasance tsari a gare shi daga Shaiɗan a duk tsawon yininsa har ya yi marece, kuma babu wani da zai zo da abin da ya fi daga abin da ya aikata face wanda ya aikata sama da abin da shi ya aikata."***

Ma'ana:

Babu abin bautawa da gaskiya sai Allah Shi kaɗai babu abokin tarayya a gare Shi, mulki a gare Shi yake, kuma godiya na gare Shi, kuma Shi Mai iko ne bisa ga kome.

Har wa yau ya zo a cikin Buhari da Muslimu daga Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya faɗi cewa:

(من قال سبحان الله وبحمده في يوم مائة مرة حطت خطاياه وإن كانت مثل زبد البحر)

***"Wanda ya faɗi: Tsarki ya tabbata ga Allah, tare da yabo a gare shi, sau ɗari a cikin yini, to, an gafarta kurakuransa ko da sun kasance kamar kunfar teku."***

Ma'anar zikirin: Tsarki ya tabbatar wa Allah kuma da gode maSa.

Ya zo a cikin Buhari da Muslimu daga Abu Musa Al-Ash'ari yardar Allah ta tabbata a gare shi ya ce Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(ألا أدلكم على كنز من كنوز الجنة فقلت بلى يا رسول الله قال (قل لا حولا ولا قوة إلا بالله)

***"Ko in shiryar da ku a bisa ga taska daga taskokin Aljanna? Sai na ce: E, ya Manzon Allah! Sai ya ce: "LA HAULA WA LA KUWWATA ILLA BILLAHI."***

Ma'anar zikirin: Babu dabara babu ƙarfi face ga Allah.

Ya zo a cikin Buhari da Muslimu daga Abu'huraira yardar Allah ta tabbata a gare shi ya ce Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(كلمتان خفيفتان على اللسان ثقيلتان في المزان حبيبتان إلي الرحمن سبحان الله وبحمده سبحان العظيم)

***"Kalimomi biyu masu sauƙin faɗa ga harshe kuma masu nauyi a cikin ma'auni kuma abin so zuwa ga Mai rahama: Tsarki ya tabbata ga Allah, tare da yabo a gare shi, Tsarki ya tabbata ga Allah Mai Girma."***

Ma'anar zikirin: Tsarki ya tabbatar wa Allah da gode maSa, tsarki ya tabbatar wa Allah Mai girma.

Ya zo a cikin ingantaccen hadisi na Muslimu daga Abu'huraira yardar Allah ta tabbata a gare shi ya ce Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(لأن أقول سبحان الله والحمد لله ولا إله إلا الله والله أكبر أحب إلى مما طلعت عليه الشمس)

***"Lalle in faɗi: Tsarki ya tabbata ga Allah da godiya ta tabbata ga Allah da babu abin bautawa da gaskiya sai Allah da Allah Mai girma ya fi zama abin so a gare ni a bisa ga abin da rana ta ɓullo a gare shi."***

Ma'anar zikirin: Tsarki ya tabbata ga Allah, kuma godiya ta tabbata ga Allah, kuma ba abin bautawa da gaskiya sai Allah kuma Allah Mai girma ne.

Ya zo a cikin Muslimu daga Samura ɗan Jundubu yardar Allah ta tabbata a gare shi ya ce Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(أحب الكلام إلى الله سبحان الله والحمد لله ولا إله إلا الله والله أكبر لا يضرك بأيهن بدأت)

***"Kalimomi mafi zama abin so ga Allah guda huɗu ne: Tsarki ya tabbata ga Allah da godiya ta tabbata ga Allah da babu abin bautawa da gaskiya sai Allah da Allah Mai girma. Kuma ba ya cutar da kai da kowane ka soma da shi daga cikinsu".***

Ya zo a cikin Buhari daga Shaddadu ɗan Ausu yardar Allah ta tabbata a gare shi, ya ce Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(سيد الإستغفار اللهم أنت ربي لا إله إلا أنت خلقتني وأنا عبدك وأنا على عهدك ووعدك ما استطعت أعوذبك من شر ما صنعت أبوء لك بنعمتك على وأبوء بذنبي فاغفر لى فإنه لا يغفر الذنوب إلا أنت إذا قال ذلك حين يمسى فمات دخل الجنة أو كان من أهل الجنة ومن قال حين يصبح فمات من يومه كمثله)

***"Shugaban istigfari shi ne: Ya Allah! Kai ne Ubangijina, babu abin bautawa da gaskiya sai kai Ka halicce ni, kuma ni bawanka ne, kuma ina kan alƙawarin da nay i maka (na kaɗaita ka da bauta) da kuma alƙawarin da ka yi mini (na shigar da wanda bai yi shirka da Kai ba gidan aljanna) gwargwadon iko na ina neman tsarinka daga sharrin abin da na aikata, ina tabbatar da zunubi n aka gafara mini, domin ba wanda yake gafara zunubai sai kai. Idan ya faɗi wannan a lokacin da ya yi marece kuma ya mutu, to, zai shiga Aljanna, ko kuwa ya kasance daga 'yan-Aljanna; kuma wanda ya faɗe shi a lokacin da ya wayi gari, kuma ya mutu a wannan yini, to, kwatankwacin haka."***

Ma'anar Istigfarin: Ya Allah Kai ne Ubangijina! Ba abin bautawa da gaskiya face Kai. Kai Ka halicce ni, kuma ni bawanKa ne, kuma ina a kan alƙawarinKa da wa'adinKa a bisa gwargwadon iko. Ina neman tsari daga sharrin abin da na aikata, kuma ina mai furucin a gare Ka da ni'imarKa da wa'adinKa a kaina, kuma ina furuci da zunubina, Ka gafarta mini, domin babu mai gafarta zunubai face Kai.

Muhammad ɗan Abdurrahman ya faɗa a cikin littafin Al-Nuraini cewa: Yana kamata a lizimci waɗannan zikirori a kowace sa'a. Amma farkon yini da ƙarshensa su ne mafi zama abin so a wajena.

### ZIKIRORI A CIKIN SALLA DA BAYAN KARE SALLA

Ya zo a cikin Buhari da Muslimu daga Abu'huraira yardar Allah ta tabbata a gare shi, cewa, talakawan Muhajirai sun zo wajen Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi suka ce:

(يا رسول الله –صلى الله عليه وسلم– ذهب أهل الدثور بالدرجات العلى والنعيم المقيم يصلون كما نصلي ويصومون كما نصوم ولهم فضول من الأموال يحجون بها ويعتمرون ويجاهدون ويتصدقون فقال (ألا أعلمكم شيئا تدركونه من سبقكم وتسبقون من بعدكم ولا يكون أحد أفضل منكم إلا من صنع مثل ما صنعتم قالوا بلى يا رسول الله قال تسبحون وتحمدون وتكبرون خلف كل صلاة ثلاثا وثلاثين)

***"Ya Manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi) – ma'abuta dukiya sun tafi da darajoji maɗaukaka kuma da ni'ima dauwamamma: suna salla kamar yadda muke yin salla, kuma suna azumi kamar yadda muke***

***azumi, kuma suna da sauran dukiya da suke hajji da ita kuma suna yin umra da ita, kuma suna jihadi kuma suna sadaka. Sai ya ce: "Ko in sanar da ku wani abu da za ku riski waɗanda suka tsere muku, kuma ku tsere wa waɗanda ke bayanku, kuma babu wani da zai kasance mafifici a gare ku face wanda ya aikata kwatankwaci abin da kuka aikata? Sai suka ce: E, ya Manzon Allah! Sai ya ce: "Ku tsarkake (Allah) kuma ku yi yabo, kuma ku yi kabbara bayan kowace salla talatin da uku uku."***

Ya zo har wa yau a cikin Muslimu daga Abu'huraira yardar Allah ta tabbata a gare shi daga Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, lalle, shi ya ce:

**(من سبح دبر كل صلاة ثلاثا وثلاثين وحمد الله ثلاثا وثلاثين وكبر الله ثلاثا وثلاثين وقال تمام المائة لا إله إلا الله وحده لا شريك له له الملك وله الحمد وهو على كل شيء قدير غفرت خطاياه وإن كانت مثل زبد البحر)**

***"Wanda ya tsarkake Allah bayan kowace salla talatin da uku kuma ya yi yabo talatin da uku, kuma ya girmama Allah talatin da uku, sa'annan ya kammala ɗari da Babu abin bautawa da gaskiya face Allah, shi kaɗai, babu abokin tarayya a gare shi, dukkan mulki da dukkan yabo nasa ne, kuma shi mai iko ne bisa komai, to, an gafarta kurakuransa, ko da sun kasance kwatankwacin kumfar teku."***

Har wa yau ya zo a cikin Buhari da Muslimu daga Abubakar Sadiƙ yardar Allah ta tabbata a gare shi daga Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi. (Abubakar ya ce):

**(علمني دعاء أدعو به في صلاتي (فقال اللهم إني ظلمت نفسي ظلما كثيرا ولا يغفر الذنوب إلا أنت فاغفرلي مغفرة من عندك وارحمني إنك أنت الغفور الر حيم)**

***"Ka sanar da ni du'a'i da zan riƙa addu'a da shi a cikin sallata" Sai Manzon Allah ya ce: Ka ce: Ya Allah! Lalle ni na zalunci kai na zalunci mai yawa, kuma babu mai yafe zunubi sai kai, don haka kayi min gafara da wata gafara daga gare ka, kuma kayi min rahama, lalle kai mai gafara ne, kuma mai jin-ƙai."***

Ma'ana: Ya Allah! Haƙiƙa, ni, na zalunci kaina, zalunci mai yawa, kuma babu mai gafarta zunubai face Kai. To, Ka yi gafara a gare ni, gafara

daga wajen Ka, kuma Ka yi rahama a gare ni, lalle Kai, Mai yawan gafara ne, Mai yawan jin-ƙai.

Yana kamata a yawaita daga wannan du'a'i a kowane lokaci amma a bayan ƙare salloli ya fi ƙarfafa.

## ZIKIRI BAYAN KARE ALWALA KUMA DA YADDA AKE KARBA WA MAI KIRAN SALLA

Ya zo a cikin Muslimu, Umar ɗan Haɗɗabi yardar Allah ta tabbata a gare shi ya ce Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(من توضأ فقال أشهد أن لا إله إلا الله وحده لا شريك له وأشهد أن محمدا عبده وسوله فتحت له أبواب الجنة الثمانية يدخل من أيها شاء)

***"Wanda ya yi alwala, sa'annan ya faɗi: Ina shaida cewa babu abin bautawa da gaskiya face Allah shi kaɗai baya da abokin tarayya kuma ina shaida wa lalle Annabi Muhammad bawan sane kuma manzon sane, to, an buɗe ƙofofin Aljanna takwas a gare shi ya shiga ga kowace ya so."***

Ya zo har wa yau a cikin Muslimu daga Sa'ad ɗan Abu Waƙƙas yardar Allah ta tabbata a gare shi daga Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(من قال حين يسمع المؤذن أشهد أن لا إله إلا الله وحده لا شريك له وأشهد أن محمدا عبده وسوله رضيت بالله ربا وبالإسلام دينا وبمحمد –صلى الله عليه وسلم– رسولا وبالقرآن دليلا غفر له ذنبه)

***"Wanda ya faɗa a lokacin da ya ji mai kiran salla: Na shaida babu abin bautawa sai Allah shi kaɗai bashida abokin tarayya, kuna na shaida Muhammadu Bawansane kuma manzonSa ne Na yarda da Allah Ubangiji kuma da Addinina kuma da Muhammadu Manzo da kuma Alƙur'ani dalili, to, an gafarta zunubansa."***

Ma'ana: Ina shaida ba abin bautawa da gaskiya sai Allah Shi kaɗai ba abokin tarewa a gare Shi, kuma ina shaida cewa Muhammadu bawanSa ne kuma ManzonSa. Na yarda da Allah Shi ne Ubangiji kuma Musulunci shi ne

addini, kuma da Muhammad tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, shi ne Manzo kuma Alƙur'ani shi ne jagora.

Ya zo a cikin Buhari daga Jabir ɗan Abdullahi yardar Allah ta tabbata a gare shi cewa, Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(من قال حين يسمع النداء اللهم رب هذه الدعوة التامة والصلاة القائمة آت محمدا الوسيلة والفضيلة والدرجة الرفيعة وابعثه مقاما محمودا الذي وعدته حلت له شفاعتي يوم القيامة)

***"Wanda ya faɗa a lokacin da ya ji kiran salla: Ya Allah Ubangijin wannan kira cikakke da wannan Sallah tsayayya Kabawa Muhammadu Wasila da Fidhila, da daraja maɗaukakiya kuma ka tadashi akan matsayi abin godiya wanda kai masa alƙawari, to, cetona ya wajaba a gare shi a ranar Alƙiyama."***

Ma'ana: Ya Allah! Kai ne Ubangijin wannan kira cikakke, kuma da salla wadda ake tsayarwa, Ka bai wa Muhammad tsani da matsayi da daraja maɗaukakiya, kuma Ka tayar da shi matsayi abin godiya, wannan da Ka yi masa alƙawari.

A cikin Muslimu akwai abin da ke nuna zai faɗi zikirin da ya gabata bayan ƙare karɓa kiran salla ga abin da bayaninsa zai zo.

Ya zo a cikin Muslimu daga Umar yardar Allah ta tabbata a gare shi ya ce Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(إذا قال المؤذن الله أكبر الله أكبر فقال أحدكم الله أكبر الله أكبر ثم قال أشهد أن لا إله إلا الله فال أشهد أن لا إله إلا الله ثم قال أشهد أن محمدا رسول الله قال أشهد أن محمدا رسول الله ثم قال حى على الصلاة فقال لا حول ولا قوة إلا بالله ثم قال حى على الفلاح فقال لا حول ولا قوة إلا بالله ثم قال الله أكبر الله أكبر فقال الله أكبر الله أكبر فقال لا إله إلا الله ثم قال لا إله إلا الله خالصا من قلبه دخل الجنة)

***"Idan mai kiran salla ya ce: Allahu Akbar Allahu Akbar, to, sai ɗayanku ya ce, Allahu Akbar Allahu Akbar; sa'annan idan ya ce; Ash'hadu Alla Ila'ha Illallah, Sai Ya Ce Ash'hadu Alla Ila'ha Illallah; sa'annan idan ya ce***

***Ash'hadu Anna Muhammadar Rasulullah Sai Ya Ce Ash'hadu Anna Muhammadar Rasulullah Idan Ya Ce Hayya Alas-Salah Sai Ya Ce La Haula Wa La Kuwwata Illa Billah; Idan Ya Ce, Hayya Alal Falah Sai Ya Ce La Haula Wa La Kuwwata Illa Billah; Sa'annan Idan Ya Ce Allahu Akbar Allahu Akbar, Sai Shi Kuma Ya Ce Allahu Akbar Allahu Akbar; Idan Ya Ce, La Ila'ha Illallah Sai Ya Ce La Ilaha Illallah; Idan Ya Faɗi Haka, Yana Mai Ihlasi Ga Zuciya Tasa, Zai Shiga Aljanna."***

Ya zo a cikin Muslimu daga Abdullahi ɗan Amru ɗan Asi! Yardar Allah ta tabbata a gare shi cewa, shi ya ji Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi yana cewa:

(من صلى على مرة صلى الله بها عشرا)

***"Wanda ya yi salati sau ɗaya a gare ni Allah zai yi salati goma a gare shi."***

Yana kamata mutum ya yawaita salati a gare shi musamman a lokacin ƙare kiran salla; amma a ranar Juma'a salatin ya fi yawa.

## ZIKIRI A WAJEN KWANCIYA

Ya zo a cikin Buhari da Muslimu daga Aliyu, Allah ya girmama fuskarsa cewa, Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya ce a gare shi da kuma Faɗima yardar Allah ta tabbata a gare su:

(إذا آويتما إلى فراشكما وأخذتما مضاجعكما فكبرا ثلاثا وثلاثين وسبحا ثلاثا وثلاثين واحمد ثلاثا وثلاثين)

***"Idan kuka zo ga shimfiɗarku, kuma kuka riƙi wurin kwanciyarku, to, ku yi kabbara (Allahu Akbar) sau talatin da uku; ku tsarkake (Subha'nallahi) sau talatin da uku; kuma ku yi godiya (Alhamdu Lillahi) sau talatin da uku."***

Har wa yau ya zo a cikin Buhari da Muslimu daga Abu Mas'udu Al-Ansari Allah ya ƙara masa yarda ya ce Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(آيتان من آخر سورة البقرة من قرأهما في ليلة كفتاه)

***"Ayoyi biyu daga ƙarshen surar Baƙara wanda ya karanta su a cikin dare sun ishe shi."***

Watau sun isar masa daga tsayuwar dare·

Ya zo a cikin Buhari daga Ubada ɗan Sa'miti Allah ya ƙara masa yarda daga Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(من تعار من الليل يعني من استيقظ فقال لا إله إلا الله وحده لا شريك له له الملك وله الحمد وهو على كل شي قدير والحمدلله وسبحان الله ولاإله إلا الله والله أكبر ولا حول ولا قوة إلا بالله العلى العظيم اللهم اغفرلى أو دعا استجيب له فإن توضأ ثم صلى قبلت صلاته)

***"Wanda ya farka a cikin dare sai kuma ya faɗi: Babu abin bautawa da gaskiya sai allah shi kaɗai bashi da abokin tarayya gareshi Mulki da yabo suke kuma shi mai ikone akan dukkan komi, kuma tsarki ya tabbaa ga Allah babu abin bauta sai Allah kuma Allah mai Girma ne babu ƙarfi babu dabara saiga Allah maɗaukaki mai girma. Idan ya roƙi, Allah gafara, ko ya yi wani roƙo za a karɓa masa, kuma idan ya yi alwala sa'annan ya yi salla za a karɓa sallarsa."***

Ya zo a cikin Buhari da Muslimu daga Abu Katada yardar Allah ta tabbata a gare shi ya ce Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

( الرؤيا الحسنة من الله والحلم من الشيطان فمن رأى شيئا يكرهه فليتفل ثلاثا عن يساره فليتعوذ بالله من الشيطان الرجيم فإنها لا تضره)

***"Mafarki mai kyau daga Allah ne, shi kuwa mugun mafarki daga Shaiɗan yake. Wanda ya ga wani abu da yake ƙi, to, ya yi tofi sau uku a hagunsa, sa'annan ya roƙi Allah tsari daga shaiɗan abin la'anta, to, wannan mafarki ba ya cuta masa."***

## ZIKIRI GA WANDA KE A CIKIN DAMUWA

Ya zo a cikin Buhari da Muslimu daga Ibnu Abbas yardar Allah ta tabbata a gare su cewa, Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya kasance yana faɗa a lokacin da damuwa ta same shi:

لا إله إلا الله العظيم الحليم لا إله إلا الله رب العرش العظيم لا إله إلا الله رب السموات ورب الأرض ورب العرش الكريم)

*"Ba abin bautawa da gaskiya face Allah Mai girma, Mai haƙuri; ba abin bautawa da gaskiya face Allah Ubangijin Al'arshi Mai girma; ba abin bautawa da gaskiya face Allah, Ubangijin sammai kuma Ubangijin ƙasa, kuma Ubangijin Al'arshi Mai girma."*

Ya zo a cikin Buhari da Muslimu daga Anas yardar Allah ta tabbata a gare shi, ya ce: "Mafi yawan du'a'in Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya kasance:

(اللهم ربنا آتنا في الدنيا حسنة وفي الآخرة حسنة وقنا عذاب النار)

*"Ya Allah! Ya Ubangijinmu! Ka ba mu mai kyau a cikin duniya da mai kyau a cikin lahira, kuma Ka tsare mana azabar wuta."*

Yana kamata a yawaita daga waɗannan zikirori biyu a kowane lokaci kuma da a kowace halayya.

## ZIKIRI A LOKACIN SHIGA GIDA KUMA DA LOKACIN CIN ABINCI

Ya zo a cikin Muslimu daga Jabir yardar Allah ta tabbata a gare shi ya ce na ji Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi yana cewa:

(إذا دخل الرجل بيته فذكر الله عند دخوله وعند طعامه قال الشيطان يعني لأصحابه لا مبيت لكم ولا عشاء وإذا دخل ولم يذكر الله عند دخوله قال الشيطان لأصحابه أدركتم المبيت وإن لم يذكر الله عند مطعمه قال أدركتم المبيت والعشاء)

*"Idan mutum ya shiga a gidansa kuma ya ambaci Allah a lokacin shigarsa, kuma da a lokacin cin abincinsa sai shaiɗan ya ce ga abokansa: Ba ku da wurin kwana kuma ba ku da abinci. Amma idan ya shiga bai ambaci Allah ba a lokacin shigarsa sai Shaiɗan ya ce ga abokansa, kun riski wurin kwana. Kuma idan bai ambaci Allah ba a lokacin cin abincinsa sai Shaiɗan ya ce: Kun sami wurin kwana kuma kun sami abinci."*

Ya zo a cikin Muslimu daga Anas yardar Allah ta tabbata a gare shi ya ce, Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(إن الله ليرضى عن العبد أن يأكل الأكلة فيحمده عليها ويشرب الشربة فيحمده عليها)

***"Lalle Allah yana yarda ga bawa da ya ci abinci kuma ya gode maSa a kan haka."***

Yana kamata ga kowane mutum da ya ambaci Allah kuma ya yawaita ambatonSa a lokacin shigarsa gida kuma da lokacin fitarsa daga gare shi; haka kuma da lokacin cin abincinsa kuma da shan abin shansa; haka dai da dukan kai da komonsa. Haka kuma ya yawaita godiyar Allah a wajen cin abinci da shan abin sha a bisa ga kowace irin halayya.

Ya zo a cikin Buhari daga Abu'Umama yardar Allah ta tabbata a gare shi cewa, Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya kasance idan aka ɗauke akushin abincinsa, a wata ruwaya idan ya ƙare daga abincinsa yakan ce:

(الحمد لله حمدا كيثرا طيبا مباركا فيه غير مكفي ولا مودع ولا مستغنى عنه ربنا)

***"Godiya ta tabbata ga Allah godiya mai yawa, godiya tsarkakakka abin sanya wa albarka, Allah shi ne Maga'isa ba Ya da maga'isa, kuma Shi wanda ake da buƙata ne zuwa gare Shi, kuma ba a wadatuwa da Shi, ya Ubangijinmu!"***

ZIKIRI DOMIN SAMUN SHIGA ALJANNA

Ya zo a cikin Buhari da Muslimu daga Ubada ɗan Samitu yardar Allah ta tabbata a gare shi cewa, Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(من شهد أن لا إله إلا الله وحده لا شريك له وأن محمدا عبده وسوله وأن عيسى عبدالله ورسوله وكلمته ألقاها إلى مريم وروح منه والجنة حق والنار حق أدخله الله الجنة على ما كان منه من العمل)

***"Wanda ya shaida cewa: Babu abin bautawa sai Allah shi kaɗai bashida abokin tarayyakuma Muhammadu bawansane kuma manzonSa ne Kuma Isah BawanSane kuma manzonSa ne kuma kalmarsa yajefa zuwa ga Maryam dakuma Ruhi amintacce kuma Aljanna Gaskiyace kuma Wuta gaskiyace, to, Allah zai shigar da shi Aljanna a bisa ga abin da ya kasance na daga aiki."***

A wata ruwaya ta Muslimu cewa aka yi wanda ya ce:

(أشهد أن لا إله إلا الله)

***"Ina shaidawa babu abin da gaskiya face Allah."*** Har zuwa ƙarshe.

Ma'ana: Ina shaida ba abin bautawa da gaskiya face Allah Shi kaɗai, ba abokin tarewa a gare Shi, kuma cewa Muhammadu bawanSa ne kuma ManzonSa, kuma lalle Isa bawan Allah ne, kuma ManzonSa ne, kuma kalimarSa ce da Ya jefa ta zuwa ga Maryamu kuma ruhi ne daga gare Shi. Kuma Aljanna gaskiya ce, kuma Wuta gaskiya ce.

## ZIKIRI DOMIN KARIYA DAGA SHAIƊAN

Ya zo a cikin Muslimu daga Sahlu ɗan Abu Salihi (Ya ce): Babana ya aike ni zuwa (Unguwar) Bani Harisa kuma tare da ni akwai wani bawa namu sai wani mai kira ya kira shi da sunansa daga cikin wata gona, sai wannan bawa wanda ke tare da ni ya juya zuwa ga gonar, sai kuma bai ga kome ba. To, sai na ambata wa babana wannan al'amari, sai ya ce, da na san za ka haɗu da irin wannan, to, da ban aike ka ba. Amma (daga yanzu) idan ka ji sauti (irin haka) to, sai ka kira salla; saboda na ji Abu'huraira yana labartawa cewa, Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(إذا نودي للصلاة أدبر )

***"Idan aka kira salla Shaiɗan yana juyawa ya ba da baya."***

Yana kamata ga wanda ya ji wani motsi na Shaiɗan ko fatalwa ko aljani da ya kira salla haka kuma ya karanta Ayatul Kursiyyi.

Ya zo a cikin Buhari daga Abu'huraira yardar Allah ta tabbata a gare shi ya ce:

**وكلني رسول الله –صلى الله عليه وسلم– بحفظ زكاة رمضان فأتاني آت فجعل يحثو من الطعام فأخذته وقلت له لأرفعنك إلى رسول الله –صلى الله عليه وسلم– فقال إني محتاج ولي عيال ولي حاجة شديدة فخليت عنه فأصبحت فقال النبي –صلى الله عليه وسلم– (ما فعل أسيرك البارحة) قلت يا رسول الله شكى حاجة شديدة وعيالا فرحمته**

**وخليت سبيله قال (أما إنه قد كذبك وسيعود) فعرفت أنه سيعود لقول النبي –صلى الله عليه وسلم– إنه سيعود فرصدته فجاء يحثو من الطعام فأخذته فقلت له لأرفعنك إلى رسول الله –صلى الله عليه وسلم– فقال دعني فإني محتاج ولي عيال لا أعود فرحمته فخليت سبيله فأصبحت فقال لي رسول الله–صلى الله عليه وسلم– ما فعل أسيرك البارحة قلت يا رسول الله شكا حاجة شديدة وعيالا فرحمته فقال أما أنه كذبك وسيعود فرصدته الثالثة فجعل يحثوا من الطعام فأخذته فقلت له لأرفعنك إلى رسول الله –صلى الله عليه وسلم– هذا آخر ثلاث مرات تزعم أنك لا تعود فقال دعني أعلمك كلمات ينفعك الله بها فقلت ما هى قال إذا أويت إلى فراشك فاقرآ آية الكرسي ﴿ ٱللَّهُ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ٱلۡحَيُّ ٱلۡقَيُّومُ ﴾البقرة: ٢٥٥ حتى تختم آية فإنك لن يزال عنك من الله حافظ ولا يقربك شيطان حتى تصبح فقال رسول الله –صلى الله عليه وسلم– (أما أنه قد صدقك وهو كذوب هل تعلم من تخاطب منذ ثلاث ليال يا أبا هريرة) قلت لا قال (ذلك الشيطان) موضع دليل قوله –صلى الله عليه وسلم– أما أنه قد صدقك)**

***"Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya wakilta ni da in tsare zakkar fidda kai, to, sai wani mai zowa ya zo a wajena, sai ya shiga yana kwasar abinci sai na kama shi, sai na ce masa, lalle sai na kai ka a wajen Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, sai ya ce ni, mabuƙaci, ne kuma akwai iyali a gare ni kuma ga matsananciyar buƙata! A dalilin haka sai na rabu da shi. Da na wayi gari sai Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: "Yaya al'amarin wanda ka kama a jiya?" Sai na ce ya Manzon Allah! Ya yi koken buƙata mai tsanani kuma da iyali sai na yi tausayi a gare shi kuma na rabu da shi. Sai ya ce: "Saurara, lalle ya yi maka ƙarya kuma zai dawo." Daga nan na san zai dawo saboda faɗar Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi na cewa zai dawo. Sai na yi dakonsa, kuma sai ga shi ya zo yana ɗibar abinci sai na kama shi na riƙe; sai na ce masa lalle sai na kai ka a wajen Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, sai ya ce; ka rabu da ni domin ni, mabuƙaci, ne kuma ina da iyali, kuma ba zan dawo ba; a dalilin haka sai na tausaya masa na rabu da shi. Sai na wayi gari sai Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: "Yaya al'amarin wanda ka kama a jiya? "Sai na ce***

***ya Manzon Allah! Ya kai koken buƙata mai tsanani kuma da iyali; a dalilin haka na rabu da shi. Sai ya ce: "Saurara, lalle, ya yi maka ƙarya kuma zai dawo. Sai na san lalle zai dawo. To, sai na yi saurarensa a karo na uku. Ana haka sai ga shi ya sake dawowa yana mai ɗibar abinci, to, sai na riƙe shi sai na ce masa lalle sai na je da kai zuwa ga Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi. Wannan shi ne ƙarshen karo na uku kana riya cewa ba za ka dawo ba amma kuma sai ka dawo. Sai ya ce min, bari in sanar da kai wadansu kalimomi da Allah zai amfane ka da su. Sai na ce masa: Mene ne kalimomin? Sai ya ce: Idan ka zo ga shimfiɗarka za ka kwanta, to, ka karanci Ayatul Kursiyyi har zuwa ƙarshen aya. Lalle, kai mai tsaro ba zai gushe ba a gare ka daga Allah; kuma Shaidan ba zai kusance ka ba har ka wayi gari. Sai Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: "Saurara, lalle ya faɗa maka gaskiya, amma kuma shi, maƙaryaci, ne. Shin ko ka san da waye kake magana a tsawon kwanaki uku ya kai Abu'huraira? Sai na ce: a'a. Sai ya ce: "Wancan Shaidan ne." Wurin da hujja take shi ne zancensa tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi. "Saurara, ya faɗa maka gaskiya."***

Kwantankwacin wannan hadisi shi ne ruwayar Tirmizi Jin-ƙayin Allah ya tabbata a gare shi a cikin littafinsa, Al-Jami'u, daga Abu Ayyuba yardar Allah ta tabbata a gare shi a inda ya ambaci wannan da fatalwa.

Ya zo a cikin Muslimu daga Haula 'yar Hakimu yardar Allah ta tabbata a gare su ta ce na ji Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi yana cewa:

(من نزل منزلا ثم قال أعوذ بكلمات الله التامات من شر ما خلق لم يضره شيء حتى يرتحل من منزله ذلك)

***"Wanda ya sauka a wani wurin sauka, sa'annan ya faɗi: Ina roƙon tsari da kalimomin Allah cikakku daga sharrin abin da Ya halitta, to, babu wani abu da zai cuta masa har ya ɗaga daga wannan wurin."***

Yana kamata da mutum ya karanta wannan a lokacin saukarsa ga kowane mazauni, kuma da a wajen barcinsa; haka kuma da a kowane muhalli, kuma ya kwankoma shi sau uku.

Ya zo a cikin Buhari da Muslimu daga Abu'huraira yardar Allah ta tabbata a gare shi daga Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(قال يعقد الشيطان على قافية رأس أحدكم إذا هو نام ثلاث عقد يضرب على كل عقدة مكانها عليك ليل طويل فارقد قال فإن استيقظ وذكر الله انحلت عقدة فإن توضأ إنحلت عقدة فإن صلى ركعتين انحلت العقد كلها فيصبح نشيطا طيب النفس وإلا أصبح خبيث النفس كسلانا)

***"Shaiɗan yana ƙulli uku a bisa ga ƙeyar kai na kowane ɗaya daga cikinku idan ya yi barci, kuma yana sanyawa ga kowane ƙulli cewa: "yi ta yin barci domin akwai dare mai tsawo a gare ka." Ya ce: Idan mutum ya farka kuma ya ambaci Allah, to, sai ƙulli ɗaya ya warware; idan kuma ya yi alwala sai ƙulli na biyu ya warware; idan kuma ya yi salla raka'a biyu sai dukan ƙullin uku su warware; daga nan sai ya wayi gari yana mai nishaɗi kuma yana mai daɗin rai; amma idan ba haka ba, to, zai wayi gari yana mai munin rai kuma yana mai kasala."***

## SA'AR DA AKE KARBA ADDU'A A CIKIN DARE

Ya zo a cikin Muslimu daga Abu'huraira yardar Allah ta tabbata a gare shi ya ce, Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(ينزل الله –عز وجل –إلى السماء الدنيا في كل ليلة حين يمضي ثلث الليل الأول فيقول أنا الملك من الذي يدعوني فاستجيب له من الذي يسألني فأعطيه من الذي يستغفرني فاغفرله فلا يزال كذلك حت يضيء القجر)

***"Allah Mai girma da buwaya Yana sauka a sama ta duniya a kowane dare a lokacin da sulusin dare na farko ya shuɗe yana cewa: "Ni ne Mai mallaka! Wane ne ke kiraNa in karɓa masa; kuma wane ne ke roƙoNa in ba shi; kuma wane ne ke neman gafara a gare Ni in gafarta masa." Ba zai gushe ba a haka har alfijir ya haskaka."***

Ya zo a cikin Muslimu har wa yau daga Jabir yardar Allah ta tabbata a gare shi ya ce na ji Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi yana cewa:

(أن في الليل ساعة لا يوافقها رجل مسلم يسأل الله خيرا من أمر الدنيا وأمر الآخرة إلا أعطاه الله إياه وذلك كل ليلة)

***"Lalle a cikin dare akwai wata sa'a wacce babu wani mutum Musulmi da zai dace da ita yana roƙon Allah alheri na daga al'amarin duniya da na lahira face Allah ya ba shi wannan abu; kuma wannan a kowane dare."***

## NEMAN TSARI KUMA DA YIN TOFI A LOKACIN KWANCIYA

Ya zo a cikin Buhari da Muslimu daga Aisha yardar Allah ta tabbata a gare ta, ta ce:

(كان إذا أخذ مضجعه نفث في يديه وقرأ بالمعوذتين ومسح بهما جسده)

***"Lalle Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya kasance, idan ya zo a wajen kwanciyarsa, yakan yi tofi a hannuwansa kuma ya karanta Kula'uzai biyu, kuma ya shafi jikinsa da hannayensa.***

A wata ruwaya har wa yau daga gare su, Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, idan ya zo kwanciya ga shimfiɗarsa a kowane dare yana haɗa tafunan hannuwansa, sa'annan ya yi tofi a cikinsu, sai ya karanta Surar Kulhuwallahu Ahad da Kul'a'uzu birabbil Falaƙ da Kul'a'uzu birabbin Nas kowace har ƙarshenta; sa'annan ya shafi jikinsa da hannuwansa gwargwadon abin da ya sami iko, yana mai farawa da kansa da fuskarsa, sa'annan gaban jikinsa. Yana aikata haka har sau uku.

Yana kamata a yi koyi da Manzon Allah a bisa dukan ayyukansa da zantukansa, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi.

Ya zo a cikin Buhari da Muslimu daga Bara'u ɗan A'zibu yardar Allah ta tabbata a gare shi ya ce Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(إذا أتيت مضجعك فتوضأ وضوءك للصلاة ثم اضطجع على شقك الأيمن وقل: اللهم إني أسلمت نفسي إليك وفوضت أمرى إليك ووجهت وجهي إليك رهبة ورغبة إليك لا منجا ولا ملجأ منك إلا إليك آمنت بكتابك الذي أنزلت وبنبيك الذي أرسلت واجعلهن آخر ما تقول فإن مت مت على الفطرة) وزاد في رواية لمسلم (فإن أصبحت أصبت خيرا)

***"Idan ka zo wajen kwanciyarka, to, ka yi alwala irin alwalarka ta salla, sa'annan ka kwanta a sashinka na dama, sa'annan ka ce: ALLAHUMMA INNI AS'LAMTU NAFSI ILAYKA WA FAWADTU AMRI' ILAYKA WA ALJA'TU ZAHRI' ILAYKA RAHBATAN WA RAGBATAN ILAYKA LA'MANJA 'WALA MALJA'A MINKA ILLA ILAYKA A'MANTU BI KITA'BIKALLAZI 'ANZALTA WA NABIYYIKALLAZI' ARSALTA, to, ka sanya su ƙarshen abin da da za ka faɗa, idan ka mutu (a wannan dare) to, ka mutu a kan halitta (ta imani)."*** Ya ƙara a cikin ruwaya ta Muslimu: ***"Kuma idan ka wayi safiya, to, ka sami alheri".***

Ma'ana: Ya Allah! Ni, na miƙa raina a gare Ka, kuma na fawalla al'amarina zuwa gare Ka, kuma na fake bayana zuwa gare Ka, ina mai jin tsoro daga gare Ka, kuma ina mai kwaɗayi a gare Ka; babu wurin tsira kuma babu mafaka daga gare Ka face zuwa gare Ka; na yi imani da littafinKa da Ka saukar, kuma da AnnabinKa da ka aiko.

## FALALAR SUNAYEN ALLAH CASA'IN DA TARA

Ya zo a cikin Buhari da Muslimu daga Abu'huraira yardar Allah ta tabbata a gare shi cewa, Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(إن لله تسعة وتسعين اسما مائة غير واحد من أحصاها دخل الجنة إنه وتر يحب الوتر)

***"Lalle Allah yana da sunaye casa'in da tara: ɗari ba ɗaya, wanda ya ƙididdige su, zai shiga Aljanna. Lalle, Shi Witiri ne, kuma yana son abin da yake witiri."***

A wata ruwaya daga gare su:

(من حفظها دخل الجنة)

***"Wanda ya haddace su zai shiga Aljanna."***

Haƙiƙa, masanin hadisi, Abu'isa Tirmizi, ya zo da su a cikin littafinsa na Al-Jami'u yana mai lissafa su a cikin hadisi wanda yake kyakkyawa.

## NAU'O'IN SADAKA

Ya zo a cikin hadisin Muslimu daga Abu'zarri yardar Allah ta tabbata a gare shi ya ce lalle waɗansu mutane daga Sahabban Manzon Allah tsira da

amincin Allah su tabbata a gare shi sun ce: Ya Manzon Allah! Ma'abuta dukiya sun tafi da lada: suna salla tamkar yadda muke salla, kuma suna azumi tamkar yadda muke yin azumi, kuma suna yin sadaka da sauran dukiyoyinsu! Sai Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(أوليس قد جعل الله لكم ما تتصدقون به إن كل تسبيحة صدقة وكل تكبيرة صدقة وأمر بالمعروف صدقة ونهى عن المنكر صدقة)

***"Ashe bai kasance Allah ya sanya a gare ku ba abin da kuke sadaka da shi? Lalle, ga dukan tasbihi sadaka ne, kuma ga dukan kabbara sadaka ce, kuma umarni da alheri sadaka ne, kuma hani daga abin da aka ƙi sadaka ne."***

A wata ruwaya:

(يصبح على كل سلامى من أحدكم صدقة بكل تسبيح صدقة)

***"Sadaka na wajaba ga kowace gaɓa ta ɗaya daga gare ku a kowace safiya: ga kowane tasbihi sadaka."***

Har zuwa ƙarshen hadisi. Sa'annan ya ce:

(ويجزء من ذلك ركعتان يركعهما من الضحى)

***"Yana isa daga wannan raka'o'i biyu da yake sallatarsu a lokacin hantsi."***

Har wa yau ya zo a cikin Muslimu daga A'isha yardar Allah ta tabbata a gare ta ta ce, Lalle, Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(قال خلق كل إنسان من بني آدم على ستين وثلاث مائة مفصل فمن كبر الله وحمد الله وهلل الله وسبح الله واستغفر الله وأزال حجرا عن طريق مسلم أو شوكة أو عظما عن طريق الناس وأمر بالمعروف أو نهى عن المنكر عدد تلك الستين وثلاث مائة سلامى فإنه يمسي يومئذ قد زحزح نفسه عن النار)

***"An halicci kowane mutum daga 'yan'adam a bisa gaɓoɓi ɗari uku da sittin. Wanda ya yi kabbara kuma ya faɗi Alhamdu Lillahi kuma ya yi hailala, kuma ya yi tasbihi, kuma ya yi istigfari, kuma ya nisantar da dutsi daga***

*hanyar Musulmi ko wata ƙaya ko ƙashi daga hanyar mutane, kuma ya yi umarni da alheri ko ya yi hani daga abin da aka ƙi adadin ɗari uku da sittin na gaɓoɓi, to, zai yi marece a wannan rana, lalle yana mai nisanta kansa daga wuta."*

## FALALAR KARATUN ALƘUR'ANI DA FALALAR WAƊANSU SURORI

Ya zo a cikin Buhari da Muslimu daga Abu'Umama Al-Bahili yardar Allah ta tabbata a gare shi ya ce na ji Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi yana cewa:

(اقرءوا القرآن فإنه يأتي يوم القيامة شفيعا لأصحابه اقرءوا الزهراوين البقرة وآل عمران فإنهما يأتيان يوم القيامة كأنهما غمامتان أو كأنهما غيايتان أو كأنهما فرقتان من الطير صواف تحاجان عن أصحابهما يوم القيامة اقرءوا سورة البقرة فإن أخذها بركة وتركها حسرة ولن يستطيعها البطلة)

*"Ku karanta Alƙur'ani, lalle ne, shi zai zo ranar Alƙiyama yana mai ceto ga ma'abuta karatunsa. Ku karanta masu haske biyu: Surar Baƙara da Surar Ali Imrana. Lalle ne, su (biyu) za su zo a ranar Alƙiyama suna tamkar girgije biyu, ko tamkar inuwa biyu, ko kuma ka ce, su wata ƙungiya ce biyu ta tsuntsaye masu miƙa fukafukansu a sama. Za su zo suna masu kariya ga masu karatunsu a ranar Alƙiyama. Ku karanci surar Baƙara, lalle riƙonta albarka ne, kuma barinta nadama ne kuma ma'abuta sihiri ba su samun iko a kanta."*

## FALALAR AZUMIN RANAR ARFA DA ASHURA KUMA DA AZUMIN KWANA UKU A KOWANE WATA

Ya zo a cikin Buhari da Muslimu daga Abu'ƙatada yardar Allah ta tabbata a gare shi cewa, Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(صيام ثلاثة من كل شهر رمضان إلى رمضان فهذه صيام الدهر كله وصوم يوم عرفة أحتسب على الله أن يكفر السنة التى قبله والسنة التى بعده وصيام عاشوراء أحتسبه على الله أن يكفر السنة التى قبله)

*"Azumin ranaku uku a kowane wata daga Ramalan zuwa wani Ramalan, to, wannan shi ne azumin zamani dukansa. Kuma azumin ranar Arfa ina fata ga Allah da ya karkare (zunubin) shekarar da ta gabata da wadda za ta biyo bayanta. Kuma azumin ranar Ashura ina fata ga Allah da ya karkare (zunubin) shekarar da ta gabata."*

## FALALAR SADAKA KUMA DA FALALAR SAUKAKE WA MATSATTSE

Ya zo a cikin Buhari da Muslimu daga Abu'huraira yardar Allah ta tabbata a gare shi ya ce, Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(ومن تصدق بعدل تمرة من كسب طيب ولا يقبل الله إلا الطيب فإن الله يتقبلها بيمينه ثم يربيها لصاحبها كما يربي أحدكم فلوه حتى تكون مثل الجبل)

*"Wanda ya yi sadaka ko da da kwantakwacin ƙwarar dabino daga abin da ya samu wanda yake mai tsarki, domin Allah ba ya karɓa sai abu mai tsarki, to, lalle, Allah zai karɓi sadakar da damarSa, sa'annan Ya yaɗa ta ga mai ita tamkar yadda ɗayanku ke renon dukushin dokinsa, wannan har sai sadakar ta kasance tamkar dutsi."*

Ya zo a cikin Muslimu daga Abu'huraira yardar Allah ta tabbata a gare shi ya ce Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(من نفس عن مؤمن كربة من كرب الدنيا نفس الله عنه كربة من كرب يوم القيامة ومن يسر على معسر يسر الله له في الدينا والآخرة ومن ستر مسلما ستره الله في الدنيا والآخرة والله في عون العبد ما كان العبد في عون أخيه ومن سلك طريقا يلتمس فيه علما سهل الله له به طريقا إلى الجنة وماا جتمع قوم في بيت من بيوت الله يتلون كتاب الله ويتدارسونه بينهم إلا نزلت عليهم السكينة وغشيتهم الرحمة وحفتهم الملائكة وذكرهم الله فيمن عنده ومن بطأ به عمله لم يسرع نسبه)

*"Wanda ya yaye wa mumini baƙin ciki daga baƙƙan ciki na duniya, to, Allah zai yaye a gare shi baƙin ciki na daga baƙƙan cikin ranar Alƙiyama. Kuma wanda ya sauƙaƙe a bisa ga wanda yake matsattse, to, Allah zai sauƙaƙe*

***masa a duniya da lahira. Kuma wanda ya suturce Musulmi, to, Allah zai suturce shi a duniya da lahira. Kuma Allah yana a cikin taimakon bawa, matsawar bawa yana a cikin taimakon ɗan'uwansa. Kuma wanda ya bi wata hanya yana neman ilimi a cikinta, to, Allah zai sauƙaƙe a gare shi hanya ta zuwa Aljanna. Kuma da ɗai jama'a ba su taru ba a wani gida daga gidajen Allah, suna karatun littafin Allah, kuma suna darasinsa a tsakaninsu face natsuwa ta sauka a kansu, kuma rahama ta lulluɓe su, kuma mala'iku sun kewaye su, kuma Allah Ya ambace su a cikin waɗanda ke wajenSa. Kuma wanda aikinsa ya jinkirtar da shi, to, nasabarsa ba za ta gaggautar da shi ba."***

Ka lura da wannan hadisi, me ya kai yawan fa'idojinsa!

Ya zo a cikin Muslimu daga Abdullahi ɗan Umar yardar Allah ta tabbata a gare su ya ce Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(أربعون خصلة أعلاهن منيحة العنز ما من عامل يفعل بخصلة منها رجاء ثوابها وتصديق موعودها إلا أدخله الله الجنة )

***"Halayya arba'in, mafi ɗaukakarsu ita ce, ba da aron akuya domin shan nononta, to, babu wani mai aiki da zai yi aiki da wata halayya daga cikinsu yana mai fatar ladanta, kuma yana mai gaskata abin da aka alƙawarta a kanta (na lada) face Allah ya shigar da shi Aljanna."***

Hassan ɗan Aɗiyya wanda ya ruwaito hadisin ya ce:

(فعددنا ما دون منيحة العنز من رد السلام وتشميت العاطس وإما طة الأذى عن طريق ونحوه فما استطعنا أن نبلغ خمس عشر خصلة)

***"Sai muka ƙirga abin da ke koma da bayan ba da aron akuya domin a sha nononta na daga: mayar da sallama da gayar da mai atishawa, kuma da gusar da abin da ke cutarwa daga hanya da sauran ire-irensu sai muka kasa cimma halayya goma sha biyar".***

## FALALAR ISTIGFARI

Ya zo a cikin Muslimu daga Abu'huraira yardar Allah ta tabbata a gare shi ya ce na ji Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi yana cewa:

(والله إني لأستغفرالله وأتوب إليه في اليوم والليلة أكثر من سبعين مرة)

***"Wallahi, ni, ina roƙon Allah gafara, kuma ina tuba zuwa gare Shi a cikin yini da dare sama da sau saba'in."***

Ya zo a cikin Muslimu daga Agarri yardar Allah ta tabbata a gare shi ya ce Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbat a gare shi ya ce:

(أيها الناس توبوا إلى الله فإني أتوب إلي الله في اليوم مائة مرة)

***"Ya ku mutane! Ku tuba zuwa ga Allah, lalle, ni, ina tuba zuwa gare Shi a cikin yini sau ɗari."***

FALALAR SALLA A CIKIN YINI DA DARE

Ya zo a cikin Muslimu har wa yau daga Ummu Habiba yardar Allah ta tabbata a gare ta ta ce, na ji Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi yana cewa:

(من صلى اثنتي عشر ركعة من يوم وليلة بنى الله بهن بيتا في الجنة)

***"Wanda ya yi salla raka'a goma sha biyu a cikin yini da dare, to, Allah zai gina masa da su gida a cikin Aljanna."***

A wata ruwaya daga gare shi:

(ما من عبد مسلم يصلي كل يوم اثنى عشر ركعة تطوعا من غير الفريضة إلا بني الله له بيتا في الجنة)

***"Babu wani bawa Musulmi da zai yi salla a kowane yini raka'a goma sha biyu na nafila ban da farilla face Allah ya gina gida a gare shi a cikin Aljanna."***

Ya zo a cikin Muslimu daga Harisu ɗan A'simu Al-Ash'ari yardar Allah ta tabbata a gare shi ya ce:

(الطهور شطر الإيمان والحمد لله تملأ الميزان وسبحان الله والحمد لله تملآن أو تملأ ما بين السماء والأرض والصلاة نور والصدقه برهان والصبر ضياء والقرآن حجة لك أو عليك كل الناس يغدو فبائع نفسه فمعتقها أو موبقها)

***"Tsarki rabin imani ne, kuma Alhamdu Lillahi tana cika abin da ke tsakanin sama da ƙasa, kuma salla haske ce, sadaka kuma hujja ce, haƙuri kuma haske ne babba, Alƙur'ani kuma hujja ne a gare ka ko a kanka. Dukan mutane suna wayewar safiya, akwai mai cinikin kansa, kuma akwai mai 'yantar da kai nasa ko kuwa ya halaka kai nasa."***

Waɗannan hadisai ne guda arba'in da biyar, yana kamata ga wanda ya yi riƙo da addininsa ya kasance masani a gare su, kuma mai aiwatarwa a gare su. Domin al'amarinsu yana da girma, kuma ladansu mai yawa ne, haka kuma suna da sauƙin aiwatarwa. Waɗannan hadisai suna da inganci ga nassi nasu kuma da isnadinsu. Wanda ya yi duba a gare su dubi na gaskiya, to, zai kasance tamkar ya ji su daga shugaban talikai tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi. Allah Ya ɗaukaka shi kuma ya girmama shi. Ina mai nema ga wanda ya tsayu ga waɗannan hadisai kuma ya amfana da su da ya haɗa da ni a cikin addu'arsa kyakkyawa, addu'ar da nake fatar Allah ya amfane ni da ita a duniya da lahira.

## YI WA ƊAN'UWA MUSULMI ADDU'A A LOKACIN DA BA YA NAN

Ya zo a cikin Muslimu daga Abud-Dar'da'i yardar Allah ta tabbata a gare shi cewa, Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

(دعوة المرء المسلم لأخيه بظهر الغيب مستجابة عند رأسه ملك موكل كلما دعا لأخيه بخير قال الملك الموكل به آمين ولك بمثل ذلك)

***"Addu'ar mutum Musulmi ga ɗan'uwansa (Musulmi) a lokacin da ba ya nan karɓaɓɓa ce: Akwai mala'ika a wajen kansa da aka wakiltar a duk lokacin da ya yi addu'a ga ɗan'uwansa da alheri, sai mala'ikan da aka wakilta a gare shi ya ce: A'min, kai ma kana da kwatankwacin haka."***

## KAMMALAWA

A nan na ga ya kamata da in riskar da waɗansu hadisai guda biyu, ɗaya Muslimu ne ya ruwaito shi jin-ƙayin Allah ya tabbata a gare shi, wannan a cikin ingantaccen littafinsa. Na biyu kuwa Tirmizi ne ya ruwaito shi a cikin littafinsa, Al-Jami'u. Zan zo da su da isnadinsu domin in shiga a cikin tsarin jama'a (ta sunna) kuma domin in sami ceto da albarkarsu in Allah Maɗaukakin Sarki Ya so.

Hadisi na ɗaya shi ne wanda malaminmu masanin shari'a wanda yake salihi, masanin Alƙur'ani ya labarta muna da shi; wannan kuwa shi ne Shamsud Dini Yusuf ɗan Muhammad ɗan Ali Al-Ja'afari Allah ya saka masa da alheri. Wannan ga abin da na karanta a gare shi a shekara ta ɗari bakwai da talatin da biyu (732). Ya ce malaminmu shugaba, Muhyid Dini Abu Zakariya-Yahaya Sharafud Dini Ahmad ɗan Muhammad ɗan Abul Fadli Al-Ja'afari ya labarta muna ga abin da na karanta a gare shi shekara ta ɗari bakwai da goma sha ɗaya. Ya ce shugaba Muhyid Dini Abu Zakariya Yahya Sharafud Dini Al-Nawawi jin-ƙayin Allah da yardarSa su tabbata a gare shi ya labarta muna a karatun da na yi a gare shi. Ya ce malaminmu, Abul Baƙa'i Khalid ɗan Yusuf An-Nabulusi ya labarta muna, ya ce Abul Kasim Alhasan Ibnu Hibatullah Ibnu Mansur ya labarta muna, ya ce malamin hadisi Abul Kasim Aliyu Ibnu Ibrahim Ibnu Abbas Alhassan mai huɗuba a Dimashƙa ya labarta muna. Ya ce bawan Allah Muhammad ɗan Yahya ɗan Salwana ya labarta muna ya ce Abubakar Abdurrahman ɗan Kasim ɗan Al-Faraju Al-Hashimi ya labarta muna. Ya ce Abu'mus'hir ya labarta muna. Ya ce Sa'idu ɗan Abdu'laziz ya labarta muna daga Rabi'a ɗan Yazid daga Abu Idris Alkhu'lani daga Abuzarri yardar Allah ta tabbata a gare shi daga Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi daga Jibrilu tsira da aminci su tabbata a gare shi daga Allah alherinSa ya yawaita kuma ya ɗaukaka, lalle Shi ya ce: "Ya ku bayiNa! Lalle Ni Na haramta zalunci ga kaiNa kuma Na sanya shi abin haramtawa a tsakaninku; to, kada ku yi zalunci. Ya ku bayiNa! Dukanku ɓatattu kuke face wanda Na shiryar, to, ku nemi shiriya daga gare Ni in shiryar da ku.

Ya ku bayiNa! Dukanku mayunwata kuke face wanda Na ciyar, to, Ku nemi ciyarwa daga gareNi in ciyar da ku. Ya ku bayiNa! Dukanku tsirara kuke face wanda Na tufayar, to, ku nemi tufayarwa daga gareNi in tufayar da ku.

Ya ku bayiNa! Lalle ne, ku, kuna kurakurai a cikin dare da yini, kuma Ni Mai gafarta zunubai ne gaba ɗaya, to, ku nemi gafara daga gare Ni In gafarta muku. Ya ku bayiNa! Lalle, ku, ba ku isa ku cutar da Ni ba ballantana ku cuta Min, kuma lalle, ku, ba ku isa ku amfanar da Ni ba balle ku amfane Ni. Ya ku bayiNa! Da a ce farkonku da ƙarshenku kuma mutanenku da aljannunku sun kasance a bisa tsoron Allah na zuciyar mutum ɗaya daga gare ku, to, da wancan bai ƙara kome ba a cikin mulkiNa da wani abu. Ya ku bayiNa! Da a ce farkonku da ƙarshenku kuma mutanenku da aljannunku sun kasance a bisa fajircin zuciyar mutum ɗaya daga gare ku, to, da wannan bai rage kome a cikin mulkiNa da wani abu ba. Ya ku bayiNa! Da a ce farkonku da ƙarshenku kuma da mutanenku da aljannunku sun tsayu a wuri ɗaya, kuma suka roƙe Ni, kuma Na bai wa kowane mutum abin da ya roƙa, to, da, wannan bai rage ba daga abin da ke a wajeNa, face tamkar abin da allura ke ragewa idan aka shigar da ita Teku. Ya ku bayiNa! Lalle, su ne ayyukanku ina ƙididdige su a gare ku, sa'annan In saka muku da su, to, wanda ya samu alheri sai ya gode wa Allah, kuma wanda ya samu wanin wancan, to, kada ya zargi kowa sai kansa.

Hadisi na biyu shi ne wanda Tirmizi ya fitar da isnadi nasa wanda ya sadu da masoyin Allah Annabi Ibrahimu tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi. Domin neman albarka da wancan, shugabanni biyu masu daraja sun labarta muna. Waɗannan su ne mahaifina kuma da malami, Afifud Dini Abdulrahman ɗan Umar Al-Habashi kuma da Burhanud Dini Ibrahim ɗan Umar ɗan Aliyu Al-Malawi yardar Allah ta tabbata a gare su kuma da mafificin sakamako, sun ce malami, ɗaukakar ma'abuta hadisi Ahmad ɗan Khairi Al-Samma'hi jin-ƙayin Allah ya tabbata a gare shi ya labarta muna. Ya ce Abul-Khairi ɗan Mansur ya labarta muna, Ya ce Kuɗubud Dini Isma'il Al-Khadrami ya ba mu labari. Ya ce masanin hadisi, Aliyu ɗan Alkaramu Al-Bagdadi ya labarta muna. Ya ce Abul Fathi Maliki ɗan Abu Sahli Alharawi ya labarta muna. Ya ce Abubakar ɗan Ahmad ɗan Abdussamad Al-ƙuri ya labarta muna. Ya ce Abu Muhammad Abdul Jabbar ɗan Muhammad Aljarrahi ya labarta muna ya ce Abul Abbas Ahmad ɗan Muhammad Al-Mahbubi ya labarta muna. Ya ce shugaba masanin hadisi, Abu Isa Tirmizi Allah ya yi jin-ƙayi a gare shi ya labarta muna. Ya ce Yasaru ya labarta muna. Ya ce Abdul Wahid ɗan Ziyada ya labarta muna daga Abdurrahman ɗan Is'haƙ daga Kasimu ɗan Abdullahi daga babansa daga ɗan Mas'udu yardar Allah ta tabbata a gare shi ya ce Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: "Na haɗu da Ibrahim masoyin Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, wannan a daren da aka yi Isra'i da ni. Sai

ya ce: Ya kai Muhammad! Ka karanta wa al'ummarka sallama daga gare Ni, kuma ka ba su labarin cewa, lalle Aljanna turɓayarta mai kyau ce, kuma ruwanta masu daɗi ne, kuma akwai filaye a cikinta, kuma abin da ake dashensu da shi shi ne: Subha'nallahi Walhamdu Lillahi Wala'ila'ha Illallahu Wallahu Akbar, Wala Haula Wala Kuwwata Illa Billahil Aliyyil Azimi.

Allah ya yi salati a bisa ga shugabanmu, Muhammad da iyalan gidansa da sahabbansa, kuma Ya yi aminci, aminci mai yawa. Amin.

## BAYANIN BAKIN KALMOMI

**ILLIYINA:** Littafi ne da ya ƙunshi ayyukan alheri na mala'iku da mutane da aljannu.

**IJTIHADI:** Koƙari a wajen bayanin wata matsala ta addini da babu nassi a kanta daga malami wanda ya cika sharuɗan yinsa.

**ISNADI:** Shi ne masu ruwayar hadisi; watau wane ya ji daga wane ……..

**MURSALI:** Ga hadisi shi ne hadisin da ba a ambaci sahabin da ya ruwaito shi ba.

**MAUSU'LI:** Ga hadisi shi ne hadisin da aka ambaci waɗanda suka ruwaito shi har zuwa ga Manzo tsira da aminci su tabbata a gare shi.

**MUBA;HI:** Abin da aka halatta; watau aka ba da damar a yi ko a bari.

**MUDA'RATI:** Mu'amala da kafirai ko fasiƙai amma ba tare da wani abu da ya saɓa wa Allah ba.

**MA'ABUTA SUNNONI:** A nan ana nufin masu ruwayar hadisai: Tirmizi, Abu'dawuda, Nasa'i da Ibnu Maja.

**MUSNAD:** Hadisin da aka jingina ga mai ruwaya tasa musamman daga Sahabbai. Akwai littattafan da suka shagaltu da haka kamar Musnad na Imam Ahmad Ibn Hambal.

**MADDA:** A wajen karatun Alƙur'ani ana samunta a wajen Alif da ya da wa.

**NASSI:** Abin da aka rubuta; amma an fi rinjayar da shi ga ayoyin Alƙur'ani da hadisan Manzo.

## SHIRYAR DA ƊALIBAI

**SULUSI:** Ɗaya bisa uku

**SUDUSI:** Ɗaya bisa shida

**SIJJIN:** Littafi ne da ya tara ayyukan Shaiɗanu da Kafirai.

# تحقيق العصمة

# لجميع طبقات هذه الأمة

# TABBATAR DA KIYAYEWAR (ALLAH) GA DUKKAN MATAKAN WANNAN AL'UMMA

Na

## Shehu Usmanu Ɗanfodiyo

Mai Fassara:

Prof. Sulaiman Musa

## ABUBUWAN DA KE CIKI

Shafi

GABATARWA........................................................321

Dalilan Kiyaye Al'umma ........................................................ 321

Hukuncin Wanda Ya Ɓatar Da Al'umma Tun Daga Sahabbai.................. 322

Rashin Gamewar Ɓarna A Cikin Aƙidar Al'umma .................................. 323

Rashin Gamewar Fasadi A Cikin Ibadarsu ................................................ 325

Rashin Gamewar Fasadi Cikin Mu'amalarsu. ........................................... 327

Hukuncin Mu'amalarsu A Babin Aure ..................................................... 328

Rabe-Raben Garuruwa Da Hukuncinta Ta Hanyar Musulunci Ko Rashinsa A Babin Bauta........................................................................................ 328

Rashin Gamewar Fasadi A Cikin Mu'amalarsu A Babin Cinikayya......... 330

## GABATARWA

Ina farawa da sunan Allah, Mai yawan rahama, Mai yawan jin-ƙai. Tsira da Amincin Allah su tabbata ga shugabanmu, Annabi Muhammadu da Alayensa da Sahabansa da aminci mai yawa.

Bawa, talaka, mabuƙacin rahamar Ubangijinsa, Usmanu ɗan Muhammadu ɗan Usmanu ɗan Salihu ɗan Muhammadu wanda aka sani da Ɗanfodiyo (Allah shi kubenta shi da rahamarSa) ya ce:

Godiya ta tabbata ga Allah da Ya kiyaye Addinin Musulunci daga dukkan abin da jahilai ke faɗi kuma Ya lamunce wannan da faɗinSa:

﴿ إِنَّا نَحْنُ نَزَّلْنَا الذِّكْرَ وَإِنَّا لَهُ لَحَافِظُونَ ﴾ الحجر: ٩

*"Lalle Mu ne Muka saukar da Alƙur'ani kuma Mu ne ke kiyaye shi."* (Suratul Hijir:Aya ta 9)

Tsira da Amincin Allah su tabbata ga shugabanmu, Muhammadu, Zaki da ya kafa 'ya'yansa Zakoki a matsayinsa a kowane zamani. Haƙiƙa, ya bayyana mana wannan a cikin faɗinsa. Wanda ke ɗauke da wannan ilimi daga halifofinsa masu adalci masu kore dukkan ɓarnar waɗanda suka ɓata da ƙaryar masu ɓarna da tawilin jahilai, kuma a bisa Alayensa da Sahabbansa duka.

Bayan haka: Wannan littafi mai suna: Tahƙiƙul Ismati, (Tabbatar da kiyayewar Allah ga dukkan matakan wannan al'umma daga taruwa a kan ɓata har zuwa ranar tashin ƙiyama da nassi bayananne daga cikin hadisi. Ina faɗin wannan kuma ina roƙon Allah da dacewa (muwafaƙa).

## DALILAN KIYAYE AL'UMMA

Ka sani wannan al'umma Allah ya kiyaye ta daga haɗuwa a kan ɓata saboda faɗinsa (Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi):

(لا تجتمع أمتي على ضلالة عليكم بالسواد الأعظم)

*"Al'ummata ba za ta haɗu a kan ɓata ba; Na hore ku da bin jama'a."* (Tirmidhi ne ya ruwaito shi tare da waninsa)

Da kuma faɗin Annabi (Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi):

(من يرد الله به خيرا يفقهه في الدين إنما أنا قاسم والله يعطي ولن تزال هذه الأمة قائمة على أمر الله لا يضرهم من خالفهم حتى يأتي أمر الله)

***"Wanda Allah Ya nufe shi da alheri, Zai ganar da shi Addini. Lalle ni ne mai rabo Allah ne kuwa Mai bayarwa. Wannan al'umma ba za ta gushe ba tana tsaye a kan al'amarin Allah face Allah ya ƙaddara ba mai saɓa musu da zai cutar da su har umurnin Allah ya zo"*** (Buhari ne ya ruwaito shi a cikin littafinsa, Sahihi).

Da faɗinsa (Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi):

(لا تزال طائفة من أمتي ظاهرين على الحق قاهرين لعدوهم حتى يأتيهم أمر الله)

***Wasu jama'a daga cikin al'ummata ba za ta gushe ba suna tsayawa a bisa gaskiya face Allah ya sa sun rinjayi maƙiyansu har umurnin Allah ya zo.***

a (Alƙali Iyad ya kawo shi a cikin littafinsa na Ashafa).

## HUKUNCIN WANDA YA ƁATAR DA AL'UMMA TUN DAGA SAHABBAI

Waɗannan hadisai tawaturi ne na ma'ana. A cikinsu akwai dalilai da ke nuni da rashin riddarsu. A cikin littafi da ake kira Jami'ul Jawami: Haƙiƙa, an hana yin ridda, dukkan al'umma a cikin kowane zamani yadda ya zo a cikin littattafai, Asimaru da sharhinsa. Wannan ya nuna cewa wanda ya faɗi wata magana da za ta nuna ɓacewar al'umma a cikin wani zamani daga cikin zamuna ya kafirta.

Alƙali Iyad ya ce a cikin Ashafa yayin da yake lissafa abubuwan da ke kafirta mutum, "Haka ne ana nuni kafirta kai tsaye duk wanda ya yi Magana mai nuni ɓacewar al'umma ." Karshen magana ke nan.

Aliyu bin Hussamu Din, wanda aka fi sani da Al-Mutaƙi ya faɗa a cikin littafinsa wanda ake kira Al-Burhan fi Allamatil Mahdi Ahiri Zaman ya ce: "Ahmad bin Hajar Al-Askalani ya ce: Wanda ya kafirta Sahabbai ko ya ɓatar da al'umma ya zama kafiri." Karshen Magana ke nan.

Na ce haka ne dukkan wanda ya yi shakka game da kafircinsa (shi ma ya kafirta) yadda Ahmad bin Hajar Al-Haytami ya faɗa a cikin littafinsa na Al-Zawajir.

## RASHIN GAMEWAR ƊARNA A CIKIN AKIDAR AL'UMMA

Ya bayyana daga abin da ya gabata cewa ɓarna ba za ta game Aƙidu na al'umma ba a kowane zamani cikin zamuna. Amma rashin gamewar wannan a cikin Aƙidu na keɓaɓɓun mutane daga cikinsu wannan a bayyane yake. Amma game da Aƙidun Amawa (mafi yawan mutane) hadisin Annabi (Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi) ya ce:

(إن أكثر أهل الجنة البله وأهل عليين أولو الألباب)

***"Mafi yawan mutanen Aljanna masu wauta ne amma waɗanda suke cikin Aljannar Iliyina masu hankali ne."***

Al-Manjuri ya ce a cikin sharhin Al-Muhassal: "Haƙiƙa, wannan hadisi na nuni ga mafi yawan Musulmi saboda su masu rafkanuwa ne domin kaifin hankalinsu bai kai su ga tabbatarwa ba balle su zama cikin masu Iliyina kuma bai zarce da su daga hanya ba balle su ɓata da kafirci ko kuma bidi'a."

Sai kuma ya ce: "Kalma Al-Balhu, jam'i ne da Alif da Lam kuma siga ce da ke nuna gamewa." Karshen Magana ke nan.

Saboda haka Ahmad Zikira ya ce a cikin Mahsal Al-Maƙasidi:

***"In ka ce wannan hukunci da aka faɗa na mutane gama-gari ne kamar yadda ya faɗa. Ba ya nufi game wa dukkan mutane cikin kowane zamani ba shi ake nufi da gamewa ba."***

***"In hukuncinsa zai zama daidai ya zama wajibi a keɓanta shi da mafi rinjaya.***

***Na ce gamewa ta tabbata da sigarta, kuma ya***
***kamata a yi hukunci da siffarsa.***
***Ɗaukar dukkansa a kan fasadi, saboda hukuncin***
***Wasu mutane a kan abin da ake nufi***
***Wannan ya saɓa wa hukuncin masu hankali***
***Da abin da da nassi tabbatace ya hukunta***
***In fasadi ya bayyana shi ne abin ƙi***
***Sai a juya shi da abin da ba ƙi ba***
***da al'amura masu sauƙi ba masu wuya ba***
***Saboda yin haka na iya mayar da al'amarin ga hatsari.***
***Manjuri ya ce a cikin sharhin waɗannan baituka: in ka ce***
***"In ka ɗauka Alif da Lamu na Al-Bilhu don gamewa ne kuma ya***
***na nuni a kan mafi yawan mutanen baya. Ba za mu yarda***

*Da cewa gamewa cikin mutane ita ce gamewa ga*
*Zamuna sai ya kai ga gamewar wannan zamani mafi*
*Yawan mutane waɗanda muke magana*
*A kansu. Mun yarda cewa gamewa cikin mutane*
*Ita ce gamewa cikin zamuna amma irin ta keɓewa*
*Na fitar da mafi yawan mutanen wannan zamani*
*Saboda fasadi Aƙidojin mafi yawan daga*
*Cikinsu da rashin kyautatawarsu gare ta*
*Ko da da kwaikwayo ne balle ma bisa ga*
*Sani."*

Amsa ita ce: Magana ingantacciya ita ce gamewa cikin mutane, gamewa cikin zamuna ce yadda ya tabbata cikin Usulul Fikhihi. Lafazin ya game dukkan mutane na kowane zamani sai mai nuni ita ce ta yi nuni da a kan haka nuni na zahiri. Bai halarta akan ce masa ba sai da dalili. A lokacin bai fita daga Amawa ba sai wanda Aƙidarsa ta ɓaci. Wannan kuma cikin sashi ba ga duka ba. In an ɗauki dukkansu a kan ɓarna saboda ɓarnar wasu ba ta inganta a hankali da nassi ba. Haka ne in ɓarna ta bayyana ga ɗaya daga cikinsu, wannan abin ƙi ne. Ya wajaba a canza ta ko da ba ta bayyana ba. Asalin abu ya zama amintacce kuma mai shiga cikin hadisi

Malam Abu Mansur Al-Maturidi ya ce: Mutanenmu sun yi ittifaƙi a kan Amawa cewa su, muminai, ne kuma masana Ubangijinsu kuma suna kusa da Aljanna yadda ya zo a cikin labarai, kuma malamai suka faɗa. A cikin littafinsa, Al-Mahsal a fadinsa: Malam Abu Mansur ya cirato Ijma'in masu gaskiya cikin littattafai.

Cewa Amawa cikin Musulmi, muminai ne kuma masana ne ga Ubangijinsu. Kuma an faɗa cewa suna kusa da Aljanna; mafi yawansu wawaye ne a faɗin Malamai da Hadisi.

Shaykh Abubakar bin Ahmad bin Furika ya faɗa a cikin littafinsa da ake kira: Kitab Al-Nizam Al-Ƙawami "Ka sani cewa Amawa bisa ga abin da suke a kai game da sanin Allah Maɗaukakin Sarki dukkansu muminai ne kuma masanan Allah ne Maɗaukakin Sarki kuma suna shiga Aljanna."

Kuma ya ce bayan wannan Magana: Matsalolin da bayanai na ilimin Tauhidi tare da bayani na masu ilimi ya musanta ta kuma ya musanta cewa ya san wani abu daga ciki ko kuma ya ƙudurta shi. Wannan ba ya nuni cewa al'amarin yadda ya faɗa ne. a'a shi ya kudurta ta kuma yana sane da ita sai

dai shi yana musun Magana da aka lura da ita "Musun wannan Magana ba ya nuni, musun ma'anarta."

Mu'tazilawa sun ce: "Ba mai zama masanin Allah sai wanda ya san waɗannan mas'aloli. Yana nufin mas'aloli na bayanin ilimin Tauhidi da yadda aka gina dalilansu. Kuma ya ce: "Duk waɗannan ƙauyanci ne saboda wannan yana sa ya zama wajibi har ya zama ba wani daga cikin Amawa wanda za a yarda da Imaninsa. Wannan saɓanin abin da Malaman addini na da da na yanzu ke kai."

Mazhabarmu ita ce abin da muka faɗa cewa ya isa ga wanda ke cikin Amawa abin da muka same su a kai na al'ada da kuma abin da aka saɓa cewa su masanan Allah ne masu ilimi.

Allah Maɗaukakin Sarki ya ce:

﴿وَمَن يُؤْمِنۢ بِٱللَّهِ يَهْدِ قَلْبَهُۥ﴾ التغابن: ١١

***"Wanda ya yi imani da Allah, Zai shirya zuciyarsa"*** Suratul Tagabun Aya: 11.

Haƙiƙa, Allah ya shirya zukatansu ga saninSa (Mai Tsarki). Wannan shi ne bayani na abin da mutanen gaskiya ke imani da shi cikin wannan mas'ala. Ka san da shi "Karshen magana ke nan a taƙaice."

Abdulwahab Sha'arani ya faɗa a cikin littafinsa mai suna Al-ƙawa'id Al-kashfiyyah: Na ji shaihinmu, shaihi na Musulunci, Zakariyyah (Allah Shi rahamshe shi) yana faɗi. "Aƙidojin Amawa ingantattu ne a ijma'in dukkan mai shari'a mai hankali isasshe. "Wannan duka yana cikin bayanin cewa fasadi ba ya game Aƙidun al'umma keɓantattunsu ko Amawansu."

## RASHIN GAMEWAR FASADI A CIKIN IBADARSU

Amma bayanin rashin gamewar fasadi a cikin ibadarsu akwai ijma'in Malamai a kansa shi ma. Amma rashin gamewar wannan a cikin ibadar keɓantattunsu wannan a bayyane ne. amma a cikin ayyukan ibada na Amawansu haƙiƙa malamai sun yi bayaninta.

Abdulwahab Al-Sha'arani ya ce a cikin littafin Al-Risalatul Mubaraka ya yin da yake lissafa al'amura (na zamani) da ke kan kowane baligi mai hankali. Daga cikinsu kada ya yi gaggawa wajen inkarin imanin Amawa cikin mutane har ya soki Aƙidojin, ya ba da fatawa da ɓacin ibadarsu da

mu'amalarsu da al'amura da wasu masu ijtihadi suka faɗa da hankalinsu da ra'ayinsu ba tare da an same shi ƙarara a cikin Alƙur'ani ko hadisi ba. Muddin su dace da maganar wani Malami daga cikin Malamai na sunna ba ya yi inkari ko da sun saɓa wa wata sunna ƙarara ko sun saɓa ijma'i ba.

In ka ce: Yaya Ibadar wanda ke cikin Amawa za ta inganta alhali ba su iya rarrabe abin da yake farilla ko kuma sunna da abin da yake mustahabi a cikin ibadarsu ba?

Muhammadu ɗan Ali Al-Ufi ya ce cikin farkon littafinsa, Jami'u Al-Fara'ili: "Malamai sun ce'wanda ya yi salla kuma ya yi ta daidai yadda Allah Maɗaukakin Sarki ya yi umurni game da ruku'u da sujada da tsayawa da zama bai bar kome ba. Sai dai ya ce ina yi ne yadda na ga mutane suke yi, sallarsa ɓatacciya ce. Haka nan wanda ya yi alwala da kyau kuma ya yi wankan janaba da kyau amma bai san farilla a cikinta ba ko kuma sunna, wanka janabarsa da daudarsa suna nan a kansa, sallarsa kuma ɓatacciya ce ba a amsa ba. Kai! Shi mai laifi ne a cikin dukkan abubuwan da ya aikata. Kuma mai saɓon Allah da ManzonSa ne. Babu saɓani wajen masu ilimi a kan haka. Haka ma aikin Hajji da azumi da sauran ibada"

Na ce: Haƙiƙa, ibadarsu ingantacciya ce. Wannan maganar wasu malamai ne, kuma ba daidai ba ne da al'amari haka yake da ya zama wajibi da Manzon Allah (Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi) ya killafa wa sahabansa wannan. Amma bai yi haka ba. Batun da bai killafa musu wannan ba. Mun san cewa ingancin ibadarsu bai dogara a kansa ba. Da kuma faɗinsa: "Babu saɓani wajen masu ilimi game da wannan." Karya ce tsintsa. Saboda saɓani a kan wannan sananne a wajen Malamai. Magana da ke cewa daidai ne ita ce ta dace yadda Malam Al-Ajhuri ya bada fatawa.

Malam Ahmadu Zaruk ya faɗa a cikin sharhin Al-Waglisiyyah: "Malamai sun yi saɓani a kan wanda ya yi ibada cikakkiya amma bai san farillanta da wanicinta ba. Shin ta yi?" Don Annabi (Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi) bai kallafa wa sahabansa da wannan ba. Abin da ya ce shi ne:

(صلوا كما رأيتموني أصلي)

***"Yi salla kamar yadda ka gani ina salla."***

Da wanincinsa. Ko kuwa bai yi ba saboda jahilcinsa da aikinsa? Sai Ahmadu Zarruk ya ce: "Magana ta farko ita ce ta fi kusa da dacewa." Karshe ke nan.

Na ce: Ya gabata a cikin maganar Abdulwahab Sha'arani cewa ya wajaba a kan kowane balagagge mai hankali kada ya yi gaggawa wajen inkarin Amawan muminai da sukar Aƙidojinsu ya ba da fatawa da ɓacin ibadarsu da mu'amalarsu da al'amura da wasu masu ijtihadi suka haifar da hankalinsu da ra'ayinsu ba tare da abin da ya zo ƙarara a cikin Alƙur'ani ko hadisi ba saboda ba ta taɓa tare da nassi da ya zo ƙarara ba a cikin Alƙur'ani da hadisi ko ijma'i. Wannan duka yana cikin bayani da ke cewa fasadi ba ya game ibadar al'umma, keɓantattu da waɗanda ba su cikin keɓantattu (Amawa).

## RASHIN GAMEWAR FASADI CIKIN MU'AMALARSU.

Amma bayani a kan rashin gamewar fasadi a cikin mu'amalarsu kamar aure da bauta da ciniki da wanicinsu haƙiƙa akwai ijma'in Malamai a kansa. Amma rashin gamewar wannan a cikin mu'amala keɓantattunsu a bayyane ne. Amma a cikin mu'amala, Amawansu, haƙiƙa, Malamai sun yi bayaninsa suka ce: "Mafi yawan ibadarsu da mu'amalarsu wadda jahili ke tsammanin rashin ingancinsa ba ya fita daga mazhabi na masu ijtihadi yadda ya zo a cikin littafin Taklis Al-Ikhwani. Abin da kuma bai fita daga mazhabobinsu ba ba ya yanke masa hukuncin rashin inganci kuma ba ya musu da mai yinsa.

Maganar Abdulwahab Al-sha'arani ta gabata inda ya ce ba a musu da Amawa muddin a cikinsu ya dace da maganar wani Malami daga cikin Malaman sunna sai dai in aikin ya saɓa wa sunna zahiri ko ya saɓa wa ijma'in Malamai.

Shehu Izzudin bin Abdulsalam ya ce: "Musu ya danganta da abin da aka yi ijma'i a kan wajabcinsa ko haramcinsa. Wanda ya bar abin da aka yi saɓani a kan wajabcinsa ko ya aikata abin da aka yi saɓani game da haramcinsa, in ya yi koyi ne da wasu Malamai game da wannan ba musu da shi. Amma in ya yi koyi da shi a cikin mas'ala da za ta warware hukuncin irin ta in jahili ne ba zai yi masa musu ba don bai yi laifi ba don ba dole ne ya yi koyi da wanda ya ce haramun ne ko wajibi ne ba." Karshe ke nan. Karshen magana ke nan.

Na ce abin da ake nufi da inkari shi ne inkari na haramun. Amma da zai yi inkarinsa, inkari na shiryawa ko ya yi umurni da shi umurni na nasiha da shiryarwa wannan ya zama nasiha da kyautatawa yadda ya zo a cikin sharhin Arba'una Hadisi na al-Nawawi.

## HUKUNCIN MU'AMALARSU A BABIN AURE

In ka ce: Yaya mu'amalar mutane za ta inganta a babin aure a cikin waɗannan garuruwa waɗanda kaɗaitar maza da mata ta yi yawa tare da kasancewarsu suna gudanar da aurensu kafin su yi istibra'i. Wannan kuma yana daga cikin abubuwa da ke ɓata aure.

Na ce: Aurensu daidai ne saboda kaɗaitar mace tare da namiji na nesa ba ya wajabta yin istibra'i sai in an tabbata ya yi zina da ita ko kumu suna ƙarfafa zato cewa ya yi haka yadda Al-ajhuri ya ba da fatawa. Wannan kuma kaɗan ne. Kaɗaitarsu mata da maza kawai ba tare da tabbatar da aukuwar zina ba ba ko kuma ƙarfafa zato a kan haka ba shi ne mafi rinjaya, akasinsa kaɗan ne. Mafi yawan hukuncin shari'a kuwa tana gudana ne a kan mafi rinjaya a mafi yawan lokaci

A cikin Al-Manhaj Al-Muntakhab an ce: "Mafi yawa shi ake gabatarwa a kan kaɗan." Shi ne sha'anin shari'armu mafi yawan lokaci.

## RABE-RABEN GARURUWA DA HUKUNCINTA TA HANYAR MUSULUNCI KO RASHINSA A BABIN BAUTA

In ka ce: Yaya mu'amalar mutane za ta inganta a babin bauta a cikin waɗannan garuruwa da cinikin 'ya'ya ya yawaita a cikinsu?

Na ce: Wannan mu'amala ingantacciyar ce saboda an raba garuruwa kashi uku.

Kashi na farko: Garuruwan da Musulunci bai tabbata a cikin mutanenta ba kamar garuruwan Munchi da Gurmi da garin Bussa da garin Bargu da garin Yarbawa da garin Gumbi da garin Kotokoli da garin Tanbago da garin Bobil da makamantansu cikin garuruwan Sudan waɗanda Musulunci bai tabbata a cikinsu ba. Waɗannan garuruwa, garuruwa ne da kafirci ya yawaita a cikinsu. Ya halarta a mallakin mutanenta ba tare da tambaya ba sai in an tabbata mafi yawan mutanenta Musulmi ne kafin a mallake su.

Shehu Ahmad Baba ya ce a cikin littafinsa da ake kira Al-kashfu Wal Bayan Li Asnaf majlub Sudan yayin da ya lissafa ire-iren mutanen waɗannan

garuruwa da muka ambata: "Dukkansu kafirai ne, ba su gushe ba a kan kafircinsu har zuwa yanzu" sai ya ce: "Babu laifi in ka mallake su ba tare da tambaya ba." Karshe ke nan.

Na ce halatta mayar da su bayi yana halatta mallakarsu a ijma'in Malamai. Duk wanda ya zo daga waɗannan garuruwa cikin bayi ya halatta a bautar da shi.

Kashi na biyu: Garuruwan da Musulunci ya tabbata a cikin mutanenta kamar Barno da Kano da Katsina da wasu sassa na Zazzau da Songhai da ire-irensu cikin garuruwa da suka samu Musulunci daga garuruwan Sudan. Waɗannan garuruwa, garuruwa ne da Musulunci ya samu rinjaye a cikinsu. Bai halarta a mallaki mutanenta ba ba tare da tambaya ba sai an tabbata mafi yawansu kafirai ne.

Shehu Ahmad Baba ya ce a cikin littafinsa da ake kira Al-Kashfu Wal Bayan Li Asnaf Majlub Sudan yayin da ya lissafa ire-iren mutanen waɗannan garuruwa da muka ambata: "Saboda su, Musulmi, ne bai halatta a mallake su ba. In an zo da bawa daga waɗannan garuruwa da aka sani da Musulunci kuma ya ce daga wurin yake kuma ya ce shi ɗa ne za a ƙyale shi, ya tafi abinsa, a yi masa hukunci na ɗa. Haka Malaman Andalus suka ba da fatawa kamar ibn Itabi da waninsa. Haka ma mahukuntan Fas suka yanka masa hukunci. Karshe ke nan.

Kuma ya sake cewa: A cikin littafin Nawazil na Abul Asbag Bin Sahl, wanda yake shahararren limami ne: "Wanda ya ce shi ɗa ne kuma ya ce ya fito ne daga garin da ake sayar da 'ya'ya da yawa, kuma mai saya ya yarda da shi cewa ya saye shi a wannan garin. Muhammadu bin Walid da Yahaya bin Abdul Aziz sun ce: "za a kallafa wa mai saye tabbatar da bautarsa." Haka ma Suhnunu ya ce. Ibnu Lubanatu ya ce: "Kawo hujja na kan mai da'awar 'yanci" Ibnu Zarbi ya ce: "Maigida shi zai tabbatar da ingancin abin da ya saya wanda yake abin da ya saya wanda yake abin bautarwa. Haka aka bada fatawa a cikin Filna na Ibnu Hafsuri." Karshen magana ke nan.

Na ce haƙiƙa ya gabata cewa halatta abin bauta yana bin halaccin mallaka a cikin ijma'in Malamai. Idan aka zo da bawa Musulmi daga garuruwan da aka sani da Musulunci kuma ya yi da'awa gare mu cewa shi ɗa ne bai halatta a mallake shi ko a mayar da ita kuyanga ba in ta kasance mace ce. Amma in ya kasance kafiri, ya halatta a mallake shi, ko da mun shigar da shi addinin Musulunci. Ya halatta a bautar da shi ko da ya fito ne daga garuruwan da aka sani da Musulunci.

Kashi na uku: Garuruwan da ba mu san hukuncinsu ba. Za a hukunta su a kan garuruwan Musulunci ko garuruwan kafirai saboda rashin saninmu ga asalinsu?

A wannan wuri akwai kokwanto. Malamin Furu'a, Makluf Al-Bilbali, ya ce: "Wanda ke son ya tsira da kansa kada ya sayi wani bawa sai bawan da ya faɗi garinsa. Shin daga shi, garin Musulunci, ne ko daga garin kafirci?" Wannan shi ne ƙarshen magana.

Masanin Furu'a, Al-hafiz Abu Is'haƙa bin Hilal, ya ce: "Hanin gabanin mallakar wanda ya fito daga garin da ba a san ko garin Musulunci ne ko garin kafirci ne na daga cikin babin tsentseni."

Na ce: In ya halatta a mallake shi a bisa abin da Abu Is'haƙa bin Hilal ya faɗa, ya halatta a mayar da ita kuyanga in mace ce saboda halarcin zaman kuyanga yana bin halarcin mallaka a ijma'in Malamai yadda muka gabatar.

In ka ce: Shin yana halatta a sayi Bafillace da ya zo mana saboda a mallake shi har wannan ya halatta a mayar da shi bawa ko bai halatta ba?

Na ce: Wannan bai halatta ba ga mafi yawansu yadda Shehu Ahmad Baba ya faɗa a cikin littafin Al-Kashf Wal-Bayan Li Asnaf Majlub Al-Sudan. "Saboda Musulunci ne addinin mafi yawan mutane a cikin ƙabilunsu in ban da wasu mutane da ake kira Wara'ajinnu da labari ya zo mana cewa su kafirai ne kuma ba mu san ko asalinsu haka suke ko sun yi ridda ne ba" Karshe ke nan.

Haƙiƙanin al'amari, Bafillace da ya zo mana bai halatta a sayar da shi don bauta sai an tabbatar shi, kafiri, ne domin akwai Musulunci wajen mafi yawansu a cikin ƙabilunsu yadda ya gabata.

## RASHIN GAMEWAR FASADI A CIKIN MU'AMALARSU A BABIN CINIKAYYA

In ka ce Yaya mu'amalar mutane za ta halatta cikin dukiyoyinsu a babin saye da sayarwa da makamantansu a wannan zamani namu tare da yawan riba da ƙwace da sata da hare-hare a tsakaninsu?

Ita ce: wannan mu'amala ta halatta.

Ahmadu Zarruku ya ce a cikin Sharhin Al-waghlisiyyah: "Bai kamata ba ga wanda ya yi riƙo da addini ya saurari abin da wasu mutane ke faɗi

game da haramcin dukiyar lokacinmu saboda rashin ilimin masu su da shari'a a kan saya da sayarwa. Saya da sayarwa ta fuskar halal a wasu wurare 'yan kaɗan. Asali kuwa dukkan abin da ke hannun Musulunci halal ne sai an tabbatar da saɓaninsa, ko kuma alamar zato. Irin wannan ƙuduri da muka yi hani a kansa yana kai ga munanan abubuwa waɗanda ba za mu tsawaita ambatonsa ba." Karshe ke nan.

Kuma ya sake cewa yayin da mawallafi ya ce: Tsentseni shi ne mutum ya bar abin da yake shakka a kansa in ya kasance halali ne kuma bai tabbatar da haramcinsa ba kamar dukiyar sarakuna da azumi a ranar Arafat ko da ya ƙarfafa zato cewa ranar Salla ce da makamanta wannan. In aka dogara ga alama bayyananna ko kuma kusa da bayyananna. In ba haka abin ba ya zama waswasi. Bai kamata a yi tambaya a kansa ba kuma ya zama abin da ke ɓoye da tambaya a kansa cuta ce gare shi. Yana ma zama haramun.

Kasuwannin Musulunci, an ɗauke su a kan halali suke. Haka ma dukiyoyin Musulmi sai in saɓani haka ya bayyana ko kuma alama bayyananna ta kasance a kanta. Abin da yake halali shi ne abin da aka jahilci asalinsa. A mafi yawan lokaci aka guji abin da zai cutar da Musulunci. Ba laifi ga mumini sai abin da ya sani ko kuma zato mai ƙarfi ba yin waswasi kawai ba.

Haƙiƙa, an sami cinikin riba da na haram da na shubha wajen kafiran amana da wanicinsu a zamanin Sahabai amma ba su guji kasuwanninsu ba saboda amincin da asali.

Kuma ya ce: An kuma yi ƙwace a Madina a zamanin Ibnu Zubairu har kwana uku amma bai tabbata daga magabata ba cewa ɗayansu ya bar mu'amala saboda wannan. Karshe ke nan.

Ya kuma ce yayin da mawallafi ya ce: Daga cikinsu akwai ciniki ana kiyaye shi daga haramun da shubha iri-iri.

Abin da take shubha ita ce abin da halarcinsa bai bayyana ba haka ma haramcinsa ko da abin da aka hana ya cuɗanya da wanda ba a hana ba kamar dukiyar zamaninmu. Asalinta halali ne sai saɓaninsa ya bayyana ko kuma zato mai alama ko kuma kusa da shi. Sai a yi aiki a kanta. Abin da aka jahilci haramcinsa na kyauta ko ciniki da makamantarsu, an yi rangwame a kansa kuma an haramta a yi bincike a kansa saboda zai cutar da mai mallakarsa da bayyana masa dalilin mallakarsa. Karshe ke nan.

Haka ma ya ce yayin da mawallafi ya ce kada ya ci kuma kada ya sha sai abin da yake halali. Malaman Sufaye sun yi ijma'i a kan samunsa. Ko da babu shi, da ba a samu waliyyai ba don babu ƙarfi gare su in ba nashi ba. Karshe ke nan.

Ya kuma ce a cikin Miftahus Saddad, Sharhin Irshadu Salik: Halali shi ne abin da ya wofinta daga zargin haƙƙoƙin Allah da haƙƙoƙin bayinSa. Shi ne abin da aka jahilci asalinsa a bisa ga ingantacciyar magana.

Haƙiƙa, ya gudana a wajen mutane cewa abu ne da ya ɓata. Malaminmu Abu Abdullahi Al-Kaurayi, (Allah Shi yi masa rahama), yana inkarin wannan inkari mai tsanani, yana cewa: Wanda akwai wani abu a hannunsa wanda bai san dalilinsa ba ko kuma daga wace fuska ya same shi ba, ya zama halali tsintsa.

Wasu malamai sun ce ɗabi'a, dukiya halali ce yadda aka halicci ruwa mai tsarki babu abin da ke sa shi ya zama najasa sai abin da ya jirkita shi. Wannan kuma ba ya haramta shi sai abin da ya jirkita shi.

Kuma ya ce: "Hakika, wasu malamai sun yanke hukuncin haramta dukiyar azzalumai amma Izzuddin Ibnu Abdulsalam ya ƙi wannan. Ya ce tsentseni ne ya kai su ga haka. Ko da mutum ya yi tsentseni a cikin addinin Allah, yaya zai bar faɗin wani abu da ba hukuncin Allah ba da ya fi masa alheri." Karshe ke nan.

Na ce: Wannan shi ne hukuncin abin da aka jahilci masu wannan dukiya. Amma shahararriyar magana ita ce halartarsa. Amma haramun shi ne wanda aka san masu ita (dukiya) babu saɓani tsakanin mutane biyu a kan haramcinta a ijma'in malamai.

Ga abin da Abdurrahman AlBarnawi ya faɗa a waƙarsa da ake kira Shurbu Zulal.

Kowace dukiyar haramun da aka san masu ita. Ba za ta zama halali ba, ya kai ɗan'uwana saboda sai dai a bisa niyya komawarmu ga inganci ga dalilansa Ubangijinsa. Ka riƙe ta ba wata sakayya. Amma wadda aka jahilci masu ita, ta halalta, kuma tana da ƙofofi masu yawa.

Abinci da aka kama yana halalta a bisa ga Zahirin ilimin fiƙihu ya kai aboki. Kuma barinsa tsentseni ne aka nuna, ga wanda ya wadata kuma yana gudun shubuha.

*Ka lizimci tsentseni, ya kai aboki kada ka bar shi*
*Saboda shi ne hanyar samun tsira*
*Shi kuma yana matakai yadda suka bayyana*
*A cikin babinsa, ka tsaya a kan abin da suka bayyana*
*Akwai magana huɗu da ta zo a cikinsa*
*Daga Ibnu Rushdi, ka dubi abin da ya bayyana*
*Shin ya isar masa kamar sadaka*
*Ko kuma kamar kamar ganima ce ga wanda ya haƙiƙance shi*
*Yana halatta ga mawadaci da talaka*
*Ko kuma mara shi ga mai sani*
*Kuma ya sake faɗa.*
*Mai ɗauka don kansa da iyali*
*Gwargwadon buƙata daga dukiyoyin*
*Ba tare da ɓarna ba ko ƙari*
*Ga wanda ke so ya amfana.*
*Wannan bai zama cin haramun ba*
*Sam sam kuma bai zama shubuha ba ga*
*Mai neman bayani;*
*Littafin Al-Fakihani da ke sharhin Risala*
*Ya faɗi wannan ka kiyaye maganarsa.*
*Wasu daga cikinsu sun tsananta wasu kuma*
*Sun sassauta*
*Addinin abu ne mai sauƙi, Mai adalci Ya faɗi*
*Haka.*
*Babu makawa Rayuwar mutum ya warware shi*

Na ce abincin sarakuna da ke bisa wannan hanya in ƙwace shi aka yi a bisa mashahuriyar magana ya zama halali. Ahmadu Zarruku ya ce a cikin Miftahus Saddad Sharhin Irshadul Salik: "Malamin fiƙihu, Abu Abdullahi Al-kaurayi ya ba mu labari (Allah Shi yi masa rahama). Cewa sarki Abul Hassan Al-Madini. ya kira malaman zamaninsa zuwa cin walima. Mutane masu sani da riƙon addini cikinsu akwai wanda ya ce: Ni ina azumi. Daga cikinsu akwai wanda ya ci amma kaɗan. Daga cikinsu akwai wanda ya ci da yawa da kitse kawai. Daga cikinsu akwai wanda ya ci komai baki ɗaya. Daga cikinsu akwai wanda ya ce: Ku zo ga abincin sarki don a samu albarka. Sai wani malami ya tambaye su ina tsammani shi, baban Ibrahim Al-Araji, ne a kan wannan.

Sai na farko ya ce: Abincin shubha ne aka ɓoye da yin azumi yadda ya zo.

Na biyu ya ce: Ina ci ne gwargwadon abin da za a yi sadaka da shi saboda ban san masu shi ba. Mai rungumarsa kamar mai ƙwace ne.

Na uku ya ce: Na dogara da maganar da ke cewa a kusan na masu ƙwace ne.

Na huɗu ya ce: Abinci ne aka kwashe a bisa ƙimar mai kwashe shi. Sai ɗaukarsa ya zama halali gare shi. Ni na samu sai ya zama halali gare ni.

Sai Ahmadu Zarruku ya ce wannan shi ne tsintsar fiƙihu da asalinsa.

Na biyar ya ce: Abinci ne da ya kamata a ba musakai domin a tsarkake wasu daga cikinsu. Na tsarkake shi kuma na sadar da shi ga ƙofarsa. Shi ya yi sadaka da abin da ya ɗauka."

Kuma Ahmadu Zarruku ya ce kuma: "Wannan shi ya kamata da dacewa saboda haɗewarsa tsakanin fiƙihun da tsentseni. A taƙaice, mutum malamin kansa ne bayan ya zama malami a matsayin shubha." Karshen magana ke nan.

Na ce Muhammadu bin Abdurrahman Al-Barnawi ya waƙe wannan a waƙensa na Shurbul Zulal yayin da ya ce:

*In ka zo ga abincin gidan sarki*
*Kana da zaɓi cikin abin da ya shahara*
*In an tara manya wasu da wasu*
*A kan walima kuma cikinsu akwai masu daraja*
*Wasu za su ci kaɗan wasu kuma da yawa*
*Za su ce ku zo ga abincin manyan mutane*
*Akwai mai ci kaɗan kamar kitse*
*Akwai mai cewa azumi yake yi in an tambaye shi*
*Wasu daga cikinsu za su haɗa fiƙihu da tsentseni*
*Wasu kuma tsintsar fiƙihu za su yi da tsentseni*
*Kowane na da basira a kan shiriya*
*Al-kaurayi ya faɗi haka ga mai son koyi*
*In ka san wannan ka san mutum*
*Malamin kansa gwargwadon hali*
*Kana da mashiga biyu*
*Ga hanyar ilimin tsantseni ga wanda ya fake da shi.*
*Tsentseni ya ɗaukaka akwai kuma yalwa a ilimi*
*Halin da kake ciki na addini mai yawa ne.*

Ghazzali ya ce: A cikin Manhajul Abidin fi kubul Amwali Saladin ka sani malamai sun yi saɓani a cikinsa. Wasu sun ce: wani abu daga cikin dukiyarsu bai halatta ga mawadaci ko talaka saboda su, azzalumai, ne. saboda mafi yawan dukiyarsu haramun ce. hukunci kuwa a kan mafi rinjaya ne. Ya zama dole a nisanta ta."

Wasu suka ce: "Ya halatta ga talakawa amma ban da mawadata."

Kuma ya ce: "Waɗannan matsaloli ba shi yiwuwa a bada fatawa a kansu sai da abu mai sauƙi"

Na ce: Bayani ya gabata cewa dukkan abin da ka san mai shi daga dukiyarsu bai zama halal a ijma'in malamai ba. Amma abin da ba ka san masu shi ba ya halatta a bisa mashahurin zance.

Ghazzali ya ce kuma: a cikin littafi da muka ambata a kan bayanin karɓar sadaka. "Yan kasuwa da wanicinsu waɗanda muka san alheri a zahirin al'amarinsu babu laifi cikin a karɓi sadakarsa."

Kuma ya ce: "Ka sani a nan akwai abu biyu na hukuncin shari'a, shi ne ka karɓi abin da ya zo maka a zahirinsa alheri ne kada ka yi tambaya. Hukuncin wani abu daga wani sai ka yi bincike a kansa matuƙar bincike har ka tabbatar babu shubuha a cikinsa a kowane hali ko kuma ka mayar da shi."

Kuma ya ce: " In ka ce: Tsentseni ya saɓa wa shari'a da hukuncinsa. Ka sani shari'a, an ajiye ta a kan sauƙi. Tsentseni kuwa an ajiye shi a kan tsanani da kiyayewa. Kuma tsentseni daga shari'a yake dukkansu asalinsu guda ne amma shari'a na da hukunci biyu: Hukunci na halarci da hukunci na mafifici da mafi kiyayewa. Na farko, hukuncin shari'a ne. Na biyu, hukuncin tsentseni ne."

Kuma ya ce: "In ka ce: In ya halalta a yi bincike a kan kome abin zai yi wuya ga mai tsentseni ko yaya ya kai matuƙa wajen yin ɗa'a." Ka sani hanyar tsentseni mai tsanani ce wanda kuma ya yi nufi ya shiga hanyar sai ya bi sharaɗinsa na yin haƙuri a bisa tsanani in ba haka ba ba zai samu biyan buƙata ba Karshe ke nan.

Na ce: Haƙiƙa ya gabata a cikin maganar Ahmadu Zarruk cikin sharhin Al-Waghlisiyah yayin da mawallafi ya ce: "Tsentseni shi ne mutum ya bar duk abin da yake kokwanto a kansa in ya kasance ba halali ba. Yana nufi haramcinsa ba ya tabbata kamar dukiyar sarakuna da makamantanta. Wanda ya dogara ga alama bayyananna ko kusa da bayyananna. In ba haka

ba ya zama waswasi, bai wajaba ya yi tambaya a kan abin da yake ɓoyayye ba. Tambaya a kansa cutarwa ce ko kuma ma haramun:." Karshe ke nan.

Ya gabata kuma a cikin maganarsa cikin "Miftahus Saddad, sharhin Irshadul Salik," cewa malaminmu baban Abdullahi, Alkaurayi ya kasance yana faɗi: "Wanda akwai wani abu a hannunsa wanda bai san dalilinsa ba kuma bai san daga wace fuska ta sadu da shi ba ya zama halali tsintsa."

A nan ne littafin Tahƙikul Ismati Li Jami'I Tabaƙatil hazihil Ummati Minal Ijtima'i ala Lallah ila Waƙti Kiyamu Sa'ati ya zo ƙarshe da nassi bayananne daga hadisi. Wanda ya lura da abin da na faɗa zai sani cewa fasadi ba zai game aƙidun al'umma ba da ibadarsu da mu'amalarsu, keɓantattunsu da Amawansu.

Godiya ta tabbata ga Allah da Ya kiyaye Addinin Musulunci daga dukkan abin da jahilai ke faɗi kuma Ya lamunce wannan da faɗinSa:

﴿ إِنَّا نَحْنُ نَزَّلْنَا ٱلذِّكْرَ وَإِنَّا لَهُۥ لَحَٰفِظُونَ ﴾ الحجر: ٩

*"Lalle Mu ne Muka saukar da Alƙur'ani kuma Mu ne ke kiyaye shi."*
Suratul Hijir:9

Tsira da Amincin Allah su tabbata ga Muhammadu, zaki da ya maye mana 'ya'yansa a kowane zamani. Haƙiƙa, ya bayyana mana wannan a maganarsa wadda ke ɗauke da wannan ilimi ga kowane halifansa masu adalci masu kore dukkan ɓarnar waɗanda suka ɓata da ƙaryar maƙaryata da tawilin jahilai kuma a bisa alayensa da sahabansa baki ɗaya.

# إرشاد أهل التفريط والإفراط

# إلى سواء الصراط

# SHIRYAR DA MASU FAIFAYEWA DA MASU SAKE ZUWA GA DAIDAITACCIYAR HANYA

Na

Shehu Usmanu Ɗanfodiyo

Masu Fassara:
Dr. Ahmad liman
Dr. Aliyu malami

## ABUBUWAN DA KE CIKI

**Shafi**

GABATARWA…………………………………………………...…….343

FASALI NA ƊAYA: Bayanin Haɗarin Afkawa Cikin Kafirci Ga Jahilaizz…………………………………………………………....343

FASALI NA BIYU: Bayanin Haɗarin Kafirtawar Da Ɗaliban Ilimi Ke Yi…… ……………………………………………………………….350

FASALI NA UKU: Mai Bayanin Abin Da Ke Ɗaukar Hankalin Masu Neman Ilimi A Kan Kafirta Ammawa Da Malamai………………..…..353

FASALI NA HUƊU: Yana Bayani A Kan Cewa Malaman Sunnah Sun Yi Ijma'i A Kan Hukunce-Hukuncen Shari'a An Gina Su A Kan Zahiri …361

FASALI NA BIYAR: Mai Bayani Cewa Ɓata Ba Za Ta Game Aƙidar Ammawan Musulmi Ba Har Alƙiyama Ta Tsaya .................................. 368

FASALI NA SHIDA: Mai Bayani A Kan Yarda Da Tauhidi Wajibi Ne Ga Al'umma……...…………………………………………...……370

FASALI NA BAKWAI: Ga Bayanin Duk Fassarar Malaman Ilmul Kalam Da Ambaton Dalilinsu Yana Daga Cikin Farilla Ta Isuwa. ..................... 373

## GABATARWA

Da sunan Allah Mai rahama Mai jin-ƙai. Allah Ya yi salati a kan Shugabanmu Muhammad da iyalansa da Sahabansa kuma Ya amintar da su amintarwa, amin.

Bawan Allah matalauci mabuƙaci zuwa ga rahamar Allah, watau Usmanu Ɗan Muhammad Ɗan Usmanu Ɗan Salihu, wanda aka fi sani da Ɗanfodiyo Allah ya rufe shi da rahamarSa ya ce:

Godiya ta tabbata ga Allah Mai girma Mai baiwa Ma'abucin falala da kyautatawa, Tsarkakakke daga abokin tarayya, da tamka, da abokai Wanda bai da mashawarci ko waziri, ko mataimaka a mulkinSa. Ya ɗaukaka daga wuri da zamani a mulkinSa da malakutinSa, Ya halicci mutum Ya sanar da shi bayani, Ya shiryar da wanda ya yi wa muwafaƙa da falalarSa, Ya cancantar da shi ga tabbatar da aƙidun imani, Ya kuma ɓatar da wanda Ya yarɓar bisa ga adalcinSa, Ya sanya shi cikin ma'abuta haramci.

Ina godiya ga Allah a kan abin da ya jiɓinta muna na baiwa da kyautatawa, ina ƙara godiya mai girma, ina shaida babu abin bautawa da gaskiya sai Allah Shi kaɗai ba Ya da abokin tarayya shaidar da ta tsatsata daga tsatson zuciya, kuma ina shaida cewa shugabanmu, Muhammad, bawanSa ne kuma ManzonSa, farantacce ɗiyan Adam, wanda ya keɓanta da ilimummuka masu yawa, da tararrun kalmomi da fasahar harshe, wanda aka ƙarfafa annabcinsa da manzancinsa da ayoyi bayyanannu da hujjoji masu yankewa, shi ne wanda itatuwa suke shaida da shi; duwatsu suke yi masa sujada, gumaka suka durƙusa domin ganinsa Allah ya yi tsira da aminci gare shi tare da iyalansa da Sahabbansa jarumai har zuwa ranar sakamako, tsira da amincin da muke fatan samun lada mai gwaɓi da kyautatawa mai girma a dalilinsu.

Bayan haka: Wannan littafi mai suna "Shiryar Da Masu Faifayewa Da Masu Sake Zuwa Daidaitacciyar Hanya" an yi shi ne a kan asullan addini, wanda shi ne asalin tsira a ranar sakamako. Wannan littafi mai adalci ne don ya tattaru a kan kwaɗaitar da mutane a kan ƙoƙari wajen gyaran aƙidunsu da karantar da iyalansu da mayar da masu faifayewa daga faifayewarsu wajen kafirta wanda kafircinsa bai bayyana ba ta hanyar zancensa ko aikinsa daga cikin jama'ar Musulmi, sai su taru gaba ɗaya a kan daidaitacciyar hanya,

kuma kaɗan ne ake samun littafin da ya tara waɗannan fa'idojin guda biyu. Na yi wannan littafi a kan fasulla bakwai kamar haka:

1. Fasali na ɗaya: Bayanin haɗarin afkawa cikin kafirci ga Jahilai.
2. Fasali na biyu: Bayanin haɗarin afkawa cikin kafirtarwa ga Ɗalibai.
3. Fasali na uku: Bayani a kan abin da ke ɗaukar wasu Ɗalibai a kan kafirta Jama'ar Musulmi da malamansu.
4. Fasali na huɗu: Bayani a kan cewa hukunce-hukuncen shari'a, an gina su ne a kan bayyanannun abubuwa ga ijma'in Ahlissunna
5. Fasali na biyar: Bayani a kan cewa ɓarna ba za ta game aƙidun jama'ar Musulmi ba har zuwa tashin ƙiyama.
6. Fasali na shida: Bayani a kan cewa ƙudurta ma'anonin asullan addini shi ne wajibi a tauhidi a kan Al'ummar Musulmi.
7. Fasali na Bakwai: Bayani a kan cewa dukan kalmomin ilimin kalam da jumlolin surorin dalilan su fardu kifaya ne.

# FASALI NA ƊAYA

## Bayanin Haɗarin Afkawa Cikin Kafirci Ga Jahilai

Ina cewa muwafaƙa a wajen Allah take, ka sani ɗan'uwa haɗarin afkawa cikin kafirci mafi yawanci ga jahilai yake, cikin jama'ar Musulmin da ba su shagaltu da gyara aƙidunsu ba, ko halartar majalisun malamai. Malam Muhammad Ɗan Abdul'Aziz Ɗan Abdul-Malik Ɗan Abu Mahally a cikin littafinsa mai suna "Al-faslul Auwal" ya ce: Dukkan malaman Musulunci sun yi ijma'i a kan cewa duk wanda ya ƙudurta a zuciyarsa wani abu da aka yi ijma'i a kan kafircin wanda ya ƙudurta shi, to, kafiri ne wanda zai dawwama a wuta. Malam Ɗan Zakariyya ya ce a cikin sharhin Al-HAJIBIYYAH: "Duk wanda ya ƙudurta kafirci ba za a yi masa uzuri ba ya yi ijtihadi ne ko a'a bisa ijma'in malaman Musulunci."

Malam Saiyidi Khalil Ɗan Ishaƙ ya ce a cikin Attaudih, kafirci yana tabbata da faruwarsa a zuciyar mutum ko da bai furta shi ba, domin yin hakan matsayi ne na ƙasƙantattun mutane." Malam Ɗan Rushd ya ce: "Duk wanda bai yi yanke da aƙidunsa ba kafiri ne" Malam Ɗan Abu Shareef ya ce: Duk wanda ya gurɓata aƙidarsa munafiki ne." Alkali Iyad ya ce a cikin Asshifa: "Wanda duk ya kore kaɗaituwar Allah, ko ya yarda da bautar wanin Allah ko ya ce Allah ba marashin farko ba ne, ko akwai wani abu tare da Shi, ko Yana da ɗa, ko mata, ko uba, ko kuma akwai wani maƙagin halitta koma bayan Allah, to, shi kafiri ne bisa ga ijma'in malaman Musulmi."

Malam Ghazali ya ce a cikin littafin Gamsassun amsoshi a kan rikitattun tambayoyi: "Masu furucin da aka jarraba kashi-kashi ne. Akwai kashin da suka furta cewa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, kuma Muhammadu Manzon Allah ne, sai dai ba su yi imani da abin da suka furta ba, domin ba su bincike a kansa ba, saboda ƙarancin kulawa, ba shakka waɗannan kafirai ne." A cikin littafin Mi'iyar na Malam Wansharasi ya ce: "Duk wanda ya furta cewa babu abin bauta da gaskiya sai Allah ba tare da fahintar ƙudurin ba, kafiri ne wanda zai dawwama a wuta" bisa ga ijma'in malamai."

Malam Sunusi ya ce a cikin Sharhin Wusɗa: An tambayi Malaman Bujayah da wasunsu a farkon wannan ƙarni ko kafinsa da kaɗan a kan mutumin da ke furta Kalmar shahada yana sallah yana Azumi, yana Hajji da sauran ayyukan ibada, sai dai yana yi ne kawai kamar yadda ya ga mutane

suna faɗa suna aikatawa, domin kawai yana furta Kalmar ne ba tare da fahintar ma'anarta ba, bai san ma'anar Ubangiji ba, ko ma'anar Manzo, ga baki ɗaya bai san ma'anar Kalmar shahada ba, yana ma iya ɗaukar cewa manzo tamkar ta Ubangiji ne, don ganin cewa a cikin Kalmar shahada da ma wurare da dama idan aka ambaci Ubangiji dole ne a ambaci ManzonSa. Shin ko wannan mutum yana amfana da zance ko aikin da ya yi a kuma gasgata haƙiƙanin imaninsa tsakaninsa da Ubangijinsa ko a'a? Sai malaman baki ɗaya suka amsa da cewa: Irin wannan mutum ba ya da rabo ko kaɗan na imani, duk yadda surorin zantukan imani da ayyukansa suka bijiro daga gare shi. Malam Muhammad Ɗan Abdul-Azizi Ɗan Abdul-Malik Ɗan Abu Muhally ya ce a cikin littafinsa mai suna Fasali na biyu: " Babu Shakka a kan kafircin wanda bai fahinci ma'anar kalmar shahada maɗaukakiya ba, yana tamkar wanda ya ce Allah yana yin aiki ne don wata illah (Dalili), ko wanda ya yi imani da samuwar wata ɗabi'a. Allah guda ɗaya ne.

Haka ma babu shakka a kafircin wanda ya yi kokwanto a cikin rashin farkon Allah ko rashin ƙarshenSa, ko kaɗaitarSa ga yin halitta, da uluhiyyah da ibadah, ko tsarkake Shi daga mata, ko uba, ko ɗa, ko cin abinci, ko shan abin sha, ko ƙarya, ko tarayyarSa da waninSa. Haka nan babu shakka a kafircin wanda ya kore wa Allah rayuwa, ko ya yi kokwanto a cikin faruwar halittu, ko ƙarewar duniya, ko gaskiyar Annabawa, ko ya wulaƙanta Annabawa, ko ya zage su, ko ya zagi littattafan da Allah ya saukar, ko ya keɓance manzancin Annabi Muhammad (saw) ga Larabawa kawai, ko ya riya cewa Sahabbai ma Annabawa ne, ko ya ɗauki cewa Waliyyi yana iya wadatuwa da ilhami daga shari'ar Annabi (saw), domin shi (Annabi) Manzo zuwa ga waliyyin da wanda ba shi ba, don haka  ba a aiki da ilhami sai in ya yi daidai da shari'ah.

Haka nan wanda ya riya cewa shi, Annabi, ne, ko kuma ya taka zuwa sama ya shiga Aljannah, ko ya ce an ɗauke wa wani waliyyi taklifi, ko akwai waliyyin da ya kai darajar wani Annabi, ko ya yi shakka a kan tayar da jiki a ranar ƙiyama da yi masa hisabi da wuta ko Aljannah, ko ya yi shakka ga tabbatar kafirai, da masu bauta daga cikinsu da malamansu a cikin wuta. Ko ya ce Annabawa ba su da mu'ujiza, ko ya ce al'amuran lahira ɓoyayyu ne ba tabbatattu ba ne, ko ya yi shakka a cikin abin da lalura ne a addinance, kamar wajabcin yin imani da Sallah da Azumi da Zakkah da haramcin giya da kisa da sihiri. Wanda duk ya sanya zato ga faruwar zatin Allah, kafiri ne bisa ga

ijma'i, su dai aƙidojin da aka yi ittifaƙi a kan kafirtawa dominsu ko waɗanda aka yi saɓani masu yawa ne, ina horon ka da sanin ilimin tauhidi.

Malam Sanusi ya ce a cikin Sharhin Kubrah: "Duk wanda bai yi ƙoƙari wajen neman ilimi daga malamai matabbata ba, musamman ilimin tauhidi zai mutu a kan wasu nau'uka na kafirci da bidi'o'i alhali bai sani ba, kuma labari bai kai kamar gani ba, domin mun ga da yawa daga cikin waɗanda ba su kyautata wannan ilimin ba (Tauhidi) alhali suna da ƙwarewa a wasu ilimummuka amma ba su kyautata aƙidunsu ba, ko da ko a kan taƙalidi ne (kwaikwayon wani) balle su yi bincike a cikinsa, to, ballatana bayi maza da mata sun koma tamkar dabbobi, ba a karantar da su baki ɗaya. Ya ci gaba da cewa abu ne tabbatacce cewa mafi yawancin mutane ba su a kan daidai a darajar taƙalidi sai dai suna a kan aƙida ɓatacciya."

Muhammad Ɗan Abu Muhalli ya ce: "Malam Sunusi ya yi tambihi a kan cewa aƙidar mafi yawan mutanen zamaninsa Ɗalibai ne ko ba Ɗalibai ba gurɓatacciya ce, wasu daga cikin aƙidun ma kafirci ne bisa ga ijma'i, wasu kuma an yi saɓani a kansu." Malamin ya yi kira, ya yi nasiha ya tsawata, ya yi maganar da duwatsu ma na iya tarwatsewa saboda, sai dai akwai mamaki a kan yadda muka rafkana daga iyalanmu, abokanmu da sauransu, da rashin mayar da hankalinmu a zuwa ga abin da yanayi yake nuni a kansu.

Mafi girman waɗannan shi ne Malam Sunusi ya yi bayani ƙarara a wasu wurare cikin littattafansa cewa ya ga da yawan mutane a kan gurɓatacciyar aƙida ta kafirci alhali ba su sani ba. To, idan haka ta kasance a zamanin wannan babban malami me za mu ce a zamaninmu, don haka mu yi ƙoƙari mu karantar da mutane gwargwadon hankalinsu da yarensu, ko da ba su iya Larabci ba, domin

(كلكم راع وكلكم مسؤول عن رعيته )

*"Dukkan ku makiyaya ne, kuma kowannenku za a tambaye shi abin da aka ba shi kiyo"*,

Kuma

(كاتم العلم يلعنه كل شئ)

*"Mai ɓoye ilimi dukkan halittu suna la'anar shi"*

Da wasun waɗannan hadisan.

Me za mu ce dangane da imani wanda ilimi ko aiki ba su inganta sai da shi amma mun rafkana har kafircin da aka yi ijma'i a kansa ya bayyana a gare mu, babu iyaka a wurin da yawa daga cikin ɗalibai, balle waɗanda ba ɗalibai ba. Amma abin da aka yi saɓani a kan kasancewarsa kafirci kamar ƙudurta wuri, ko jiha, ko jiki, ko tasirin halittu da ƙarfin da Allah ya sanya musu, waɗannan dukansu ɓata ne da karkacewa bisa ga ijma'in Ahlussunnah, sai abin da aka yi ijma'i a kan kasancewar sa kafirci ya fi tsanani.

Malam Sunusi ya ce a cikin sharhin Kubra: "Kana samun jahiltar mafi yawan aƙidu a wurin mafi yawancin waɗanda ba su neman ilimi, ko cuɗanya da mutanen alheri suna ƙudurta jiki da jiha ga Allah, ko kasancewar aikin Allah don wata manufa, ko kasancewar maganar Allah harafi ko sauti, ko Allah yana magana wani lokaci, wani lokacin kuma Ya yi shiru, tamkar halittu, da wasun waɗannan daga cikin aƙidun mutanen ɓarna. Wasu daga cikin aƙidunsu, malamai sun yi ijma'i a kan cewa kafirci ne, wasu kuma sun yi saɓani dangane da su. Na ce idan ka fahimci wannan, za ka san cewa duk wanda ke hana mutane koyon aƙidunsu, to, shaiɗan ne ɗan fashi a hanyar Allah, yana son jahili ya tabbata a kan ɓatattun aƙidunsa. Wannan shi ne abin da iblisu yake buƙata, wanda kuma ya yi aiki don tabbatar da buƙatun iblisu, to, abokinsa ne kuma halifarsa a fasadi.

Malam Sunusi ya ce a cikin sharhin Wusɗa : Malam Muhammad Ɗan Umar Ɗan Abu Muhalli ya ce a cikin littafinsa mai suna Al-faslul-Auwal: "Haƙiƙa, shaiɗanun mutane da aljannu suna haddace Alƙur'ani amma ba su fahimtar aƙidunsu, shaiɗan ya hore su a kan bayin Allah, suka ruɗar da su, suka tabbatar da su a kan ɓarna, suka kore su daga neman ilimi da ɓatocinsu waɗanda ambatonsu zai tsawaita." Sannan ya ce "zan ambata maka kaɗan daga cikin ɓatocinsu don ka kiyaye sai in ce Gargaɗi."

Gargaɗi na farko: Suna cewa duk wanda ya ce ba abin bautawa da gaskiya sai Allah mumini ne zai shiga Aljannah ko da ya jahilci aƙidu, don faɗar Annabi (saw),

( أمرت أن أقاتل الناس حتى يقولوا لا إله إلا الله)

***"An umurce ni da in yaƙi mutane har sai sun ce babu abin bautawa da gaskiya sai Allah",***

Da faɗarsa

(من كان آخر كلامه لا إله إلا الله دخل الجنة)

***"Duk wanda maganarsa ta ƙarshe ta kasance cewa babu abin bautawa da gaskiya sai Allah zai shiga Aljanna."***

Amsa a nan ita ce sun karkatar da ma'anar hadisan ne domin dukkan sahabbai da malaman Musulunci sun yi ijma'i a kan cewa wanda ya furta kalmar shahada yana shiga Aljannah ne kawai idan ya fahinci aƙidun imaninsa, kuma faɗar Annabi (saw) cewa:

(من كان آخر كلامه لا إله إلا الله دخل الجنة)

***"Wanda maganarsa ta ƙarshe ta kasance Kalmar shahada zai shiga Aljannah,"***

An ƙayyade shi ne da sharaɗin fahimtar ma'anar ta tare da tsirar aƙida daga lalacewa.

Gargaɗi na biyu cewa wasu daga cikin waɗanda suka shagaltu da Alƙur'ani tare da lalacewar aƙidunsu sun yi raddi ga maganar Ɗan Zakariyya inda ya ce: "Alƙali Ɗan Rushd ya yi hukumci ga mutanen da ba malamai ba da kafircin wanda ya kafirta su a wannnan matsayin." Wannan baitin ya ba da dama ga wanda ya isar da shi zuwa gare ni don ya zaci cewa ma'anarsa shi ne duk wanda ya ƙudurta kafircin wanda ya furta kalmar shahada ba tare da i'itiƙadi ba kafiri ne amma wannan ɓataccen bai san cewa malaman Musulunci na farko da na ƙarshe su ne suka yi ijma'i a kan kafircin wanda ya furta wannan kalmar maɗaukakiya ba tare da yin yanke da ƙudurinta ba, abin da yake nufi da cewa Alƙali ya yi hukumci har zuwa ƙarshen maganar waɗanda ke ƙudurta kafircin mutanen da suka fahimci aƙidunsu tare da dalili. Ba ya inganta a kafirta wanda ya kafirta muƙallid (mai kwaikwayon waninsa), shi ne wanda ya fahimci addininsa ba tare da dalili ba, domin saɓanin malamai a kan wannan sananne mai matuƙar abin da za a ce game da shi a ingantacciyar magana shi, mumini ne, amma wanda muke magana a kansa shi ne wanda ya furta kalmar ba tare da ƙuduri ingantacce ba. To, shi, wannan, bai ma shaƙi ƙamshin taƙalidi ba balle ya san dalili.

Gargadi na uku: Mun kasance muna karantar da maza da yara ƙanana, mata ma suna halarta ta bayan shamaki, muna bayyana musu aƙidunsu da

maganar da kowa ke fahimta. Sai shaiɗanun mutane suka ce wannan ɓarna ce, suka mayar da karantar da su imanin da komai ba ya inganta sai da shi ɓarna. To, idan ya kasance mace za ta iya tafiya Hajji da Sharuɗɗansa, me za ka ce dangane da imanin da Hajjin ba ya inganta sai da shi? Kuma zamanta a gida tare da kafircin da zai dawwamar da ita cikin wuta ba ya amfaninta, alhali kuma suna ganin mata wajen ɓarnace-ɓarnacen bukukuwa, raye-raye, bushe-bushe da haɗewar mata da maza, da watsi da kuɗi da fitarsu cikin ƙawa a wurin sallar idi, tare da cewa duk wanda ya taimaka a kan waɗannan abubuwan da biyan wata buƙata ko wata kalma ko ya yi shiru alhali yana iya hanawa, to, shi ma mai saɓo ne. Amma idan suka ga wasu matan suna tafiya wajen neman sanin wajibansu domin 'yantar da kawunansu daga dawwama a cikin wuta sai su ce wannan ɓarna ce. To, a sani wajibi ne a kan kowane namiji ko mace shi nemi ilimin abin da ya wajaba a kansa na Sallah ko waninta, balle ma imani. Ya ce a cikin Madkhal: "Wajibi ne a kan mutum ya karantar da matansa, ɗiyansa, bayinsa, da duk wanda ke ƙarƙashinsa, ya sanar da su abin da ya wajaba a kansu na imani, kyautatawa, alwalla, Sallah, Azumi, hukumce-hukumcen haila da biki, da duk abin da suke buƙata na harkokin yau da kullum, da abin da ke faruwa na bidi'o'i. Idan shi ba malami ba ne, to, ya koya daga malami amintacce sai ya koyar da su abin da ya koya. Idan bai yi haka ba ya bai wa matarsa dama ta fita ta nemi ilimi, idan ya ƙi, ta fita ko ba tare da izininsa ba, kuma shugaba ya tilasta shi a kan hakan kamar yadda yake tilasta shi a kan ciyarwa, domin neman ilimi ya fi ciyarwa."

Gargaɗi na huɗu: Wasu daga cikin shaiɗanun mutane masu shagalta da haddar Alƙur'ani koma bayan aƙidunsu suna cewa: Wanda ya ƙudurta kafirci ba a ce masa ya je ya nemi ilimi, kuma ba a faɗakar da shi sai da yardarsa. Wannan kuwa ɓata ce mai girma. Malamai sun ce: Horo da alheri da hani daga mummuna a kan sharuɗɗansa wajibi ne a Alƙur'ani da Sunnah, da ijma'i. Sannan ya ce: Ka sani wanda ke karantar da mutane yana da buƙatar kaifin basira don ya bayyana musu gaskiya da abin da suke fahimta, ko da da ajamanci ne, domin abin da ake buƙata shi ne ɗanɗanar aƙidu a zuciya ba haddace su kawai ba. Na ce wanda ya lura da wannan fasalin zai san cewa jahilan mutane waɗanda ba su shagaltu da inganta aƙidunsu ba, ko halartar majalisun malamai suna a kan haɗarin aukawa cikin kafirci, kuma duk wanda ke kange su daga neman sanin aƙidunsu shaiɗan ne ɗan fashi a hanyar Allah, yana son jahili ya dawwama a kan gurɓatacciyar aƙida. Allah

Ka gwada muna gaskiya, Ka azzurta mu biyar ta; Ka gwada muna ɓarna, Ka azzurta mu nisantar ta.

# FASALI NA BIYU

## Bayanin Haɗarin Kafirtawar Da Ɗaliban Ilimi Ke Yi.

Ina farawa tare da dogara ga Allah. Ka sani akwai haɗari ƙwarai cikin kutsawa da ɗaliban ilimi ke yi musamman masu neman ilimin Tuhidi (ilimul-kalam) waɗanda ba su dogara ga malami mai zurfin bincike a kan ilimi mai zurfi, balle ya sanar da su cewa hukunce-hukuncen shari'a, an gina su ne a kan zahiri. Kuma ba a kafirta wani mutum Musulmi saboda saɓo, sai fa idan ya bayyana kafirci ta hanyar zance ko aiki. Bai kamata a munana zato a kan imanin wani mutun daga cikin Musulmi ba sai idan ya bayyana ta hanyar magana cewa shi mai ɓoye kafirci ne saboda akwai wasu miyagun aƙidu da ya ɓoye.

Malam Abdul'aziz Al-andalusi ya ce: "Kafirtawa tana zamowa da sigar ba da labari kamar ka ce wa wani: kai kafiri ne, ko ka ƙudurta ga zuciyarka cewa wane kafiri ne" sai na ce (inji Shehu Usmanu Ɗanfodiyo): Haƙiƙa, kafirta Musulmi wanda bai bayyana kafirci ba ta hanyar magana kamar musanta wani wajibi wanda Manzon Allah (saw) ya zo da shi, ko ta hanyar aiki kamar yin sajada ga gunki, ko jefa Alƙur'ani cikin ƙazanta. To, kafirta wanda ba wannan ba haɗari ne ƙwarai, don yana kai mutum ga kafirta. Domin Buhari da Musulimu da Abudawuda da Tirmizi da Ibn Hibbana da Ɗabrani da Baihaƙi da Dailami da Al-Dwarabuɗi da Ibn Najjar sun ruwaito cewa: Manzon Allah (saw) ya ce:

(إذا كفر الرجل أخاه فقد باء به أحدهما)

***"Idan mutum ya kafirta ɗan'uwansa nan take ɗayansu ya zama kafirin."***

Shehu Takiyuddini ya ce: "Wannan hadisi ya ƙunshi ƙyace mai girma ga wanda ke kafirta wani daga cikin Musulmi alhali ba kafiri ba ne." Imamu Al-Gazali ya ce a cikin littafinsa, Ihya'u: "Ma'anar wannan hadisin shi ne idan ya kafirta shi alhali ya san shi, Musulmi, ne." Malam Mutawlli ya ce "da zarar wani ya ce wa wani Musulmi ya kai kafiri ba tare da wani tawili ba." To, mai faɗar ya zama kafiri saboda ya ambaci Musulunci da sunan kafirci. Malam Nawawi ya yi hikayar wannan magana cikin Arraudwa.

Sai na ce (inji Shehu Usmanu): "Bai kamata a samu saɓani ba cikin kafircin wanda ya zurfafa cikin jahilci har ya kai ga cewa: "Yau ba wani shiryayye bayan ƙasa sai ni." Kamar yadda labari ya iso gare mu cewa, wani

daga cikin jahilan masu neman ilimi ya yi rantsuwa cewa "wallahi yau sama ba ta yi inuwa ga wani shiryayye ba sai shi." Muna neman tsari ga Allah daga jahilci da kuma jahiltar jahilci domin wannan magana ta kai shi ga danganta al'ummar Musulmi gaba ɗaya zuwa ga ɓata. Haƙiƙa, wannan magana ta mayar da shi kafiri, haka ma wanda ya yi kokwanto cikin zaman sa kafiri, kamar yadda Malam Ahmad Ɗan Hijiri Al-haitami ya faɗa a cikin littafinsa mai suna Azzawajir ya ce: Malam Abdul-mumin Ɗan Salim ya faɗa a cikin littafinsa, Al-fawa`id Al-isɗifa'iyyah sharhu Al-ƙasidati Al –jazairiyyaha, gun faɗar mai ƙasidar:

1. Babu saɓani tsakanin malamai a kan cewa wanda ya kafirta Musulmi, to, ya zama kafiri. Wannan shi ne ma'anar hadisin da ya gabata.
2. Domin cewa ya zama kafiri bai da saɓani saboda ya kafirta mutanen sunnah, wanda duk ya kafirta shiryayyun, to, shi ne kafiri.

Malam Aliyu Ɗan Husamiddin wanda ya shahara da suna Al-muttaƙi ya faɗa cikin littafinsa, Al-burhanu fi Alamati Almahdi Akhira Azzaman, cewa "Malam Muhammad Ɗan Muhammad Al-haɗɗabi Al-Maliki Allah ya ƙara masa yarda ya yi fatawa cewa wanda duk ya yi ƙudurin kafircin duk al'ummar Musulmi saboda sun saɓa ga abin da ya tafi a kansa na kuskure sai ya ga cewa sun fita Musulunci a kan wannan sun zamo kafirai. To, ya kafirta a kan wannan ƙuduri na ɓata, don haka ana nemansa da tuba har kwana uku idan bai tuba ba a kashe shi."

Malam Ahmad Ɗan Hijiri Asshafi'i Allah ya yarda da shi ya yi fatawa cewa wanda duk ya kafirta Musulmi, to, ya zama kafiri sai a yi masa haddi idan bai tuba ba. Wanda ya kafirta sahabbai ko ya danganta al'ummar Musulmi zuwa ga ɓata, to, ya zama kafiri. Malam Abussurur Ahmad Ɗan Adɗiya Al-hanafi ya yi fatawa ya ce: Wanda duk ya kafirta Musulmi waɗanda suka saɓa wa abin da yake a kai na kuskure, ya yi ƙudurin kafircinsu don sun saɓa masa, to, ya kafirta, domin duk wanda ya yi ƙudurin cewa Musulmi kafiri ne, to, kamar ya yi ƙudurin cewa addininsa (Musulunci) kafirci ne. Saboda haka wannan ya sanya shi zama kafiri, za a gudanar da hukunce-hukuncen kafirci a kan sa kamar neman tuba, ko kashe shi idan bai tuba ba.

Malam Yahaya Ɗan Muhammdd Al-hambali ya yi fatawar cewa duk wanda ya kafirta al'ummar Musulmi don sun saɓa wa abin da yake a kai na ƙuduri ɓatacce, ya kafirta su don haka, to, ya yi ridda ya kafirta. Allah ya

kiyaye mu. Malam Yahaya ya ƙara da cewa: “Idan masu kafirta Musulmi suka dage a kan kafirtawar da suke yi, to, ya wajaba ga Sarkin Musulmi da masu zartar da hukunce-hukuncen shari’a su zartar da hukuncin masu ridda a kan su, kamar neman tubansu cikin kwana uku idan ba su tuba ba, sai a zartar da hukuncin kisa a kan su, domin masu ra’ayi irin nasu su kwatsu don jama’ar Musulmi su sami hutawa daga masu irin wannan ra’ayi na bidi’a.”

An tambayi Malam Ɗan Rushudi a kan hukuncin waɗansu malaman Ilmul-kalam waɗanda ke cewa wajibi ne ga malami da waninsa ya karanci littattafan ilmul-kalam kafin sanin duk wani al’amari na addini, kamar alwalla da sallah da sauran ibadodi har suna kafirta wanɗa bai yi hakan ba. Sai ibn Rushadi ya bada amsa da cewa: “Haƙiƙa, tsintsar kafirci shi ne wannan ra’ayin nasu.” Malam Manjuri shi ya yi hikayar wannan magana cikin littafinsa, Sharhu Al-Muhassal. Sai na ce (inji Sarkin Musulmi) duk wanda ya lura da abin da ke cikin wannan fasali, to, lalle zai san haɗarin da ke tattare da afkawa cikin kafirta Musulmi, musamman ga ɗaliban ilimi masu neman sanin ilmul-kalami (Tauhidi) ba tare da jagorancin malamai masu zurfin bincike a kan hukunce-hukuncen shari’ar Musulunci ba, an gina shi bisa zahirin shari’a. Ya Allah Ka nuna muna gaskiya, Ka ba mu ikon bin ta; Ka nuna muna ɓata, Ka ba mu ikon nisantar ta.

## FASALI NA UKU

### Mai Bayanin Abin Da Ke Ɗaukar Hankalin Masu Neman Ilimi A Kan Kafirta Ammawa Da Malamai

Ina farawa da neman taimako da dacewa daga Allah.

Abin da ke ɗaukar hankalin su a kan wannan ra'ayi na kafirtawa shi ne abin da suka gani cikin littattafan ilmi-kalam cewa wanda duk ya yi ƙudurin ra'ayi kaza ya zama kafiri, wanda ya jahilci kaza ya zama kafiri. Wannan ya sa suka munana zato ga aƙidojin ammawa daga cikin Musulmi, har suka kafirta su, suka nisanta su daga imani, saboda wancan abin da suka karanta cikin littattafan ilmul-kalam har suka kafirta duk wanda bai kafirta waɗannan mutane ba, saboda idan bai yi hakan ba, wai ya ƙaryata abin da ke cikin waɗancan littattafai ya kafirta domin duk wanda bai kafirta kafiri ba, to, ya zama kafiri.

Waɗannan ɗalibai ba su yi zurfin bincike ba, cewa abin da ke cikin littattafan ilmul-kalam na kafirtawa wanda malamai suka yi ittafaƙi ko suka yi saɓani a kai ana fuskantar da shi a kan jimlar jama'a, ba a fuskantar da shi a kan ɗaiɗaikun mutane. Haka ma ba su yi leƙo a kan rashin kafirta kafiri; wanda ya zo cikin waɗancan littattafai cewa yana kai mutum ga kafirci idan bai kafirta wanda ya bayyana kafirci ba ta hanyar zance ko aiki. Haka ma ba su yi zurfin bincike ba, a kan cewa hukuncin kafirci wanda ya zo cikin waɗancan littattafan yana kasancewa ne tsakanin bawa da Ubangijinsa, ba tsakanin bawa da ƴan`uwansa bayi ba.

Yana daga cikin abin da ya ɗauki hankalin waɗancan ɗalibai abin da Malam Muhammad Ɗan Umar Ɗan Abdul'aziz Ɗan Abi-Muhalli ya ce a cikin littafinsa mai suna Al-Fasal Al-Auwal min Aƙwalil-Ulama'il-mauhibati cewa, Malam Ɗan Ƙasim Ɗan Aliyu ya ce: "Duk wanda bai fahimci ma'anar kalmar shahada ba, bai rabe tsakanin halitta da Mai halitta ba (Ubangiji) kuma bai tabbatar da tashin alƙiyama ba, to, kafiri ne bamajushe, yankansa ba ya halatta haka a auren shi, sai fa idan ya tuba, ya kuma nemi ilimi sannan ya sake shiga Musulunci tare da aƙida mai inganci."

Haka ma zancen Abu Zakariyya cikin littafinsa mai suna Annawazil, cewa "Wanda duk ya rayu tsakanin Musulmi yana faɗin Kalmar shahada yana sallah yana azumi, amma bai san ma'anar kalmar shahadar ba, to, bai da

rabo cikin Musulunci, za a yi masa hukunci kamar hukuncin bamajushe, sai dai ba za a kashe shi ba sai idan ya ƙi neman ilimi. "Haka ma zancen Malam Ahmad Ɗan Isa cewa: "Wanda ya yi sallah ya yi azumi ya yi hajji amma bai san abin da kalmar shahada ta ƙunsa ba, to, shi sai in ya ƙi neman ilimi." Da kuma zancen Al-maliki cewa: "Kafiri nauyi biyu ne wanda ya yi tsaurin kai da kuma jahili, dukkan su masu dauwama cikin wuta ne babu saɓani tsakanin malamai a kan wannan. Jahilin ya san da jahilcinsa ko bai sani ba." Da kuma zancen Asshiekh Al-waglisi wanda ke cewa: "Duk wanda ya yi furuci da sheda biyu (Kalmar shahada) amma bai san abin da ta ƙumsa ba, to, babu wani malami da ke cewa shi, wannan mutum mai imani ne, haka nan wanda ya yi ƙudurin wani abu wanda malamai suka yi ittafaƙi a kan wannan abin kafirci ne, to, yin furuci da kalmar shahada ba ya amfanin shi."

Waɗancan ɗalibai ba su yi zurfin bincike ba, cewa duk zantukan waɗannan malamai ba su nufin kafirta ammawan Musulmi kai tsaye, a'a abin nufi shi ne cewa duk wanda bai san abin da kalmar shahada ta ƙunsa ba, na ma'anar asalin addini wanda Alƙur'ani da sunnah suka bayyana ƙarara, to, kafiri ne a kan hukuncin da ya shafi tsakanin shi da Ubangijinsa, haka idan ya bayyanar da kafirci, to, za a hukunta shi irin hukunci Bamaguje sai dai ba a kashe shi sai idan ya ƙi neman ilimi.

Akwai daga abin da ya ɗauki hankalin waɗancan ɗalibai a kan kafirta Musulmi, faɗar Muhammad Ɗan Umar a farkon littafina mai suna Al-fasl Al-auwal, inda yake cewa: "Ka sani cewa, kafirci wanda malamai suka yi ittifaƙi a kansa ya bayyana ga mafi yawan ammawa da mata da mafi yawan masu neman ilimi ba tare da sun lura da manufar maganarsa ba, cewa ba ya nufin kafirta ammawa Musulmi kafircin wanda ya bayyana shi ta hanyar zance ko aiki." Akwai daga abin da ya ɗauki hankalin ɗaliban kuma, zancen wannan malami cikin farkon littafinsa mai suna Al-fal Assani, inda yake cewa: "Ka sani mu mun sani nau'o'in kafirci waɗanda malamai suka yi ittifaƙi a kansu balle ma wanda aka yi saɓani a kai, wanda da yawa daga cikin masu neman ilimi ke afkawa cikinsa da kuma jahilai da mata abin ba ya lissafuwa." Waɗancan ɗalibai ba su yi zurfin tunani ba cewa, wannan malami ba ya nufin kafirta ammawa Musulmi sai dai yana nufin cewa ya sami nau'o'in kafirci waɗanda malamai suka yi ittifaƙi a kansu da waɗanda suka yi saɓani a kai duk waɗannan nau'uka biyu waɗansu mutane na bayyanar da su ta hanyar zance. Sun gano haka ne lokacin da suka yi musu tambayoyi da nufin yi musu jarabawa don aza su a kan hanya ta sawaba. Akwai daga abin da ya

ɗauki hankalin waɗancan ɗalibai faɗar wani malami cewa: "kafirai kashi biyar ne:

1. Jahilin da ya san bai sani ba
2. Jahilin da bai san bai sani ba
3. Mai kokwanton al'amuran addini
4. Mai zato a kan al'amuran addini
5. Mai wahami a kan al'amuran addini

Sai malamin ya ce "waɗannan biyar duk kafirai ne bisa ijma'in malamai." To, su, waɗancan ɗalibai, ba su fahimci maganar wannan malamin ba, cewa kafircin waɗannan kashi biyar tsakanin su da Ubangijinsu ne, bai keɓanci hukuncin duniya ba, wanda aka gina a kan zahirin shari'a domin ba mu iya sanin ɗaiɗaikun waɗannan mutane domin waɗannan nau'o'in mutane biyar sun siffantu da siffofin da zuciya ta ƙunsa siffar zuciya ko, gaibi ce, sai fa idan wani abu na kafirci ya bayyana ta halshensu.

Haka ma akwai daga abin da ya ɗauki hankalin waɗancan ɗalibai, zancen Abubakar Ɗan Muhammad Ɗan Abubakar a cikin littafinsa mai suna Hujjatul Mas'ul an Ilmittauhidi, inda yake cewa: "Misalin wanda ke faɗin kalmar shahada ba tare da sanin ƙa`idojinta ba, kamar mai jin ƙishirwa ne ya kama kiran ruwa-ruwa" sai wannan malamin ya nassanta, cewa wannan mutum kafiri ne bisa ijma'in malamai. Sai dai waɗancan ɗalibai masu kafirtawa ba su yi leƙo a kan cewa wannan malamin ba ya nufin kafirta ammawa Musulmi sai dai yana nufin cewa wanda ya yi furuci da kalmar shahada amma bai san ƙa'idojinta waɗanda Alƙur'ani da sunnah suka nassanta ba. To, misalinsa kamar mai jin ƙishirwa ya kama kiran ruwa. Wannan ba zai amfana mai komi ba. Saboda haka mai faɗin kalmar shahada ya zama dole ya san ma'anarta don ta amfane shi, kamar yadda mai jin kishirwa ya zama dole gare shi ya sha ruwa, ba ya rinƙa kiran ruwa kawai ba. Sanin ma'anar wannan kalmar shi zai amfane shi lahira, amma a nan duniya, to, za ta amfane shi ko bai san ma'anarta ba, domin za a gudanar da hukunce-hukuncen Musulunci a kansa, kuma za a ɗauke shi Musulmi matuƙar bai bayyana kafirci ba ta hanyar zance ko aiki.

Akwai daga abin da ya ɗauki hankalin waɗancan ɗalibai zancen Malam Muhammad Salihu Ɗan Abdurrahman Ɗan Sulaimi Al-auhali a cikin ƙasidarsa wadda ta shahara a cikin wannan ƙasa inda yake cewa:

1. Idan ka fita batun abin da nake gaya ma, to, saboda rashin arzikinka ne, don haka ba za ka samu saduwa da abin da kake nufi ba.
2. Kana faɗin kalmar shahada amma ba ka san ma'anoninta ba, to, kaiconka-kaiconka.
3. Domin faɗinta da kake yi bai amfanin ka da komi. Don haka rayuwarka ba ta da wani amfani idan ka rasa lura da ma'anar wannan kalma.

Waɗancan ɗaliban ba su gane nufin wannan malamin ba, cewa ba ya nufin kafirta ammawa Musulmi sai dai yana nufin idan ka bar aiki da wannan nasiha da shiryawa ba ka nemi sanin abin da Alƙur'ani da sunnah suka nassanta na asalin addinin, to, ana haramta ma saduwa da alheri da rabauta da samun ni'ima a ranar lahira. Domin faɗin kalmar shahada kawai ba ya isa wajen ingantar imani sai ka haɗa da sanin ma'anarta domin samun amfanin faɗin yana tare da sanin sharuɗɗanta. Amma a duniya faɗin kalmar shahada zai amfane ka ko da ba ka san ma'anarta ba domin za a gudanar da hukunce-hukuncen Musulunci ga mai faɗinta ko da bai san ma'anarta ba domin za a yi masa hukunci bisa zahirin abin da yake bayyanawa sai fa idan ya furta abin da ke kafirta shi.

Akwai daga abin da ya ɗauki hankalin waɗancan ɗalibai faɗar Malam Al-aujali a cikin littafinsa, Dalilil-Aƙa'id, inda yake cewa:

1. Duk wanda ya rataya ga faɗar wani malami a cikin wannan hanya ta Tauhidi, to, ya sha gurɓataccen ruwa a mashaya.
2. Sheɗan ne ya ruɗi wannan mutum ko kuma girman kai ne ya ruɗe shi don ya hana masa neman ilimi.
3. Domin babu abin da ke isa cikin abin da ya shafi tauhidi sai ilimi. Wannan shi ne abin da malamai suka bayyana.

Waɗancan ɗalibai ba su yi zurfin tunani ba ga wannan magana domin malamin ba ya nufin kafirta ammawa Musulmi, manufar maganarsa shi ne duk wanda ya yi taƙalidi a babin Tauhidi, to, ya sha gurɓataccen ruwa, domin abin da ake nema a ɓangaren Tauhidi shi ne ilimi wanda aka haɗa da bincike da tunani, ratayawa ga zancen wani ba ya isa. Ko da yake akwai saɓani tsakanin malamai amma wannan saɓani ya keɓanta ga hukuncin lahira ne amma imanin da ke isa wajen hukuncin duniya shi ne furuci da kalmar shahada kawai.

Akwai daga abin da ya ɗauki hankalinsu faɗar Malam Muhammad Al-wali a cikin littafinsa, Al-manhal, inda yake cewa: Shehu Sanusi bai yarda da maganar farko ba sai dai ya ƙarfafa magana ta biyu, daga cikin saɓanin malamai cewa wanda ya yi taƙalidi a babin Tauhidi mai imani ne ba tare da saɓo ba. Magana ta biyu ta ce shi mai imani ne amma mai saɓo wannan shi ne zancen da Malam Sanusi ya ƙarfafa.

Amma waɗancan ɗalibai ba su gane cewa malam ba yana nufin kafirta gamammun jama'ar Musulmi ba sai dai yana nufin rashin yarda da maganar farko cewa wanda ya yi taƙalidi a cikin Tauhidi mai imani ne ba tare da saɓo ba sai ya ƙarfafa cewa mai irin wannan imani kafiri ne a cikin littafinsa mai suna Al-umdah Sharhul-Kubra, sannan daga baya ya dawo daga wannan ra'ayi na cewa kafiri ne sai ya ƙarfafa magana ta biyu cewa mai taƙalidi mai imani ne amma mai saɓo. Ya bayyana haka a cikin littafinsa, Sharhul-wusɗah. Sannan duk wannan magana ana nufi da ita ne abin da ya shafi tsakanin bawa da Ubangijinsa, ba ta shafi tsakanin bawa da 'yan'uwansa bayi ba, kuma ba ta shafi zahirin shari'a ba.

Yana daga abin da ya ɗauki hankalin waɗancan ɗalibai zancen Shehu Sanusi a cikin littafinsa, Al-kubrah ,inda yake cewa: "Taƙalidi ba ya kuɓutar da mai yin sa." Da kuma faɗarsa: "Kada mai taƙalidi ya ruɗu da abin da yake yi." Da kuma zancen Malam Muhammad Attahiru Ɗan Ibrahim a cikin littafinsa, Al-kubarah, inda yake cewa:

1. Mafi yawan malamai sun tafi a kan cewa taƙalidanci ba zai isar da mai yin sa ba ranar lahira daga dauwama a wuta.
2. Domin ana tsoratar wa mai yin taƙalidi faɗawa a cikin kokwanto idan musifu sun same shi sai su kai shi ga yin ridda.
3. Idan ya dage a kan taƙalidi tare da yin ibada bai nemi ilimi ba, ana ji masa tsoron warwarewar imani sai ya zama kamar Yahudawa.

Waɗancan ɗalibai ba su yi leƙo a kan manufar maganar waɗannan malamai ba, domin ba su nufin kafirta gamammun jama'ar Musulmi sai dai suna nufin kafirta mai taƙalidi, kafircin muƙallidi kuma al'amari ne tsakanin shi da Ubangijinsa, ba tsakanin shi da 'yan'uwansa bayi yake ba. Akwai daga abin da ya ɗauki hankalin waɗancan ɗalibai faɗar Shehu Ahmadu Al-Muƙary a cikin littafinsa, Idwa'atuddujunnah, inda yake cewa: Abin nema ba zai samu ba sai da sanin abubuwan nema guda bakwai.

Waɗancan ɗalibai ba su yi leƙo a kan cewa maganarsa ba ta nufin kafirta gamammun jama'ar Musulmi sai dai malam yana nufin cewa: ba abin da ke isa wajen raddi ga masu falsafa (masu cewa talikai ma ba su da farko) sai sanin abubuwa guda bakwai, malam ba ya nufin cewa ba yana nufin cewa imani ba ya cika sai da sanin waɗannan abubuwan ba, ko da a ce abin haka yake bisa ƙaddarawa mara kyau, to, da zai zama tsakanin bawa da Ubangiji ne, ba bisa zahirin shari'a ba ne.

Yana daga cikin abin da ya ɗauki hankalin masu kafirtawa faɗar Shehu Ahmad Ɗan Abdullahi Al-jaza'iry inda yake cewa cikin ƙasidarsa:

1. Ku sani Tauhidi shi ne asalin tsira a lahira. Wannan magana tabbatatta ce gun dukkan Musulmin da suka gabata.
2. Annabawa da Manzanni gaba ɗaya sun haɗu a kan yin addini da Tauhidi a cikin addinansu.

Da kuma faɗar Shehu Sanusi a cikin sharhin ƙasidar Al-jaza`iriyyah inda yake cewa: "Dukkan Annabawa sun yi ittifaƙi a kan cewa babu tsira lahira sai da Tauhidi." Haka ma ba su yi leƙo a kan cewa maganar wannan malami ba ta nufin kafirta gamammun jama'ar Musulmi sai dai suna nufin cewa: Tauhidi shi ne asalin addini kuma shi ne asalin tsira a lahira. Annabawa sun yi ittifaƙi a kan haka. Maganar waɗannan malamai a kan sanin Ilmul-kalami ba ta taƙaita kawai a kan fahimtar asullan addini ba, waɗanda Alƙur'ani da sunnah suka nassanta. Ba za mu iya leƙo a kan wanda bai san ma'anar kalmar shahada ba, sai fa wanda ya bayyana ta hanyar magana. Akwai daga cikin abin da ya ɗauki hankalin masu kafirtawa maganar mai littafin Al-jawahiril-hisan inda yake cewa: "Duk wanda ya jahilci ɗaya daga cikin rukunnan imani guda shida, to, shi kafiri ne mai dauwama a wuta kuma Aljannah ta haramta gare shi." Wannan magana tasa ba ta nufin kafirta gamammun jama'ar Musulmi sai dai tana nufin wanda ya jahilci waɗannan rukunai ya zama kafiri tsakaninsa da Ubangijisa, a hukuncin lahira, ba a hukuncin duniya ba wanda aka gina a kan zahirin shari'a domin ba za mu iya gane wanda ya jahilci waɗannan rukunnai bisa ayyana shi sai wanda jahiltar su ya bayyana ta hanyar maganarsa, ƙari bisa ga haka maganar malamin tana nufin wanda ya jahilci waɗannan rukunnai bisa manhaji na Alƙur'ani da sunnah, ba bisa manhaji na Ilmul kalami ba.

Akwai daga abin da ya ɗauki hankalin masu kafirtawa faɗar wasu shehunai wanda Malam Abu-Imrana Al-jauraby ya faɗa a cikin littafinsa

Aƙidatul-muwahhiddin, inda ya ce: “Duk wanda bai da shedu a kan sanin ilimin Tauhidi, to, ƙafarsa ta darje cikin ramin halaka.” Ma’ana duk wanda bai san ilimin Tauhidi ba sai ya karkata zuwa ga taƙlidi, to, ya saki hanyar tsira, ya faɗa cikin halaka. To, masu kafirtawa ba su yi leƙo a kan manufar wannan magana ba domin wannan magana tana nufin kafirta muƙallidi, shi ko kafircin muƙallidi ba tsakanin bawa da ‘yan’uwansa bayi yake ba. Akwai daga abin da ya ɗauki hankalin masu kafirtawa, zancen Shehu Abu-Hamid Al-Gazali wanda Abu-Imrana Al-jauraby ya faɗa a cikin littafinsa, Aƙidatul-muwahhidin, inda yake cewa: “Farkon abin da ke wajaba bisa ga mukallafi sanin wanda yake wa bauta (Allah) sannan yin bautar, domin bai kamata yin bauta ba, kafin sanin wanda ake wa bautar, saboda haka ya zama wajibi sanin Allah da sunayenSa da siffofinSa, da sanin abin da ke wajaba da abin da ke korewa da abin da ke halatta ga haƙƙinSa. Domin kada ka bauta wa Ubangiji a kan wata siffa wadda ta koru gare Shi, ibadarka ta tafi ga banza. Allah Ya kiyaye mu. Haka ma yana daga cikin abin da ke ɗaukar hankalin masu kafirtawa zancen Malam Muhammad Al-ɗagugi a cikin littafin Shafiyatul Kulub inda ya ce:

Yaya kake bauta wa wanda ba ka sani ba, wannan aikin naka hasararsa ta girma kuma ta yi yawa. Masu kafirtawa ba su fahimci ma’anar waɗannan maganganu ba, domin ba su nufi kafirta Ammawan Musulmi ba. Waɗannan maganganu ba bisa zahirinsu suke ba, domin zahirin waɗannan magangannu shi ne bawa ba ya bauta wa Ubangiji sai ya san abin da ke wajaba da abin da ke koruwa da abin da ke halatta ga Ubangiji kamar yadda masu ilmul-kalam, suka bayyana. Malamai sun yi daidai a kan cewa wannan ra’ayi kuskure ne domin kafiri idan ya musulunta daidai lokacin sallah, za a umurce shi da yin ta nan take. Haka ma idan lokacin azumi ne, wannan bisa ijma’in malamai. To, idan ka fahimci wannan, za ka gane cewa maganar waɗancan malamai ba bisa zahirinta take ba, domin idan an ɗauke ta a kan zahiri, to, za ta kai ga kure. Saboda haka ka sani manufar waɗancan malamai ita ce bada labari a kan mukallifi ya yi ƙoƙari wajen inganta imani ta hanyar neman ilimi da zai ƙarfafa aƙida tasa, idan bai yi haka, ba ana ji masa tsoron faɗawa a cikin kafirci sai fa idan Allah ya kiyaye shi, domin haka Imamul Gazali ya ƙara da cewa: “Tana yiwuwa ka yi ƙudurin wata siffa ga Ubangiji alhali Ubangiji ya saɓa wa wannan siffar sai ibadar da kake wa mai wannan siffar ta tafi ga banza domin shi ba Allah ba ne, sai fa idan Allah ya tsare bawa daga faɗawa ga irin wannan haɗari.”

Akwai daga abin da ya ja hankalin masu kafirtawa faɗar wasu Shehunai wadda Malam Abu-Imrana Al-jauraby ya faɗa cikin littafinsa, Aƙidatul muwahhidina, inda ya ce: "Ibada ba ta inganta sai bayan sanin wanda ake bautawa, haka nan sanin shari'a sai bayan sanin wanda ya wajabta, haka nan sanin littafi sai bayan sanin wanda ya saukar da shi, haka nan sanin Annabi sai bayan sanin wanda ya aiko shi." Masu kafirtawa ba su gane cewa wannan magana ba ta nufin kafirta Ammawan Musulmi, abin nufi da wannan shi ne ibada ba ta inganta sai bayan sanin Allah sai dai ba bisa manhajar da masu ilimul-kalami suka shata ba. Duk wanda ya yi ƙudurin haka, to, ya jahilci shari'a sannan kuma sanin Allah ga zuciya yake. Dun haka Shehu Sanusi ya faɗa a cikin Sharhul-Wusɗa inda yake cewa: "Bai kamata mu munana zato ga wani mutum daga cikin Musulmi ba, daga cikin gama-garin mutane yake, ko waninsu domin sanin Allah ga zuciya yake sai idan abin da zuciyarsa ta ƙunsa ya bayyana ta hanyar maganar ta mugunyar aƙida, a nan ya wajaba a tausasa wajen koyar da shi domin gusar da wannan cutar gare shi. Akwai isuwa ga abin da muka faɗa ga duk wanda Allah ya haskaka basirarsa. Allah Ka gwada muna gaskiya, Ka ba mu ikon bin ta; Ka gwada muna ƙarya, Ka ba mu ikon nisantar ta.

## FASALI NA HUƊU

### Yana Bayani A Kan Cewa Malaman Sunnah Sun Yi Ijma'i A Kan Hukunce-Hukuncen Shari'a An Gina su A Kan Zahiri

Ina farawa da neman muwafaƙa ga Allah, ka sani ba a kafirta duk wanda ya bayyana Musulunci, kuma ba a munana zato gare shi, wannan mutum ya zama daga cikin gama-garin mutane ne ko kuma waninsu, wannan shi ne abin da Alƙur'ani da sunnah da ijma'a suka bayyana.

Allah Maɗaukaki ya ce a Alƙur'ani mai girma:

﴿وَلَا تَقُولُوا۟ لِمَنْ أَلْقَىٰٓ إِلَيْكُمُ ٱلسَّلَـٰمَ لَسْتَ مُؤْمِنًا﴾ النساء: ٩٤

*"Kada ku ce wa wanda ya yi muku sallama kai ba mai imani ba ne." Nisa'i:94*

A sunnah kuma Imam Al-Bukhari ya ruwaito daga Anas Manzon Allah (saw) ya ce:

(من صلى صلاتنا واستقبل قبلتنا وأكل ذبيحتنا فذلك المسلم الذي له ذمة الله وذمة رسوله فلا تخفروا الله في ذمته)

*"Wanda duk ya yi irin sallarmu ya fuskanci alƙiblarmu ya ci yankanmu, to, wannan shi ne Musulmi wanda ke da alƙawarin Allah da ManzonSa, don haka kada ku warware wa Allah alƙawarinSa."*

Haka ma Imamul Buhari ya ruwaito daga Anas Allah ya yarda da shi, Manzon Allah (saw) ya ce:

(أمرت أن أقاتل الناس حتى يقولوا لا إله إلا الله وإذا قالوها وصلوا صلاتنا واستقبلوا قبلتنا فقد حرمت علينا دماؤهم وأموالهم إلا بحقها وحسابهم على الله)

*"An umurce ni in yaƙi mutane har sai sun faɗi Kalmar shahada, idan sun faɗe ta, kuma sun yi irin sallarmu, suka fuskanci alƙiblarmu, to, jininsu da dukiyarsu sun haramta gare mu sai dai hisabinsu kuma yana ga Allah"*

Da kuma hadisin da Imamul Buhary ya ruwaito daga Abu Sa'id Al-Khudry, Manzon Allah (saw) ya ce:

(أني لم أومر أن أنقب عن قلوب الناس ولا أشق بطونهم)

*"Ba a umurce ni ba da yin tonon zukatan mutane da tsage cikakkansu."*

Amma ijma'i kuwa, malaman Ahlul-sunnah sun yi daidai a kan cewa duk wanda ya yi furuci da Kalmar shahada, to, za a gudanar da hukunce-hukuncen Musulunci a kansa kamar Auratayya da yi masa wanka da Sallah idan ya mutu da turbuɗe shi a maƙabartar Musulmi, matuƙar bai bayyana kafirci ba, a aikace kamar yin sajada ga gunki ko da zance kamar musun wani wajabci da Manzon Allah (saw) ya zo da shi.

Malam Abdulsalami Ɗan Ibrahimu Al-laƙany ya ce cikin littafinsa, Ithaful-muridi-bijauharatil tauhidi, "Imani wanda ke isar mutum ga rayuwar duniya shi ne yin furuci da Kalmar shahada don haka wanda duk ya yi furuci da ita, to, za a gudanar da hukunce-hukuncen Musulunci gare shi a duniya, ba za a ce masa kafiri ba sai fa idan ya bayyana abin da ke kafirta shi kamar yin sajada ga gunki" Malam Alƙaly Iyad ya faɗa cikin littafinsa, Al-ashafa, inda yake cewa: "Hukuncin Musulunci ya rataya ga shedar halshe ga duk abin da ya rataya ga hukunce-hukuncen duniya, wannan shi ne abin da shugabannin Musulmi suke aiki da shi, domin ba a ba ɗan-adam iko ga abin da ya shafi gaibi ba, ba a umurce shi da yin bincike a kan gaibi ba, har ma Manzon Allah ya yi hani a kan yin hukunci ga abin da yake gaibi ne kuma ya yi zargi a kan haka." Ya faɗa cikin wani hadisi ya ce:

(هلا شققت عن قلبه)

*"Me ya sa ba ka tsaga zuciyarsa ba"*

Shehu Sanusi ya faɗa cikin littafinsa mai suna Al-umda Sharhul-Kubra inda yake cewa: "Hukunce –hukuncen duniya, an gina su a kan zahirin shari'a a kan haka. Sunnar Manzon Allah ta tafi a kan rashin binciken zukatan mutane, domin wannan asirin sai lahira zai bayyana, yinin da za a bayyana asirai." Sai na ce (inji Shehu Usmanu) idan ka fahimci abin da ya gabata, to, za ka san cewa duk wanda ya bayyana Musulunci da faɗin Kalmar shahada, to, ma'amala da shi ta halatta bisa hujja ta Alƙur'ani da sunnah da ijma'in malamai matuƙur bai bayyana kafirci ta hanyar zance ko aiki ba. Wannan hukuncin haka yake a zamanin da ya gabata domin matsala ce wadda ake gabatar da nadiri (abin da ya ƙaranta) a kan galibi (abin da ya yawaita) a cikinta, domin rahama ga al'umma. Malam Ahmad Ɗan Aliyu Ibn

Abdurrahmana Al-manjory ya ce cikin Sharhu Manhajil-Muntahab. (Al-Gazali ya ce yana daga cikin abin da ake gabata nadiri kasancewa aure mustahabbi don fatar haihuwar Musulmi Sahihi, domin abin da yake galibi a wannan lokaci shi ne jahilci da rashin bin shari'a da yawan saɓo, to, da za a yi hukunci a kan wannan galibi, to, da za a haranta aure, musammam idan an ɗauki zancen mai kafirta muƙallidi tare da haka malamai sun tafi a kan halatta aure domin fatar samun salihi sai aka gabata nadiri a kan galibi.

Shehu Muhammad Ɗan Umar Ɗan Abdul'aziz Abu-muhaly ya yi taraddudi a kan wannan matsala cikin hukuncin wanda halinsa ya zama rufe daga cikin Ammawan Musulmi, cewa ko ana gabatar da abin da yake galibi a kan nadiri, sai a haramta auren irin wannan mutum a kuma haramta cin yankansa, koko ana lura da nadiri sai a halatta, waɗancan abubuwa gare shi. Wannan malamin ya faɗa cikin littafinsa mai suna Al-fasalul-Auwal inda ya ce kafircin irin wannan mutun bai bayyana ba, ga jama'ar da suka gabata don haka suka halatta aurensa da yankansa amma wannan zamani wanda jahilci da kafirci suka yi yawa a cikinsa ba za a yi ƙiyasin sa da wancan zamani ba, saboda haka malamai suka yi taraddudi a kan hukuncin wanda halinsa ya zama rufe, suka ce shin ko ana gabatar da galibi a kan nadiri? Idan an ɗauki wannan ra'ayi sai a haramta aurensa da yankansa. Idan kuma an gabatar da nadiri a kan galibi, to, sai a halatta su. Wannan ra'ayi kuma shi ne mafi ƙaranci. Wannan malamin ya ce mun kasance muna sayen nama ga wanda muka sanar da shi tauhidi da aƙida amma muna taraddudi ga wanda halinsa ya zama rufe amma wanda kafircinsa ya bayyana, to, babu wata magana game da shi sai na ce (inji Shehu Usmanu) "Ban ga wata Magana ba sai wannan malamin ya ci gaba yana cewa "duk wanda ya mutu kafiri zai dauwama wuta babu saɓani tsakanin malamai a kan haka ko da ba wanda ya san da shi sai Allah" Wannan malamin ya faɗa cikin wani littafinsa, inda ya ce: "Ka lura da faɗar malami a cikin babin ciniki inda suke cewa wanda ya yi da'awar ingancin ciniki shi ke da magana, da sharaɗi idan fasadi bai zama galibi ba, ka kuma lura da maganar malamai cikin abin da yake galibi idan ya gitta wa abin da yake shi ne asali."

Shehu Usmanu ya ce wannan ra'ayin yana umurni a kan ɗaukar Ammawan Musulmi a kan galibin al'amari da kuma yin yanke a kan kafircinsu, to, ban ga wanda ya tafi a kan wannan ra'ayi ba sai jahilan masu neman ilimi waɗanda suka tafi a kan kafirta Ammawan Musulmi waɗanda ba su yi leƙo a kan abin da masu ilmul-kalam suka faɗa ba. Haka kuma suka

kafirtar da wanda bai yi iƙirari a kan kafircinsu ba. Shehu Usmanu ya ce "Mun yi cikakken bayani cikin littafinmu mai suna Nasihatu Ahli Zamani mun bayyana abin da zai warkar da wannan matsalar kuma mun faɗa farkon wannan fasali cewa duk wanda ya bayyana Musulunci da yin Kalmar shahada, to, yin ma'amala da shi ta halatta, matuƙar bai bayyana kafirci ba ta hanyar zance ko aiki, yana cikin Ammawan Musulmi ko keɓaɓɓunsu, ko da cikin zamanin ƙarshe yake, zamanin da jahilci ya yawaita, kamar yadda Malam Karafi ya bayyana." Saboda haka Shehu Sanusi ya ce cikin Sharhul-Wusɗa "Bai kamata mu munana zato ga imanin wani Musulmi daga cikin Ammawan Musulmi ko waninsu saboda sanin Allah ga zuciya yake, sai fa idan ya bayyana cewa shi mai ɓoye kafirci ne, To, a nan ya kamata a tausasa wurin yi masa nasiha da sanar da shi aƙida ingantatta."

Haka ne Shehu Al-hassan Ɗan Mas'udu Al-yosy ya bada amsa ga mutanen garin Sajalmasa sanda suka yi masa tambaya, a kan wane ne ya kamata a ci yankansa a kuma ba shi aure kuma a rufe shi a maƙabartar Musulmi, matuƙar wani abu bai bayyana ba wanda ke saɓa wa zahirinsa sannan mutane suna tambaya su wanene ammawa? Malam Muhammad Ɗan Umar ya faɗa cikin littafinsa, Al-fasalul Auwal, ya ce "Wallahi ba na iya lissafe wanda na same su suna kafirai daga cikin ɗalibai, balle Ammawan Musulmi da mata da bayi sai ya ce ban zaton haka sai da Allah ya gwada min wani mutum wanda ya yi ta sauke Alƙur'ani, wata rana sai ya karanta addu'a ya ce: "Alƙur'ani, Jibrilu ne ya saukar da shi ga Imam Aliyu, sai aka ce masa, to, shi, Imam Aliyu Manzon Allah ne? Sai ya ce na'am sai aka sake tambayarsa wane ne Ubangijinka sai ya ce Shugaba Muhammad (saw)." Malam ya ce sai muka yi jarrabawa ga ɗalibai da ammawa, muka sami jama'a da yawa ba su san ma'anar kalmar shahada ba, ba su san ma'anar kaɗaitar Allah ba, ba su san abin da ake nufi da manzanci ba.

Shi, wannan malamin, ya faɗa cikin wani littafinsa: "Wani daga cikin mutanen garinmu, an ba shi mata tana sallah domin har tasbaha tana da, bai yi mata jarrabawa ba, saboda zaton ba jahila ta ba. Wata rana sai muka tambaye ta game da Manzon Allah sai ta ce "Manzon shi ne ya halicci duniya, kuma shi ɗan Allah ne?" Wannan malamin ya ce: "Akwai wani mutum wanda ke wa mutanen yankan layyarsu sai wata rana na yi mishi tambayoyi sai na same shi kafiri don haka sai na hana shi ci gaba da yin yanka." Wannan malamin ya faɗa cewa wannan jarrabawa alhairi ce idan ta tayar da fitina, to, sai ka taƙaita ta ga waɗanda ke cikin umurninka da wanda

kake da iko a kan shiryar da shi. Wannan ra'ayi na Malam Ɗan Umar ya yi daidai da ra'ayin wasu daga cikin malamai waɗanda ke cewa: "Idan ka yi kokwanto a kan yawaitar kafirci cikin mutane, to, ka yi masa jarrabawa, wanda ya hana yin haka, to, ya sabbaba dagewar mutane a kan kafirci." Sanda wannan malamin ya buɗe ƙofar tambaya ga ammawa a kan aƙidarsu, to, wasu daga cikin ɗalibai sun dangana ƙarya gare shi har suka danganta shi ga abin da bai faɗa wa Musulmi ba. Don ya faɗa a wani littafinsa: "Sun yawaita kore mutane gare ni har suka faɗi abin da bai faɗuwa ga Musulmi, kamar haramta ruwa da nono tare da cewa sun san muna shan waɗannan Kai har sun kai ga cewa mun ce duk mutane ɗiyan zina ne, Allah ya gafarta muna sannan Allah ya gafarta musu wannan ƙaryar da suka yi. Ya ce har Shehu Sanusi tare da ɗaukakar matsayinsa da wulayarsa an yi masa ƙarya, to, balle mu."

Shehu Usmanu ya ce wannan tambaya da jarrabawa wadda Ɗan Umar ya tafi a kai shi da waninsa daga cikin malaman wannan zamani ya saɓa wa aikin Manzon Allah da Sahabansa da waɗanda suka biyo bayan su cikin kowane zamani da lokaci domin maganar Alkaly Iyal wadda ya yi cikin Ashafa ta gabata cewa hukuncin Musulunci ya rataya ga mutum da zarar ya yi furuci da kalmar shahada ga duk abin da ya rataya ga hukunce-hukuncen duniya. Wannan shi ne abin da shugabannin addini da masu hukunci suke a kai domin ba a ba ɗan'adam dama ba a kan binciken asirin mutane, ba a hore su a kan wannan bincike ba asali ma Manzon Allah ya yi hani a kan yin irin wannan bincike kuma ya yi zargi a kansa har ya ce

(هلا شققت عن قلبه)

***"Me ya hana ka tsaga zuciyarsa, ka gani idan babu imani a ciki"***

Shehu Usmanu ya ce abin da yake sannane a babin yin nasiha ga ammawa shi ne sanar da su shiriya ta yadda hankalinsu ke ɗauka ba tare da bincike ko yi musu tambaya ko jarrabawa ba, domin da yawa mai yin tambaya zai dace da mai in-ina ko mai ɗimaucewa ko wanda bai iya bayani ba, domin tambaya tana sa wani ya rikice kamar yadda Shehu Al-hasan Al-yosy ya ce a cikin bayaninsa inda yake cewa: "Na shuɗe da garin Sajalmasa sai na tarar da wata irin fitina ta faru tsakanin ɗalibai da Ammawan Musulmi domin su, ɗalibai, sun yi dubi a kan maganganun wasu shugabanni masu lizimta yin dubi a kan ilimin tauhidi, kuma suna tsoratar da jahilan da masu yin taƙalidi. Wannan ya sa suka fara wa jama'a jarrabawa da tambayoyi a

kan aƙidarsu, suna lizimta musu bayyana abin da shi ne sawaba, da yawa za su ci karo da wanda bai iya bayani ba, ko kuma wanda ya jahilci wani hukunci wanda zai sa a soki aƙidarsa, a munana zato gare shi sai a ɗora watsa jahilcinsa ko kafircinsa tsakanin mutane."

Al-yosy ya sake faɗi ya ce: "Shugaban wannan fitina ya zo wurina wata rana sai ya tambaye ni a kan abin da suke a kai sai na ba shi amsa, kuma na yi masa nasiha na ce masa mafi yawan ƙungiyoyin addinin da suka ɓace sun ɓace ne ta wannan ilimin saboda haka idan kana nufin ka amfani mutane, to, ka tabbatar da su a kan aƙidar addini daidai yadda hankalinsu ke ɗauka; ka kuma koyar da su addini yadda suke fahimta kamar yadda hadisin Annabi ya bayyana, kuma ya kamata ka bar wannan jarrabawa da tambayoyi da zurfin bincike wanda sunnar ma'abuta addini cikin kowane zamani ba ta tafi a kai ba. Nan take sai wannan Magana ta ratsa shi ya cirata daga wancan abin da yake a kai."

Malam Ɗan Aburrija ya ce: "Wanda duk ya nufi ƙulla aure tsakaninsa da wanda ya bayyana Musulunci amma yana tattare da jahilci mai iya kai ga kafirci, to, ya wajaba gare shi yin bincike haka ma wanda ya yi nufin cin yankansa sai dole ya binciki aƙidarsa." Wani daga cikin malamai ya ce: "Ya kamata ga wanda ya yi aure kar ya sadu da matar sai ya binciki musuluncinta da imaninta. Idan ta yi bayani to, ta zama matarsa, idan ta kasa, to, ta nisanta gare shi." Wannan malamin ya ce: "Da mutum ya auri ƙaramar yarinya sai ta balaga kuma ta kasa bayanin abin da shi ne Musulunci, to, ta nisanta gare shi."

Haka nan abin da ya zo cikin Al-yami'ul Kabir da Al-muhidu da Al-hawy da Gunya da Al-fatawa da Al-zahira da Fuslul-imady cewa, "idan mace ta balaga sai aka biɗi ta siffanta Musulunci sai ta kasa, to, ta nisanta ga mijinta" Shehu Usmanu ya ce wannan akwai rashin fahimta cikin wannan domin mafi yawan ammawa da ke rayuwa cikin ƙasar Musulmi, to, ana halittar su a kan imani ko da sun kasa bayani da halshensu, saboda haka ba mu wajabta musu yin bayani ko bincike a kan dalilai, ba ka lura cewa ammawa, an halicce su a kan sanin aikin gaɓɓai tare da cewa ba su iya cikakken bayani a kan haka. Malam Abdul'aziz shi ya bayyana wannan har ya ƙara da cewa: "Wani daga cikin magabata ya ce: Bai kamata ba yin irin wannan tambaya ga ammawa kamar a ce: Mene ne Musulunci? Mene ne imani? Sai dai a yi masu bayanin haƙiƙanin Musulunci da imani da abin da

ke wajaba ga haƙƙinsu sai a ce masa ka gasganta wannan idan ya ce na'am, to, ya isa ga halaccin ma'amala da shi a matsayin Musulmi."

Shehu Sanusi ya faɗa a cikin littafinsa, Al-wusɗa, ya ce "da yawa daga cikin malamai ba su iya bayanin abin da ke cikin zukatansu na ilimi, to, balle ammawa." Ya Allah Ka gwada muna gaskiya Ka ba mu ikon bin ta; Ka kuma gwada muna ɓata, Ka ba mu ikon nisantar ta.

## FASALI NA BIYAR

### Mai Bayani Cewa Ɓata Ba Za Ta Game Aƙidar Ammawan Musulmi Ba Har Alƙiyama Ta Tsaya.

Malam Abdulwahab Ash-sha'arani ya ce a cikin Littafinsa mai suna "Al-ƙawa'idul Kashgiya." Na ji Malaminmu kuma Malamin Musulunci, 'Zakariyal Al-ansari' Allah ya yi mai rahama yana cewa: "Aƙidun gama-garin mutane ingantattu ne bisa ga ijma'in masana shari'a." Baban Mansur Almaturdi ya ce: "Malamai sun yi ijima'i a kan gama-garin mutane muminai ne masana Ubangijinsu, kuma su ne mafi yawan 'yan aljanna kamar yadda hadisai suka nuna da ijma'in Malamai. A kan haka ne Malam Ahmad Ɗan Zakariya ya yi nuni a cikin littafinsa mai suna Muhassilul Makasidi da cewa Malan Abu Mansur ya ciranto Ijma'in masana gaskiya cewa gama-garin Musulmai masu Imani ne masana Ubangiji ne kamar yadda ya zo a cikin mafi yawancin hadisai cewa su ne mafi yawan 'yan aljanna."

Malam Manjuri ya ce a cikin littafinsa mafi yawan 'yan aljanna gama-garin mutane masu imani, nuni zuwa ga zancen Manzon Allah. Wasu malamai sun cirato da ƙarin cewa: "Mafi yawan 'yan aljanna su ne masu natsuwa da hankali."

Sannan Malam ya ce wannan hadisi yana nuni zuwa ga gama-garin Musulmi domin su, rafkanannu, ne daga saɓon Allah, iliminsu bai kai zuwa ga su bambanta wasu al'amurra ba ballantana su kasance cikin 'yan illiyin, ba su kauce wa hanya ba, ballantana su ɓace da kafirci ko da bidi'a, Kalmar "albillah." Janiko kuma tana cikin lafuzza masu nuni ga mafi yawan Musulmai saboda haka maƙasudi idan ka ce wannan hukunci yana nuni ga mafi yawan Musulmi ga zahiri kamar yadda yake nunawa wannan ba ya nuni ga mafi yawa a cikin gama-garin Musulmai na cikin kowane zamani domin wannan ba ya nuna gamowa idan ya inganta an hukunta haka gare shi. To, ya zama dole a keɓance shi da koro Jahilai. Malam ya ce gamewa tabbatatta ce da lafazin sai a yi hukunci gare su da abin da lafazin ya nuna ɗaukar su duk a kan ɓarna saboda ta bayyana, to, hakan abin musu ce, kuma sai a canza ta da abin da ba a musu domin wannan yana daga cikin al'amurra masu sauƙi ba masu wahala ba domin in ba haka ba al'amarin zai iya kai zuwa ga halaka.

Malan Manjuri ya ce idan ka ce sa alif da lam a cikin Kalmar "albillah" don nuna gamewa ne kuma shi mai nuni ne a kan mafi yawan

waɗanda suka gabata sai dai ba mu miƙa cewa gama-gari a cikin mutane yana nuni ga mafi yawan mutane a cikin yana nuni ga mafi yawan mutane a cikin kowane zamani har ya ɗauki mafi yawan zamunna. Mun yarda cewa gama-gari a cikin mutane yana nuni ga mafi yawan zamunna sai dai ba mu da'awar keɓantuwar da fitar da mafi yawa daga cikin wannan zamani, saboda fatawar aƙida mafi yawa daga cikinsu da rashin tabbacinsu a kanta ko da ko da ratayuwa balle a kan sani; amsa ingantarciyar magana ita ce mafi yawa a cikin mutane yana nuni a kan mafi yawa a cikin zamunna kamar yadda ya tabbata a cikin Usulul fiƙihi domin lafazin gama-gari ne ga mafi yawa a cikin kowane zamani. Kuma mai nuni a kan kauce mata sai da hujjah kuma ba ya kamata a fitar da mafi yawan Musulmi sai wanda aƙidarsa ta lalace a cikin wani sashe ba ga dukkan lamari ba. Ɗaukar dukkan Musulmai a kan ɓata saboda ɓacewar wani sashe daga cikinsu ba ya inganta a hankali ko kuma abin da aka cirato idan ɓatar ɗayansu ta bayyana. To, wannan abin ƙyama ne ya zama dole a canza shi idan kuma ba ta bayyana ba yana nan a matsayinsa na asali da shiga ƙarƙashin hadisin da ya gabata domin canza ɓata yana kasancewa ne da abin da mai saɓon ke saɓo kuma ba zai yi musunsa ba na hujjoji bayyanannu masu sauƙi, makusantan jahillai kada a haɗa su da fassarar malaman Ilmul Kalam waɗanda manufa ba za ta tabbata a gare su ba kada a kawo wasu rikice-rikice ko da za a fita daga gare su domin jahili ba ya ƙara komai game da ita sai ɓata, Ya Allah Ka gwada muna gaskiya, gaskiya ce Ka azurta mu da yin aiki da ita; Ka gwada muna ƙarya, ƙarya ce Ka azurta mu nisantar ta.

## FASALI NA SHIDA

### Mai Bayani A kan Yarda Da Tauhidi Wajibi Ne Ga Al'umma

Ina mai neman dacewa ga Ubangiji. Ka sani haƙiƙa Allah Maɗaukakin Sarki bai sa bautarmu a cikin tauhidi ba da abin da idanu ke gani na haruffa waɗanda ake rubutawa a cikin Alluna da littattafai. Haka kuma Bai sa bautarmu a cikin abin da kunnuwa ke ji ba na sautuka, hakan Bai sanya ta ba a cikin abin da bakuna ke furuci da shi ba na lafuzza. Haƙiƙa, Allah Maɗaukakin Sarki ya sanya bautarmu a cikin fannin tauhidi da abin da zukata ke ƙudurta shi na asallan addini waɗanda aka nassanta a cikin Alƙur'ani da Hadisi. Ita, bautar, wajibi ce a cikin fannin tauhidi kaɗai, ba a cikin Ilmul Kalam ba, domin ita ce abin da magabata suke a kan sa da kuma malaman baya. Abin da yake wajibi ga al'ummah ta tabbatar da kaɗaita Allah a cikin zukata, ba fahimtar lafazin ba kawai, duka ɗaya ne ta hanyar Alƙur'ani mai girma ko Hadisi ko maganganun magabata Musulmai.

Malamin Musulunci Al-sayid Al-hasan Dan Mas'udu Al-yusi ya ce a cikin littafinsa mai suna Al-muhadarat: "Jahilcin ɗalibai ya watsu a cikin garin Sajalmasah, tabbas ɓannarsu ta bayyana a cikin kaɗaita Ubangiji suka shiga suna tabbatar da Aƙida ga mafi yawan Musulmai, sai labari ya watsu a wurin wani cewa duk wanda bai shagaltu da ilimin kaɗaita Allah ba a kan tsarin da suka tabbatar, to, shi, kafiri, ne. Kuma labari ya watsu a wurinsu cewa duk wanda bai san ma'anar Kalmar shahada ba ta korewa da tabbatarwa a kan tsarin da masana suka tabbatar, to, shi, kafiri, ne" saboda haka tsoro mai yawa ya shiga ga mafi yawan Musulmi."

Lokacin da na shiga garin Sajalmasa, mutane suka zo min gayya-gayya suna kai kokensu ga wannan al'amari sannan ba kowane mutum zai kai matsayin fahimtar maganganun malamai ba. Sai na ce musu haƙiƙa Allah Maɗaukakin Sarki ya sanya bauta gare ku ta hanyar ƙudurta gaskiya a cikin zukatanku, shin ba ku shaida Allah Maɗaukakin Sarki samamme ne ba? Sai suka ce haka ne. Shin ba ku san Shi kaɗai yake a cikin mulkinSa, ba Ya da abokin tarayya tare da Shi, duk wani abin bauta wanda ba Shi ba ƙarya ne sai suka ce haka ne. Sai ya ce wannan shi ne tabbas a wurinmu babu shakka a cikinsa. Sai na ce musu wannan shi ne ma'anar Kalmar Shahada wadda ake nema daga gare ku, ku yarda da ita duka ɗaya ne. Kun fahinci wannan daga ma'anar lafazin ko a'a domin Kalmar Larabci ce ba ta da wata manufa a cikin Hausa. Ya ishi bawa ya fahimci manufarta kuma ya yi amfani da ita. Haka

nan sauran sha'anin tauhidi wanda ake neman a ƙudurta shi, ba a sharɗanta a gare ku ba fahimtar lafazi wanda ake magana da shi ba a cikin littattafan malamai ko cimma iyakokinta domin fahimtar waɗannan maganganu, wani ilimi ne na daban ba a ƙallafa wa gama-garin mutane ba fahimtarsa; a lokacin da na karɓa musu da wannan amsa sai suka juya suna masu godiya ga Allah.

Saboda haka Shaihin Malami Sanusi yana cewa a cikin littafinsa, Al'umda Sharhul Kubra: "Wace mashiga ga lafazi wanda aka aza ga wani abu na tauhidi har a lazimci daga jahiltar wani abu ne na tauhidi ya mayar da maganar alfahari ya ce maganarsa wannan maganar waɗanda wahami ya kama. Ya ce tauhidi, ana sanin sa ne ta hanyar zurfafawa ko wasu fassarori waɗanda malaman zamani suka zo da shi amma magabata ba su kula da waɗannan ma'anoni ba domin manufa ita ce sanin gaskiya da abin da yake lazimtar ta kawai. Saboda haka duk abin da ya taho ta lafazi ko ba da lafazi ba da wata magana keɓantatta kuma ba da ita ba idan manufa ta cika babu buƙata zuwa ƙari. Amma malaman zamani sun farar da wasu fassarori masu wahala a lokacin karatu da koyar da shi domin sanin gaskiya, an tsayar da shi a kansu sai na ce ya gabato cewa abin nema dole ga al'umma shi ne samun malaman tauhidi waɗanda aka faɗa a cikin Alƙur'ani da sunna a cikin zukata ba ilimin jayayya ba."

Abin da ke bayanin waɗannan cewa talikai tun daga al'arshin Allah zuwa ƙasa samammu ne Shi ya samar da su da ikonSa; Ya fitar da su duka daga rashi zuwa samuwa. Shi, Allah Maɗaukakin Sarki, Mai wajabcin samuwa ne Magabaci ne ba Shi da farko Wanzajje ba Ya da ƙarshe; Ya saɓa wa duk talikai; Shi ba jiki ba ne ba Ya da siffa ta jiki ba Ya da sashe ba Ya da wuri; Samamme ne kafin talikai; Mawadaci ne kai tsaye; Shi kaɗai ne a cikin zatinSa; ba Ya karɓar rabuwa; Shi kaɗai ne a cikin siffofinSa; wani ba ya siffantuwa da irin siffofinSa/ Shi kaɗai ne a cikin ayyukanSa babu abin da ka tasiri a gare Shi saboda haka mala'iki ba ya tasiri a wajen siffanta abu ko kashe shi. Annabi ba ya tasiri wajen shiryar da wani; ɗayantaka ba ta jayo dauɗa ko ƙishirwa. Haka nan rana ba ta da tasiri wajen zafafar da ruwan alwalla ko busar da ɗanye; tufafi ba su da tasiri wurin suturtar da abu; magani ba ya tasiri wurin warkarwa babu wani abu mai tasiri wurin mutun sai da ikon Allah.

Allah Maɗaukakin Sarki Mai iko ne da ikonSa; Mai nufi ne da nufinSa; Masani ne da saniSa. Rayayyne da rayuwarSa; Mai ji ne da irin

jinSa ba da kunnuwa ba ko fatunsu ko ƙusurwar da ke shiga cikin kai; Mai gani na da irin ganinSa ba da ijjiya ba; Mai magana ne da irin maganarSa ba da harshe ko leɓɓa ba, Wanda ya siffantu da dukkannin siffofin kamala; Mai zaɓi ne wajen aiki ko barinsa. Yana wajaba ga haƙƙin manzannin tsira da amincin Allah su tabbata a gare su gaskiya da riƙon amana da iyar da saƙo da cikakkar kamala irin ta ɗan'dam. Yana koruwa ga haƙƙinsu, ƙarya da yaudara da ɓoye wani abu na Manzanci da naƙasa irin ta ɗan'adam. Yana halatta ga haƙƙinsu ci da sha da aure da saye da sayarwa da rashin lafiyar da ba ya kai zuwa ga tawaya da sauran al'amurran da ke gitta wa mutune.

Mala'iku dukkansu tsararru ne ga dukkan saɓon Allah, su ba maza ba ne kuma ba mata ba ne ba su ci ba su sha, littattafan sama dukkaninsu gaskiya ne; mutuwa da Ajali gaskiya ne; tambayar Munkaran da Nakiri gaskiya ce; Azabar ƙabari da ni'imarsa gaskiya ne; ranar Alƙiyama, gaskiya ce; tayar da matattu a cikin wannan yini na alƙiyama, gaskiya ce; tara mutane a cikin yinin Alƙiyama, gaskiya ne, bayar da littattafai, gaskiya ne; auna ayyuka gaskiya ne; yin Hisabi gaskiya ne; shimfiɗa siraɗi gaskiya ne; tafkin alkausara, gaskiya ne; ceto, gaskiya ne, wuta da dawwamarta tare da mutanenta, gaskiya ne; ganin muminai ga Ubangiji, gaskiya ne. Dukkanin abin da manzanni suka zo da shi tun daga Annabi Adamu har zuwa Annabi Muhammadu (saw) gaskiya ne. Waɗannan su ne tushen tauhidi waɗanda Allah ya yi bayani da ManzonSa da waɗanda muka ji Allah Maɗaukakin Sarki ya yi bayaninsu kuma Manzon Allah ya tabbatar da su a cikin sunnoninsa kamar yadda muka bayyana haka a cikin littafinmu mai suna Mira'tuɗullabi wa umdatul ulma'i. Yana wajaba a kan kowane baligi ya fahimci ma'anoninsu kuma ya yarda da su. Malam Muhammad ya ce ka sani wanda duk ke koyar da mutane mabuƙaci ne zuwa ga fahimta don ya bayyana gaskiya ga mutane ga abin da suke fahimta domin abin nema saka tauhidi a cikin zuciya ba haddacewa.

# FASALI NA BAKWAI

## Ga Bayanin Duk Fassarar Malaman Ilmul Kalam Da Ambaton Dalilinsu Yana Daga Cikin Farilla Ta Isuwa.

Ya gabata abin da yake wajaba ga bayi a cikin ilimin Tauhidi shi ne sanin asulin addini kaɗai. Malam Abdulrahman Suyuɗi yana cewa a cikin littafinsa mai suna "Anniƙaya," ilimin tauhidi ilimi ne mai bayani a kan abin da yake wajaba ga bayi. Malan Abdulsalami ɗan Ibrahim ya ambaci ma'anar ilmul kalam a cikin littafinsa mai suna "Itihaful-muridi bi jauharatil Tauhid" "Ilmi ne da ake samun dama da shi a kan tabbatar da shikashikan addini ga wani da lazimta masa su ta hanyar ambaton hujjoji da ije rikice-rikice." Wannan ilimi da fassarorinsa da malaman zamani suka farar kamar lafazin magabaci da kuma har abada da ba zai gushe ba da tabbatacce da kuma masani da faruwa da kuma jauhari makaɗaici da jiki da gittawa da wajibi da horuwa da halat da wajibobi na wasu siffofi da kawo dalilansu da sauran abubuwan da suka anbata. Wannan duk yana daga cikin fassararsu. Wannan duk bai wajaba ga bayi saninsa ba domin shi, mustahabbi, ne.

Malam Sayyadi Ahmad Ɗan Zakariya yana cewa a cikin littafinsa mai suna Muhassilul Maƙsidi, hukunci kutsawa ko shiga cikin wannan ilimi da ambaton dalilansa da manufa mai kyau da kuma raddi a kan rikice-rikice cikin natsuwa. Waɗannan duka mustahabbi ne babu jayayya. Masu yin wannan su ne malamai tabbatatu masana a cikin ilimin Tauhidi da kuma Alƙur'ani da hadisi da maganganun malamai. Malam Manjuri yana cewa a cikin Sharhul al-Muhassil yana wajaba ga kowane yanki wanda zuwa inda wani yanke yana da wahala na samuwar waɗanda za su tsayuwa da wannan ilimi su tunkari da'awar 'yan bidi'a, su hana masu karkacewa daga gaskiya idan wani yanki ya keɓantu da wannan ilimi, to, ya zama wajibi su fita, babu shakka cewa waɗannan siffofi ba za su tabbata ba sai ga wanda ya ƙware da ilimin Alƙur'ani da hadisi da kuma abin da aka cirato daga wurin malamai saboda alaƙar ilimummuka, da buƙatar sashe zuwa ga sashe.

Saboda haka Malam Sayyadi Alhassan Alyusi yake cewa a cikin littafinsa mai suna Almuhadarat. "Ba a sharɗanta ga mafi yawan mutane ba fahimtar lafazan kan tauhidi waɗanda ake magana da su a cikin littattafan malamai ko cimma hakikanin ma'anarsu wadda aka san su da ita domin fahimtar waɗannan maganganu da gewayowa da sanin haƙiƙansu, ilimi ne na daban ba a kallafa wa mafi yawan mutane ba. Saboda haka Malan Sanusi

yake cewa a cikin littafinsa mai suna "Nurul S'adati Sharhu Sugurahu" ba a sharɗanta sanin dubawa ba a kan hanyar malaman falsafa na kawo dalilai ko jeranta su da tunkuɗe shubahar da ta zo a kansu ko samun iko a kan fassara abin da ya tabbata a cikin zukatansu na daga mahanga makusanciya." An hikayantu a cikin littafi mai suna Alummadatu Sharhul Kubra: "Ka sani cewa Ilmul Kalam, ilimin na mayar da Shibhohi da warware shakkoki daga nan mafi yawan mutane suka ce ilimi ne na mustahabbanci a kan mutanen kowane yanki da saduwa wurinsa yana da wahala."

Daga nan littafin Shiryar Da Mutanen Faifayewa Da Sakaci Zuwa Ga Daidaitacciyar Hanya ya ƙare. Manufata ga wallafa shi, tattara ilimin haƙiƙa da shari'a da kaɗaitar da mutanen faifayowa a kan yin ijtihadi wajen gyara Tauhidin mutane da koyar da iyalinsu da kamewar mutanen sakaci daga barin kafirta duk wanda kafircinsa bai bayyana ba ta hanyar zance ko aiki na daga cikin Musulmai domin su dawo bisa ga hanya madaidaiciya su bar abin da suke a kansa, Manufata ga wannan duka, shagaltar da su a cikin birni na kariya daga faɗawa a cikin kafirci domin manufar sheɗan ga mutane masu sakaci na jahilci kada su damu da gyara tauhidinsu ko kuma halartar wuraren malamai domin rashin haka yana daga cikin abin da ka ja zuwa ga kafirci. Manufata a cikin wannan littafi ga masu sakaci daga cikin ɗalibai na kafirta mafi yawan mutane ko da ko kafircinsu bai bayyana ba ta hanyar zance ko aiki da kafirta duk wanda bai kafirta su ba. Wannan yana ja shi ma zuwa ga kafirci.

Wanda ya karanta wannan littafi kuma ya fahimci abin da ke cikinsa, kada ya karkata zuwa ga sakaci da faifayewa. To, ya zama daga cikin masu tafiya madaidaiciya a kan gwadabe madaidaici. Godiya ta tabbata ga Ubangijin da Ya shiryar da mu ga wannan tafarki, ba mu kasance masu shiriya ba ba don da Allah ya shiryar da mu ba, Allah ya gwada muna gaskiya, Ya azurta mu da ikon biyar ta; Ya gwada muna ƙarya, ƙarya ce, Ya azurta mu da nisantar ta.